https://www.wattpad.com/996128765?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=Mai_Dambu&wp_originator=UxWDh15pyw%2FzRRiTXr%2BIGdYXtvNNAH6ZFKV6HA11n8RLhG2lGrhzaYWwZ4KrRM2BZeNoAey%2FEDIl5f5Y6edjvlTZlXnZZC6B0X96Y0nOs6TSR5eAJMGnH%2BCaFpLflqF5

ZANEN QADDARA TA..!!
Labarin Aure a Arewacin Najeriya

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..

Ban sani ba ko zaku amfana da darasin cikin labarin, shi yasa na zab'i mu gudu tare mu tsira tare sadaukarwa ga Masoyana musamman mutanen da suka sayi Ruwa biyu And😂 zaku yi hakuri dani domin wallahi akwai doguwar tafiya 😂 masu sauri kuma ku jira na gama amma littafin kyauta ce ga Masoyan ruwa biyu. Suma nasan zasu yi hakuri da sabiha mai buzu buzu 😂
Tsalle daya ake...
Babi na D'aya.

Shiru nayi ina sauraron sauraron Nasihar da malamin Tafsiri yake mana, akan rayuwar aure a lokacin, musamman lokacin manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama, da yadda mata suka mu'amalanci mazajen su.

Kuka nake sosai, musamman da naji yadda Matar da Manzon Allah yace Julabibi yaje ya nemi aurenta, iyayen ta suka dan so jan jiki akan auren. Hawaye ne ya zubo min musamman yadda Mahaifina ya rasu da bakin ciki na, ba kome ya janyo min haka ba, sai yadda Matar da Manzon Allah yace abawa Julabibi, tacewa Iyayen ta.

"Abba na! Manzon Allah ne fa yace Julabibi yazo niman aurena, kuma kuce ko ba nan ya turo ba, Abba Manzon Allah ne fa ya nima Mishi aure na, me yafi haka gata, Na Amince zan aure shi."

Wani irin kuka ne ya kwace min lokacin da Malam yake fadar haka, har muryana na tashi a cikin ajin kowa sai juyawa yake yana kallona, sabida yadda na daura kaina akan kujeran ina kuka.
"Anum Muhammad Bello! Lafiya kuke kuka?" Malam ya tambaye ni, tashi nayi nace.
"Afuwa malam! Zan iya tafiya gida!"
Murmushi yayi sannan yace.
"Zaki iya tafiya"
Daukar jakata nayi, na fito a hankali ina shashekar kuka, kafin nayi kuka, nayi hutu na kai sau bakwai. Kafin na isa gidan mu dake bayan makarantar Rariya dake unguwar bakin kura na cikin garin Bauchi.

Tun daga bakin shagon Maude naga matasan da suke sayar da shayi kofar gidan mu, suka taso tare da amsar jakata.
"Aunty Anum! Meke damunki ko jikin ne?"

"Babu kome! Kawai hakkin shi da na mahaifina ke bibiyana, na kasa samun sukuni, Yaushe Maude zai dawo gare ni? Ni ba wai na koma rayuwar shi ba yafiyar shi da yar shi nake nima!"

"Hmm, sai hakuri dama abinda ake jiyewa kenan, kai zaka kirkiro matslar ka, sai ka ga kamar Allah ne ya kirkira maka."
Ya fada mata haka tare da rakata cikin gidan.

Sannan ya fita ya hado mata shayi me kauri tare da soyayen kwai. Da bread ya bawa yara suka kawo mata, kallon abincin tayi kuka na kuma zuwa mata, kyakyawa ce fara irin jajjanyen nan ce. Gaban goshin ta, kwance yake da gargasa.

Manyan idanunta wanda suka waddaci fuskarta, sai hanci dogo me shegen kyau, gashin ta da ya kasance ja, saboda yanayin ta zai tabbatar maka da cewa.
Ita din ba cikakkiyar Bahaushiyah bace. Koda tana hade da Hausawar ita ruwa biyu ce.
D'ago labule aka yi cikin harshen Yaren Igala, tace mata.
"Anum! Meye kike nufi? Zaki zauna ne ina miki aiki baki da abin yi sai zama a daki ana kawo miki abinda ranki yake so."

"Mama wallahi bani da lafiya, daurewa nake kawai." Cikin jimami irinta mahaifiyar da take da kaso saba'in cikin dari na laifin da yar autarta ta aikata, yasata kauda kai tare da cewa..
"Allah ya sawwaka, kuma ko fito daga dakin, domin zama da kike a daki yasa yanzun duk inda na shiga ake nuna ni da sunan uwar me kanjamau"

A wani irin sauri na d'ago kai me cike da ban tsoro. Jikina yana rawa bakina yana rawa nace mata.
"Mama! Nice nake da Kanjamau? Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, na shiga uku na lalace. Wayyo Allah na, shi kenan mutuwa zanyi.". Ba fada cikin wani irin kuka,.jikina yana rawa shi yasa mana duk yan ajin suke gudu na ashe suna min kallon mutuwa ce.

Wayyo Allah na, na kuma daura hannu akaina, tare da sake kuka ina ihu. Jikina yana rawa, fitowa Umma tayi ta shigo dakin, ganin yadda nake kuka, tare da matse kaina cikin matsanancin kuka.
"Anum! Albarkar Ubangiji, me ya faru?" Rike hannunta nayi tare da rawan jiki nace mata.
"Umma ashe kallon me kanjamau ake min? Umma kowa guduna yake! Umma don Allah ya zanyi, Umma na cuci kaina, Umma ya zanyi da hakkin Baba Malam, Umma, mutuwa zanyi wallahi mutuwa zanyi, Umma zuciyata zata buga. Umma!!"
Cak numfashin ta ya tsaya, a rikice Umma ta fito daga dakin tana faɗin.
"Maman Aminu! Zoki taimaka min, yarinyar nan ta suma fa!"

Tab'e baki tayi sannan taja tsaki, sannan ta wanke hannunta kasancewar ta tankaden gari, a hankali suka shirya ta, sannan suka dauke ta tare da kiran Babban Yaron gidan, Hafiz. Sannan suka leko waje aka kira napep aka dauke Anum. Aka sakata a napep.
.....
TH-BAUCHI
Emergency aka wuce da ita, zuwa Suka yi aka biya kudin sayan Kati, tare da kudin ganin likita, bayan sun gama dakyar aka turo wata nurse aka duba ta tare da saka mata ruwa, sannan aka basu gado.

Maman Anum tana gajiya da zama ta dawo gida tana tsaki, tare da mai da hankali gurin girkinta. Tare da kananun magana ita ba tsanar Anum bane. Asalima bata da yar da take so sama da Anum, yaranta bakwai a cikin gidan, Malam Bello. Amma dukkan su babu wanda yayi mata laifin da Anum mata.

Kwalla ne ya zuba daga cikin idanun ta, tare da Cigaba da aikinta, hankalinta a rabe yake haka ta gama aikin amma, kuma dan ta bawa masu amfani da laifin anum akanta haushi yasata had'iye zuwa gareta tana gamawa ta kira Aminu yazo, ya dauki abincin ya kai musu asibiti,
Ya shigo da yaran shi Na'im da Na'ima, suka shiga mata kiriniya.

"Mama, don Allah ko zaki je ki duba ta, wallahi Anum zuciyarta ya kumbura sosai," ya faɗa a sanyayye,
"Allah ya bata lafiya!"
Ta faɗa mishi tare da bashi abincin da zai kai asibiti.
"Mama!"
"Aminu kenan, lokacin da Anum take matsalar aurenta, me kuka ce min? Nice nake sakata take kashe auren ta, hmm. Nice na saka Anum taki amsar Yarinyar ta, Ni...Ni ...Ni...Ni...Ni."

Jikin shi ne yayi masifar sanyi, wich mean tana rike da abinda aka mata.
"Mama ki yafe mata mana." Ya faɗa muryan shi na rawa,
"Don Allah!"
Ya faɗa a sanyayye.
"Ni dama ai na yafe mata."
"Mama muje ki ganta mana"
Mikewa tayi tana fada mishi, cewa.
"Ina son zuwa, Lakwaja fa domin na samu labarin Mawedo ta haihu."

Kallonta yayi tare da sunkuyar da kai,
"Allah ya kai mu."
Ya faɗa a raunane, sannan ya dauki kayan abincin ya fitar dashi ya saka a motar, sannan yazo ya kama yaran shi suka fita tare,

Sai bayan fitar shi, ta zauna tayi kuka, ta kuma tai kuka. Sannan tayi alola tai sallah isha, bayan ta idar ne, ta daura da shafa'i da wutiri, tana zaune har lokacin da matar Alhaji suka shigo suna bayan gidan su ne, da yake gidan Babban gida ne a unguwar. Kuma gashi dama can baya anyi koyarwa na almajirai baya rabuwa da almajirai.

×××
A asibiti kuwa jikin da sauki domin tayi barci har ta farka, aka kawo mata abinci.

Komawa gefe nayi, ina kallon yan uwana, dukkansu maza biyar, mata bakwai dani takwas.

"Anum ciki abinci mana, Haba Hauwa'u na, kici ko kadan ne!"
Inji Ya Hafiz, kofin tea na amsa tare da kafa kaina, ina sha ina kallon wata rayuwar da na sake ya kwace min, cirewa nayi tare da kallonsu.
"Ba zaka ce ya dawo min da yarinya na ba? Ni wall Yarinya na zaku amso min!"
Ina fadar haka tare da kuka, ina ture kome, sai da ka min alluran barci, kallon su nayi sakamakon barcin da ya lullube ni.

"Wai da gaske ina da kanjamau?"
Daga haka barci ya kwashe ni.

Shiru dakin yayi tare da sunkuyar da kansu, kafin Aunty Hadiza ta d'ago kai tace.
"Don Allah ina Anum taji wannan labarin? Ina ƙoƙarin kar ya isa kunnen ta amma sai da ya faɗa."

"Hmm! Karku ga laifinta, Maman ku ce ta gaya mata. Tunda taji haka ta gigice baki daya, amma wallahi babu wanda ya tasa zancen"
Kallon Umma suka yi, tare da cewa.
"Yanzun Mama ce tayi haka da saninta."
Girgiza kai tayi, sannan tace musu.
"Karku ga laifinta, kune kuka aikata haka, kunne kuka tunzura tsakanin su, Anum ba laifin laifinta Maman ku tare da Malam suka b'ata Anum, shi malam yayi haka ne kasancewar ta karama da tazo cikin manyan irin ku.

Anum yanzun ta cika shekaru ashirin da hudu, daga shekaru sha bakwai kome ya tabarbare mata, a ce a karancin shekaru iri ne na Anum, tayi aure biyar ga na shida akanta.

Ya tafi bai dawo ba, wallahi ban tab'a ganin Zanen kaddarar da yake shate da ban mamaki, ban tab'a jin ko ganin kaddarorrin masu girma irinta Anum ba, tana karamar ta tasan damuwa masu yawa. Wallahi na tausaya mata Sosai."

"Amma Umma ki bar tausaya mata, domin abinda Anum tayi yayi yawa, yarinyar da ta haihu ta juyawa yarta baya, kowacce uwa tana sadaukar da rayuwarta domin yarta, amma Abun juyawa Yarinyar baya tayi, ki duba girma irin na Maude karfi da jarumta, bawan Allah nan sai da ya zuba gwiwar shi biyu a kasa yana rokonta, yana kuma rokon ta amshi yarinyar nan.

Nan limamin masalacin izala yazo har kofar gida yasa aka kira Anum yayi mata nasiha ya bata yarinyar, tace wallahi ba zata amsa ba. Ya kuma hada ta da limamin masalacin Sheikh Aminu bakin kura, ya roki Yarinyar nan amma fir taki birninta ta koma gidan wancan mutumin da bai san darajarta ba."

Haka Ya Abubakar, yayi ta faɗa kamar zai dake su,kuma duk haushin Anum ne kawai da yake cikin shi a rai, yarinya dai shegen taurin kai.
Bata farka ba sai dare, a hankali take bin ko ina da ido, kasancewar tana jiyo sautin muryan mutane ya sata kuma ware idanunta. Tana jin wasu suna gaisawa tare da tambayar ya me jikin. Kokarin tashi tayi aka ce mata.
"Koma ki kwanta, sannun Allah ya baki lafiya."
"A'a Umma jikina ciwo yake min na gaji da kwanciyar haka."

"Toh bari na saka miki matashi a bayanki" gyad'a mata kai tayi tare da mik'ewa dakyar, sannan ta jingina da matashin, ruwa ta kawo mata a cikin buta da yar baho tayi alola, tare da bata hijab ɗinta, dan tasan ko da zata ce taci abinci ba ci zata yi ba, sai ta gabatar da salollin da yake kanta. Tunda ta fara take zubda kwalla. Tare da kai kukanta gurin Ubangiji, duk da sallah a zaune take amma sai da ta sauke tun daga azhar har isha, sannan ta cigaba da addu'a, tana share kwalla.

Shigowar wasu tawagar maza kusan su shida tare da jami'an tsaron yasata tadda sallah dole, murmushi daya daga cikin su yayi, tare da gaida Umma, tare da tambayarta ya jikin Anum? Tace mishi.
"Jiki da Sauki Alhaji Ibrahim, matsalar dai da sauki kawai rashin sukunin zuciya ke damunta"

Shiru yayi sannan yace mata.
"Kuma ya dace yanzun ta fara daukar hakuri da wannan tunanin ba, dan babu wanda ya isa ya kaucewa kaddarar shi. Hmm idan zata iya tayi min magana sai na tuntube Abokina Kwamishina Shari'a, zai iya kai al'amarin ta zuwa ga babba Alkalin jaha, kuma zai raba auren ba tare da wani matsala ba "

Wani irin duka kirjin ta yayi bata san lokacin da ta d'ago kanta tana kallon shi ba, a yau ta kuma tabbatar babu adalin mutum kamar Maude, mutum ne da yasan darajar kanshi da kuma mutanen da suke rayuwa da shi.

Sallama tayi tare da kankance Idanunta, sannan tace.
"Nagode da concerns, amma ka sani ko shekara duba zai yi ina anan ina jiran shi please stay away daga inda nake bana son damuwa kuma bana son ganinka, haka yana tuna min da bayana don Allah na roke ka, karka kuma zuwa."

Ta yaya ma zata kuma aikata kuskuren baya, a cikin hankalin ta, ai ko na baya ma, tayi haka ne sabida muradin zuci, tare da rashin sanin darajar kai, amma a yanzun da tasan ciwon kanta, Maude ya tafi ya barta da ciwon zuciya wallahi bata jin zata iya daukar kasadar da ta dauka, wannan ma ya ishe ta, wannan ma ya wadatar da ita, tana niman yafiyar Ubangiji akan wanda tayi Allah ya yafe mata ba zata kuma kai kanta izuwa ga hallaka ba, tana ji tana gani ta zama abin kyama lokaci guda ana shirin laka mata sharrin da take niman kashe mata rayuwa, innalillahi wa'inna ilaihi rajioun.

Anya tayiwa rayuwar ta, adalci kuwa? Anya tayiwa iyayenta adalci kuwa? Yaushe hakkin mahaifinta zai daina bibiyar ta? Yaushe kukan da yan uwanta suka yi akanta zai daina bibiyar ta? Ta lalata sunan gidan su. Ta b'ata tarbiyyar gidan su, ta kuma yiwa yaranta tambarin da har abada ba za a daina kallon su da shi ba, karfi da yaji ta lalata goben ta. Zaka iya zana abu da pencil ka goge! Amma da zaran ka zana da biro ba zai tab'a gogewa ba haka Zanen kaddara yake.

Babu wanda ya isa ya goge maka dan kar wani abu ya same ka, Ubangiji da ya tashi halittar ka sai da ya cika maka kome baka, Arzikinka talaucin ka, kaddarar ka! Sannan ya diba maka wa'adin ka, yadda matukar ya cika babu sauran jira ko karin lokaci.

Da ace tun farko ta hango wannan yanayin a lokacin da take ganiyar kuruciyarta, toh ba makawa da ta sake lalle, da ace yanzun ne abubuwan da ta aikata zasu faru, da wallahi ba zata kuskura ya bar shi ya faru ba, dukda akwai ratar ƙaddara!

Ana iya samun damar gyara kusakurai amma ba kowa Allah yake bawa wannan damar ba, sai wanda yaso kuma wanda yayi niyya!

Me yasa wannan tunanin bai zo mata ba? Me yasa wannan nazarin bai tab'a kawowa a ranta ba? Me yasa ta biyewa makircin kawaye da da na wasu? Me yasa Mahaifiyarta ta gaza fahimtar da ita kusakuran da take aikatawa? A yau tayi dana sanin kasancewar ta kyakyawa me kyau da haiba! A yau tayi danasanin rashin mai da hankali ta ribanci lokacin ta, tun kafin lokacin ya kure mata? Yau tana ji tana gani amma duniyar da ta zaba ta juya mata baya!

Mutumin da bata dauka a kome ba, shine yau take niman dacewa ko zata ganshi, me yasa a lokacin da yazo mata da alkhairi bata fahimci haka ba? Taya aka yi bata fahimci Alkhairin shi ba, sai yanzun da yayi mata nisan nisa! Yayi tafiyar bazata a rayuwarta, lokaci guda yayi mata baya ba zani, yan bata aikata abinda zai kaita ya baro bata ba?

A cikin shekara guda kome ya juye mata, ta rasa mahaifinta me mugun kaunarta.
Share kwallar da suka zubo mata tayi sannan tace mishi.
"Don Allah ka barni da ciwon da yake damuna"

The line of Destiny
#Truelifestory
#ZanenQaddarata
#Mai_Dambuhttps://www.wattpad.com/999953572?utm_source=android&utm_medium=link&utm_content=share_published&wp_page=create_on_publish&wp_uname=Mai_Dambu&wp_originator=tEKwF%2FnkkbMYNxlXlMxQ4wdwG9YtjbXz5x4fnK1eop0i5ygnT%2FlJ0cFATDw61uNJl%2FJFwi6Ul6b1Sd4Xfda0O2QRVKfR7zXzG%2F7qQ7LgZXo5nS%2FNWhaoiH3VRvMxwLeI
ZANEN QADDARA TA..!!
Labarin Aure a Arewacin Najeriya

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..

Da ciwo a rayuwata!
Babi na Biyu
"Don Allah ka rabu dani, kaje kawai bana son ganinka, nasan da ciwo a rayuwata, ta yadda duk wanda ya rab'e ni sai na goga mishi me yasa ba zaka fahimce Ni ba?
Me yasa ba zaka tafi ba? Me yasa har yau ake da burin sai ka mallake ni? Anya ban sadaukar maka, wasu abubuwan masu yawan gaske ba? Indai haka ne toh na cancanci ka rabu dani, kaje kayi rayuwarka ka barni na ji da ciwon da zuciya take, don Allah ka tafi kayi nesa dani.

Karka kuma tuna ni,idan da hali kamanta dani, kaje kayi rayuwarka da XOXO tare da masu kaunarka, ka barni na jira tsammanin zuwan shi. Nasan nayi laifi masu yawa, amma don Allah ka tafi kabar na cigaba da niman yafiya. Meye amfanin bad'i ba rai.

Me yasa ba zaka gane abinda nake nufi ba, don Allah kaje bana son kara ganinka a rayuwata, iya haka ma ya ishe ni."

Ta rushe da kuka, sosai wanda duk yadda kake da rashin imani sai zuciyarka ta girgiza. Duk yadda taso tsayar da kukan yaki Asalima sake samun damar fitowa yake, zata iya cewa tun rasuwar Malam rabonta. Dan har sai da aka mata alluran barci, tana barci tana jan shasheka.

Shigowar yan uwanta manyan maza yasa Kwamishina mik'ewa tare da mikawa Yayunta maza hannu, suka gaisa a mutunci kamar yadda suka saba idan suka haɗu. Kallon juna suka yi tare da cewa.
"Umma ya jikin nata, naji tana shashekar kuka."
"Wallahi zuwa na ya sata kuka, Insha Allah ba zan kuma zuwa ba, amma zan turo iyalina tare dasu Hishmah da Hisham."

"Allah ya kai mu da rai da lafiya," inji Umma, juyawa yayi ya fita har ya kai bakin kofar ya juya yana kallon Anum, cikin sanyin jiki, ya girgiza kai ya fita. Masu kula da lafiyar shi, suna take mishi baya.
"Umma waye ya gaya mishi bata da lafiya?" Inji daya daga cikin yayunta.
"Bashir ban sani ba, kawai ya ganshi yazo ne." Ta bashi amsa a takaice, tsaki yayi sannan yace mata.
" Sam bana kaunar Bawan Allah nan, amma rabo ya haɗa mu dashi, kuma ban kuma jin haushin dan banza ba, sai da naji ya auri XOXO."

"Allah ya kyauta, bana son daurawa kai damuwa ban da damuwa ina ruwanka da shi, sirikinka ne tunda ya auri kanwarka sai ka kame kanka indai ba niman karanta kake ba.

Kaga yadda suke da Aminu haka yayi hakuri da abinda yayi mata, balle kai da rashin jituwarku da Anum yayi."

Shiru yayi murmushi daya daga cikin su yayi sannan yace mata.
"Umma! Nifa abinda Anum tayi banga laifin ta ba, sabida ita kanta Maman mu taki zuwa dubata, sannan tana jin zafin Anum ne sabida rashin shayar da Yarinyar nan, kuma abinda na sani da ace Anum ta amshi yarinyar toh ba makawa ba zata nutsu ta fahimci girman Soyayyar da Malam yayi mata ba.

Ko jiya ta turo min sako tana kuka tare da cewa, ita tana sane da itace ajalin Malam, ba kamar yadda ake fada bane, hatsari yayi ba! Wallahi duk sai naji ta bani tausayi, duk da fushin da nake da ita, sai naga babu amfanin na cigaba da wofantar da ita. Domin Allah ya gani ba ita bace sanadin malam hatsari ne yayi kuma ya zo dai-dai da ya fita da b'acin ranta, shi yasa take ganin kamar itace tayi sanadin shi."
"Eh mganarka haka yake, Usman amma kuma ai laifinta kafewa da tayi akan ba zata shayarda yarinyar shi ya fusata kowa, sannan Ni da kaina naji ba wani bane ya gaya min tana faɗin wallahi babu rabon shayar da yar matsiyaci a jikinta, dan haka duk abinda zai yi yayi.

Kuma da na karanci al'amarin sai na fahimci, tana fama da kansa Allah yayi mata ne, tana tutiya da abinda Allah ya bata ne, da ace Allah bai bata kyau da tsarin halitta ba, da babu abinda zai saka ta rena Maude."

"Yusuf kenan! Kana wasa da ƙaddara, matukar Allah ya zana maka haka a cikin ƙaddarar ka babu yadda zaka goce mishi, shi yasa ake fatan kyakyawan kaddarar."
Inji Nura.
Su hudu ne, mazan tunda suka fara su uku na hudun wanda yafi su Shekaru bai ce kome ba, asalima mik'ewa yayi tare da kallon agogon hannun shi. Ya mike tare da cewa.
"Allah ya kyauta, Ni da wannan mutumin zai ji da ya hakura da zuwa gurinta, sabida yanayin da take ciki bata bukatar damuwa."
"Yawwa Ya Sadiq nima abinda nake nufi kenan, a barta ta samu nutsuwar zuciya."

Inji Bashir. Haka suka yi tattaunawa har kusan tara na dare, kafin suka fita daga asibitin dake suna emergency ne, kallon Umman Sadiq yayi sannan yace mata.
"Zan turo Rulwani da bargon yanzun nan yau ban ga Aminu ba,!"
"Eh shi yayi ta dawainiyya da mu, ya kawo abincin amma bai kuma dawowa ba, ina ganin halin da Yarinyar take ciki ne yaki dawo dashi."

"Toh ba damuwa, Sai da safe." Yace mata, ta amsa da.
"Allah ya tashe mu lafiya"

A hankali ya fito, daga cikin yaba kallon yan uwan shi da suke jiran shi, yana zuwa ya bude motar ya shiga, dukkansu suka shiga ababen yawan su, suka bar asibitin koyarwa na jami'ar Abubakar tafawa balewa.

Bayan minti goma sha biyar, can sai ga wani matashin Amma ba yaro bane domin ya kai irin talatin da daya ko da biyu. Cikin b'ata rai ya gaida Umma sannan ya kalli inda Anum take kwance yacewa Umma.
" Ba dai abinda nake ji a gari bane yake damun ta?"
Wani banzan kallo Umma tayi mishi sannan ta cigaba da abinda take.

"Umma ina magana kin ki kula ni?"
"Wallahi ka fita idanu na, kafin na fitar da kai da karfin tsiya, mara kunya kawai, idan shi yake damunta kai sai ka shirya zama da masu lafiyar, Rulwani bana son abinda ake fa? Bana son damuwa fa"

"Toh Umma Allah ya huci zuciyar ki!" Daga haka ya ajiye barguna biyun ya koma gefe, yana kallonta, mik'ewa tayi ta dauki daya ta lullubeta da shi, sannan ta koma gefen tana cigaba da cin abincin ta.
"Umma!"
"Ina jinka"
"Umma!"
"Kunne ke ji!"
"Hmm! Dama nace zaku jima ne a asibitin?"
"Anan zamu tabbata!"
"Kai Umma kome nayi sai ki zafaffa, kawai tambaya nayi fa!"
"Idan banji duka ba, ba zan daina zafaffawa ba!"
Shiru yayi tare da cewa.
"Toh shi kenan, tunda Anum ba zata yi laifi ba,.kowa kaiwa Anum magana, sai a shiga jin haushika."
"Tashi ka tafi tunda baka da hankali."
Ba musu ya bar asibitin tare da mata sallama, dan matuƙar akan Anum ne Umma sai ta iya kaiwa mutun duka babu gaira Babu dalili.
...
Haka suka kwana a cikin asibitin, Umma kan ita sallah ma take, dan tasan karfe huɗu na asuba zasu farka ace kowa ya fito waje za ayi shara, da goge goge.
Haka ce ta faru kuwa, asubar farko aka tashe su, Ita mara lafiya na gado, ku kuma masu jinyar su, za a koraku waje.

--- Da sassafe Maman Aminu tazo, dauke da abin karyawa tare da kayan Anum kala biyu, sai na Umma.
"Sannu Maman Abubakar, ya kwanar sauro?"
Dake tasan Mama bata da wani hausa sosai, dan haka tace mata.
"Alhamdulillahi! Ya kema kika kwana?"

"Lafiya lau, ya me jikin?" Ta tambaye tare da kallon kofar Emergency,
"Da sauki kenan zamu ce ba, tunda kirjin yayi mata sauki!"

Tab'e bakinta tayi sannan ta tura mata abincin gabanta, tana faɗin.
"Ga abin karyawan ku!"
"Mungode!"
Nan suka yi shiru, kafin can Aminu yazo, nan suka tab'a hira dan bai tsammani zuwan Maman su ba, kawai ya dai ganta ne har da abin karyawa, dan haka cikin lalluma da rarrashi ya shiga bata baki tare da nuna mata, idan laifin da Anum tayi ne yaci ace ta yafe mata, amma mata magana akan lafiyarta, tashin hankali ne. Ba laifi nasihar ta shige ta, tare da yi mishi alƙawarin zata k'iyayye gaba.

A iyakan rayuwata na aikata laifukan masu mugun yawa, na b'ata sunana da sunan gidan mu, na yiwa kaina tambari da munannan aiyuka,.sam ban saurari soyayyar da iyayena ke min ba, nayi ta aikata kusakurai masu girma, har yau ina tsanar kaina da kaina, nayi rashin jin maganar iyayena wanda shi kawai ya ishe ni ganin bakin cikin rayuwa.

Da ace abinda na aikata zai gogu wallahi na nasaka kilina na goge shi baki ɗaya daga cikin rayuwata, Ni da kaina na zana ƙaddara ta, na kuma goge shi kai ba

zan tab'a yarda na aikata abinda zai tab'a mantawa a ƙaddara ta ba, naga kaddarorrin rayuwa masu yawa da girma, sakamakon bijirewa mahaifina.

Naga sabuwar rayuwa masu yawa, na kuma fada tashin hankalin rayuwa, nayi laifi masu yawan gaske, wanda haka ya ruguza min rayuwata, ina da zan ga Baba Malam, na bashi hakuri? Ina da zan kuma ganin shi yace min nayi abu koda kuwa shine hanyar mutuwata zan aikata.

Banyi Zina ba, amma kasancewar nayi rayuwar da take tare da ma'abota shi, yau ana jifana ne da dattin zina, ban tab'a kawowa a raina zan yi mugun abu ba, amma yau sakamakon rashin jin Maganar iyayena ya sa ana min kallon mazinaciya.

Duk rayuwar da zaka dauki nauyin rayuwar wasu, ka dauki al'adar wasu ka daurawa kanka Tabbas wata rana kai da kanka aka wayi gari duniya ta juya maka baya.

Duk da iyayena sune mafarin ƙaddara ta, amma a zahirance ba hakan bane sabida su, soyayyar da suke nuna min, da ace sun tankwarar da Ni, toh da yau haka bai faru dani ba.

Yan uwana ciki daya, da kuma mahaifana, sun taka rawar gani a rayuwata, sun nuna min soyayyar da ta hananin ganin laifin kowa, shi yasa nake ji a a raina ba zan tab'a yarda wani ya koyawa dan shi irin soyayyar da aka nuna min wanda bai janyo min kome ba sai damuwa.

Ba laifi bane Iyaye dan sun so yaran su, amma kasancewar irin mu soyayyar da ake gwada mana, Soyayyar yaran karshe SOYAYYA ce da matukar iyaye basu tsaya da gaske ba, toh akwai matsala, kamar yadda aka nuna min nawa.

Share kwalla nayi, a yau nake tirr da kasancewata auta, wanda bahaushe ke kira da mowar yaya, na taso cikin soyayyar da ta gaza amfanar dani kome, na wayi gari ban san lokacin da kome ya warware min ba, da ace nasan haka ce zata mamaye rayuwata, da ban fara amsa sunan autar malam ba.

A yau kome ya faru dani ne sakamakon wannan yanayin da na tsinci kaina, na tsani kalmar autar malam, na tsani rashin zuwana a matsayin Ya ta tsakiya sai ta karshe wacce ta tattaro kayan bakin ciki a haihuwarta.

Wani irin kuka ne ya kwance min, yau na zama abinda na zama ne sakamakon rashin adalci da banyiwa Iyayena da mutumin da ya maidani mutum, na rintsa idanuna ga hasken da yazo mini, na bude akan duhun damina maganin me kwaɗayi, kowa ya dibo da zafi aka ce bakin shi, yau na kwaso abinda ya dame Ni?

Tun bayan tafiyar shi shekara daya kacal kenan, ban kuma hada tsabga ta kowani namiji ba. Amma yau nice ake zargin da abin maza, Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, Ya Allah nayi kusakurai da yawa Ubangiji Karka kama ni ta wannan hanyar, kalmar tayiwa rayuwata giɓɓi, haka na wuni ina kuka koda likita yazo duba ni, ya samu jini na ya haura, kadan dan haka yace kar a dame ni da yawan magana ina bukatar hutuwa.

Duk da fushin da yan uwana, suka dauka bai hana su zuwa dubani ba, asalima sun zo dukkan su, amma fushi suke dani, dakyar Aunty Hafsah da Safiya suka gaishe ni. Aunty B da take kusan tsaye akai na, duba magangunar tayi sannan tace min.
"Anum, don Allah ki rage nauyin tunanin da yake damunki, zuciyarki fa ta kumbura."

"Toh Aunty B! Zan gwada.."
Maganarce ta makale, sakamakon shigowar Aminai na, wanda sune umul a'ba'isin fadawa ta wannan hanyar tare da Aunty Aina'uh Kishiyarta, da muka zauna a gidan Kwamishina, uwargidan shi. Sai Mahaifiyar shi, Hajiya Turai.

Beauty da XOXO, murmushin mugunta na gani akan idanun su, kafe su nayi da ido, sannan na dauki Kofin tea da aka hada min na fara sha ina murmushi, isowarsu. Kallon Tagwayen ta da suka koma kamar marayu tayi, sannan ta mika musu hannu, sai da suka kalli XOXO da tare da sauran matan.
"Kuzo gurin Mama!"
Nace musu, had'iye yawun tsoro suka yi, sannan suka coge a gurin, kallon XOXO nayi domin nasan aikinta ne, juya cokalin dake cikin cup din Tea din nayi jikinta ne ya dauki rawa, tace.
"Yan biyu kuje gurin Mama!"
A hankali suka tako, kallon ta nayi sannan na sake murmushi, kafin na ajiye cup din, ina kallon ta sauke boyayyen ajiyar zuciya.

D'ago su nayi muka zauna, ban kuma kallon su ba, amma cikin iko nace musu.
"Zaku iya tafiya, ku turo Ibrahim yazo ya dauke su, sannan idan suka dawo, ina da labarin abinda yake faruwa dasu, idan da alamun watan tozarta masu zaman hayan dogon gida zai fara, a Cigaba da tab'a min bugun zuciyata."

A fusace suka juya nacewa Beauty.
"Kazamar rayuwa bata dace da uwar da ta haifi Yaya mata ba, sannan da ake yawo dani a cikin bakin kura, ina sane da! Beautiful face."

"Hajiya Turai! A gayawa Ibrahim gaskiyar maganar da. Maman Aymaan! Ki rike kimar ki, da gaskiyar ki Allah zai datar dake alkhairi. " Ban kuma magana ba, har suka fita, sake rungume yarana nayi ina jin wani irin tausayin su a raina, sabida su na kuma tabka kuskuren da nayi, babu wanda yayi min magana a cikin yan uwa na. Ganin yarana sun taimaka min sosai gurin saukar jini na, domin har dare muna tare dasu.

Bayan isha yazo ya dauke su, har zai tafi nace mishi.
"Bayan hakkin Jama'a da yake jingine bisa kafadarka, nauyin yaran da aka raba su da Mahaifiyar su yana bisa kanka, Ka bibiyi rayuwar su, don Allah karka sani jin kai kuka na inda za a tsaya min."
Juyawa yayi tare da gyada min kai, ya fita daga asibitin.

Wani siririn hawaye ne ya zubo min, lokacin da na fahimci. Har da shi a matsayin wanda ya b'ata lokaci na.

---, kwana na biyu aka sallame ni, sakamakon jini na da ya sauka, haka ya faru ne ta sanadin yaran da Ibrahim yake kawo min, ranar da na koma da su, a ranar naga sauyi daga fuskar Mama da Yan uwana, waɗanda muke ciki ɗaya dasu, ban damu ba na share batun su.

Sati na daya Zakiyah matar Ya Sadiq ta haihu, nasan babu abinda zai dawo min sai tashin hankali, aka'idar gidan mu idan aka haihu ranar suna a nan gidan zaayi abincin suna, dan haka tunda na fahimci haka na kaura cewa fitowar waje ranar sunan gudun kar yayuna mata da muke daki daya su azabtar dani da bakaken Magana.

Dan haka yau da ta kama sunar ina....

#Mai_Dambu[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA...!!
Rayuwar Aure a Arewacin Najeriya

Mai_Dambu
Farga daji....
BABI NA UKU

Ina jin hayaniyar yan uwana, amma sabida kasancewa ta, mujiya a cikin su, ya sani kara lafewa a gadona, ina had'iye yawun, sakamakon kamshin soyar namar da ake na sunan Ikilima matar Ya Abubakar, wacce ta haifi d'a namiji aka sami shi sunan Baba Malam.

"Mama yar sarki me rigar mutum ba zata fito bane ayi aikin da ita? Wato ga bayinta su gama mata, ta zauna ta cinye?" Inji Aunty Hafsah, yayata ce da muke ciki ɗaya.

D'aga labulen Yaya Binta tayi dan ita ce ya ta farko a cikin gidan mu, ta kalle ni na tashi zubur ina zare idanuna da suke cike da kwalla. A hankali ta sake labulen sannan tace musu.
"Da bata yi aikin sai ya kashe ku? Hafsat da Safiya kuna bani mamaki. Da akace karta na yawan shiga damuwa shine bari kuyi ta sirka mata rashin mutunci?

Hmm! Zuciyarta yana tabuwa da abinda kuke mata, idan rayuwarta ce baku so! Shi kenan, zaku iya Cigaba da abinda kuke."
Daga haka ta wuce dakin Mahaifiyar su. Cikin jin haushi Safiya tace.
"Yarinya ta gama rashin kunyarta tare da mana sanadin mahaifin mu, amma ake ganin bata yi kome ba, har abada ba zan tab'a yafe mata ba, taji kunci da Baba Malam yaji lokacin da yake rokonta arzikin da bai mata ba, amma fir taki kula shi."

Haka suka yi ta mita, tare da jin haushin yar autar su. Wato Anum.

... Duk ina jin su, amma bani da ikon fitowa wajen domin ina fitowa zasu min caaa, dan haka na cigaba da zama a d'akina. Har zuwa azhar da na fito alola, naga yadda suke kallona, jikina ne ya dauki rawa, kamar zan kifa, dan har tsalleke abubuwan nake sakamakon tsawar da Aunty Hafsah ta daka min.
"Ke wata irin dabba ce? Kin zo kina niman zuba mana, ruwan butar a cikin abincin da muke banza akuya, karya k...."

"Hafsat!" Ya Aminu ya daka mata tsawa, cikin jin haushi ta ce mishi.
" Ba ajiyar bace? Ko ba karyar bace? Wallahi har kunyar nunawa kawayena wannan yar iskar cikin mu daya, sabida yadda ta zama taxi.."

"Kina da yaya mata, sannan kina zagin yar uwarki ciki ɗaya, sabida ajizanci." Take kowa yayi mata caaa, ni kam nasan haka zai faru, da bi bango na isa d'akina, na zauna tare da sake kuka me mugun ciwo, wanda su kansu yan wajen duk sai da suka ji yo ni.
Kallonta kowa yayi cikin jin haushin abinda ta aikata, sannan suka ce mata.
"Yayi miki kyau!"
Maman su da take jin abin a cikin ranta, share su tayi amma tasan duk abinda Khadijah Anum tayi ba laifinta kadai bane har da nata,a matsayin ta na Uwa ta gaza tsawa yar autarta ta zama abin alfahari.

Itace ta gina mata kome na rayuwar da tayi, ita ce ta nusar da ita abinda zata aikata, ita ta nuna mata kudi da kyau sune cikon muradinta,. Ba lallai sai ta zama mace ta gari ba, zata iya zama mace mafi daraja indai zata hadu da me daraja.

Haka ta share kukanta a cikin dakin ta, dan bata son yaranta su gani wutar k'iyayyar da take ruruwa a tsakaninsu ya kuma tashi.

--- bayan sun gama kome, suka shirya tare da barin gidan, suka nufi gidan da ake taron sunan wanda yake Makara huta, dake garin bauchi. Suna shiga aka shiga tambayar su.
"Ina Anum? Aunty Hafsah"
Inji wata budurwa wacce ba wuce shekaru ashirin da hudu ba, duk da bata girme Anum ba, amma kuma zasu iya zama kusan shekaru daya.

"Shukrah, yaushe kika zo daga Kano?" Murmushi sannan tace mata.
"Yau kwana biyu kenan, don Allah Aunty Anum zata zo ne?"
Tab'e baki Hafsat tayi sannan tace mata.
"Ban sani ba, ko zata zo ashe."

Ta wuce Shigowar Mahaifiyar yarinyar ta mike tare da amsar jakarta, tana faɗin.
"Ammih Aunty Khadijah Anum ba zata zo bane?"
Shiru tayi sannan tace mata.
"Kuma na manta da sakonki, Amma Insha Allah zata zo dan naji tana cewa idan kanta yayi mata sauki zata zo."

"Toh Ammih, Allah yasa kin san yanzun Aunty Anum ta zama wata iri ne tsoro ln shiga mutane take."
Kallon ta Uwar tayi sannan ta girgiza kai, ta wuce komawa gurin Kawayenta tayi tana gaya musu, bata zo ba amma Insha Allah idan ta kama suje bakin kura sai suje.

"Toh ishashiya, kowa ya tafi gidan sunan shine ba zaki tafi ba!" Inji Mamarta.
Sunkuyar da kai tayi sannan tace mata.
"Don Allah Mamah ba.."
"Ok shima Zumuncin so kike ki lakata min kashin kaza? So kike a Cigaba da cewa nice nake hanaki shiga yan uwanki."

"Don Allah Maman Aminu ki bar yarinyar ta samu kanta mana, wannan wacce irin rayuwa ne, tunda bata jin dadi ta hakura mana!"
"Umma zani Insha Allah. Bari na shirya."
A gurguje na shirya tare da saka wata shaddata, wacce aka mata aikin surfani, sai hijab me yashi.
Babu wani kwalliya na fito tare da daura niqab nayi musu sallama, ina fitowa daga cikin gidan na sami Abba K2 yana zaune a bakin shagon Oga Maude, kallona yayi sannan ya ajiye kofin shayin yana faɗin.
"Uwargida, ina zaki?"
"Zamu gidan Yayana ne ana suna." Na bashi amsa a takaice bai na kokarin barin gurin su,

Tashi yayi daga gaban shayin, ya shiga keke napep din shi, ya sha kaina da keken.
"Muje ko"
"A'a kaje kaci.."
"Karki damu sabida ke nake aikin da babu ke haka zan cigaba da sara suka, a kashe ni a banza,.dan haka ki shiga muje."

Ban musanta mishi ba, dan yaran suna bani wani irin girma ne na musamman, gani suke kamar nice ogan su ma. Har kofar gidan Ya Abubakar ya kawo ni, kuma abinda zai daure maka kai shine bai dauki kowa ba, sai ni yana ajiye ni yace min.
"Uwargida yaushe zan zo daukarki!"
"Karka damu zan sami motar da zata..."
A birkice ya kalle ni tare da tsuke fuskar shi yace.
"Ina nan ina jiranki duk lokacin da zaki koma sai na koma."
.sake bakina nayi domin kuwa ya bani mamaki, akan me zai zauna,
"Ka dawo bayan isha."

Na fada mishi haka, dan kar ya b'ata lokaci, a gurin zaman gadina, duk da nice na janyowa kai na, da ace hannun agogo zai dawo baya lashakka zan gyara kuskure na.

Labarina babu abin dauka a cikin shi, domin cike yake da ƙadarorin masu girma, kowani dan Adam da irin tashi ƙaddarar amma yawa ƙaddarar nice na zanata wanda har yau na kasa goge shi.
"Laa, Aunty Anum!" D'aga niqab dina ina kallon yar Yayar mu.
"Shuky yaushe a gari?"

Cikin farin ciki da gani na ta shiga rawan jiki tare, da bani amsa, yayuna mata uku musamman yan dakin mu, tsaki suka yi tare da dauke kan su, duk da yaran su, suna murnan ganina, isa nayi gaban su na dauki yaran tare da musu wasa.
"Ajiye min Y'ata! Da kin san zafin shi ba zaki sake a tafi da shi wata duniya ba."

Murmushi nayi a karo na farko da naso majin zafin kalamanta, nace mata.
"Zanen ƙaddara ta kenan! Amma haka bai hanani kaunarta ba, kome zaki gaya min ki min a cikin gidan mu, inda ba zan kulaki ba, nan kuma cikin jama'a ne, zuciya bata da kashi kina min zan rama." Daga haka na ajiye yarinyar na bar su tsaye cikin damuwa da mamaki, suna jin haushina, amma kuma halin da nake ciki, ba zai hana su min rashin mutunci ba.
Gurin mejego na shiga muka gaisa dasu Ya Amina, Ya Rabi, da Ya Bintu, zama nayi ina narkewa a jikin Ya Maryam.
"Kin san Allah Autar malam, ki rabani da son jiki. Kun hadu da shukrah."

"Eh!"
"Wai zata zo ki mata nasiha akan zaman aure ne. Tazo gurina nace mata bani da wannan tunanin, tayu ke asamu wani abu daga gare ki, idan mutum ya duba daga yanayin rayuwar da kika yi."

Tana maganar ne amma kasa kasa, da sauri na d'ago kai nace.
" Kuma kika ce Ni? Amma ai naga rayuwar auren da nayi babu kome cikin shi sai damuwa da son zuciya!" Na fada a raunane.

"Babu son zuciya cikin ƙaddara, duk da kina da laifi, sai dai ki sani ƙaddara itace igiyar da ya jaki zuwa ga wannan rayuwar, idan Allah bai zana miki haka cikin ƙaddarar ki ba, toh babu abinda zai sanya haka ya faru, zanen ƙaddara kenan, ki same ta naga har da Kawayenta suka zo, ita daya tana shirin aure nan da sati biyu, daya kuma tana fama da matsalar mijinta da baya iya ciyarwa sai dai iyayenta su kawo musu, yaci kuma ya kwashe musu albarka."

Kallonta nayi sannan na mike tare da cewa.
"Toh bari na gani."
"Yawwa yar albarka."
Fita nayi suka bini da kallo cikin tausayi da damuwa.

"Wallahi Yarinayr nan tausayi take bani, ga baki daya ta firgice da yan uwanta, ganin dodanni take musu, don Allah Aunty B kunyi musu wani abu su kyaleta ta huta, kiga duk fushin Baban Ayman haka ya hakura tunda yaji zuciyar ta zata iya bugawa sabida damuwa, ku wanda kuke akan shi yayi tafiyar shi ai sai ku kyaleta haka."

Tattaunawa suka yi tayi, har zuwa wani lokaci, kafin suka share batun.

Ina fita ta mike muka shiga wani falon da babu cunkoso mutane, zama muka yi suna kallona, nima kuma kallon su nayi kafin Shuky tace min.
"Aunty Khadijah, sunan ta, muna kiranta da Anum, kyautar Allah.!" Jan fasali tayi tare da nuna musu ita, sannan tace mata.
"Mu nan, Kawata ce zata yi aure shine muka je gun Aunty Salamatu, wai muzo gurin."

Shiru nayi tare da nazarin ta inda zan fara musu bayanin.
"Wato shi Al'amarin aure girma ne dashi tare da fadin gaske, duk yadda mutum zai gwada muku matukar bai tab'a shiga wannan bangaren ba, toh babu abinda zai gaya muku sai hakurin. Abu na farko da zaku fara shine kuyi auren ku da Kyakyawan niyya,karki yarda kiyi auren dan yana da kudî! Karki yarda kiyi auren da yana da kyau! Karki yarda kiyi auren da shi wani ne! Karki yarda kiyi auren dan zai miki lefen kece reni! Kuyi auren domin bautar Ubangiji, haka zai sanya ku rabauta, karki yarda ki aure shi dan samun Freedom! Babu yancin da yafi ki bautawa Allah a cikin zamantakewar aurenku!

Karki yarda ki aure domin ya cancanci haka ne, a'a ki aure shi domin Allah kuma kiji a ranki koda shi gwamna ne ko shugaban kasa, zaki zauna dashi ne a matsayin miji da mata, a karkashin kulawar Addininki!
Rayuwar Aure yayi ne! Domin babu rayuwar da yafi rayuwar aure dad'i, a rayuwar aure babu, abinda zaki yi bai zama lada da Alkhairi ba, amma a wannan lokacin rayuwar aure ya zama niyasu, sabida yadda muka sake addinin mu da Ibadar mu, da ace mutanen baya sun san da haka toh bazasu tab'a barin mu,. Haka ba sai sun mana addu'a akan zamani, sabida a lokacin su ana girmama auren fiye da kome a duniya, amma a wannan lokacin auren ma wulakanta shi ake, da zaka tambayi wani dan me zaka yi aure? Zai ce maka kawai zai yi ne sabida ya dace da haka, ko kuma zai yine sabida Yarinayr zata kawo mishi kayan daki da Gara, har hada suke da junan su.

Da zaran anyi auren sai kaga kwanaki ƙalilan an fara samun matsalolin rayuwa, ka rasa ta ina aka fara, bayan daga mune abin ya fara, karki yarda mutumin kirki ya subuce miki bayan kina sane da shine zai ririta alamarin ki, karki yarda da wanda zai zauna kullum yana gaya miki yayi mafarkin ki, bayan ba aurenki zayi ba.

Shukrah karki yarda wani ya baki damar da zaki ki auren Mutumin kirki, bayan kema kinyi imanin mutumin kirki ne, irin su ƙalilan ne muke dashi a cikin al'ummar mu. Toh Alhamdulillahi anzo fagen aure, kowa zai ce miki kiyi hakuri halin maza sai su, tun kafin ki isa gidan mun gama razana ki da mabanbanta Halayyar maza, da fadar wasu munanan halayen su.

Shin kin tab'a tambayar Mamanki wani irin halin Mahaifinki yake dashi? Toh ai idan halin shi mugun nufi ne, haka kuwa tayi hakuri da shi ta zauna a haka dashi, idan halin shi na kwarai ne, haka zaki zauna da naki, duk duniya babu wanda ya isa ya baki shaidan zuciyar mutum sai Allah, dan haka kiji a ranki zaki zauna dashi ne da zuciya daya. Anzo fagen aure!

Anyi aure, an haihu daya biyu uku, wai sai kiji matsala ya dame ki, kina kukan ya zaki yi,kece Posting a grp na Whatsp! Kece kaiwa IG, kece kaiwa Facebook. Kin tab'a zama kinyi nazarin zaki magance wannan matsalar? Wadannan Groups da kike Turawa 75% na cikin su Yan mata ne da suke niman mijin aure kin dauki damuwarki kin kai musu! Shin akwai wani bayan Allah ne? Babu tabbas babu, akwai me magance miki matsalar ki ce? Babu tabbas babu, Amma akwai Allah, Tabbas akwai shi. Kin tab'a yin azumi domin Allah ya yaye miki damuwa? Toh indai har kinyi wallahi zaki iya akan damuwar mijin, kin dauki Matsalarki kin gayawa mutane, sannan sun ce miki gaskiya ki rabu da mijinki nan baya sonki da zuciya daya, shin kin tab'a ganin matar auren da ta shekara goma a gidan mijinta ta bawa wata mace shawarar ta kashe aurenta? Sabida duk lalacewar auren shine kimarta, bari na gaya muku wani abu, yan fashi da manyan masu laifi, wallahi suna da matan su na sunnah kun tab'a ganin matar su tafi toh tace mijinta dan fashi ne? A'a ba zata tab'a barin kowa yasan halin mijinta ba, sabida boye sirrin shi.

Amma zaka samu mijinki yana zuwa kasuwa, domin niman na kanshi daga karshe zata yi Posting don Allah ku boye sunana, mijina bayi da kirki. Mijina ya cika masifa, mijina kaza yaushe Hausa Fulani suka koma haka? Wallahi tunda nake yawon aure aure, ban tab'a kawo kara gida ba, sabida bana son Kowa yasan damuwata, sai dai idan kunje kuga halin da nake ciki. Ban tab'a ganin zamani ne cike da mamaki kamar wannan zamanin ba.

Kun mai da rayuwar Freedom kamar yadda kuka tsarawa kanku. Kun mai da aure kamar takalmi, wai har budurwa zata baki shawara bayan ita bata zauna da namijin ba, kunsan falalar da Allah yayi mana, toh ku barshi a haka karku what man can do, Woman can also do it, wannan kamar kunyi fito na fito da yar Allah ce, kina da uwa kina da Uba, kina da yan uwa, ki zaɓi abokin shawarar ki karki kaiwa kowa kukanki sabida Akwai Allah.. rayuwar mu da ban mamaki take, wai sai kaji ana ce maka maganin mallaka, Yes kiyi maganin gyara, amma duk Wanda yace miki, zai baki maganin mallakar miji, karya yake miki domin ko kin same shi kwana biyu, zai lalace kuma zai ci Ubanki, karki yarda kawarki ta kawo miki wani abu dan mallakar mijinki, domin cutar dake zata yi babu wani mallakar shi da zaki yi.

Idan baki mallake shi ba, ita zata mallake shi ta aure miki shi. Kuma a zauna lafiya, babu yadda kika iya.

Kince baki son kishiya ba laifi amma ki sani dole yayi aure, domin idan bai yi ba, zai bi matan layi, kuma zai kwaso miki damuwa, babu yadda kika iya.

Uwar mijinki, Allah sarki uwar miji. Har ulcer ake ce miki, zunzurutun rashin kunya da mutunci, kin mai da mahaifiyar mijinki da yan uwan shi abokan adawarki, toh my Sister karki manta kema uwace, iya haka ma ya ishe ki, kamar yadda kika hana shi kyautatta mata, haka d'anki zai auri yarinyar da zata miki, kuma baki da abinda zaki iya, sabida rashin adalcin da kika nuna mata.

Na rasa gane wani irin kyashi da Hassadar da take damun mu, bamu kaunar muji mazajen mu zasu kyautata yan uwansu, take kishi da bakin ciki zai motsa kin tab'a tunanin kema kina da dan uwan namiji abinda kika yiwa wasu shi za a miki, mata muji tsoron Allah, zamu mutu mu tarar da Ubangiji, mu girmama auren mu, mu cire cutar kai da hassada mu rike auren mu da kima.

Maza kuma kuji tsoron Allah, baka auri mace dan ta rike kanta ba, wallahi muji tsoron ganuwar mu da Allah, domin duk wanda ya auri mace yasan ci da shan ta yana wuyar shi, amma sabida rashin amana ka sauke ƙana jiran danginta su kawo maka ka cinye kuma kabi yarsu da zagi da cin mutuncin, shin idan aka yiwa Yarka haka zaka ji dadi? Zaka yi farin ciki? A'a kawai dai ka auro mace kayi ta gana mata

azaba, daga karshe kace kai ba zaka zauna da ita ba, sai ta biyaka kudin da ka kashe, anya kana tuna bayanka kuwa? Toh idan barci kake ka farka, tuni. Domin kuwa idan ka sake Allah ya kamaka da hakkin wulakanta aure, sai kayi DANASANI mara amfani.!

Karku manta da wasiyyar Manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama, idan yace yafita hakkin mu, ya zo mana da addinin musulunci, ya kuma isar da sakon shi, sannan yabaku amanar matayenku, ku zauna dasu da amana, karka yarda Manzon Allah ya kamaka da hujjar shiga hakkin aure.! Da wannan nake kawo karshen yar ƙaramar nasihar da na kawo muku da fatan zaku karu dashi"
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA...!!
Rayuwar Aure a Arewacin Najeriya

Mai_Dambu

Kowa ya tuna bara..
BABI NA HUDU
Wani banzan shewa Ya Hafsah ta saka, cike da izgilanci sannan ta taki gabana, zata ci zarafina.
"Akaramakiya, Hamshaqiya, Sayyida, Ustaziya Khadijah, Eyye Ashe Anum ta iya wa'azin zaman aure bamu sani ba?

Matar da ta gaza zama a d'akinta, yarinyar da tunda kuruciyarta take dauko magana, karewa har cikin..."

"Ke wacce irin sakarya ce? Ke wacce irin mahaukaciya ce? Yo Allah na tuba, me zaki gaya min? Me zaki fada a gaban jama'a? Wai naka ke yake shirin tozarta ka a gaban mutane, gaya musu wacece Khadijah! Tayu ba zasu sake gani na ba, ke kuma ga kishiyar ki nan ta sami abin goranta miki gara ni, wallahi duk inda na shiga bana boranta Ni mowar miji ne, tun daga cikin gidan mu ya kamata ki fahimci Ni autar Yaya ce , bana tab'a zama bora ko a gida ko a dawa. Idan kece da wuta da aljanna don Allah Hafsah idan nazo ki rufe aljanna ki wurgani cikin wuta. Jahila kawai."

Daga haka na mike tare da ɗaukar jakata, na fara ƙoƙarin barin gidan sunan, ban ma kira wanda ya kawo ni ba, zunzurutun raina ya b'aci, kuma a yanzun bana son tuna bayana ne. Idan na tuna yadda na b'ata tambarin gidan mu sai naji na gaji da kome na rayuwa. Tunda na fita na sami napep na shiga, goge kwallar da take fuskana nayi, tare da kallon gefen hanya.

Beauty na gani, sanye da wata swiss gefenta Alhaji Dan Azumi ne, dauke kaina nayi tare da cewa a raina.
"Allah nagode da ka cire ni a wannan kazamar rayuwar, Allah Nagode da ka barni da Imani na, Allah ko makiyi na, karka wurga shi cikin wannan yanayin shi yasa Bala'i tayi mana Yawwa."

A hankali napep din ya sauke ni a kofar shagon Oga Maude, haka kawai yau nake matukar jin kewar shi, yana cikin raina wanda ban san lokacin da haka ya min diran mikiya ba. A hankali na sauka tare da saka hannu a jakata zan ciro kuɗi.
"Jeka malam."

D'ago kai nayi naga Rulwani ne, dauke kai nayi, tare da nufar cikin gidan.
"Shegen rashin mutunci, ai kyace kin gode ko?"

Tab'e baki nayi tare da cewa,
"Daka biya na saka ne? Ko kuma nace maka ba zan iya biya bane? Kai kaji gurin!"

Daga haka nayi wuccewa ta cikin gidan mu, ina jin shi yana bolokoko, ina ruwan ayagi me fada ko daga zaune a tab'a.

... Ina shiga na sami fadar Mama,.kamar zata cinye ni wai na ci mutuncin Hafsah a cikin jama'a me yasa ba zanyi hakuri ba, dan tayi min fada har ina mata gori, shiru nayi tare da wuccewa d'akina, ina jinta tana kuka.
"Bayan b'ata min suna da kika yi haka ma bai ishe ki ba, sai kin tozarta yar uwanki a cikin gidan suna a gaban jama'a kika zage ta."

"Mama, wallahi ba haka bane, kawai ta gaya miki son ranta ne, amma wallahi ban zage ta ba."

"Ki min shiru! Karki kuma gaya min maganar banza, taya zaki ci mutuncin yar uwarki a gaban jama'a? Daga gaya miki gaskiya, ke wacece da ba a gaya miki gaskiya ba. Ni zaki kawowa karya!

Wallahi zan saka Bashir yayi miki mugun duka, sakarya kawai mara hankali ba gwara ita ba, tana zaune a dakin mijinta, kuma tana min duk wani abinda ya dace ke ince rashin rabonki ne ya hanaki Fahimtar Arzikin da Allah yayiwa mijinki."

Kallon ta nayi baki sake, hawaye na zuba daga idanuna, lekowa Umma da Goggo Hamah, tare da kallon Mama ta sani a gaba zata dake ni.

"Toh ai sai ki kyaleta, lokacin da ta kika lalata abinki ai babu wanda ya sani, yanzun da kuma duniya tayi muku juyin masa shine bari ki goranta mata, ai duk abinda Khadija tayi bata da laifin ki ne, kwaɗayin duniya ya kai ku ya baro ku. Yanzun kin wani zo zaki dame mu da Hausar ki da bata ishe ki ba, don Allah ki kyale jama'a su huta haba don Allah."

Juyawa tayi tare da fita, Mama ta zuba min ido, cikin tsannanin b'acin rai, yau akai na ake gaya mata magana, kafin na ankara sai ganinta nayi tana zubda kwalla. Jikina ne ya dauki rawa tare da girgiza mata kai nima ina kuka.

"Don Allah!"
"Ya isa haka! Kije na cire hannuna daka kanki, kije duniya ta ishe ki riga da wando, Anum Ni ake gayawa magana sabida ke? Idan dan soyayyar da na nuna miki ne kije na barki da duniyar." Tana kaiwa aya ta ficce, ina tsaye a inda ta barni wani irin kuka ne yazo min tare da nadama mara amfani, zama nayi cikin mutuwar jiki. Duk da kiran sallah da ake bai sanya na tsayar da kuka ba.

Na kai minti goma sha biyar, har aka fito masalaci ina kuka, kafin na mike na bar gurin, fitowa nayi na yi alola na koma cikin dakin, tunda na zauna nake kuka, ina taryo abubuwan da suka gabata na rayuwata, da ace a lokacin ta bata fahimci kallon tausayin da Baba Malam yake mata ba, me yasa bata fahimci kallon tausayin da Maude yake mata ba.

Idan ta tuna lokacin da yake Maude yake cewa.
"Khadijah! Wannan rayuwar da kika dauka karya ce, Khadijah ni me kaunarki ne, kuma ina kaunar farin cikin ki ne, KHADIJAH zan iya samun matar da suka fiki, Khadijah ina da su, amma zuciyata bata kansu, sai ke don Allah ki taimake ni ki haifa min cikin jikin ki lafiya Wallahi zan baki mamaki a rayuwarki!"

Dariya ta saka tare da gyara kwanciyarta bayan ta matsa daga inda yake, ta juya mishi baya tace.

"Cikin ƙaddara ko? Toh zan haifa maka shi meye a ciki daga duniya sai Abuja, zan haifa maka abinka amma wallahi ka sani babu rabon sharyawa a jikina, na gaya maka. Duk abinda zaka yi kayi daga yanzun amma ba zan shayar maka da abinda zan haifa ba. Me kake dashi? A cikin su Hishmah Dubai aka kai ni sayayya kayan haihu,a can na haihu kai me ka tara? Me kake bukatar nayi da Kaddararren auren ka, banda cin Amana taya zamu shirya abu da kai ka dawo kace baka san zance ba.

Sake ka daura aniyar sai ka tozartani shine ka dawo da cewa ba zaka sake ni ba, wallahi zaka rabu dani domin tun fil azale bana kaunarka, kuma bana sonka ka gane mana..."

Jikin shi na rawa ya matso kusa da ita, tare da janyo ta jikin shi.
"Karki ce haka! Naga soyayyar gaskiya a idanunki don Allah karki ce baki kaunata, ni ana sonki zan cigaba da sonki, KHADIJAH Dubai fa, haba sai dai England kayan haihuwar abin cikinki, wallahi na shirya baku farin ciki, zan d'aga ki daga cikin gidan na mai dake gidan da kike bukatar rayuwa, Khadijah zan baki motar da tafi wanda na amsa, don Allah ki amince dani. Mu rayu lokacin da na gayawa Dattijo kina da ciki, cewa yayi na kai ki nijar ki haihu, amma nasan ba zaki tab'a amincewa ba, don Allah ki taimake ni, ki kula da lafiyar abin cikin ki da kuma ni. Kaddarar ki ce ta kawo ni, da kuma kaddarar cikin jikinki ya kawo ni tsawon shekaru a garin bauchi.

Ina da rayuwa da dangina, don Allah karki juya min baya, ina sonki zan baki kome kece matar da nafi so da kaunarta, don Allah karki ce zaki juya.."

"Maude! Wallahi kaji na rantse maka billahil azim, ba zan shayar da wannan wulakantattacen cikin jikina ba, ai kaci iya kudinka, kuma ka sami abinda kake bukata, ba dai jikina bane damuwarka ai samu.

Kuma nasan har abada ba zaka kuma sami mace irina ba, dan haka matsa min na sauka daga hanya na sauka zan kwanta a kasa ka rike katifar, tunda dashi kazo yawon cira ko? Toh indai zai kara maka jarin shayi da burodi ka dauka kara, dan na san fatara da talauci ya kawo ka najeriya ko? Gashi daga zuwa ka auri Sumayyah, gashi nan kazo ka kara dani."

Lumshe manyan idanun shi yayi cikin damuwa lashe bakin shi yayi, tare da zuba mata ido, zata sauka ya dawo da ita, hannu d'aya ya saka ya zare rigar jikinta, bai barta ba sai da ya sami dukkan nutsuwar da yake bukata, sannan ya janye daga gareta ya sauka zuwa ban daki ya barta tana shashekar kuka, cike da bakin ciki.

..... "Anum!!!" Kiran da Umma tayi mata ya katse mata tunanin da take yi ta mike a hankali ta fita, tare da mik'ewa tsaye ta fito waje.
"Kina ina Mamarku ta fadi innalillahi wa'inna ilaihi rajioun." Ji tayi kamar zuciyarta zata fado daga kirjinta maza tayi ta rike kirjin ta, jikinta na rawa, numfashinta yana sama da kasa.
"Ke kan kiyi asara rayuwa! Uwarki ma ba zaki barta ta rayu cikin salama ba, sai kin kashe ta kamar yadda kika kashe mun d'an uwa, wannan wani irin masifa ce.

Anya babu hannun a jikinki, yarinya sai kace yar Allah bani."

Had'iye yawu tayi tare da kai hannu zata tab'a Maman su, aka buge hannunta, aka yi tare da nuna ta da yatsa.
"Ke kan! Wallahi bamu san wani irin zunubi muka yi aka bamu ke ba, kin kashe mana mahaifi yanzun ma mahaifiyar mu baki barta ba Anya Anum kina niman lahira kuwa? Toh kar na kusku..."

"Bashir! Anya kuna yiwa kanku adalci kuwa? Meye laifin Anum, ai tayi kyan kai."

"Zainabu ki barshi yayi magana! Me aka yi da yarinyar da ta kashe Ubanta da bakin cikin! Wallahi ka mata shegen duka, me zayi da ita." Inji Goggo Hamah,
"Dakata Hamah,ke baki kashe wutar rikicin gidan kiba, ba zaki zo kice zaki kashe na wasu ba, dan haka ki ja bakin ki, babu ruwan ki a wannan karon, domin ba zaki tadda husuma ki tafi ki bar mu cikin Jalala ba. Sai mai kuna meye tayi muku?
Wannan yarinyar bata muku kome ba kuke tsana da tsangwama? Meye laifinta? Anan Hafsat Da Safiya jikin su na rawa suka kira uwarku, suna gaya mata abinda ya faru! Kai Jama'a? Anum ce baku son gani a raye ko Uwarku? Tunda nake da Anum aurenta biyar bata tab'a zuwa gidan nan da sunan kawo kara ba. Kai kana ihun ka karta tab'a ta akan me? Uwarta ce yarinyar nan tunda mutumin nan ya tafi da tarehi bata kuma barci ba wai kasheta kuke so zaku yi ne? Toh idan Anum bakin cikinku bai kasheta ba toh uwarku zaku kashe tunda ba zaku tab'a dauka maganar matsalar ku da Anum kuna gaya mata ba, wallahi ita bata kashe ta ba, toh ku hankalin ku ya kwanta."

Daga haka ta koma d'akinta ta dauko hijab ɗinta, ta saka, tare da cewa.
"Ka riketa mu kaita bakas!"

Jikin shi ne yayi masifar sanyi, duk masifar da yake ji zai yiwa Anum sai gashi Umma ta dakatar dashi tare da gaya mishi gaskiya, nima na basu zuwa asibitin,muna zuwa aka karb'eta, cikin lokaci ƙalilan suna fara bata kulawa na musamman, ina kallon kome kamar kiftawa da bismillah, kome ya lalace.

Dakyar na dawo gida, na kwanta, can cikin dare. Garin yayi sanyi kasancewar muna cikin lokacin damina ne, dan muna dawowa daga asibiti aka fara ruwan sama, wani irin feelings naji kamar me, tun bayan tafiyar Maude ban kuma jin wani abu a kan shi ba, sai yau. Dan haka ina kwance har barci yayi nasarar tafiya dani.

Wani irin mafarki nayi da Maude kafin kace me, har naji Ni cikin wani duniya na daban, tsawar da aka buga wanda yayi sanadiyar farkawa na daga mafarki mafarkin da nake, tashi nayi zaune, sannan naji gaba daya bana cikin nutsuwa, tashi nayi na tab'a flask dina na ji da ruwan zafi, dan haka na juye a babban butana. Na fito tsakar gida, a hankali na nufi ban daki nayi wankan tsarki, sannan na fito a hankali ina rawan sanyi, walkiyar da aka yi ya sani ja da baya, sakamakon kicibis da nayi da...
#Mai_Dambu...
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..

Kuskuren Baya...
BABI NA BIYAR
Cikin wani irin faduwar gaba, ta tsaya tana kallon Goggo Hamah, sannan ta wuce d'akin ta, ta rufe kofar ta kirjinta na bugawa, Allah yasa tayi wanka da alola ne.

Sallar nafilla tayi, sannan ta kwanta cike da tunanin makomar rayuwarta, a hankali barci ya dauke ta.

Kiran sallar farko, ya tashe ta. A hankali ta mike tare da nufar waje ta kama ruwa da alola, sannan ta nufi d'akinta ta fara sallah, kasancewar babu Umma da Mama yasa

tana idarwa ta fito daga d'akinta ya shiga hada musu abin karyawan tana idarwa ta tattara ta kai d'akinta, sannan tayi wanka ta shirya cikin atamfa riga da skirt, ta daura babban hijab dark pink, karamin heart face dinta ne ya fito sosai.

A hankali ta dauki basket din zata fita, taga yayunta uku har da Rulwan, rike da manyan bulalai. Cire nikkab din fusakarta tayi tare da kafe su da ido.
"A gidan uban wa kika kwana juya?" Kallon Bashir da Musa tayi, tare da cewa.
"Ni kuma? Ban je ko ina b..." Rufe ta da duka Bashir yayi irin dukar nan da akewa maza, tare da kwallo da ita, wani irin taurin zuciya take dashi, domin mik'ewa tayi tana kallon shi, tare da rike bulalar.
"Kai ba ubana ne! Kai ciki daya muka fita, Karka kuma duka na domin wallahi zan iya sakawa a maka abinda zai dame ka."

Cikin jin haushi Musa ya shiga dukarta, kamar sun sami baiwa, sosai suke dukarta, Rulwan ne ma yake musu magana, idan kaga yadda suke abin da suke ba zaka dauka Da Babba a cikin gidan ba. Amma Baaba Hamah tana kwance abinta.

Allah cikin ikon shi sai ga Ya Binta da Yaya Sadeeq, sun shigo.
"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, Bashir, Musa! Meye tayi muku?"
"Bin maza take! Jiya ma bata kwana a gidan nan ba"inji Baaba Hamah daga bakin kofar shiga d'akin.

Kallon Juna Ya Binta suka yi da Sadeeq, murmushi suka yi sannan Tace.
"Meye shaidar ki? Baaba meye shaidarki katangar gidan nan dai ba karami bane? Kuma tun Anum tana budurwa aka karasa shi, yayi tsayi, maza fa? Baaba shaidar Zina nada girma kin ganta da wani namijin ne?"

"Hajiya Binta! Kuma toh gaskiya ban ganta ba, kawai dai na ganta ta fito wanka ne talatimin dare? Kuma naga ita ba miji ba, taya zata."
"Idan ya kasance al'adar tace ta dauke fa zata yi sallar dare?" Ya Sadeeq ya jefa mata tambayar haka, take jikin Baaba Hamah yayi sanyi, su kansu Musa da Bashir, jikin su ne yayi mugun sanyi.
"Shine kika kira su, kika gaya musu kin kamata ta dawo daga yawon dare."

"Ko auren Alhaji Mudi wuntin dada rabo ne ya kaita gidan shi, amma Anum ba matar da zata sake rayuwar ta a waje ba, ƙaddara da shaidanun kawaye suka kaita ga sake jikinta ga wani namijin. Anan kina jin abinda Alhaji Mudi Wuntin dada, banda ƙaddara da rabo me zata yi a gidan shi, wallahi kuji tsoron Allah, dukarda kuka mata Allah sai ya bi mata hakkinta."

Daga haka ta juya zuwa dakin da Anum take, cikin murmushin takaici, tace mata.
"Tsalle daya ake a fada rijiya, sai kayi duba baka fita ba, dan haka tattara kayanki ki koma gidana. Tunda sunce zaki kashe mamarku."

Haka ta kwashe kayan ta, tass sannan ta tattara ta kai motar Aunty Binta, ta dawo. A hankali ta kalli kofar dakin Malam hawaye na zuba mata, sai gani take kamar gashi yana mata murmushi,. Kuka ne ya kwace mata, tana yi Jikinta yana rawa, ta juya tare da barin gidan baki daya, taje cikin motar Aunty Binta a zauna tana kuka.

Tunda Aunty Binta ta shiga, bata ce mata kome, ita kanta tausayin Anum take, tana tausayin rayuwar yarinyar, tayi kuskure a baya, amma tun daga lokacin da taji labarin rasuwar Baba Malam, dauke wutar da tayi har akayi addu'ar bakwai bata magana da kowa. Kamar mahaukaciya haka ta koma lokacin.

Sai da suka hada da rokon Allah, amma ga baki daya rayuwarta ya koma abin tausayi.

Haka tayi ta rayuwa, ga tsangwamar mutanen gidan su, ga na yan Unguwar, karshe ma cewa akayi ta shiga kungiyar asiri ne ta biya bashi da mahaifinta,ai duk wanda ya haɗa shirgi da ita sai taga bayan shi.

Dalilin da ya hanata zaman aure kenan. Wannan abun yana cikin dalilan da suka addabi rayuwar Anum, ta takura kanta da rayuwarta.

Tunda ta koma gidan, Aunty Binta, bata cika fita daga daki ba, duk da gidan cike yake da yan mata, amma haka bai sakata sake jiki da kowa ba, sai Aunty Binta, yanayin da take ciki ya kuma dawo mata da ciwonta, musamman idan taga yadda yan uwanta suke nuna tsanarta karara akan fuskar su.

... Yau ma taje asibitin, ta samu ciwon Mama ya. Haka ya faru ne sakamakon rashin hankalin da Baaba Hamah tayi, inda take gayawa su Hafsah abinda ya faru da Anum, wai tana fita yawon dare, shine ɗan Bashir da Musa sun mata fada Binta da Abubakar suka shiga mata tare da hada kayan ta,ta koma gidan Binta, nan suka shiga zagin su Aunty Binta da Abubakar.

Abinda ya d'aga hankalin Maman su kenan basu sani ba, tana sauka a gado zata ban daki ta yanki jiki ta fadi. Shine daga zuwanta suka mata tozarcin da ta kasa koda kuka, sai ajiyar zuciya. Tsabar tashin hankali, haka ta dawo gidan Aunty Binta, kamar ba zata kwana ba. Itama dole aka kaita asibitin.

Rayuwar da Anum ke gani ba zaka tab'a dauka, sun sota da kamar ya ba, sabida yadda suka nuna mata kaunar. Asalima kaunar da suke mata irin soyayyar nan da ake cewa uwa ba kwab'a, Uba babu tsanani.

Soyayyar da aka nuna, mata wanda duk abinda take so, shi ake so, soyayya irinta yaran da babu abinda suka sani sai sangarta da sakalci, wani irin tashi Anum tayi wanda bata san kwab'a ba, ko hantara ba. Anum ta tashi bata san kome ba sai zunzurutun rashin kunya, da fitsara.

Dan haka kwananta biyu, aka sallame ta, sannan ta dawo gidan Aunty Binta, tana zaune. Da yamma dan tayi alkawarin ba zata kuma zuwa ba, sai an sallame Mama, ita kanta Maman ta,.tana mugun kewarta.

Amma yadda yan uwanta suka gina zuciyar Mahaifiyar su, da kin abinda Anum tayi yasa take boye kewar Anum din.

***

Tana daga daki taji Yar kishiyar tsakar gidan Aunty Binta tazo gidan, alamun tayi yaji. Tunda tazo take sake surutun abinda mijinta yake mata.

"Wallahi, Maman Shukrah. Ba halin nayi abu zai hauro min, wai dan yana niman aure, ba halin ya shigo gidan, yayi ta masifa kenan, wai kaya a watse."

D'ago labule nayi ina kallon ta, nayi ita kanta a hargitse take, domin bra ɗinta har saman kafad'arta, daga nesa na fahimci irin matan nan ne masu kyau, amma duk ta dishe, ga mace har mace, amma idan kaga zanin jikinta Super vlisco ne fa, amma yayi mugun fita hayacinta.

Sake labulen nayi tare da kwanciya ta, ina jin Mahaifiyar ta ta ta biyo ta, da yaron ta karami yana kuka shi kanshi idan ka ganshi zaka dauka ba danta bane,toh ban yi mamaki ba, domin tunda naga kayan jikin shi na fahimci kalar uwar shi, domin

wandon jikin shi ta shadda ce Gezani, amma wallahi ya fita hayacin sa,rigar yar kanti ce a jikin shi a kala ana sayar da rigar 3k.

Jinjina kai, nayi tare da sake d'ago labule naga kitson kanta, tana dariya tabar gidan, shigowa Shukrah tayi, tana tsaki.

"Aunty Anum! Kiga sakarci kowa yasan halin Badi'a da kazamta, amma kiga don Allah wai yaji tayi sabida mijin yace ta gyara."

"Toh ai tayiwa kanta, tana da masu share mata kuka ne, kyaleta."

Daga haka ban kuma magana ba, na gyara kwanciya ta, sabida yarinyar bata da wani hankali, da dare Aunty Binta ta tafi asibiti aikinta, naji anata shari'a da mijin Badi'a, anan yake gaya musu abinda take ga mugun kazamta, ga shegen rowa, tare da son jiki.

Sam gidan shi babu inda zaka zauna kaci abinci, sannan idan ya kawo madaran karyawa, wallahi tana buɗewa anan zata ajiye mishi tayi gaba abinta, yace tana da masu aiki amma ba zai hana kaga ko ina a kazamce ba, yayi juyin duniya ta gyara taki, ga shi, har hakkin auren shi bata bashi sai yayi mata bori, shi bawai baya sonta bane a'a yadda ta maida kanta wata mara adalci. Yadda yake bayanin bata musanta ba, shiru tayi tana zare idanu. Nan Baban Shukrah ya bata hakuri, sannan ya juya ya bar gidan. Ita kuma aka mata fada, sai lokacin ne Mahaifiyar tane ta kawo ta dakin da muke, ta kalle ni, tace.

"Anum don Allah ga Badi'a, wallahi dakin mijinta shine rufin asirinta, bawai tonawa kai asiri ba, ai Kinga yadda Alhaji yake dauke da dawainiyar mu, ga na iyalin shi yau aka ce baya nan asirin mu ya tonu, amma idan ta zauna a d'akinta yaron nan yana da kirki. Ga ta nan ai."

Mamar tana fita, na kalle ta tare da sake murmushin takaici.

"Badi'ah kina sha'aninki."

Shiru tayi sannan nace mata.

"Tsakanin ki da Allah mijinki yana cutar ki?"

Cizon lips dinta tayi sannan ta girgiza kanta.

"Kema kin yarda baya cutar ki?"

"Eh Aunty Anum!"

"Toh me yasa kika rena shi?"

Idanunta ne suka kawo kwalla,

"Ko baya gamsar dake ne, a shimfidin ku?"

"A'a wallahi;"

"Toh meye ya kawo reni a tsakanin ku?"

"Wallahi babu kome Aunty!"

"Jin dadi ko?"

"A wannan lokacin mata suna bin maza domin su kwanta dasu, babu ko sisi, shine ke zaki wulakanta naki? Baki rasa ci ba, baki rasa sha ba. Shine zaki tozarta auren ki? Kin san iya adadin sab'awa Ubangiji da kika yi? Kawai rayuwar yanci ko?"

Girgiza kai tayi, can kanenta suka shigo har da Yayarta da suke Uba daya ta shigo itama bazawara ce, kallon su nayi, tare da kallon agogon bangon dakin, kafin nace musu.

"Kun zo kun baza kunne da baki da hanci kuna kallona, bayan koda nayi muku fadar ba dauka zaku yi ba, dan haka tattara shirmen ku, ku bar min d'akina."

"Don Allah Aunty ki mana fada wallahi zamu dauka Hajiya Yaya duk ta damu."

Tashi nayi na zauna, tare da kallon su, kafin na sunkuyar da kaina, na fara matsa yatsuna suna kara, sannan na kalle su daya bayan daya nace musu.

"Duk wanda kuka ga tana ihun Ba'a mata adalci ba ku fara duba meye asalin rayuwarta?

Me ta rasa a rayuwarta? Shin aure ibada ce? Ko rayuwar yanci ce? A iya sanina ni dai nasan ibada ce, amma ban sani ba ki Badi'a tana da wani abinda yake bukata a rayuwar auren!"

Girgiza min kai suka yi. A hankali na lashe bushashen lips dina,.sannan na zuba musu ido. Kafin na fara cewa.
"Ban sani ba ko zaku dauki darasi a cikin Zanen qaddara ta ba, amma bari na duba kadan daga cikin rayuwar da nayi a baya,"

Rayuwar Anum.
Zaune take a kofar gidan, ta saka kwanon tuwon shinkafa fara yar dass, miyar taushe wanda yaji kabewa da yakuwa, gashi yasha manjan asali na kasar Idda, sai wani daukar ido yake, yarinya ce yar shekara goma cif a kofar gidan, ta zauna tana shashekar kuka, .zaka rantse da Allah zaneta aka yi, a'a kawai tsabar kiyayyar ta da tuwo ne, sake shure kwanon tayi abincin ya koma gefe ta kuma tsalla ihu, kamar an yanka namar zuciyarta, ta fashe da kuka.

Had'a shayi yake, amma gabaki daya jikin shi rawa yake, shi mutum ne da bai kaunar jikin kukan yara, dan haka ta window kofar shagon, ya leko yana kallonta sanye da riga da skirt na kanti, kanta ya sha kitson zare. Idan ta d'ago ta kalli mulmulen tuwon shinkafar gabanta sai kuka ya kuma kwace mata.

Kallonta yayi cikin nutsuwa, har tsigar jikin shi yana mik'ewa, a hankali ya fito, daga cikin shagon ya kalleta murmushi ne ya kwace mishi yadda ta zuba tagumi, zuwa yayi ya tsuguna yadda zai kare mata kallo yace mata.
"Yarinya me kuka! Meye sunanki?"
D'ago kai tayi tare da saukewa kasa tace.
"Anum!"
"Me yasa ki kuka?"
"Wai naje na gama shan wahalar makaranta sannan a ce naci tuwo Wallahi bazan ci tuwo ba!"
"Toh me zaki ci?"
"Taliyar Maman Dija"
"Ta nawa zata ishe ki?"
"Nera talatin!"
"Shikenan nan"
"Eh shi kenan!"
Ciro hamsin yayi ya mika mata, da sauri ta mike, zuwa cikin gidan ta dauko kwano tare da fita da gudu, tana murna, girgiza kai yayi cikin nutsuwa.

Haka ya koma shagon shi ya cigaba da aikin sayar da shayin shi,. Har ta sayo ta dawo tana isowa ta mika mishi ashirin din tace mishi.
"Me shayi kaga ban maka godiya ba, Nagode fa yau sai dai Mama taci tuwonta."

Murmushi yayi tare da girgiza kai, yana kallonta ta wuce da sauri, Anum kenan.

Haka ta cinye taliyar ba tare da ta tuna da kowa ba, sanan ta shige dakin Umma ta kwanta, Domin kar Mama tace tayi Sallah, domin ta ki jinin sallah, tana yi ne dan ya zama mata dole tayi, amma da dan ita ce ba zata yi ba, kuma Mama ba kyaleta zata yi ba..
#Mai_Dambu
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai...

 Feel Free.... Free book ne😂
Maude.
BABI NA SHIDA.

Mike kafa tayi ta tare da sake baki ta fara sharar bacci, tun karfe ɗaya na rana, take barci har biyu, asalima yadda ta konta ba zaka dauka cewa akwai mutum a dakin ba. Haka ta wuni.

** "Ila ban tab'a ganin wannan yarinyar ba, sai yau."
Ya tambayi abokin shi da suka haɗu kwanan shi yayi mishi sanadin samun shagon kofar gidan su Anum.
"Khadijah! Itace karamar yarinya a gidan nan, Kanwar su Alhaji Abubakar ce, taGna gidan shi ne ko nace bata cika zama a unguwar nan ba sai a gidan yayunta."

"Ai shi yasa ban cika ganinta ba, amma akwai rikici naga za ayi rigimammiya ta karshe!" Ya faɗa yana hada shayi ga wani matashi. Suna wannan maganar ne cikin harshen buzanci.

... Karfe hudu na yamma, ta fito tana tsalla ihu, zaka rantse yagar namar jikinta ake, amma ina kawai ance taje makaranta ne, wato islamiyya, take wannan ihun. Girgiza kai yayi sannan ya kalleta tana tsaye da yar jakar buhun siminti.
"Toh Sarkin kuka,zo ki gaya min me aka miki!"
"Ni bazanje islamiyya bane!"
"Akan me?"
"Mama taki bani kudin tara, Umma kuma ta dake ni wai banyi sallah ba, kuma da safe nayi sallah dukkan na yau."
"Yau naga abin duniya, Ni Maude.. ai ba a yin sallah haka"
Sake baki tayi tana kallon shi kafin ta sunkuyar da kai tana jan kukan da zatayi.
"Toh nawa ne kudin tarar?"
"Zan sayi calbin malam! Hanjin ligidi! Tsami gaye, aya da gyad'a. Dan malele!"

"Duk a cikin ki zaki zuba Dijamah?" D'ago manyan idanunta tayi kafin ta fara jin wani sabon kwalla na zuwa mata ta, ta fashe da kuka.
"Toh... Toh....toh... Ya isa haka ai ban ce ba zan baki ba, zan baki nace meye na tara mana jama'a."

Sai ka rantse da Allah, dukar ta yayi, haka ya ciro Naira hamsin ya bata tare da rakata har islamiyya rariya da yake bakin kura, tana shiga get din makarantar ya juyo abin shi.

..... Tunda suka shiga aji Beauty take kallonta.
"Yau kin zo da kudin tara ne?"
Tura baki tayi sannan tace.
"Mama da Umma sunki bani kuma sai na gayawa Malam"

Kallon rashin wayo XOXO tayi min, kafin tace min.
"Yau wallahi karki gayawa Malam kizo zan kai ki gurin Baba lado, idan kina son kudin tara zai na baki yana saka miki hannu anan d'inki".
Wani shegen yawun tsoro ta had'iye, tare da zare ido waje, ta koma can gaban ajin ta zauna.
"Anum!"

"Babu ruwanki dani! Idan ya Abubakar yaji wannan abun yanka Ni zai yi kamar yadda ake yanka kaza, kuma yace a wutar jahannama ake wurga masu aikata haka. Ni babu ruwana."

Ta fadi haka tare da canza gurin zaman ta.
(Kira ga iyaye! Mu kula da yaran mu,musan da suwaye suke mu'amala. Kuma mu gaya musu illar zina da masifar shi.)

Duk yadda suka so shiryawa da Anum taki kula su, asalima tsoron su take dan gani take kamar suna aikatawa ne shi yasa suka mata tayin itama tayi joining dinsu.

Koda aka yi tara, fita tayi wajen makarantar tayi sayayyar abinda zata ci, sannan ta juya ta koma cikin ajin. Akan kansu sun san halin Anum da shegen taurin kai da kafiya, duk da XOXO shekaranta zai kai sha uku, haka Beauty zata kai shekara goma sha daya. Anum ce me shekara goma.

Malam Muhammad Bello.
Asalin dan garin Badara ne a can karamar hukumar kirfi na jahar Bauchi, matar shi Umma Mariyah itace ya aura tun saurayi da budurwa. Sai Mama Hauwa'u. Ita a bazawara ya dauke ta, kasancewar ita yar kabilar Igala na jahar kogi.

Umma tana da yara bakwai Aunty Binta, Abubakar, Aunty Aminatu, Aunty Rabi', sai Aunty Maryam sai dan autan tan ta Rulwanu,

Dakin mu kuwa cike yake da zaratan maza, Aminu shine Babba sai Usman, BASHIR, Yusuf, Hafsah, Safiya, Sai Ahmad, Musa. Abdul Hakim yana can Imo yana aiki, sai Muttaka sai Ni ce auta Anum KHADIJAH MUH'D BELLO....

Lokacin da aka haife ni yayi duk Yaran gidan mu sun girma dan sun kusan kammala karatun su, aka haife ne. Domin lokacin Ya Binta yaranta shida, Aunty Amina tana goyon Takwarab malam, Aunty Maryam kuma ta yaye Fatimah.

Nice karama sosai dan nazo akan girma ne, dan haka kowa ya tattara soyayyar duniyar nan ya aza min a kaina.

Kasancewar itace auta duk wani tab'ara da sangarta ya kare a cikin ta, ba abin damuwa bane Anum tayi ta zuba ihu, tare da rikicin gangan. Ko kuma tayi ta nimo rigiman yara.

Bata cika zama a cikin gidan su ba, tafi zuwa gidan yayunta ta zauna, idan ka ganta a can sai ka rantse sune suka haife ta.

Tun tasowarta Abubakar yana yawan musu nasiha akan babu kyau wasa da maza, hakan yayi tasiri akanta da kuma yanayinta na karamar Kanwar su.

XOXO.
Wacce sunanta Abidah mahaifiyarta tana aiki ne a gidan Alhaji Ghali me sugar, Mahaifinta yana sayar da buhu da tsofin kaya ne a kasuwar muda kasan bauchi, asalin su yan Bauchi ne.mazaunan garin yalwan shaandam fadar da aka yi shekarun baya ya dawo dasu gida.
XOXO kyakyawa ce fara doguwa, kasancewar mahaifiyar ta, bata zama dasu da ita yasa yarinyar ta dauko hanyar lalacewa, dukda haka sai da aka sami

wani mara imani yana bata naira talatin yana wasa da jikinta, haka ya haifar mata da girma so fast kana ganinta kasan tana hulɗa da maza.

Yarinyar tana mugun rawan kai, da iyayi yarinya karama ce amma zaka rantse uwar mata ce, ga iya manyance. Gidan da suke haya irin babban gidan nan ne, kuma akwai matan aure da zawarawa a cikin gidan, akwai yan matan amare, akwai gwauraye matasa marasa aure har da yan cirani anan duka a gidan.

Sannan wani abun takaici gidan a gwamutse yake, idan nace a gwamutse babu Yaren da babu Hausawa, Inyamurai, yarbawa, fulani, da wasu Yaren garin bauchi.

Dogon gida, basu iya fada ba ga munafunci da gulma, an iya ririta magana, duk yadda kaso kaji gulma idan ya wuce dogon gida ba zaka tab'a jin shi ba kuwa, ga rashin tarbiyya yaro karami idan ya lallaiyayo maka ashari'a sai ka zata a zamanin maguzawa ne, ita kanta Adama Maman Abida, ta iya munafunci da gulma, ga sata kamar jinin b'era, sannan ba abun damuwa bane ta zauna tayi gulmar mutum, idan ta ganshi ta nuna nan duniya babu irin shi.

Matasan da suke zaune a gidan, duk tayi gulmar su karshe yaron cikinta yake fitowa yana auna mata ashari'a.

A haka da take zagin yaran wasu da dibe musu albarka gani take baya sauka a kan nata, ga dai XOXO yarinya ce amma Idanunta ya buɗe da wasan banza, idan kaga yadda maza suke yi da ita sai ya baka tsoro, sannan ita kanta ta iya niman maza da iyayi da kwainani, idan tana magana zaka rantse da Allah babbar mace ce.

Sannan daga kofar gidan maza yan cirani suke zaune, abin takaici da tausayi idan suka dawo daga sayar da raken su, haka zasu kirata suyita jagulata, har sai sun kauce hanya sannan suke kyale ta,

Beauty wacce sunanta Halima, irin gatsen nan ne, domin ko kama sunan Beauty bata yi ba,. Kawai ana gaya mata ne saboda yanayin ta.
Mahaifinta malamin makarantar primary rariya ne, mahaifiyarta tana sayar da kayan miya a cikin gidan su dake bayan rariya primary school.

Da yamma kuma tana fitar da danyen awara, tana soyawa da dare a bakin titin bayan gari.

Wato idan kana niman maha'inciyar mace kasamu Maman Halima, toh an rufe an shafa fatiha. Matar tana da mugun kwaɗayi ga masifar bala'i, ga cin bashin tsiya kuma idan kaci nata ta hanaka barci.

Ga karya da kazamta, amma kuma a haka bata zagin y'ay'an mutane, ita dai burinta kar ayi babu yarta, tun beauty nada shekara tara ta fara saya mata man bleach cewar ta yarta bata da kyau dole ta haɗa da wanka. Wani abun da ta manta dashi, shine Allah yayiwa beauty Baiwar gashi har gadon bayanta.

Dake rumada ne irin bayin fulanin nan, amma wallahi idan tayi tsifa sai ka rantse da Allah gashin doki ta saka, gashi baƙi sidik, gashi bata samun kulawar da ta dace, amma idan kaga gashin sai ya burgeka.

Ko Anum da mahaifiyarta ta kasance yar ƙabilar Igala, gashin ta ja ne saman shi kasar shi baƙi.

Beauty da XOXO tasu tazo kusan daya domin kuwa halayyar iyayen su ya jefa su kazamin rayuwa..
.....
Maude.

Maude dan kasar nijar ne, buzu ne kyakyawa ne, babu laifi idan kasan ajey mijin kajol toh haka maude yaƙe, karfafa ne. Yana da kiran jaruman maza, wanda kana kallon su zaka Fahimci mazaje ne a tsaye a gaban ka, mutum ne da matukar yana tafiya zaka iya hango nutsuwa, kamala, dattako, domin a yanzun yana niman shekaru arba'in a duniya, bai cika walwala ba. Amma yana da kyawawa halayya, yana da hakuri da kawaici..
Wani abun da mutane suke kara girmama shi, mutum ne wanda yake da addini, idan yana karanto Alqur'ani sai ka rantse da Allah, bakon Balarabe ne.

Idan kuwa aka tab'a shi, toh ka girmama abinda zai sanya yayi magana, shi yasa yake zaune lafiya da kowa, kuma shagon shi cike yake da matasa, ana hira. Musamman ya sayi tv ya saka sabida masu zuwa shan shayin shi suna kallon kwallon.

Yan iskan bakin kura shakka shi suke badan kome ba, sai dan sun fahimci bai da dad'i, domin kuwa sun tab'a zuwa bayan gari suka yi fada yan kwanar kwaila, da yan bakin kura suna zaune kawai sai ga matasan bakin kuran sun tawo zasu tafi fada da yan kwaila, kawai me zai faru!

Sai suka tsaya a bakin shagon shayin shi, zasu mishi diban albarka, yace musu.
"A'a jijiya kuyi tafiyar ku kawai, nan gurin sana'a tace."

"Toh idan munki fa, kasan Allah zamu kaddamar maka." Inji jijiya.
"Da dai zaku tafi zai fi alfanu."
"Kai ku watsar da kayan shayin shi yayi abinda zai yi."

Masu shan shayin duk sun watse, murmushi yayi sannan ya cigaba da abinda yake, yana jin wani irin yanayi, wanda rabon shi da fuskarta haka shekaru biyar baya.
Yana jin Dan sara sukan ya shigo shagon da niyyar watsar mishi da kaya, wato da maude ya rike hannun Yaron ya murɗa baya, ya tima mishi dun-du a bayan shi sai da ya kwara amai, a gurin ya suma.
Kallon su yayi fararren idnun shi,.suna kuma rinewa izuwa jajjur, tunda ya zuba musu ido.

Da gudu suka bar shagon har rana me kaman ta yau basu kuna dawowa ba, kuma bai fasa abinda yake yi ba, sai ma karshe dawowa da yaran suka yi zasu zama yaran shagon shi.

Zama dasu yayi cikin nutsuwa da sanin ya kamata yace musu.
"Bangan siyasa ba naku bane, ki kashe junan ku, Ni bako ne ina da rayuwa na, ina da kane irinku. Amma dayawan su, suna makaranta da aikin kamfani ko aikin gwamnati.

Dan haka kuyi kokarin daina shan kayan maye ku kama sana'a yafi kashe juna da kuke yi.

Bana jin dadin ganin kun lalata tarbiyyar ku da rayuwarku, ba zaku gane rayuwa tana da muhimmanci ba, sai lokacin da kuka wayi gari kana raye amma baka da ikon

sanin halin da wani naka yake ciki nan ne zaku gane muhimmancin rayuwar da kuke wulakantawa."

Yayi musu nasiha sannan ya kuma kara da tambayar su me suke son yi. Kuma suka gaya mishi abinda suke bukata yace su bashi lokaci yayi nazari....

Wannan kenan...

Tafe take rike da calbin malam, dayan hannunta madaran kuka ne.. ta kalli wani yaron irin yaran nan ne masu katon kai, da gudu ta watsa mishi madarar kuka, tace mishi.
"Rabe me kai uku daya doya daya dankali daya Allah ne ya bashi."

Aikuwa yaron ya biyota da mugun gudu, ta falla a guje sai shagon Maude, tana shiga bata tsaya ba,.sai a bayan shi, jan wani majina tayi sannan tace mishi.
"Maude Abokina boye Ni kace bana nan"
Ba musu yayi hakan, tare da leka yaron. Sai zare ido yake tare da goge madarar kukan da ta watsa mishi.
"Toh zo nan ayi shara'a, dan zan iya zaneka idan ka tab'a min Kawata."
Cikin kuka yace.
"Ce min tayi me kai uku!"
"Dijamah haka ne!"
Rike rigar shi tayi ta baya.
"Toh tayi laifi bari na baka bread da bota ko"
Aikuwa Anum ta daka tsalle tace ba za a bashi ba.
"Wallahi ka bashi na rantse sai na kwashe kafarshi,.kuma na daina abota da kai."

Lallabata yayi ta shige gidan su, ya sallami yaron.
"Alazi wahidin!!!! Iya Dan Malam na sallama!"
"Anum idan nazo gurin sai na fasa miki baki da shegen murya kamar na babanin akuya."
"Ruwanu ruwanu ruwanu, baka iya aiki ba sai cin tuwon umma da Malam ruwanu me katon kai,.da katon baki."

Haka ta cigaba da tsokanar yayanta Rulwanu, bai kulata ba dake Umma na gurin, sai Mama ce ta fito daga dakin Malam ta rike mata kunne, aikuwa ta callara kara zaka rantse da dukarta aka yi nan kuwa zunzurutun makirci ne da ta fara koya a gurin su beauty da XOXO. Amma Mamah bata mata kome ba...
#Truelifestory
#Mai_Dambu
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..

BABI NA BAKWAI.
Kuruci dangin hauka....

Cikin jin haushin sharrin da take shirin mishi ya mike tare da falla mata mari, aikuwa ta kuma callara kara, tare da watsar da kayan makarantar islamiyya da ta fito.

Rige rige ake tsakanin Umma da Maman Aminu, ganinta suka yi tana ihu da birgima zaka rantse da Allah, shegen duka aka mata.

"Wayyo Allah na, wayyo Allah na. Wayyo ya kashe ni, na mutu na lalace, wayyo fuskana, Allah ya isa min mugu kawai Azzalumi me shan wiwi."
"Kambu ina wasa dake ne? Yaushe kika ga nasha wiwi, wallahi sai naji miki ciwo dan kaniyarki."

Kafin ya rufe baki Umma ta dauko bakin wuta ta rufa mishi da gudu ya fice daga gidan, yana huci. Tare da alqawarin sai yaci kaniyar Yarinyar nan idan ya kama ta, yana fita ta kyalkyale da dariya, cikin takaici Umma ta Zungure goshinta, aikuwa tayi kwalkwal da idanu cikin fada tace mata.
"Yaushe kika koyo makirci? Khadijah har kin san ki saka kuka ba tare da anyi miki kome ba? Toh idan kika kuma sai.."

"Maman Sadeeq! Yarinya ce fa? Ban ga amfanin a dinga mata fada ba." Inji Malam wanda ya shigo gidan yanzun, cike da mamaki Umma take kallon shi,
"Malam tun icce yana danye ake tankwara shi, idan ya girma ba zan mana dad'i ba, Anum shekara goma ace ba za a mata fada ba?"

"Maman Sadeeq! Ni banga amfanin tasa Anum a gaba ana mata fada ba, idan tayi hankali zata gyara." Ya fadi haka tare da cire takalmin shi ya shige dakin shi, ita kuma Maman Aminu ta wuce kitchen tana iza wutar tuwun da ta daura, Anum ta shige dakin Malam tana b'abbaka dariya, suka bar Umma A tsaye a gurin. Jikinta a mace ta koma d'akinta.

Umma wacce sunanta Mariyah yar garin dewu ce, iyayenta manyan mutane ne a garin dewu, asalima fulanin can ne, mace ce me dinbun hakuri da sanin ya kamata, tana da halin girma da mutunci. Gashi abinta bai rufe mata idanu ba, Umma irin mutanen nan ne, masu shegen zurfin cikin, sannan tana da hangen nesa. Allah yayi mata baiwa da idan tace karka yi abu toh wallahi karka yi domin kuwa daga baya da kanka zaka bata labarin abinda ya fara idan ya kwab'e maka.

Saba'in Maman Aminu da Allah ya daura mata jarabar son abun duniya, yaranta da ta aurar gani take mazajen su basu dace da su ba, kawai malam yafi karfin tane, shi yasa ta dauki burin duniyar nan ta daura akan KHADIJAH,ta kuma hada da gaya mata ita kyakyawa ce kamar fure, Kullum Mama idan ta zauna da Anum ce mata take.

"Ke lu'ulu'a ce,.kin fi sauran yan uwanki, kin fisu farin jini, dan haka ka mata yayi ki auri mutum me daraja, wanda zai d'aga darajar ki sama da ta kowa, duk wanda yayi fushi sake tabbas baya kaunarki ne, Ni da Malam muna sonki dan haka ki nutsu ke kane jari na ce ke"

Wadannan zantuntukar take gaya mata, dake yarinya ce Anum sam hankalinta bai cika daukar shi ba, asalima yarinyar tana da mugun wasa, Maman Aminu tana da Babbar yarta Mawedo tana aure a can kogi a garin dakina.

Rabon su Aminu ya kai Malam aikin can ya ganta ya aurota, kuma zaman su masha Allah, domin Allah ya azurta su sa yara.

.... "Malam ni bana son Oga Chide !" Ta fada kamar zata fashe da kuka, a hankali ya zuba mata ido, wani irin abu tayi da idanunta. Take ta bashi tausayi yaji a ran shi ba zai barta ta koma Oga Chide ba.
"Wani makaranta kike so?"
Dake Oga Chide wani makaranta inyaramuri ne, a nan Ibro quarts, dan haka ya jefa mata tambayar da yake ran shi.
"Malam Ni dolphin nake so."

Ta faɗa tare da zubda kwalla, har da shasheka.
"Shi kenan, Uwata."
Ya ce mata,
Da ihunta ta fice daga d'akin, tana daka tsalle.

Bayan fitar ta ya d'aga wayar shi na tafi da gidanka ya kira Abubakar ya gaya mishi yadda suka yi da Anum, sosai ran Abubakar ya b'aci yayi ta faɗa, dake Malam ya san me yake yi nuna mishi yayi, a'a shi ne yake son sauya mata, makarantar bawai dan ita ba.

Wanda kuma ba haka bane, kawai KHADIJAH bata niman Alfarmar Malam ya haɗa da na kowa ne, shi.

A yanzun da take da shekara goma, rigimar da take yi sai ka rantse da Allah, yar shekara biyar ce, ga rashin jin Bala'i.

Ita kanta Maman ta bata san maude yana bawa Anum kudi ba, har aka maida ta Dolphin. Zoku ga dauki da murna rawan kai da rashin kunya ya dadu, bata cika shiga harkan kowa a cikin unguwar ba sai Maude, wanda shi yake dafa mata Indomic da safe da tea,.ya bawa Rulwanu ko wani daga cikin yaran shi su kawo mata, ya kai cikin gidan.

Wa anum, taci ta gatse su a tunanin su malam ne yake sawa ana bata, sai da abun ya ishe Umma ta zubawa malam ido tana dama kunun tsamiya da safe, shi kuma yana dokin kofar kitchen ɗin, dake Malam simple Man ne kuma bai zafaffawa rayuwa ba, idan matan shi basu gama girki ba, yakan zauna ya jira su, suna hira dashi aka shigowa Anum da kofin shayin tare da soyayen kwai da burodi.

Amsa tayi ta gyara zama zata fara ci, Umma ta kalle shi tace mishi.
"Malam wallahi wata rana zaka yi kuka da Anum fa? Taya ga abin karyawan nan a cikin gidan zaka na amso mata shayi daga waje?"

Juyawa yayi tare da kallon Anum, dan dama da Umma ta titsiyeta cewa tayi Malam ne yace kullum tana amsar shayin.

Kallonta yayi cikin nutsuwa, sannan ya zubawa Maman Aminu ido wacce ta b'ata rai akan abinda Umma ta faɗa.
"Ni nasaka malam Maude yana bata shayi, dan naga bata son tuwo da kunun da ake damawa!"

Zuba mishi ido Anum tayi cikin mamaki yadda ya kare ta, murmushin jin dadi tayi tare da yankan wainar kwai da Maude yayi mata shi kamar bai san zafin nima ba, tana gama karyawa ta koma d'akinta, tare da kallon basket din ta.

"Mama viju kawai na gani da karamin panke?" Ta faɗa tare da b'ata rai,
"Toh me kike so?"
"Ni wallahi ba zan tafi makaranta da wannan abincin ba, naje yara su rena ni!"

Kallonta Maman ta tayi tare da cewa.
"Toh me za ayi miki yanzun?"
"Nifa ba zanci wannan panke bane, kawai a dafa min indomie ko kuma naje gurin me shayi ya bani."
Ta faɗa tana kallon fuskar Mamanta.
"Yawwa Jeki kawai gurin shi nasan zai baki."

Da gudu ta fita, rike da skull basket din ta, tana fita suka haɗu da Umma, b'ata rai tayi Anum tayi tare da fita da gudu, girgiza kai Umma tayi tare da mata fatan shirya, musamman Malam da Maman Aminu, sune suke son lalata tarbiyyar yarinyar su.

Allah ya gani tana mugun son Anum, tun daga ranar da aka haife ta, kai karewa hatta yaye Anum itace tayi, domin mutane basu cika yarda ba ita ta haifi Anum ba, gani suke kamar yarta ce ba Maman Aminu bace ma ta haifeta.

.... Tana fita ta nufi shagon Maude, ta tsaya zata mishi kuka, bai ma lura da ita ba, yana fama da d'aga shayin shi.
"Ke Abun zoki wuce kafin na sab'a miki!"

Kamar dama jiran Rulwanu take yayi magana ta fashe da mugun kuka, sake kofin shayin hannun shi yayi da ruwan zafi, tare da juyawa gareta, bai tab'a jin wannan yanayin ba tunda yake a rayuwar shi sai akan Anum, kirjin shi kamar ana mishi lugude.
"Dijamah me yasaki kuka? Ba zaki makarantar bane? Rulwanu ne ya miki magana ranki baya so? Kiyi min magana mana"
Tuni ya tsallake mutanen shi ya durkusawa yayi a gabanta, yana ji kamar sheka mishi ruwan zafin shayin shi ake a jikin shi. Cikin raunane murya yace.
"Waye ya tab'a min ke zaki makara fa?"
Kamar wacce ta tashi da ciwon baki ta bude bakinta dakyar tace mishi.
"Wai da panke da viju zanje makaranta kuma kawaye na rena ni zasu yi..."

"Ila! Juye min wancan soyayyen indomie da sadine din, ka kuma soya mishi wani, a saka miki ketchop!"
Gyada kai tayi, "toh ka zuba mata ketchop a gefen shi."
"Amma Maud..."
"Ila umarni na zaka bi ko Ni zanbi naka!"

Hannun shi ya kai goshinsa yace.
"Yallabai!"
"Meye haka"
"Kayi hakuri."
Da sauri ya amshi box dinta,
"Anum idan kika kukan banza, kinji nan dina ji nake kamar zai fashe don Allah ki daina kukan banza baki ga kin girma bane."

Tura baki tayi idanun ta na kawo ruwa.
"Toh shikenan! Karki yi kuka."
Mika mata box din aka yi ta bude tace.
"Aww kai jibi yadda ake min shi stylish, nagode Abokina Maude."

Tana fita ta juya tare da d'aga mishi hannu, tana murmushi, da gudu ta nufi inda motar da Ya Abubakar ya turo a kai ta makarantar.
"Malam Maude! Nagode sosai da dawainiyar da kake da Uwata!"
Cike da kunya ya kama sosa kanshi, yace.
"Ai yiwa kai ne kuma, yarinya ce qarama tana fara girma zata bar kuruciyar da take."

Haka malam ya mishi godiya tare da wuccewa gurin aikin shi.
"Oga Maude! Da alamu ka fada soyayyar yar jinjiran malam Bello."
"Kai haba, yarinya ce fa kawai dai ina kewar yaran gidan mu ne."

Tun daga lokacin, Maude ya dauki nauyin karyawan Anum da na makarantar ta, a cikin gidan kuwa duk abinda tayi ganin ake dai dai ne, hatta yayunta maza da mata babu me iya mata fada, asalima kallon karamar yarinya suke mata, karshe Umma sai da tayi musu fata fata,.kafin aka hana maude ba saka mata abin cikin makaranta.

"Anum ba zata dawo gurin mu ba, wai yayanta ya hanata wasa da maza!" Inji Beauty tana kallon XOXO,

B'ata rai tayi tana kallon shagon Me shayin da Anum ta mai da mishi cup din shayin shi da plat din da ya bata soyayen kwai.

"XOXO!"

"Kinga kyale ni, matukar ina ganin abinda nake so Anum tana kwace min sai naji kamar na kashe ta." Zaro ido Beauty tayi cikin tsoro,

"Babu kyau maganar kashe mutum!"

"Amma ai kinsan na gaya miki ina son wancan me shayin yayi ta tab'a min nan dina me yasa shi yafi son tab'a na Anum?"

"A'a bafa kome yake mata, kawai tana zuwa gurin shine karb'an shayi." Inji Beauty,

"Toh yau sai na sakata kuka a cikin ajin mu."

"Amma XOXO, kawai dan ta rabu samu sai mu mata abinda zai sata kuka?"

"Tafi ki bani guri tunda ba zaki taya ni fada da ita ba."

"Shi kenan."

.... Aikuwa karfe hudu na yamma ta fito zata islamiyya, ta tsaya a gaban shagon Maude, ya mika mata nera hamsin, murmushi tayi mishi sannan tace mishi.

"Nagode wata rana zan rama maka." Ta fadi haka da gudu, ta bar gurin aikinta kenan bata tafiya a nutse, gudu yafi kome dad'i a rayuwarta,

Tana shiga get din makarantar, ana fara tsare lati dan haka ta nufi ajin su, tana shiga yara suka zuba mata ido, wich mean anyi gulmar ta kenan,

Dan haka ta isa kusa da karimah ta zauna, ta tashi ta bar mata gurin. Dake yarinya ce da bata daukar iskanci tace mata.

"Dalla Malaman su dawo ki zauna uwar me nayi miki?"

Kallonta karimah tayi tare da kallon XOXO karimah tayi sannan tace mata.

"Ai ke kina wasan kwakule da me shayin kofar gidan ku, dan haka daga yau..."

Cikin tsananin masifa ta tacame wuyar yarinyar, tare da kai mata duka, kamar Allah ya aikota, dukda su XOXO sun shigawa yarinyar bai hana Anum dukarta ba, tana ihu sai ta gaya mata inda ta gansu sunyi wasan kwakule. Yarinyar da taji wuya, tace mata.

"XOXO ce tace mu gaya miki haka."

Sake yarinyar tayi tana kallon XOXO, bawai tafi karfinta bane, kawai tana image yadda ta kula mata sharri...

#Mai_Damu...

Aslm barka mu da wanan lokaci nice takuwa Ayusha idris wace kuka fi dani da Mrs Muhammad Bashir kamshi traditional herbal medicine and more

Mata *yan* *uwana* *kuzo* *gadama* *tasamu* *wace* *zamuyi* *yaki* *da* *wanan* *cutar* *da* *ta* **adabemu** *ba* *kowace* *cuta* *bace* *wanan* *bace* *cutar* *sanyi* *wanan* *cuta* *tana* *takurawa* *mata* da *maza* *yaran*

mu **da** *manyan* *mu* *to* *gaskiya* **mata** *fa* *sai* *mun* *dage* *mun* *magance* *matsalar* *da* *tada* *me* *mu*

Ayau *nazo* *muku* *da* *ingantattun* *magungunan* *sanyi* *da* *basu* *da* *illa* *sanyi* *ko* *wani* *iri* *ne* *yana* *maganin* *shi* *insha* *Allah* *sai* *agwanda* *akansan* *na* *kwarai*

Munzo *muku* *da* *maganin* *sanyi* *mesa* *kaikayin* *gaba* *da* *kurajen* *gaba* *da* *sanyi* *mai* *dauke* *ni'ima* *da* *karancin* *sha'awa*

2sanyi *mesa* *nauyin* *jiki* *yawan* *kasala* *ciwan* *Mara* *kaikayin* *jiki* *ciwan* *kai* *idan* *sanyi* *ya* *busa*

Da *sauransu*

Munan akano muna aka kayan mu ko inna afadi najeria har dama makwaffatmu nijar cameeroun da chadi
Muna maraba da masu siyan dai dai ko sari*Aslm barka mu da wanan lokaci nice takuwa Ayusha idris wace kuka fi dani da Mrs Muhammad Bashir kamshi traditional herbal medicine and more*

Mata *yan* *uwana* *kuzo* *gadama* *tasamu* *wace* *zamuyi* *yaki* *da* *wanan* *cutar* *da* *ta* **adabemu** *ba* *kowace* *cuta* *bace* *wanan* *bace* *cutar* *sanyi* *wanan* *cuta* *tana* *takurawa* *mata* da *maza* *yaran* *mu* **da** *manyan* *mu* *to* *gaskiya* **mata** *fa* *sai* *mun* *dage* *mun* *magance* *matsalar* *da* *tada* *me* *mu*

Ayau *nazo* *muku* *da* *ingantattun* *magungunan* *sanyi* *da* *basu* *da* *illa* *sanyi* *ko* *wani* *iri* *ne* *yana* *maganin* *shi* *insha* *Allah* *sai* *agwanda* *akansan* *na* *kwarai*

Munzo *muku* *da* *maganin* *sanyi* *mesa* *kaikayin* *gaba* *da* *kurajen* *gaba* *da* *sanyi* *mai* *dauke* *ni'ima* *da* *karancin* *sha'awa*

2sanyi *mesa* *nauyin* *jiki* *yawan* *kasala* *ciwan* *Mara* *kaikayin* *jiki* *ciwan* *kai* *idan* *sanyi* *ya* *busa*

Da *sauransu*

Munan akano muna aka kayan mu ko inna afadi najeria har dama makwaffatmu nijar cameeroun da chadi
Muna maraba da masu siyan dai dai ko sari

Domin Neman Karin bayani sai ku tuntube mu ta wanan number 07066959285 kira ko WhatsApp
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..

Furren kan juji..

BABI NA TAKWAS.
Had'iye kukan da yazo mata tayi tare da ɗaukar jakar makarantar ta,ta bar ajin ma balle makaranta.
Ko kallon yan makaranta da suke mata magana ba tayi ba, tana isa bakin shagon Maude ta tsaya, hawaye na zuba mata.

Da gudu ta shige cikin gidan, tana callara ihu wanda yasa Umma da take tuka tuwon dare, sakewa tana salati tare da gyara zaman zanin..
"Lafiya kike zunduma ihu haka?"

"Umma ba Abida bane tacewa Yan ajin mu wai me shayi yana wasan kwak..."
Had'iye sauran maganar tayi tare da sake ihu tana kuka.
Shiru gidan ya dauka, tare da kallon Anum,
"Dama kina wasan banza ne?"
"Ban tab'a yi ba, wallahi ita ce tace min muje gurin Baba lado."

Maude da ya shigo gidan da niyyar tambayar ta, me ya faru, yaji kome dan haka ya juya ya fice daga gidan, yasa aka kira Mishi Abida, dauke kai yayi yasa Ila ya zane mishi su. Ciki da wajen su. Sannan ya kore su.

Anum tayi kuka, tayi rikicin karshe ma tayi alkawarin bata kuma kula Maude, tun yamma take kuka da rikici har karfe takwas na dare koda malam ya dawo yaga yayunta maza, a gidan sun zo gaida su malam amma bata fito ba.
"Umman su Ina kyautar Allah take?"

Ajiye mishi ruwan wanke hannu tayi tare da zuba mishi ruwan butar siliba, yana wanke hannun shi.
"Ina tambayar ki baki kula ni ba?"
Shiru tayi, sannan ta kuma zuba mishi ruwan sannan tace mishi.
"Tana dakin Maman Aminu, ban san me ya faru ba, ta dawo d'azun tana kuka wai yarinyar nan Abidah tayi mata sharri, nasan halin Anum akwai kafiya da taurin kai, amma kuma yanayin da suka yi maganar ne ya bani tsoro naki magana.

Domin tazo da wani zantuntuka masu girma, wanda ya dace ace manyan sun shiga maganar amma aka yi biris da shi zai iya dawowa babban al'amari!"

"Nana Khadijah!" Ya kwala mata kira,
Fitowa tayi tana matsar kwalla, alamun har yanzun bata dai jin haushin abinda Abida tayi mata ba, cogewa tayi daga bakin kofar dakin su, tana jan majina, tsabar sakalci, sai ka rantse da Allah bata fi shekara bakwai ba, dan yadda take jan majinar abin a mata duka ne.

Gashi fuskarta yayi jajjur, saman idanun ta ya kumbura sakamakon kukan da tayi, a takaice dai.

Anum Sharrin da aka mata ne yake ya kushinta, ta rasa inda zata fada a dauka mata mataki,

"Zauna nasan baki ciki kome ba, uwar kuka." Zama tayi tare da kallon shi tace mishi.
"Baba Malam bana jin yinwa!"
"Me kuka bata taci?"
Kallonta Umma tayi sannan ta maida dubanta ga malam tace mishi.
"Ai bata cin tuwo!"

Saka hannun shi yayi a dokin kofar shi ya ciro mata soyayyar doya da kwai sai cinyar kaza da hakarkari. A hankali ta bude tare da kallon shi sai ga kwalla sharr sharr. Cire hannun shi yayi cikin tuwon ya ce mata.
"Me ya faru?"
A hankali take gaya mishi abinda ya faru, tana rusa kuka kamar ana yankar namar jikinta, bai ce kome ba haka kuma ya hana yaran shi magana da matar, yace.
"Sha'anin yara sai ana kai zuciya nesa, domin zasu cigaba da fada da junar su,karshe kuma mu iyaye idan bamu yi hakuri ba, sai mu nunawa duniya cewa an tab'a na mune.

D'azun ina shigowa Malam Maude ya same ni, da abinda ya faru, bai ji dadin shi ba. Amma na nuna mishi babu kome yarinta ke damun su, amma shima ya dauki mata dan ya zane yaran, dan haka kome ya wuce ku Cigaba da abinda kuke da ko? Bana son ki fara fuskarta matsalar Unguwar nan dake.

.. kinyi qarama da fuskarta matsalar cikin unguwar nan, dan haka kar na kuma jin kinyi fada da wani a cikin makarantar ku, kinji ko!"
Haka yayi ta mata nasiha, tare da janta da hira tana gamawa a ka'idar gidan dole zata koma Cikin d'akinta, ta kwanta bayan tayi alola akan idanun Umma dan sun santa ba son sallah take ba.

Dan haka tana sallah isha, ya kwanta ko bude jakarta bata yi ba makarantar ta bata yi ba, dan ranta ya gama baci. Fushi take da kowa ma, bayan ta shiga daki ne Maman Aminu tace.

"Gobe zan je na sami Adama, Ni bana son wannan abun, gabaki daya yarinya ta fita hayacinta." Kallonta Malam yayi sannan yace mata.
"Da kin bar zancen nan domin ai na gaya miki Maude ya dauki matakin da ya dace."

"Amma ina ganin kawai a hanata tsabga da yaran!" Inji Aminu,
"Nima nafi tunanin haka, domin ita daya Xoxo nan bata da nutsuwa ina..."

"Idan baka zaka fadi Alkhairi ba toh kayi shiru,haka Manzon Allah ya ce mana!" Shiru Ya Abubakar yayi ba iya shi ba hatta su Bashir da Musa, domin matukar Umma tana guri ba zaka tab'a cin namar wani ba, haka suka gama hirar su, suka masu sallama.

--- Washi gari.
Yusuf da Ahmad tare da Muttaka sai Abdul Hakim,suka shigo gidan. Yusuf yana zaune da iyalin shi a bayan bulkeshina, Ahmad kuma yana Ibrahim bako, Abdul Hakim, kuma yana Jahun. Tare da na shi iyalan.

Muttaka kuma yana sabon layi,. Dukkan su Allah ya albarkaci rayuwar su da rufin asiri, Musamman matan mazajen su ba kananun masu kuɗi bane.

Suma suna shiga gidan suka fahimci autar su an tab'a ta, domin daga yanayin yadda ta gaishe su, haka ya fahimtar da su, koda aka kawo mata tea da bread daga shagon Maude, kicking din kofin tayi tare da dakawa Rulwanu tsawa.
"Kace mishi bana son tea din kar ya kuma kawo min."

Ta gaya mishi tana masifa, daukar kofin Umma tayi tare da dungura goshinta, yar nima ta sake kuka kamar an caka mata mashi.
"Kiyi kukan jini ma, wallahi kika sake raina ya b'aci sai na zane ki, yar nima babu wanda yake Iskancin da kike yi a cikin gidan nan, idan an yi magana ki bare baki kamar tsohon zani.

Ke har kin isa ki dakawa yayanki tsawa, dauki kofin ki kai mishi ko na shiga jikin...."

"Umman su!" Malam ya kira sunanta.
"Dakata malam! Babu ruwanka da fadar da nakewa Anum, kaƙi naka duniya taso shi, kaso naka duniya taƙi shi, ban ga amfanin soyayyar da kuke gwadawa Anum ba, matukar ba za a tsawarta mata ba, yarinya ta sangarce sai abinda ya gadama take yi, ita yar gidan Uban waye da zata na taka kowa toh wallahi matukar baka dakatar da wannan abun ba, tabbas wata rana sai kayi dan sani, kuma lokacin baka da yadda zaka yi domin lokacin ya kure, muku."

Sannan ta koma kan Anum ta balbale ta da fada, haka yasata daukar kayan ta fita waje, tana zuwa shafin shi ta dangwara mishi ta juya tare da barin shagon.

Fushi sosai take dashi, shima a bangaren shi gani yake kamar yayi mata wani katon laifi, dan haka sai ya damu, gashi mutane dayawa na gaya mishi ai sonta yaƙe, dariya kawai yake domin kuwa yafi yarda da cewa shakuwa ce.

Yau da gobe bai bar kome ba, su XOXO sun fita hanyar Anum suka kuma rabata da duk wata kawarsu na shin su, haka ya bata haushi. Ta kuma cakume XOXO da dambe dakyar aka kwaceta. Karshe Malam Ya'u rariya, ya kori Anum a makarantar. Tunda ta shigo tana rusa ihu, Umma ta zuba mata ido. Tuni ta had'iye kukan,

A karon farko da Maman Aminu taji dadin hukuncin da Umma ta yanke, domin halin Anum ya fara damun ta.

... Shigowar Malam yace.
"Subhanallahi! Mariyah lafiya kike dukar Autar malam?"
Aikuwa ta kuma kara narke murya tana ihu, sai da ya amshi bulogarin, ya wurga waje cikin fada Umma tace.
"Maza fita ki amshi wanke wanken!"
Jikinta na rawa ta fita, aikuwa haka tayi wanke wanken son ranta, dan wani bai fita ba, amma dake Umma itama ta kafe haka tayi ta bar gurin ta koma dakin ta.
Mai_Dambu
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..

Masha ruwa magirbi...!!!
BABI NA SHA UKU.

Tana shiga daki ta yanki jiki ta fadi, wai Aljamunta sun tashi. Dariya Umma tayi sannan ta shiga dakinta, ta dauko dorina.
Tayi mata shegen duka, wanda babu wanda ya iya cewa kome, sannan ta korota waje, tun daga ranar Anum ta daina Aljanun karya.

Shi kanshi Malam mutanen da suke zuwa Mishi akan Anum mamaki yake, dan akwai wata safiyar asabar sun fito masalaci, suna tattauna yadda al'amuran suka tabarbare da Maude.

Sai ga wani mutum yazo mika musu hannu yayi suka gaisa, sannan ya cigaba da cewa.
"Suna na Alhaji Idi Ghana, dan wajena Hafiz yaga Yarka Khadijah yana so, shine nace bari nazo muyi magana ɗaya.

Yaro na dai yanzun yake Jami'a, kuma ban san yadda zan gaya maka ba, amma ina son ka d'an cewa ita Khadijah ko zata nemi maganin hana daukar ciki, kafin ya gama Jami'a kasan yaran yau da so..."

Wani irin shake mishi wuya Maude yayi jikin shi har yana rawa.
"Anum din ce zaka ce a gaya mata ta fara daukar matakin kare daukar ciki? Wallahi na kuma ganin Ɗanka da ita sai na b'atar da shi har Abada."

"Sake shi Malam Maude, Allah na shirya kaje na yafe maka, amma kajawa d'anka kunne dan tabbas wannan gargad'in ba iya kai aka wa ba, har dashi."

Sake mishi kwalar riga yayi, tare da cewa.
"Kaji me yace maka?"
Barin gurin Alhaji Idi Ghana yayi, tare da jan tsaki.
"Wato kasan me? Duk cikin yarana sha bakwai babu me aikata abinda Khadijah take aikatawa. Da zan sami mutumin da zai barta tayi karatu wallahi da na bashi Anum, ina jin tsoron Allah ina jin tsoron Zamani, karta lalace na dauki Bara gurbi na bawa mutanen kirki."

Kallon Malam yayi kafin ya sadar da kanshi kasa yana cewa.
"Zata samu mana, mutanen kirki suna dayawa a cikin al'umma. Insha Allah zata sami wanda zai bawa rayuwarta gudunmawa."

Daga haka basu kuma magana ba, har malam ya shiga cikin gidan, shi kuma ya koma shagon shayin shi, yana aiki yana sake tsaki, dakyar ya gayawa ila abunda yake damun shi.
"Ass. Maude yarinyar nan fa ba zasu baka ita ba, sannan ka duba yanayin yayunta ai kasan ba zasu yarda su baka aurenta ba, domin masu kuɗi yayunta mata suka aura kaga kenan kai ba kowa bane sannan idan ka fito musu a matsayin niman aurenta kasan ba baka zasu yi ba. Idan da hali ka bani sako na tura gida a tawo da Charifah!"

Dauke kai yayi bai ce mishi kome ba. Nazarin yarinyar yake yana auna abinda samarika suke mata, da kanta yake rawa haka, abu na farko da yazo mishi kyautar da suke bata, murmushi yayi sannan yaji a ranshi zai shiga niman aurenta da yardan Allah.

Dan haka shima ya faɗa jerin masu neman ta, shi kan da aure ne sauran kuma da tsiya ne, a dauke ta zuwa party, itace wannan saurayin gobe zaka ganta da wani saurayin, gashi kashe mata kudi suke, Anum bata zina amma yadda take abinta dole kaji a ranka zina take aikatawa.

Sannan wani abun da zai baka mamaki ita fa ba soyayya take bi ba, domin ido da ido ta gayawa wani dan gidan alkali Nura tace mishi.
"Ni babu abinda ya dame Ni da wasu kwayoyin cuta masu suna love! Ina da kyau, dube ni daga sama har kasa. Dan haka duk wanda ya ajiye ni a gidan shi ya ajiye ni

ne saboda na zamewa gidan shi fitila, And ina da lokaci da zan Gara life son raina, ka ajiye soyayya ayi rayuwa."

Abin mamaki ya bashi yarinya karama,ta iya magana kowa yana son ayi soyayya amma Anum ita tafi gane asalin abin cikin aljuhunka.
Da ire-iren waɗannan kalaman sai kaji tsoron ta, ita kuwa ko a jikinta. Karshe na kara nutsuwa tayi da cin kudin samari. A gefe guda Maude ma ya yunkuro da karfin shi.

Kafin ya same ta, sai da yayiwa Malam magana, bayan sallar juma'a ya dawo gida, ya same shi da maganar yana niman auren Anum!
"Toh malam Maude, ba zan hanaka Anum ba, amma ka nemi soyayyarta Ni kuma Insha Allah zan tsaya maka ka aureta."

Cike da kunya ya sunkuyar da kanshi kasa, yana murmushi yace.
"Insha Allah zan yi kokarin niman yardanta."

Suka yi sallama, malam ya shiga gida shi kuma ya koma shagon shi yana jin a ranshi ya same ta ma.
Da Malam ya shiga cikin gidan, bayan yaci abincin rana, ya labarta musu abinda Maude yazo dashi.

Aikuwa Maman Aminu tace bata san da zancen ba, bai kulata ba ya cigaba da gayawa Umma yadda suka yi, dukda Umma ranta bai yi na'am da Abinda malam yazo dashi ba, sabida tana ganin haka ba zai yiwu ba.

Taya za a dauki yarinya a bawa dan wata kasa, kuma wanda ba'a san kome akan shi ba, amma idan ta duba nagartan shi sai taga ya cancanci girmamawa da auren Anum. Dan haka ta nime zab'in Allah a cikin al'amarin amma tace mishi.
"Kasan bata cika sha biyar ba ko? Kawai shirmen ta take kawai, dan haka a bata lokaci tasan kanta zuwa sha shida."

"Nima abinda nayi tunani kenan, amma nace Mishi ya nemi soyayyarta tukun" inji Malam.
"Bafa zata auri me shayi ba! Wallahi ba zata zauna da me shayi ba, akan me yarinyar da."

"Kiyi fatan Alkhairi ko kuma kiyi shiru." Ya gayawa Maman Aminu haka.

--- Lokacin da Anum ta dawo gida, taji labarin a bakin Mamanta hankalinta ya tashi sosai, dan har ta kusan sati bata fita..ranar Birthday din saurayinta Khalil take gayawa Xoxo, kallonta tayi tana dariya tace mata.
"Ni kuwa naga ba wani abun damuwa bane, kawai kici kudin banza a wuce gurin, idan kin cinye jarin shayi da bread sai kice baki san wannan zancen ba. Ki gayawa Maman ki, kiji me zata ce."

Haka suka rabu, ta dawo gida, ta samu Umma bata nan, taje tashan babaye duba yayanta da aka kawo daga dewu, Maman Aminu tana kwashe tuwon dare, da sauri ta shige d'akinta ta cire kayan da ta daura katon Hijab akai, ta fito bayan ta goge makeup din fuskarta.

Zama tayi tare da cewa.
"Mama Sannun da aiki."

Murmushi tayi mata sannan tace mata.

"Yau kin dawo akan lokaci baki sake malam ya dawo baki nan ba, idan haka zaki Cigaba da dawowa ai babu wanda zai takura miki."

Dariya Anum taya sannan ta nuna mata wani zoben witer gold da khalili ya saya mata, me shegan kyau da tsada.

"Mama kinga zoben yana da kyau da tsada, sannan kuma ni ina ganin maganar me shayin nan me zai hana mu tatsi kudin shi ko babu kome ai munci banza, tunda yasan dai nafi karfin ajin shi. Kafin lokacin Khalil ya gama karatun shi sai muyi aure."

Kallon Anum tayi cike da mamaki tace.
"Me yasa ban fahimci hakan ba? Sai da kika kawo min shawaran gaskiya kinyi tunani."

Dariya suka saka tare da tafawa, Maman Aminu ta Cigaba da daurata akan yadda zata ci kuɗin Maude da nuna mishi dunduniya babu kamar shi, sai sun talauta shagon shayin tass tayi tsallen bad'a she tace bata yin shi.

Wannan tattaunawa sunyi shi basu san malam ya shigo gidan ba, dan haka ya tsaya har suka gama sannan ya koma waje. Yana jin wani irin tashin hankali,. Ba tare da ya nuna ya san kome ba, ya zuba musu ido yana kallon takun su. Yana jiran yaji me zasu zo mishi da shi. Ko Umma bai gayawa ba.

Abinda ya sani yana masifar kaunar Anum tare da tausayinta, tun daga lokacin malam ya saka damuwa sosai a ran shi, musamman yadda ya fahimci shine kashin bayan faruwan Al'amarin Anum. Wannan damuwar da ya shiga yasa shi samun matsala na yawan ciwon kai. Dama gashi mutane na yawan kawo mishi abinda Anum take, sai gashi yaji da kunnen shi Mahaifiyarta itace take nuna mata duk wani abinda zata yi.

** After few days.
Sai ga soyayya irinta bogi da damfara, karon farko Anum tasaka maude ya saya mata waya me tsada, lokacin sumsang ce da Nokia, sai motorola. Zuba mata ido yayi sannan yace mata.
"Anum bani da kudin da zan saya miki wayar dubannin nera, ina laifin ta dubu goma."

Wani shegen kallon renin hankali tayi mishi, sannan tace mishi.
"Kasan dalilin da yasa na amince muyi SOYAYYA? Sabida tun ina karama kake so na, ace yanzun ba zaka iya saya min wayar dubu talatin sama da haka ba, Thanks God da na fahimci irin mutumin da nake tare dashi, dubi hannuna! Kasan nawa ne zoben toh dubu saba'in ake sayarwa, kuma Saurayina yaro karami ya saya min kai haka babba katoto sai iyayi da shishigin kana sona amma ba zaka iya kashe min kudi ba.

Toh me nasama yaci balle na kasa, na shiga cikin kawayena suna min gori!"

Ta faɗa cikin rashin kunya, tare da kafe shi da ido, idan kaga yadda ta saka shi a gaba, hmm zaka dauka ko D'anta ne ko kaninta, zunzurutun renin hankali.(Kuma wallahi a wannan lokacin abinda yake faruwa kenan, saurayi zai zo gurin yarinya tayu tun tana yar karama suke mutunci da zaran ya furta yana sonta, bala'i ya faru. Rashin kunya da mutunci duk zata mishi, ku Fahimci wani abu duk wanda zai soka ba karamin daraja kaci ba)

Wani karamin murmushi yayi irin na b'oye yanayin da yake ciki, sannan yace mata.
"Wai ni da a tunanina ko zaki koma makaranta ne, idan yaso sai kiyi jarabawar karshe a wani makarantar kin fahimce ni, idan yaso sai na saya miki wayar ba!"

Sake baki tayi tana kallon shi, kamar wawuya.
"Lallai kuwa! Wato ga jahila, haka ma yayi ka biya min a Farih College, zan zana!"

Ta juya bata mishi magana ba, lashe bushashen lips d'inshi yayi tare da bin bayanta da ido, haka ya fita, daga soron gidan ya koma shagon shi.
"Oga Maude da ka hakura da wannan yarinyar har nan muke jin muryan ta, kawai dan kace kana Sonta sai reni ya shiga tsakanin ku.

Wallahi ka bani damar na dauko maka ita ka kaddamar mata, ka cikawa rigarka iska. Yarinya karama ta zama karu..."

"Jijjiya! Tashi ka tafi achabarka, Allah ya bada sa'a." Inji Maude dan baya jin dadin ranshi baki ɗaya.
"Oga Maude, bafa baka yarinyan nan zasu yi ba, sabida idan kaga yadda yan uwnta suka auri manyan mutane zaka rike bakinka, sannan kuma ko yayunta maza ka duba mana.

Ai gaskiya ta faɗa me na sama yaci balle na ƙasa, rijiya ba gurin wasan makaho bane kayi tunanin abin..."

"Kai kasan waye shi? Kasan matsayin da ya taka na rayuwa? Me yasa kuka bawa son abin duniya dama, ka tab'a ganin wanda ya ajiye."
"ila!" Ya kira sunan shi a sanyayye,
"Assa..."
"Bana son damuwa! Zan tafi gida, ka kula da shagon sannan kuma bana son naji wani abu ya fito bakinka don Allah!"

Ya fadi haka tare da barin shagon jikin shi a mace,.yana nazarin abinda ya bari a baya, ya fado wannan duniyar, "Anum kece Qaddara ta! Kece kika dauko ni daga duniyata zuwa duniyarki me yasa ba zaki Fahimci girman soyayyata ba?"

Haka yayi ta tafiya, har ya isa gidan yana shiga ya samu ana gulmar XOXO da suka bar gidan tare da Anum, wacce ake cewa ta doke su Xoxo a Iskanci da bin maza, kuma ba haka bane. Dakin shi ya shiga ya kwanta kawai, yana nazarin Anum me zai mata ya burge ta?

.....
"Malam Iliya, ka gayawa dan uwanka ya rabu da yarinyar ba bashi zasu yi ba, cikin kudin shi zasu yi haka suke, basa bawa talaka auren yar su. Daga manyan yan kasuwa sai manyan aikatan gwamnati, sannan shuka yayi zari dube yarinyar nan da bata cika ashirin ba zai fada soyayyar ta, hmm"

"Idan yar su kanwa ce su jikata su sha, idan kaga Matar shi Nana Aicha wallahi ko me aikinta tafi wannan mara kunyar da kuke ganin wata tsiya ce. Balle kuma Charifah."

_So yau ina busy idan na sami lokaci zaku jini da 14 Anya kuwa fahimtar Labarin kuwa😂😂dan baku fahimta na ajiye na huta _
#Mai_Dambu

[1/31, 11:28 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
Sannu sannu bata hana zuwa..
BABI NA SHA HUƊU.

Dariya suka saka Mishi tare da masa kallon mahaukaci, domin gani suke kamar duk abinda zai fada karya ne, sannan wani abun da ila bai gane ba, suna bakin cikin ai su basu samu damar shiga a gurin Anum ba taya shi bako zai samu shi?

Wannan dabi'ar mutane ce, da zaran suka ga sun kasa, toh duk wanda yazo wuce su, sai sun san yadda suka kashe maka kwarin gwiwar ka,.toh abinda yake faruwa kenan a wannan lokacin, domin ai duk masu cewa Anum tafi ƙarfin Maude babu wanda ya tab'a kallon shi a matsayin namiji.

Ila kuwa abinda yasa yake magana saboda yasan waye Maude, ban da ƙaddarorin rayuwa ai rijaya ba gurin wasan yaro bane, banda dalili me ƙarfi ai ko yar wanke wanken matan Maude Anum bata kama kafarsu ba, yarinyar da a ce ya samu haihuwa da bai haifi wanda suka girme ta ba, amma dake Allah alimun gaibih ne gashi nan ya kawo shi duniyar da ba a san darajar shi ba.

Idan kyakyawan nasaba da danganta ce, yana da shi. Mutumin da ya fito babban gidan masu tsananin ƙarfin iko da sanin darajar rayuwa, sabon tsanar Anum ce ya kuma mamaye zuciyar shi, ji yaƙe kamar ya shiga yayi mata mugun duka. A halin yanzun ya fara fahimtar halin mutanen da suke tare dashi.

Gashi bai da ikon ya saka shi su bar garin, amma babu kome dan yasan a yanzun anan din Maude ya baza albarkan shi anan.

*** Kusan raba dare yayi tun da yayi sallah nafilla, yake zaune akan abin sallar yayi shiru. Wannan shine karo na bakwai da yayi istahara, akan lamarin shi da Anum yana kuma jin kusancin su a zuciyar shi, lumshe idanu yayi sannan ya bude akan wani karamin hoton Anum sanye da unifoam din islamiyya, ranar da suke musabaka.

Shafa hoton yayi tare da furza da iskar bakin shi, yana mamakin kan shi, ina miskilancin shi ya tafi? Ina jarumtar shi yaƙe? Da zai zauna yarinyar da ya haifa take juya shi son ranta, yayi imani da Allah idan da ace rayuwar shi ta baya ce wannan yarinyar ba kome bace, sannan bata isa kusantar inda yake ba.

Dukda duhun dakin, bai hana shi jin kamar ya takarkare ya fasa ihu ba, domin bai san lokacin da Anum tayiwa zuciyar shi rubdugu ba, shi da kan shi ya sha ƙaryata kan shi akan ya kamu da soyayyarta, amma yau da ta tsaya take mishi tijara, sai yake ganin ashe shi ba kome bane, namiji akan macen da yake so ba kowa bane.

Ajiyar zuciya ya sauke yana hango rayuwar da ya tsallake yazo bauchi. A hankali ya haura bakin katifar shi ya kwanta rigingine, yana kallon sama. A hankali barci me ƙarfi yayi gaba dashi.
.....
Fitowa tayi zata yawon daren da ta saba, suka yi kicibis da Malam, sake jakar tayi tare da tsayawa kamar Status, jikinta yana rawa.
"Koma ki kwanta Allah ya shiryna min ke!" Ya gaya mata, babu kunya ta juya ta koma d'akinta, Allah sarki bai iya rintsawa ba.

Haka ya kwana yana Sallah tare da saka kunne ko zata fito, har aka kira sallah farko, sannan ya tafi masalaci.

Yana dawowa ya samu bata tashi sallar asuba ba, ya buga mata kofa.bude kofar tayi simi simi ta wuce tayi alola.

Sannan tazo ta wuce dakin ta, tayi sallah tunda ta shiga ta rufe Kofar taki fitowa. Har ya fita Allah sarki da zai fita ya ajiye dari biyu yace a bata.

Dan yasan ba fitowa zata yi ta amshi kudin abin karyawan ta ba. Haka ya tafi cikin damuwa da tashin hankali. Yana barin gidan taji Umma tana sallama zata ganjuwa barkan yar makotar su. Tasan idan Umma tana gida bata isa ta fita ba, kuma ba zata tab'a barinta ta fita ba. Dan haka cikin sauri ta shiga ban daki tayi wanka a guje ya fito tana jin Mama tana ce mata.
"Anum zan shiga Islamiyya, ki kula da abincin dake kan wuta."

Bata ce mata cikanki ba, har ta fita, tana fita ta shirya cikin wani blue legis jeans, sai farin armless wanda ya matse mata jikinta ya fitar da kirjinta sosai, dan wani karamin bra tasaka, sannan ta gyara gashin kanta, ta fito tare da saka wata dogon hill, ta shiga kitchen ɗin tana tsaki.
"Ko zanyi aure ai bazan tab'a rayuwar itacce da murhu ba." Haka ta ja itaccen ta koma d'akinta ta fesa turare. Sannan ta dauki wata After dress, ta daura akan kayan jikinta bayan ta dauki karamin jaka tafita. Kallon Maude tayi lokacin da ta fita bakin shagon shi. Cikin tsantsar renin hankali tace.
"Yunwa nake ji, ka bani 2k zanje vanilla na karya."
Kallon mutanen da suke shan shayin yayi, sannan yace mata.
"D'azun na bada kudin aka tafi sarin burodi"

Wani wulakantaccen kallo tayi mishi, sannan tayi juyawarta zata bar gurin, bata yi tafiya me nisa ba ta haɗu da Beauty. Kallon juna suka yi tare da sake dariya.
"Bani wayar ki na kira Lil." Dake su duk an saya musu waya itace dai babu a hannunta kuma tana tsoron karb'a a hannun Khalil,kar malam yasa a mata shegen duka.

Bude wayar tayi ta saka layinta a ciki, sannan ta koma gefe ta kira shi, sun jima suna tsaye kafin yazo. Bude motar shi tayi tare da kallon shi tace mishi.
"Yinwa nake ji lil!"
Murmushi yayi sannan ya kai hannun shi kan cikinta, da sauri ta kai buge hannun shi.
"Ni bana son haka!"
"Sorry Baby!"
Jan motar yayi bayan ta bawa Beauty wayarta, suka bar unguwar, tunda suka fita yake kaita gurin cin abinci, taci Anan tasha ice cream. Haka suka gama yawon su. Tsautsayi yasa suka nufi Bauchi club wai ana wani wasa.

Tana zaune sai ga Hafiz Ghana, nan ya fara kokarin ganin ya tab'a jikinta, ta hana shi dake khalil baya kusa daga nesa ya hango su. Zuciya bata da kashi yana zuwa ya fasa kwalba, ya yanki fuskar Hafiz Ghana dashi. Aikuwa aka saka ihu, ganin yadda yankar ya tab'a fuskar shi saura kiris da idanun shi yasa Khalil jifa da kwalbar ya gudu, itama ta ficce da gudu. Aka watse aka bar yaron a cikin jini yana zuba,

Dakyar aka sami wayar shi aka kira Number baban shi, yazo aka kai shi asibitin ni'ima.

Yaron ya zubda jini sosai, dan haka yana farkawa baban shi ya tambaye shi me ya faru, bai boye ba ya gaya mishi..

Lokacin da Anum ta isa gida kayan jikinta kawai zaka kalla kasan ta fito daga yawon banza ne, kallo daya yayi mata ya sake kwan da yake kad'awa, ya fito kamar zai fadi.

"Lafiya gaya min."
"Dalla bani hanya, an ce maka babu kome." Yasan a firgice take amma haka bai hana shi sake tambayar ta ba. Tayi mishi fitsara ta shige cikin gidan, umma na tsakar gida, ta shiga. Sau daya ta kalle ta, yadda take rab'e rab'e, bata kuma kallonta ba.
Wai a haka ma ɗan tana hana idanunta barci kenan, akan Anum. Haka ta shige d'akinta ta cire kayanta ta zauna jikinta yana rawa, idan ta tuna yadda Hafiz Ghana yake shure shure sai taji wani irin tsoro ya kamata.

.... Karfe biyar da minti arba'in da biyar, yan sanda suka dira a kofar gidan Malam Bello, tare da Alhaji Ghana, suka tawo..
"Ku shiga ku fito min da yarinyar."
Dai dai isowar malam kofar gidan tare da yaran shi maza, kallon juna suka yi, Alhaji Idi Ghana ya shiga zazzaga musu tijara da wulankanci.

Kasa hakuri yayi jikin shi har rawa yake, yana kallon yadda Malam yake kaskantar da kan shi, tafasasshen ruwan zafi ya diba, yazo gaban Alhaji Idi Ghana, ya kashe shi ya fadi, babu ko Dar bai ji ba, ya shake wuyar mutumin nan sai da ya juye mishi ruwan zafin sannan ya koma shagon shi ya kira Yan sanda yayi musu wanka da kudi ai dama ance Kudi kumbar susa,. Sai da su duniya take zama lafiya, idan babu su baka isa kataka wani ya share ba, karshe dai Anan suka bar Alhaji Ghana.

A kofar gidan malam, a ranar hankalin Ya Abubakar da Musa ya tashi, dan shi kan yayi zuciya zai dake ta, sai da Umma ta dakatar da shi. Ran shi ya b'aci kamar zai kama da wuta, zazzaɓi ne ya rufe malam.

Domin jinin shi yayi mugun hawa, amma tsabar son da yake mata. Yaki cewa kome, asalima tsoron kar yayunta su tsane ta, sai ma kokarin ganin ya hana Abubakar da Musa, tasa zancen ko a gaban matan su ne. Sabida kar yau da gobe, su fara tsanar ta.
Dakyar aka kashe case din, domin Maude yayi namijin kokari gurin kashe zancen ya kuma hana ayi maganar a gaban shagon shi, kowa sai jin haushin wannan banzan soyayyar da yake mata yake ji, amma shi ko a jikin shi, ya kance musu "mun san darajar na gaba damu, dan haka babu iya kallon a ci zarafin al'umma mu kyale mutum."
Kwanakin malam biyar a gida, sannan ya koma gurin aikin shi, malam a tsaye yake jinya amma yana ƙoƙarin boye damuwar shi babban matsalar shi Anum bata kosa bane, amma ta kosa da baɗala.

Tun daga ranar aka kara tsayin katangar gidan, sannan aka zuba mata ido, ga Umma yanzun ta dauke mata wuta, sosai take mata bana wasa ba.
**
Mika mata foam yayi ta kalla da wasu takardun.
"Akwai me napep din da zai na kai ki yana kawo ki, sabida kiyi kokarin daukar abinda kika rasa na shekara daya."
.kallon shi tayi a wulakance..
"Toh banda rashin zuciya meye na biya min waec, Ni bana son shishigi da gulma, idan an saka sai kayi kana wani nuna kai na Allah ne, nan kuwa babu abinda yake ranka sai jikina daga ranar da ka samu ko kallo bai isheka ba."

.tana fadar haka ta juya tare da barin Maude a tsaye rike da takardan da ya kawo mata ji yaƙe kamar zuciyarshi zata buga, yana kallon yadda take mishi rashin kunya bai iya katabus. Dan haka bai kuma bin takanka ta ba,

Karshe ya bawa Malam takardun sai duk kunya ta kama shi, bayan kwanaki ta fara zuwa makarantar, toh makaranta ne na yaran manyan, dan haka akwai masu zuwa da wayoyin su.

Ranar da ta dawo tazo ta tsaya mishi.
"Kasan makarantar yaran manyan ne zai turani bani da waya?"
Murmushi yayi sannan ya ciro wata bakar leda ya mika mata, a wulakance ta amsa, sanan ta juya cikin gidan su, ko nagode bai samu ba, tana shiga ta bude wayar LG.

Wani irin ihu ta saka tare da fitowa daga ita sai rigar makarantar da yar skirt, ta bar hular ta a cikin gidan, wadatattun gashin kanta da aka mata kitson cuku, ya sauka har wuyar ta, ga wani gurun wuya da ake dashi wanda ya kara mata kyau, murmushi tayi yan manyan jorarrun hakoranta, ya bayyana.
Juya ido yayi tare da girgiza mata kai, da sauri ta juya inda yake ta saka hannunta a bayan shi ta rungume shi kanta a bisa kafadar shi, tana dariya, domin yana zaune ne a kujeran shayin shi.
"Mutane na kallon mu!"
"Nagode sosai! Ka fitar dani kunya ka nunawa duniya cewa Ni din mowa ce, a duk inda nake!"

Murmushi yayi sannan yace.
"Toh kanki ba hula balle dan kwali, gashi kayan makarantar me haske ne, a taimake ki a koma haka na gode."

Dariya tayi ta fita, da gudu tana murna, girgiza kai yayi tare da cewa a ranshi..
Khadijah indai kyauta ce muradinki kin samu har karshen rayuwata

Ai da ta nunawa malam wayar yayi murna yazo har shagon yayi mishi godiya, Maman Aminu kuwa ganin haka sai da ta mata fada karta sake ta fara son shi domin kuwa ba zata iya daukar kasadar abin kunya ba, ace yarta dukiyarta takare da auren me shayi, wannan ai faduwar darajar tace.. ga fura da nono amma babu ludayin damu.....
#Mai_Dambu
[1/31, 11:28 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
Na shiga ban dauka ba...!!
BABI NA SHA BIYAR.

"Kai Mamah kudin shi zan tatsa fa, zanci rabo nake kafin Allah ya kawo min wanda ya fishi,ina zan kai wannan damuwar, ya nace sai kace talauci." Tana fadar haka tana juya wayar hannunta, wani irin murmushi take fiddawa me daukar hankalin.

Haka Mama ta gama fadarta Anum bata damu ba, dan itama yar nima ta iya shariya, washi gari suna zaune tana cin shinkafa da miyar hange aka yiwa malam, umma tana wanke sawunta. Wani yaro yayi sallama rike da kofin tea da tiren kwai da indomie.

"Dahiru! Sannu kacewa Maude nagode!" Har zai fita yaron ya mika mata wata karamar farar takarda a wanda ya fidda shi daga aljuhun shi yace.
"Inji Oga Maude!"
Dariya tayi, dan ta saba amsar takardun shi sun kai amma bata tab'a buɗewa ba, dariya tayi ta buɗe.
`Amincin Allah ya tabbata a gare ki, kyakyawan fuska ma'abocin murmushi da Kawa! Ki duba sakona a wayarki!" Sai yanzun ta tuna wayar fa har da layin etisalat.

Tana buɗewa sakon soyayya ce,dariya tayi ta mishi har tana tintsarawa, tana mishi kallon Gara koda yake tasan bashi zai rubutawa ba, zai bada a rubuta mishi ne, dan haka ta share zancen bata kuma bin takai ba.

Bayan kwana biyu, Safiya ta haihu. Tattarawa Anum tayi ta koma gidan,Nan yayunta aka yita zunzutatta, tare da wani kambama ta zaka rantse wata me ilimin ce kome kamila, nan kuwa kyan fuskarta kawai yake rudar su. Kawayen Safiya da Hafsat idan suka zo Barka sai shige mata suke, musamman ganin yadda take sanye da dan kunnen gold da zoben shi. Anan wata take tambayar Safiya.

"Badai Anum ce ta girma haka ba? Kai masha Allah, ta gama secondry school ne?" Ta kafe Safiya.
"A'a tana kai ne, ma. Insha Allah Soon zata gama." Gyara zama tayi kuwa ta fara neman hanyoyin da zata nemi su hada kan Anum da Baban Yaron mijinta da yake zaune a kasar waje.

Rimi Rimi aka ayi magana, bata gurin. Sannan yayunta suka ganin yadda Matar take. Aikuwa take aka amince, har aka ɗauki maganar za a kai gurin malam.

**Ana jibi suna Anum tazo gida,dan dama sunyi waya da Maude zata zo, yana ganinta ya barwa Ila hidimar shayin, yazo gurinta.

"Yan matan Maude! Kwana biyu baki je makaranta ba, me yasa?" Cak ta tsaya dama tana waya ne kallon shi tayi daga sama har kasa, sannan ta tab'e baki,shekar kamshin turaren shi tayi tare da bude idanun ta.

"Amma ai na gaya maka yayata ta haihu? Wai tsaya Bokon nan lahira zani dashi?" Ta tambaye shi tana kallon fuskar shi.

Yadda yaƙe zaneta da idanun shi ne yasata yin kasa da kanta cikin sauri, dan kaifin idanun shi yayi tasiri a jikinta.
"Ko koyi girmama nagaba dake, ko ba dan Ni ba, sannan ko a can zaki iya zuwa makarantar ki,zama babu karatun ba zai amfane ki da kome ba.

Amma Arziki ne ace kana da ilimin addinin da na zamani, sannan, akwai aikanki ki anjima za a kawo miki daga gurin tela na fitar sunan."

Daga haka ya juya abin shi, yasan koda zai bata kyautar da zai fi haka sai ta gadama tace ta gode.

Bayan ta shiga cikin gidan, yana jin wani irin yanayi a ranta, amma haka ta yakince shi ta watsa a gefe, ta shiga kitchen ta kwashi abinci ta koma gefe ta fara ci, karo tayi da dutse, ta tsame hannunta tana kallon Umma da take dariya.

Yau sai dai kiyi hakuri, dan Shukrah ce tayi abincin kuma ta koma gidan su. Raurau tayi da idanunta, ta mike tare da ɗaukar gyale ta fita, tana zuwa daidai

window da yake shagon ta buga mishi. Wato a duniya idan kana niman mara kunya ka sami Anum kawai ka godewa Allah. Yana bude window ta sake mishi kuka.

Kura mata ido yayi, kafin yace mata.
"Me yasa?"
"Yinwa!" Ta faɗa a sakalce,
"Me zaki ci?"
"Soyayyen kwai, da namar tukunya, sai seven ko!"
"Dahiru zai kawo miki."
Juyawa tayi ba tare da tace mishi ta gobe ba, Bayan minti goma sai ga yaron ya kawo mata, har zai fita tace mishi.
"Kacewa Oga Maude ina son cin kilishi."
"Toh Auntyn mu!"
Share shi tayi ta zauna, ta fara cin abincin kallonta Umma tayi Allah ya gani bata da kwadayin ire-iren waɗannan abun.

Dan haka koda Mamn Aminu ta fito ta samu abinci kaca-kaca a gaban Anum, zama tayi ta saka hannu suka fara ci, kawo mata kayan da aka yi ne yasata amsa.

Diamond ne guda daya sai Classic, tare da Phonixs hitaget me fanti ruwan ash, riga da zani anyi mata ɗinkin pieces. Sai takalmin da haka, sai wani karamin kayan kwalliya, da chocolat bata tab'a ganin irin shi ba, kiran Xoxo tayi awaya tazo ta gani. Umma kallon su take kawa, Mama kayan bai burgeta ba,.domin ita bukatar ta Anum ta haɗu da wanda yafi Maude haduwa.

Da Xoxo tazo Unguwar daukar kayan tayi ta kai mata, murmushi tayi amma har ga Allah kayan gani take kamar ita ya dace tasamu kayan ba Anum ba. Dan haka tab'e baki tayi sannan tace mata.
"Zan tafi, naga kaya sunyi kyau."

Tana fadar haka tayi tafiyar ta, ta rasa gane wani irin kashin Arziki ne da ita, duk yadda yaso ganin Anum sai taga kamar kara bunkasa take,

..... Ranar suna da wuri Anum ta koma, bayan maude ya bata nashi gudummawar, har take ce mishi.
"Maude wai wani irin turare ne Kake amfani dashi wallahi ko kudi ka bani zaka samu yana kamshi turaren"

Murmushi yayi sannan ya mika mata leda sannan yayi mata fatan Alkhairi, rau rai tai da idanunta. Tare da matsawa jikin shi sosai. Kafin ya ankara ta d'an jingina da jikin shi, a rikice ya kalleta. D'ago kai tayi tana kallon shi. Tare da shakar kamshin turaren shi.
"Baka gaya min sunan shi ba!"
Allah sarki a binka da mutum me cikakken lafiya, duk sai yayi gaba daya kome ya kunce mishi.

Da dabara ya janyeta a jikin shi, yana kallon yadda take tura mishi baki, shafa bakin yayi cikin wani irin romantic, yana jin he was miss more moment, a hankali shaiɗan ya shiga kawata mishi dan bakinta, ba zai iya cewa yayi losing control din shi ba, amma qaddarar shi da Anum wata aba ce ta musamman da take yawo a jinin shi, a hankali ya kai bakin shi kan nata. Zato idanu tayi cikin sauri dan ta tsani kiss. Ture shi tayi cikin b'ata rai tace mishi.
"Kai Ni bana son Iskanci, na tsani wannan kazamtar, wani a hada baki kai naka jin kyamar abine ne."

Dauke fire yayi cikin damuwa, ya janye tare da barin ta a zauren , har ya isa bakin kofar yace mata.
"Idan kin shirya na turo mutane na gurin Malam!"

"Ta..." Kome ta tuna sai kuma tace mishi.
"Karka damu!" Ta juya da sauri ta bar gurin shi, cikin gida ta kai kayan tare da nuna musu, sannan ta shirya zuwa gidan sunan, ta kaiwa yayarta Safiya nata sakon da ya bata. Hmm Umma da Malam zuba masu ido yayi domin dab sunan Hafsat tazo mishi da maganar kawar su, bai ce mata kome ba.

...Toh ranar sunan ne aka kuma gaya mata wanda ake son hada su, kan uba zo kuga Anum tana wani Blushing, zata auri wanda. Za a kaita kasar waje. Kanta yayi wani tankwalelen ji take kaf unguwar bakin kura babu big beby. Dan haka tun da aka gama suna take rayawa a ranta ta tafi Chicago.

..... Bayan suna da kwana biyu, ta dawo, shigowar Xoxo idan ta gaida Umma tana hada dambun shinkafa, ta gaida ita. Kamar zata mata magana sai kuma ta bawa kanta hakuri ta juya ta cigaba da aikinta, can suka fito.
Umma bari na raka Abidah waje"
"Kin san ALLAH! Kika wuce minti talatin sai na fasa jikin ki." Umma ta gaya mata kai tsaye. Kallon juna suka yi da XOXO, dake Allah ya daura mata tsoron Allah da tsoron dukar Umma, tace.
"A'a Abidah jeki kawai."
Tana zare idanu,

"Kai Maman Sadiq, tsananin ba shi yake gyara yaro ba, kawai addu'a shine ma..."
"Hmm! A gaban su kike gaya min magana Maman Aminu? A kan idnun su.".tayi maganar tana wani irin murmushi me ciwo,
"Kuje karki dad'e."

Umma bata ce kome ba, amma da Anum tazo fita daga gidan tace mata.
"Zaki yi kuka wallahi."
Bata iya fita ba, ta juya tana kallon Umma dan tunda ta fadi haka ita a tunanin ta umma dukarta tayi, sai da Maman ta tace taje karta jima.

Ta fita da sauri, tun Umma tana hada dambun, suka fita har ta daura,. Ta kuma dake karago ta tankade da rariyar biski. Tana yi tana kallon Maman Aminu da take ta leka soro, murmushin takaici tayi ta Cigaba da abinda take yi.

Karfe uku sai ga zugar yan mata,.kana ganin su kaga yan bariki (Allah ka shirya mana haularmu □□) sun saka Anum a gaba lallai sai ta fito musu da kudin su. Yadda suka shigo gidan tana kuka, tare da rantse rantse bata dauki kudin ba, yasa Umma dauke kanta.
Mamarta kuwa ta shiga hayagaga, anyiwa Anum sharri. Kukan da Anum take ya takura Umma sosai, ita kan bata san wani irin kauna takewa Anum ba, kallon su tai sannan tace musu.
"Me ya faru?"
"Kinga Baba, mun ajo ne aka tara kudin ajon kawai, zuwan wannan me shegen kyau ta sunkuce mana." Inji wata yarinya bata wuce sa'ar Anum ba.
"Kuma kun duba baku gani ba!"
"Hmm!" Ta kalli Umma, dan da farko da tayi maganar Umma tana daura tuwon dare ne, ido biyu da tayi da Umma sai tayi mata kwarjini da kamala.
"Kika ce kun duba?"
"Eh!"
"Nana Khadijah! Kin dauki kuɗin su?" Umma ta wurga mata tambayar,

"Wallahi na rantse da Allah, Umma ki duba ni ma!" Ta faɗa cikin kuka. Kallon su Umma tayi tsaf da XOXO wacce take bayan mutane, tacewa Yan matan su shiga dakinta su zauna su bar Xoxo da Anum,
Babu musu suka shiga ita kuma ta tura Xoxo da Anum dakin Anum, suka shiga tacewa Anum.
"Maza cire min kayanki!"
Babu musu ta cire kayanta tass, daga ita sai pant da bra,
"Saka ki je dakin Malam ki jirani!"
Bayan tasaka tafita, Umma ta kalli XOXO da tsoron Umma ya kamata.
"Nasan kice kika dauki kudin nan! Bani ko ki gaya min inda yake aje a dauko zan rufa miki asiri nace musu ba biya sune!"

Cikin wani irin rawan jiki ta ciro pieces na kudin yadda ta kasa shi a jikinta, cikin wani irin bakin ciki take kallon yarinyar.

Tana mika mata,.tace mata.
"Abidah, ni nasan alaƙar ku cutarwa ce,.kina zaluntar zuciyar da babu sharri a cikin ta, amma ki sani Allah zai bi mata hakkinta, wallahi hakkin Anum ya tashi kamaki, sai kinyi da gaske. Allah baya barin wani da hakkin wani, kina cutar Khadijah ainun, amma ba kome kece jarabwarta, shi yasa take jin maganarki.

. Hmm Allah zai saka mata fa, wallahi na kuma ganinki da ita ko kika kuma kiranta, na rantse da Allah sai na kama Mahaifiyarki da Mahaifinki sai na saka an daure su.. kinsan Muttaka ai? Kin san yana aiki da yan sanda ne? Toh wallahi na rantse da Ubangiji sai na saka an rufe min su. Na kuma ganinki da Anum zan saka Rulwanu yayi miki dukar kawo wuka, kuma naga wanda ya isa ya hana shi."

Nuna mata hanyar fita daga dakin tayi, yarinya karama da bata wuce shekara goma sha takwas ba, nonuwar ta kamar wacce ta shayar.

Koranta umma tayi ta kuma sami yaran tayi musu wankin babban bargo, ta kuma tabbatar musu suka kuma niman Anum sai ta saka an rufe su.

Kamar munafukai suka bar gidan, tare da mamakin a inda aka aka sami kudin. Mugu dan masara sai ga XOXO.
#Mai_Dambu
[1/31, 11:28 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
Mare ni kad'an....!!
BABI NA SHA SHIDA.

Idan na sauko a canza min suna □□

XOXO da taga asirinta bai tonu ba, ta shiga bin Kawayen su tana gaya musu Anum ce Barauniyar su.

Tun bayan da abun ya faru, Anum ta shiga hankalinta na kwana biyu. Ga saurayin da aka ce za a hada su ke suna Hamid yazo yana Abuja, gefe daya ta fake Maude, ta daina kula shi idan dai ba yatsar shi zata yi ba.

Yadda yayi kwalliya tare da karya hular shi, ya tsaya a gabanta. Saka shi tayi a gaba tana dariya, shima murmushi yaƙe. "Don Allah Maude wani irin turare ne haka

kasan ranar sai da Ya Usman yayi maganar turaren ka, da yaji kamshin a jikin ledar kayan da ka turo min."

Murmushi yayi sannan yace mata.
"Turarena yar duri ce, kuma daga, Saudiya da Oman ake samun shi, yana da kyau da tsada hmm kudin shi."

"Tsaya Maude, wallahi kana da abin dariya yo ko tabirin shayinka ka sayar ai bazaka samu kudin zuwa umra ba, balle aikin hajji."

"Zaki umran ne?" Ya tambaye ta cikin sigar gaskiya da gaskiya.
Kallon shi tayi tana dariya,.tare da nuna shi.
"Yanzun don Allah banda kanzon kurege ta ina zaka iya biya min kudin Umra, kaga maude ka bar yaudaran kanka, domin kalaman ka dariya suke bani." A takaice dai Anum karya tashi take son yi. Dake tana jikin kofar gidan ne, shi kuma yana bakin Kofar gidan.

Takawa yayi har gabanta, ya tsaya . Hannun shi shi ya kai kan k'ugunta, a zabure ta kalle shi. Me data cikin soron yayi yana kallon fuskarta, kokarin ture shi ta fara.

"Kaga Maude!"
"Zaki Umran ne?"
"Wannan sai a mafarkina zai tabbata, don Allah cire hannunka a k'uguna bana son haka."

Kara matseta yayi da jikin bangon tana jin yadda zuciyar shi take wani irin buguwa.
"Baki ji yadda zuciyata take bugawa bane? Baki ji yadda take cike da kaunarki ba? Ambaton ki take ba dare ba ran!" Yana mata maganar ne bakin shi dai dai kunnenta.
"Dalla Malam kyale ni bana son Iskanci"
"Waye dan iska!"
"Ni ban zageka ba"
"Koma meye idan Allah ya nufa zamu zauna inuwa d'aya, zaki tantance haka, Anum ki bani daman mu gina rayuwar mu cikin kaunar juna! Ki amince min mu raya duniyar mu. Insha Allah zan gina miki farin ciki, zan bakin abinda baki nima ba da izinin Ubangiji."

Dariya ta saka mishi tare da ture shi..
"Da teburin shayinka? Nawa zai kai balle a saya min abinda nake so? Maude ni fa, nafi kaunar rayuwa sama da soyayya, ka Fahimta mana"

"Na fahimci irin rayuwar da kike bukata, ba shine kuke kira Luxury life ba?" Ya tambaye ta.
"Better!"
"For You!"
"Kace kai ma ka fara jin Broking English gaskiya kaci a tafa maka! Tun ku yan Nijar official language dinku Faransanci ne!"
"Eh gaskiya kan zama da yar Najeriya ya sani koyan Harshen turancin dole dan na fahimci autar malam baturiya ce."

Ya fadi haka yana matsawa daga jikinta..
"Maude akwai ashoben da zamu yi kudin shi dubu goma, kudin dinki dubu bakwai."
.cike da mamaki yake kallonta yana faɗin.
"Anum ke daya kinci dubu sha bakwai, gaskiya a rage min babu kudi ba."

Cikin tsiwa ta zuba mishi ido, amma dake tana niman abu ne, kallon shi tayi kamar zata saka mishi kuka tace mishi.
"Ai shikenan! Zanje na nemi wanda zai bani kudin kasan da haka ka matsa min lallai kana sona yanzun kasani na kori samarukana sannan kana kuma nuna min renin hankali."

Yadda Anum take nuna ya hanata rawan gaban hantsi abun ya dame shi, bai ce mata kome ba ya bar zauren gidan.

..... Washi gari ta shirya ta tafi makaranta, domin ta Fahimci idan tana son abu ta fara zuwa makaranta, wato yaudarar maude ya bata.

Aikuwa sati biyu ajere ta tafi makarantar, ranar juma'a ya bawa Rulwanu dubu sha bakwai ya kai mata da wani kwalbar turare da yadin shadda light blue.
Mika mata yayi tare da cewa..
"Gashi inji Atm card dinki wallahi Anum zamu yi uwar watse dake, kowa yasan halin da kike jefa bawan Allah nan, idan kina son abu ko bai dashi sai ya nima anya da imani a kirjin ki."

"Kan Uba! Ni na roke shi? Da zaka sani a gaba kamar Ubana kana min fada bari kaga Iskanci." Tattara kayan tayi fuuuuu tayi waje, Maman Aminu tace.
"Haka nake son mutum, ai bashi bane autar maza,.maida mishi kayan shi."

Wani irin takaitaccen kallo Umma tayiwa Rulwanu, tare da cewa..
"Sai ka zuba ruwa kasha ka hada husuma!"
Zai mata bayani ta d'aga mishi hannu, dole yayi shiru.

--- "Maude wato bawa Rulwanu kayan kayi yazo yaci mutuncina?"
Numfashi ya sauke sannan yace mata.
"Koma window cikin gidan muyi magana"

Koda suka dawo cikin gidan, rarrashinta ya shiga yi har su Yaya Abubakar da Bashir da Abdul Hakim suka zo daru take mishi, suma basu ji dadin rashin kunyar ba, dan haka cikin lalluma suka jata cikin gidan suka shiga rarrashinta, kallon yadin shaddar Bashir yayi cikin nutsuwa yacewa Abdul Hakim.
"Kasan wannan yadin kwananan na ga tallar shi a wani bincike da nake a google! Kasan nawa kudin yafi dayan shi a kudin najeriya?"

Tura baki tayi sannan tace.
"A'a dari biyar ba, dake ya mai dani sakarya shine zai kawo min yafi me zubin sky, wato ga yar kauyen kayau, ai wallahi ba dan kun dawo dani ba, da yaga yadda ake rikici da rai ina kallon shi wato ya maidani jidali."
Takaici yasa Rulwanu juyawa yanar gidan yana ji da Allah zai bashi dama daya da yaci Uban Anum daidaigwargwado (😁amma Umma itace matsalar shi yanzun ta fara Mishi fada da Niman make shi..kwafa yayi.

Ita kuwa ya zauna a tsakanin su, tayi ta zuba tab'ara sai da Umma ta daka mata tsawa ta tashi tana tura baki zata yi kuka,
"Ayya Umma! Har..".
"Haka kake kallon su Bello suyi abinda suke so? Tambayar ka nake Abubakar,.nace haka kake kallon su Ha'uwa suyi abinda ransu ke so? Toh indai ba zaku taya ni akan Anum ba karku kuma shiga maganar ta"

Sai dai basu ga wani abun da yasa Ummu take d'aga hankalinta ba, kawai dai ta cika uzurawa ne, amma ai Anum bata da matsalar kome, umma ce kawai me wannan matsalar tare da takurawa Anum.

D'aga yadin Abubakar yayi, sanan yacewa Bashir.
"Wannan yadin nera hamsin ake sayarda yadi ukun nan fa? Lallai shayi tana kai mishi!"

"Hahaha! Baka tab'a jin kamshin turaren shi bane, Yawwa ga kwalbar. Na tab'a jin kamshin sa sau daya lokacin da mukayi tafiya da tawagar me girma gwamna zuwa abuja,. Jikin mataimakin shugaban kasa naji kamshi domin na zauna kusa dashi sosai."Inji Abdul Hakim,
"Kai Hakim! Karya dai ba dabi'ar ka bace?" Inji BASHIR,
"Wallahi ba da wasa nake maka ba, ni da hancina na tab'a jin shi kalar turaren bana mata bane, Anum!!" Ya kwala mata kira,
Fitowa tayi tare da kallon shi.
"Wannan turaren kece kika ce kike bukatar shi?"
Cikin sakarci tace..
"Tab me zanyi da turaren karamin kwalba? Kawai zan ajiye ne ina sakawa a man shafawa na."

"Saya yake ko?" Tab'e baki tayi zata bashi amsa Umma tace musu.
"Haramun ne shiga abinda babu ruwanka." Tsit suka yi,

Ita kuwa ta koma d'akinta,.tattara kayan suka yi tare da ajiye kowa ya shiga fita kamar munafuki. Dama bikin yar mijin Hafsat ne ta nemi kudin a gurin Maude.

Haka ranar taki zuwa makaranta, ta shirya zuwa, Bakaro inda Hafsat take aure, ta kai mata kudin, bata dawo ba sai dare, tana isowa ta kalli shagon shi babu mutane, shiga tayi ta zauna a kujeran bai sani ba.
"Maudeeeee!" Ta kira sunan shi da karamin murya, har tsakiyar kan shi yaji muryanta, jikin shi babu laka ya juya dan ji yaƙe kamar bai mallaki gangan jikin shi ba. Zuba mata rikitattun idnun shi yayi yana binta da wani irin sansassanyan kallo.

"Hmm!" Yace mata yaki magana, ya cigaba da abinda yake.
"Maudeeeee!" Kin kulata yayi sai da tazo ta tsaya a gefen shi.
"Maude yunwa nake ji, a fasa min kwai da balagu, sai tea yaji amma a saka min sugar."

"Me ya hanaki zuwa makaranta yau?" Ya tambaye ta a tausashe.
"Banyi niyya ba!" Ta bashi amsa.
Dauke kai yayi tare da cigaba da aikin shi.
"Fita min a shagona!"
Ya juya tare da riko arms dinta ya turota waje, kar na kuma ganin kafarki nan."

"Ni ka kora? Ni zaka ciwa mutunci? Ni zaka turo daga cikin shagonka, hell You!" Tasss aka wanke ta da mari, a rikice ta d'ago kanta, malam ta gani. Bakinta na rawa tace.
"Malam!"
"Mijin da zaki aura kike gayawa Malam? Abubakar bai isa ya tsaya a gaban shi da maganar banza ba, ke wacece da zaki mishi rashin kunya? Ki wuce kafin nasa a zane min ke"

Da gudu ta shige cikin gidan tana ihu, tare da birgima, kuka take tare da cewa Wallahi bazata auri maude me shayi ba, ko maza sun kare.

Abinda ya fusata malam kenan,.ya shiga zaneta da duk abinda yazo hannun shi. Kuma irin dukar nan ne me kan Uwa da wabi, sai da Umma ta kira Maude .
"Haba Baba! Anum nawa take da zaka mata wannan dukar? Yarinya ce karama fa, don Allah idan an ciza sai abusa, su mata mikar dasu sai da hikima."

Zunzurutun cirarra da malam yake kamar zai fadi sai da Umma ta dibo mishi ruwa a randan kasa, sai ajiyar zuciya yake saukewa abin tausayi. Sannan aka d'aga Anum lokacin ta suma, kallon hancinta da fuskarta yayi wanda ya sha duka, ya shafa mata ruwa a fuskar.

"Malam Maude! Idan ka shirya ka turo mutanen ka?" Cike da al'ajabi ya kalli malam, sabida bai tab'a tsamanin haka ba, kuma bai kawo haka a ranshi ba.
" Baba!"
"Maude ni nace ka turo mutanen ka, sadakin ta kar ya wuce talatin dan ban san me zan baka ba, tayu na rufe cuta na baka, kana da damar bincikar lafiyarta."
"Wallahi ba zata sabu ba, yarinya na ta auri mara asali da bai da kowa!"

Kallon su Badi'a da shukrah tare da su Faiza Anum tayi, kanta sunkuye tana shashekar kuka, taja hancinta sannan ta duba wayarta tace musu.
"Karfe biyar saura na safe kun sani na tab'o rayuwar baya." Jan hanci tayi tare da dauke kanta daga kallon da suke mata, kallo ne irin na tausayin mutumin da ya ga rayuwa, ita kuma bata son wannan kallon, dan yana kuma gigita mata rayuwa.

"Aunty Anum?" Badi'a ta kira sunanta, kuka ne ya kwace mata, ta dakatar da ita.
"Nice na zabi na baku labarina, don Allah ku barni haka zan baku labarin. Yanzun ina jin barci da son hutawa."

Ta mike tare da nufar ban daki, tayi alola da wanka, sannan ta fito ta samu duk sun watse, sallah Asuba tayi da nafilla da ta rasa ta jima tana addu'o'in, kafin ya kwanta a gurin, tana jan zuciya. Lumshe idanun tayi tare da tunawa da kyakyawan fuskar Yarta cikin pink showel,.me daukar hankalin, yar cute face ɗinta kamar na Ubanta, ga fuskarta jajjur gwanin sha'awa,

Sai gashin da ya sauko har giranta, murmushi tayi tare da ganin tsagwaron kaman da Maude... "Asadullah Haidar Turab! Murmushi kai kadai da suna haka, Haidar dina. Aliyu na Zakina ka tafi kabar ni cikin tashin hankali da damuwa, zan cigaba da rike aurenka har karshen rayuwata" wasu irin kwalla masu zafi suna zubo mata.

*_Kuyi hakuri babu tsawo ina azumi ne♥ idan na kai dare kuma zan iya gajiya da rubutawa na kwanta_*
#Mai_Dambu[1/29, 5:52 PM] +234 806 066 1296: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
_Take shafin shine Uwa mabada Mama koda Uba sarki ne! Uwa rumfa sha shirgi, Uwa Duniyar Y'ayanta, Uwa Aljannar Y'ayanta! Itace Haske! Itace farin ciki! Duk wani tantirin dake yake alfahari. Duk wani mutumin kirki dake yake alfahari! Uwa Turmin tsakar gida shaluguden mahassada! Uwa Me dariya da dariyar D'anta me murmushi da murmushin D'anta, ya cije ki kince Auwch ya fashe da dariya kin saka dariya dan kar yayi kuka! Wannan shafin Sadaukarwa ce ka MAMA! UMMA! UMMI! AMMIH! INNA! ANNE! BA'ABA! MOMMY! MUMMY! MOM! UWATA! UWARMU!

UWARSU! UWARTA! UWARSA! YA Allah ka jikan Iyayen mu mata! Da suka sadaukar da rayuwar su domin mu!□□□□□ Please Say Amin_
BABI NA SHA BAKWAI.

Wani irin kuka ne yazo min, tabbas nayi kuskure, na zalinci kaina, sannan na cutar da kaina fiye da yadda ake tsammani, da ace hannun agogo yana juyawa da na juya kaddarata ta dawo min baya.

Gyara kwanciyar ta tayi tana sauke ajiyar zuciya, sannu a hankali barci yayi gaba da ita.

A can asibitin kuwa, Safiya ce ta kalli Hafsat.. "wai Auta bata da lafiya?" Tab'e baki tayi sannan tace mata. "Toh ko nice na kasa mata ciwon? Ina ruwana da ita, ta mutu ma i don't care."
"Amma Hafsah kina da bakin zuciya, ina ce har dake a cikin masu nunawa Anum tayi abinda take so! Ke har guduwa kika ce tayi wato yau da ta lalace zaki juya mata baya, dan ráshin Imani da tausayi!"

Shiru tayi sannan tace.
"Umma!"
"Karki yarda kiyi min maganar banza na mare ki,. Ai naji duk abinda kuka yi da Hama, toh bari na gaya miki kashe muku uwa zata yi, ita kuma Anum zaku saubanta rayuwar ce, kuna ganin kamar abinda kuke daidai ne? Toh kuka uwarku take da kewar Yarta babu yadda ta iya ne daku yasa take b'oye kaunar yarinyar a zuciyarta.

Amma idan za a cire son zuciya tafi kaunar KHADIJAH sama daku!" Tana fadar hakan ta juya ta koma cikin asibitin, ta samu Baba Hama tana gayawa Mama abubuwan da Anum take, ita kuma Maman Aminu ta kafeta da idanunta jajjur, tana kallon ta, duk da kokarin b'oye hawayenta bai hana su sauka da mugun gudu ba.

"Hama! Zoki bar mana Asibiti kije can kiyi ta gulmarki Allah ya yaye miki!" Fita tayi cikin jin kunya da haushi, domin kuwa korafi bai karbu ba..

"Maman Sadeeq! Nagode!" Ta faɗa da muryan ta da yake rawa, a hankali ta sake kuka, me mugun ciwo.
"Me yasa na lalata mata rayuwa? Me yasa ban fahimci zata iya fadawa matsalar rayuwa ba? Na gama b'ata mata lokacin ta da tarihinta, amma Maman Sadeeq, don Allah karki bari sauran yan uwanta su san da haka, zasu cigaba da kuntatta mata. Na sani sun tsane ta,. amma nice sila, Maman Sadeeq tsoron hakkinta nake ji, kar na mutu Allah ya tuhume ni da hakkin Khadijah!" Ta faɗa cikin kuka, me mugun cin rai.

Duk yadda taso barci ta kasa, sabida numfashin ta dole sai da aka d'aga gadon, zata fara barcin ta kalli Umma sannan tace mata.
"Don Allah ki saka a zo min da ita ina mugu mugun kewar ta,!"

"Insha Allah, Binta zata kawo miki ita, karki damu Allah zai yafe mana kusakuran mu," shiru suka yi kafin Maman Aminu tace mata.
"Wato duk yadda kika so tsayawa yarinyar nan tayi kyan kai, haka naki tare da juya alamarinta baya, gashi na kaita na barota. Domin nice nayita hure mata kunne akan tana haihuwa zata rabu da me shayi. Bansan cewa jidali nake kara mata ba.

Ban tab'a sanin cewa zata iya juyawa Jaririyar baya ba, amma nasan da kuruciya, shine."

Goge kwallar ta tayi tare da lumshe idanunta, tana kuma hasko dogon lokacin da ta dauka tana mata fada akan ta daina zuwa shagon Maude bayan ta dawo gida, lumshe idanun ta, a karo na biyu a lokacin taso fahimtar Anum tana son zama da maude kawai bata da yadda ta iya ne yasa ta juya mishi baya.

Dan ta kunnenta, tasha jin Anum din tana gaya mishi abinda yake damunta gashi ba ita daya ba, ga Kwamishina da ya takura mata da zancen yaran su, idan ana niman muguwa aka same ta, toh tabbas sai dai a rufe shafi, domin da kanta ta zalunci yarta, gashi har yau bata tab'a jin Anum tace itace ta sakata aikata abinda ya faru ba. Kwalla ne ya zubo mata, a hankali ta juyar da kanta, tana me jin haushin abinda tayiwa rayuwar yar karamar yarta.

Umma kuwa ganin Maman Aminu tayi barci, ta juya ta fita tare da kiran wayar Binta, ta gaya mata ta kawo mata Anum, tana son taga jiki.
"Umma indai bai zama dole ba, abarta kawai karta zo ta d'aga mata ciwon ta."

"Ungo naki, Ni sa'arku ce? Kar na kuma ganin wani ya shiga al'amarin mu da Anum!"
Allah ya wuci zuciyarki." Inji Safiya.
Bata yi sababi ba, saboda asibiti ne, amma tabi su da harara tare da tsaki, lokacin da ta koma cikin dakin. Shiru tayi tana kallon Maman Aminu da take sauke numfashi. Addu'o'in fatan sauki tayi mata, sannan ta koma ta zauna a kujeranta.

** "Ban gane ba Abidah? Ina takardun da na ajiye anan?" Cikin tsannanin tsoro ta dubi inda ya ajiye takardan babu shi babu alamar shi, had'iye yawun tashin hankali tayi sannan tace mishi.
"CM wallahi ban gani ba, kuma abinda na sani, anan ka ajiye."

Wani irin kallon Banza yayi mata sannan yace mata.
"Tunda nake da Aina'uh da Anum basu tab'a tab'a min kaya na ba, amma ke na rasa wacce irin Barauniya ce, ban isa nayi ajiya ba sai ki dauka toh wallahi idan baki fito min dasu ba, idan na shigo gidan nan ranki zai yi dubu ya b'aci, dan Ni ba sakarai bane."

Yana gama fad'ar haka ya juya ya ficce zuwa part din Mahaifiyar shi.
"Lallai kuwa, nice Adama zata kashewa aure? Toh ta ajiye a ranta nice ajalinta."

Fuuu ta juya zuwa d'akinta, sai lokacin ta lura da yan biyu da suke makure a daki, dan tasaka su a jikin kofa ta matse su, ko numfashi basa ja. Tana buɗe kofar suka zube kamar mutanen da aka saka a cikin deep freeza.

A razane ta kuma saka ihu, ta fita tana niman dauki, lokacin da Ibrahim yazo a razane ya dauki yaran shi ya fito da Hishmah, sannan ya koma ya dauko Hisham,. Ya saka su a motar shi. "Ibrahim!"
Bai saurare ta ba, yaja motar shi ya fita, yana fadar Allah ya basu lafiya. Alwadata ya kai su, aka amshe su, kasa zama yayi yana ta yawo a cikin a bakin kofar asibitin.

Fitowar Likita tare da mika mishi hannu, "alhamdulillah, yaran sun farka sai dai kuma" a firgice suke domin suna tsoron yadda Anum zata birkita musu hankali.
"Dr me ya!"
"Ku biyo ni Office!"

Bin shi suka yi Hajiya Turai da Ibrahim, zama yayi tare da da gyara zaman glass din idanun shi.

"Ina Mahaifiyarsu take? Me yasa take azabtar dasu da yunwa tare da duka, yanzun ita macen." Girgiza kai yayi tare da zare glass din idanun shi yace musu.
"Wallahi duk jikinta akwai shedar kunar wuta, me yayi zafi da ba zata yi hakuri ba haka."

Jikin Hajiya Turai ne ya dauki rawa, tana kallon Ibrahim wanda ya kafeta da idanun shi rinannun,
"Hajiya taya haka ya faru? Hisham da Hishmah a dakinki suke meye ya kai su d'akin Abidah?"
"Ibrahim!"
"Ya isa haka! Dr nagode sosai, sai dai na rabu da mahaifiyar su, shekara biyu ake nima kenan"
"Toh gaskiya Yaranka suna bukatar kulawar ka, don Allah ka duba Alamarin."

Gyada mishi kai yayi,likitan ya mika mishi takardar magani, sannan ya fice,

***
Karfe sha biyu na rana, naji wayata tana kara kamar a mafarki, na lallubar tare da kaiwa kunnena.
"Aunty Anum! Don Allah kiyi hakuri ba gulma bane, dama nakira ki na gaya miki Hisham da Hishmah suna asibiti, wancan bakar munafkar tayi musu duka, tare da watswa musu ruwa suka ta tsayuwa tun asuba a bayan kofa."

"Marka!" Na kira sunan ta a raunane, "yanzun suna ina?"
"Ai Alhaji ya kai su asibitin da yake kai su nan!" Lumshe idanuna nayi sannan na bude shi.."nagode sosai"
Na katse kiran, tare da mik'ewa ina ji yau koni ko Abidah, yau sai na mata abinda uwar da ta haife ta bata tab'a mata ba, dan haka ina tashi na shiga ban daki, nayi brush tare da wanke fuskana.

Ina fitowa na sami Aunty Binta a tsaye tana rike da waya.
"Lovely Sister, inji Umma wai tana son ganinki a asibiti duba jikin Mama."
"Toh Aunty Binta, amma bari na duba jikin su Hishmah suna alwadata, an dake su."

"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, waye yayi musu wannan aikin?" Inji Aunty Binta,
"Ji ki da wani batu, matar uban su mana!" Na juya da sauri na dauki wayata da yar ƙaramar pose dina, na fita da sauri.

A unguwar su Aunty Binta akwai masu gyaran mashin dan haka gurin su na nufa tare da rokon su, su bani kabil. Suna bani na bar unguwar.

Unguwar sarakuna nan na nufa, ana sauke ni a kofar gidan na buga me gadin na gani na, ya washe bakin shi.
"Hajiya! Wallahi abubuwan sai kara lalacewa suke."
"Malam Nafi'u!"
"Na'am!"
"Ga wannan kasha ruwa dashi!"
Babu musu ya bude min kofar gidan na shiga ko part din Aina'uh ban kalla ba, na nufi part dina da XOXO ta same shi a matsayin nata. Cire hijab nayi na mafe shi a bakin barandar ta,.na kalli Part din Ibrahim, dauke kai na nayi, dan na manta da batun mun tab'a rayuwa dashi.

Murɗa kofar part din nayi tana kwance, ba barci take ba amma ta shiga cikin damuwa..ina shiga na rufe kofar Part din yadda ko anji Ihu babu me kawo mana dauki sai mun kashe kan mu.

Gyara tsayuwa nayi tare da sake mata bulala, kamar daga sama taji saukar shi a Jikinta, duka nake mata, zaneta nake kai na daki XOXO a ranar kukan da ta sani na tsawon shekaru yau na fanshe abuna,tun ana jin ihunta har suka daina ji.

Aina'uh da Malam Nafi'u tare da Marka sun buga sunyi magiyar ban kula su ba, asalima kamar kara min karfi suke da. Haka na cigaba da jibgar shegiya.
"Anum!" Naji muryan Ibrahim,
Ko ta kanshi ban bi ba, yayi kiran Duniyar nan. Ban kula shi ba, sai da naji muryan Ya Aminu ya sani jifa da bulalan, na bude musu kofar, abinda ya fara min shine dauke ni da mari.

"Ki godewa Allah baki da ishshen lafiya da na miki kwatankwacin abinda kika mata, Anum me kike nima a duniya? Meye matsalar ki? Kin saka yar mutane a gaba da duk.."
"Aminu bata yi kome ba! Na kiraka ne dan nasan kaine Kawai zaka iya dakatar da ita daga barnan da zata yi, amma wallahi ban ga laifinta ba, da zaka ga halin da wancan halittar ta jefa min Yaran mu, sai kaga dacewar abinda Anum tayi.

Kawai na kiraka ne ka tafi da ita, Ni idan nayi hukunci za a iya cewa na rabu da mace sabida Yaran Anum, amma ita Uwar su idan tayi hukunci ya fito duniya taji kowa zai iya cewa sabida rayuwar yaranta tayi, a wannan duniyar da uwar da ta haifeka ake hada kai a cuce ka, Anum Nagode sosai, amma ki duba magana ta, ki dawo muna bukatar ki, idan kina bukatar saki wallahi Ni da kaina zan nemi malamai da Alkalai su raba tsakanin ku."

Ko kallo bai ishe ni ba, ba wuce shi tare da barin gurin na dauki hijab dina da waya ta na fita daga gidan, a hanya Ya Aminu ya dauke ni,.muka wuce gidan Anunty Binta, sai lokacin na samu damar kuka, tsayawa yayi a gefen hanya ya mika min hanky na cigaba da kukan, har ina jan zuciya.
"Ba kin dake ta ba? Toh kukan na me? Kiyi hakuri da Qaddarar ki mana, kiyi hakuri da yadda Allah ya jarabce ki mana...
#truelifestory
#Mai_Dambu.
*Dubun Gaisuwa ga Masu bibiyar labrin zanen ƙaddara ta musamman Fitilar Hikayata MD! Furrucina Fans B! Sai Jadeera na grp din Matan Quarts wannan Matar Ubangiji ya barni dake! Insha Allah dake zamu tafi Daula biyu! Kina bani abinda nake buƙata a labari □□□! Ku kadai ne zan bugu kirji nace naga Comments din ku Diyoyin albarka Maman Balkisu ina godiya ga□ □ *
[1/29, 5:54 PM] +234 806 066 1296: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA SHA TAKWAS
...
"Babu wanda ya isa tsalleke kaddarar shi, Anum ki godewa Allah, yau kina raye kuma zaki gyara kuskuren baya, kiyi farin ciki da kina raye zaki gyara abinda kika b'ata, fushi da fada ba naki bane, Anum bana jin dadin rayuwa ta, idan naji labarin kina fada akan namiji.

Koda yake yau akan Yara ne, amma don Allah indai ba zaki koma gidan Ibrahim ba, ki daina taka doka, yanzun idan yazo ga tsautsayi kika kashe ta fa? Me zaki cewa duniya bayan kin fi kowa sanin abinda ya faru dake. Ina rokonki Arziki babu amfanin fada tunda ba zaki koma mishi ba, don ALLAH ki sanyawa zuciyarki salama, kiyi hakuri da rayuwa."

Gyada kai take kamar kadandagriya, hawaye na zuba mata, tace.
"Nagode!"
"Karki damu, ina tare da ke!"
Murmushi tayi sannan tace mishi.
"Na yarda da haka tun ba yau ba!"
Bai ce mata kome ba, ya kaita gidan Aunty Binta, kallon su tayi amma bata tambaye su meke faruwa ba, saboda Tarbiyyar Umma ce, bata bincike. Sai da Aminu ya gaya mata abinda ya faru, kallon Anum tayi taga bata kalle ta ba,kanta a kasa.
"Idan Umma taji wannan labarin, zaki iya kare kanki ko?"
"Zan gaya mata da kaina." Ta faɗa musu haka ta wuce abinta.
"Anum bata ji har yanzun, ban san lokacin da zata daina aiki da zuciyarta ba, gabaki daya ta gama da yarinyar nan, domin dukar kawo wuka tayi mata, jikin Yarinyar ya farkashe.

Amma kuma Yallabai bai wani damu ba, dan ya kira Ni ne na dakatar da ita, ba wai na hanata daukar matakin ba, kuma na fahimci tayi dukar da biyu ne, dama tana cike da yarinyar kuma ta tab'a mata yara."

"Kasan yaran basu da lafiya ne, musamman ita macen tana fama da sikila, shi yasa Anum bata kaunar dukkan abinda zai tab'a lafiyar su, kaga wancan satin ba karamin case muka yi da Mudi Wuntin dada ba, Ya dauki Isma'il wai ya kai shi almajiranci.

Karka ga yadda suka yi da Usman, amma ita dake bata da cikakken lafiya na hana a gaya mata, abin tausayi ko tausayin yaron bayi ba, ya dauke shi har garin Kebbi wai almajiranci, babu shiri muka dawo dashi yana gidan Usman yanzun.

Ina jin su, zama nayi tare da sake kuka mara sauti ƙaddara ta ba iya ni kaina ta tsayawa ba, hatta yarana rayuwar su tana cikin gararin rayuwa. Ashe dalilin da yasa Maude yaƙe gaya min cewa.
"Kinga ke matar Arziki ce, duk namijin da Allah ya nufa zai samu Arziki dake, sai kin haihu dashi, kiyi nazarin abin cikin ki mana, idan har zaki haifa mana. Ba sai mu hada da wancan Yaron Isma'il ba, mu rike abin mu babu wanda zai ce bamu ne muka haifa ba.

Amma hankalin ki yana jikin wadancan da suke da gata, nasan basu da lafiya, amma ki nazarci waye Ubansu da kuma wancan waye uban shi, Ibrahim yake ko? Zai iya faffutikar ganin lafiyar yaran shi, shi kuma wancan da yake rayuwa cikin kunci da bakin ciki ya kike tunanin zai kare, ki Fahimci abinda nake nufi, sai mu dauko shi mu rike shi Kinga kina kokarin karatu shi kuma sai na san yadda zan nima mishi makaranta me tsada na jefa shi, yayi karatun shi idan Allah ya buda min ya tafi Madina ya karanci b'angaren addinin Musulunci ko me Dijamah tace?"

Kallon renin hankali tayi mishi, sannan tace..
"Maude! Kana da labarai na kazon kurege, yanzun don Allah banda cutar kai a ina zaka samu kudin da zaka kai Isma'il Madina, toh naji da shawaran ka, amma ba zanyi aiki dashi a,kaga wannan cikin, ji nake kamar na cire shi lokacin shi bai yi ba, ina dalili za a takura min sai na zauna da kai ko kunya ba..."
"Toh naji na takura miki ke meye ya kawo ki shagona karfe goma sha daya na dare!"

"Takardan Sakina nazo amsa!"
"Yarinya fadi gaskiya kin dai zo karb'an aji garau, kuma zaki dame shi dan zillo take yi taga abincin ruhinta."

"Tir baka da kunya wallahi," ya gaya mishi.
"Eh bani da kunya ban kai ki ba, dan yanzun ina fara kai ki bangon duniya zaki fara niman cinye min bakina, Ni abinda yake damuna wannan bin kirjin ki naga kamar sun kusan tashi aiki anya zasu iya shayar min da Yarona ko yarinya na,"

"Maude ina da abin yi fa! Ka bani takadrdana, zan wuce zuwa cikin gidan." Ta faɗa.
Tana kai hannunta kirjin shi tana shafa tsokokin da suka cure guri guda.
"Kika son su ne?"
"Sunyi min kyau ne!"
A hankali ya kai bakin shi kunnen ta, kome ya gaya mata ta wani rike mishi wuyar shi tana sauke ajiyar zuciya, fuskarta dauke da murmushin jin dadi, a hankali da hikima da dabara, ya shiga raya daren cikin wayo, bata san duniyar da Me shayi ya dauke ta ba, sai da taji ta a duniyar Sama, kafin ta Fahimci ya lula da ita duniyar maji daɗi.

Hawaye ne suka zubo mata,tana kewar gwarzon namijin duniya, tana kewar namijin da ya sanya ta fahimtar wacece ita, Tana alfahari da samun shi a matsayin mijin da ya gwada mata soyayya a saman gadon su. Ya koya mata yadda zata mu'amalanci rayuwar aurenta, a cikin aure hudu idan ta cire na farko da tayi dashi, tabbas shirme tayi ta aikatawa, domin kuwa tayi amfani da damar ta, na rashin hankali tayi ta ganin ba so take aure ba, yan canji take aure.
"Aunty Anum!"
Kallon Shukrah tayi da ta ajiye mata abinci tana kallonta,
Zama tayi sanan ta fara cewa.
"Aunty Anum, kina yawan saka damuwa a ranki dukda Ummi bata tab'a gaya mana halin da kika shiga ba, amma nasan wallahi kin fada ƙaddarar rayuwa, don Allah kici abinci karki bar damuwar wasu ta tab'a lafiyarki domin muna sonki sosai.

Sannan Baban Baby,.ina ji a jikina yana nan yana faffutikar ganin ya dawo gare ki."
Murmushi tayi me ciwo sannan ta kurb'i ruwan shayi,
"Idan kuma ya mutu fa? Idan kuma baya raye fa? Idan an kashe shi fa? Asadullah ya sha gaya min gudun ceton rayuwar shi yayi, sai gashi ya faɗa kaddarata. Ni kuma ban duba waye shi ba, nayi ta gara rayuwar shi. Dama Ila ya gaya min ban dace da rayuwar Asadullah ba, kawai ya faɗa soyayya dani ce, a lokacin da bai dace ba.

Shukrah Ni guba ce, duk wanda na tab'a sai na kashe shi, Shukrah hatta yarana ban bar su ba, suma b'ata musu suna nake, na gaji da rayuwata, ina da ana rokon mutuwa da na roki tawa na huta, da wannan rayuwa."

"Subhanallahi! Waye ya gaya miki ana rokon mutuwa, kinsan dalilin da Ubangiji ya barki a raye? Ya barki ne ki nemi tuban shi, kuma ki shirya gyara kuskuren ki na baya, sannan ki gyara goben ki domin cimma nasarar da kuka fadi a kai.

Aunty Anum, Allah yana sonki da rahama wallahi, bana tunanin Baban Baby ya rasu, duk inda yake yana dawainiyya da kewarki, Ai yasan kinyi nadamar abinda kika aikata kuma zai yi wuya ki kuma aikata makamancin abin da ya faru,.ki rike Allah yana tare dake kuma ki gode mishi domin ya kuma baki dama ta biyu ne domin gode mishi da Ni'imar da zai miki, ai babban abun godiya kenan,. Allah ya bani dama na biyu domin nagode mishi,"

"Alhamdulillahi!, Allah na tuba ka yafe min kura kurai na, badan na isa ba, badan kome ba, ba dan na cancanci haka ba. Sai dan Rahama da jinkai na kane. Allah Nagode maka, Alhamdulillahi" na fada a raunane..

A hankali ta gama shan tea, sannan ya shirya suka bar gidan zuwa asibiti, tun daga jikin masalaci ta hango Mawedo,.suna sauka ta fita da sauri Allah sarki dan Uwa me dad'i, tashi tayi itama tazo ta rungume Anum,. wacce zata fara kuka.
"Ban zo dan na saki kuka ba,.nazo ganin jikin Mama ne, don Allah karki karya min zuciya."
"Toh Ni dai wannan sakalcin Autar malam yawa yake dashi sake min Yayata."

"Aunty Kinga Rulwanu ko, Tunzurun banza kawai haka zaka tsufa babu macen da zata aure ka, domin ka tashi aiki "
Ta faɗa cikin kuka me hade da dariya, Murmushi Umma tayi da ta hango yau Anum tana dariya. Itama dariya take duk da bata san meke sanya su farin cikin ba,.har suka isa gurin ta, Anum ta isa jikinta tana sauke ajiyar zuciya. Shafa kanta take tare da tufa mata addu'a.
"Anumullah waya saki kuka?"
"Umma XOXO ce!" Sake shafa kanta tayi.
"Nasan ba zata saki kuka da lafiyarki ba,.me tayi"
"Umma tayi kome!"
"Allah ya shirya ta!"
"Ba zata shiryu ba, amma na mata tabon da ba zata manta ba, dan na zane ta, yadda kullum ta ga ciwon ba zata manta da abinda ya faru da ita ba,!"

Addu'o'in ta Cigaba da tofa mata, tana shafa bayanta, ta kuma hana kowa magana, tana sauraren Anum din, yadda take gaya mata abubuwan da yake damunta, da kuma abinda tayi.

"Allah yayi miki albarka, yasa. Ki girma ki daina biyewa makircin mutane kina ɗaukar doka a hannunki, babu kyau kar na kuma jin haka kinji Kyautar Allah!" Gyada kai tayi tare da cewa.
"Umma Yinwa nake ji tea kawai na sha na fito."
"Mitseww!' Hafsat taja tsaki tare da da barin gurin.
"Umma kin san har yau wasu basu Fahimci, irin arzikin da suka ci a gurina ba."
.buge mata baki tayi "bana son sakarci." Inji Umma,
Kwal kwal tayi da idanunta, tare da kallon Umma,a
"Umma na!"
"Ya isa haka tashi muje kiga Maman Aminu."
"Hmm! Yanzun ina zuwa ciwonta ya tashi zaki ji yaranta suna cewa zan kashe musu uwa! Allah ya bata lafiya!"
"Yaushe muka fara sa'in'sa dake?" Duk sai Safiya da Bashir tare da Musa suka ji babu dad'i, bayan tabar gurin ne ita da Umma Musa yace.
"Sam tsangwama bai dace da rayuwar yarinya irin Anum ba, sabida lokacin da Umma take faffutikar ganin ta bata tarbiyya ki muka yi muka shiga ganin laifinta har muna ganin tafi cutar da ita, bamu tab'a kallon alkhairin ta ba, asalima kawai nuna haka muke da cutarwa.

Yau Anum tafi son zama cikin su Aunty Binta ne sabida har yau basu tab'a cewa itace ta kashe musu Uba ba, basu tab'a nuna mata sun tsare ya ba, asalima suna tattalin lafiyar tane ne, amma baki daya mun juya mata baya, wannan ban da ta sami Umma dasu da ba karamin baudewa zata yi ba, ta nuna babu wanda ya isa ya tankwara ta, don Allah mu rage k'iyayyar nan"

Ya faɗa musu, tare da kallon su Dukkan su. Tab'e baki Hafsat tayi sannan ta mik'e tare da cewa.
"Idan har nice zan yafewa Anum, wallahi gwara ta mutu zai fi min dadin fadar wannan fadararriyar karuwar gidan mu ya mutu kuzo ku mana gaisuwar mutuwarta."

Tana gama fadar haka ta juya tare da barin gurin, tana kuma jin tsanar Anum a ranta.

Lokacin da suka shiga Umma tana gaba, Anum na baya, kallon Mama Umma sannan ta d'an matsa Anum ta iso gabanta, mika mata hannu tayi, da sauri Anum ta isa gurinta, tare da zama a bakin gadon.

Sunkuyar da kai Umma tayi tare da share kwallar da ya zubo mata, domin takai matsayin tausayin Anum da Mahaifiyar ta, musamman yadda Anum din take kuma shigewa jikin Maman ta, tana sauke ajiyar zuciya da kwalla.
Lalaci Mood 😀 Wallahi na fara gajiya
#Mai_Dambu
[1/29, 5:54 PM] +234 806 066 1296: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA SHA TARA.

Shafa bayan Anum tayi, sannan ta kalli Umma da ta juya musu baya. "Nagode sosai Maman Sadeeq!" Ta kuma gyara kwanciyar Anum a jikinta, suna wani irin kuka na ban tausayi a cikin d'akin.
"Khadijah, kin yafe min?" Ita Umma tayi da sauri dan son karya mata zuciya.
"Mamana! Mama! Babu abinda zaki yi min na kasa yafe miki shi, sai dai kece ma zan roke ki, ki yafe min." Shafa kanta tayi cikin jin wani nutsuwa na shigarta.
"Baki min kome ba Anum, Allah ya miki Albarka;"

Tashi tayi tare da zama a gaban Mamanta, tana murmushi kwalla na zuba mata, tana jin wani irin nutsuwa itama ya shigo mata, sallamar Hafsah ne ya sanya su, suka d'aga kansu suna kallonta.
"Kutt! Zaki kashe mana ita ne!"

Kallon Maman Aminu Anum tayi tare da yi kamar zata fasa kuka, har da wani kwallar ta, sannan ta mike zata fita.
"Dawo Anum."
"Mama wannan me kyan d'an macijin!"
"Ke mugun halinki bai saka naki ki ba, akan me zan kita? Bana jin a yanzun zan iya dogon magana Autana zuba min abincin da Aminu ya kawo yunwa nake ji!"

"Aikuwa Mama Muci tare dan nima yunwa nake ji!" Ta fadi haka a sanyayye. Dan har yanzu na bar da shakkar Maman Aminu a ranta.

Cike da mugu mugun bakin ciki Hafsat ta bar ward ɗin, Anum da Maman ta suka ci-gaba da cin abinci su, duk sai suka takura da juna, bayan sun gama Anum ta wanke mata hannu, sannan ta saka mata ruwa tayi alola, ta shimfida mata abin sallah ta tattara kayan ta fito waje. Kallon juna suka yi da Hafsat wacce suke sa'in'sa da Safiyya.
"Kije duniya tafi gabaruwa ji, duk abinda ka shuka shi zaka girba. Allah yana kallon baya barci kuma baya gyangyadi, indai bata da hakkin ki, zaki ga yadda

Ubangiji zai yi dake ba dai kince zaki shiga hurumin Ubangiji ba, maza jeki Hafsat daga yau ba zan kuma tsanarta ba, ina sonta kuma zan zauna da ita a haka." Ta kai kashen Maganar ta da kuka, juyawa tai ta bar gurin, nikam wanke kayan da muka b'ata nayi sannan na juya tare da kallon Aunty Safiyya da tayiwa Umma sallama.

Tana share kwalla, an tambaye ta ba'asi taki magana dan dole suka zuba mata ido, har ta isa inda motar ta yake ta bude zata shiga juyawa tayi tana kallona sannan ta yafito ni.

Ajiye kayan nayi na nufi gurinta, shiga motar tayi, nima na shiga.
"Zaman me kike a gidan Ya Binta?"
"Nan ne yafi min kwanciyar hankali" na bata amsa,
"Kin karb'o sakamakon N.C.E d'inki?"
"Eh na amsa tun bayan na haihu." Na fada,
"Ko zaki fara koyarwa a makarantar da Abban Ilham ya buɗe?"
Kura mata ido nayi, cikin wani irin yanayi sannan na sake murmushi nace mata.
"Wanda ya ajiye ni ya ja min layi da goggaya kafaduna da wasu kartin. Idan na kuma fita da linzamin auren shi wich mean ban san darajar auren bane.

Aunty Soffy duk bayan kwana goma ana kawo min kudin balance na keke napep, har Mutane biyar kuma suna kawo min duk sha shida kowani mutum daya, ganin haka zai takurani na basu account dina ta can suke tura min, Maude bai tafi ya barni da wahalar auren shi ba, ya ajiye min abinda zai yi bukata dashi, sannan kuma kin san akwai takardun gidan bayan dogon gida, akwai gidan kajin shi da suke zango, daya na yalwa Aunty kudin turo min suke, duk abinda suka kashe suna lissafi da ya Muttaka, kawai ina kwance kudi ke shigo min sai na kara da rashin godiyar Ubangiji, haka ma ya ishe ni banyi karatu dan nayi aiki ba, nayi ne dan amfanin kaina da yarana nagode da taimakon da zaki min."

Rike hannuna tayi, sannan tace min.
"Kina nufin Yanzun kina son shi ne?"
Dariya tasani har ina kallonta, na kuma kallonta sannan na juyar da kaina ina matsa hannuna tare da tuno wani lokacin da yake tambayana.
"Wai na tambaye ki, me yasa baki kaunata?"
Kallon shi nayi irin ga sha-sha-sha, na fashe da dariya.
"Ni? Allah ya yaye min tsakanina da namiji kudin aljuhun shi!"
"Khadijah kina sona fa"
"Ni ce nake sonka? Lallai kayi mafarki idan ka farka ta wanke idanunka."
"Toh idan babu so, me yasa kike rikice min, har kike biyo Ni shagona? Me yasa idan nayi maganar Hajjo ranki ke b'aci kiyi fushi, karki manta juya ce min kika yi ana cutar ki, ita da nake kwana da ita ke kinyi fushi ne, Khadijah naga soyayyata a kwayar idanun ki, kuma na gamsu da.."
"Don Allah ka ka daina gaya min haka ni wallahi bana sonka tab'jam nice zanyi kishin ka ma? Ni? Toh naji bani takardana na bar maka shagonka!"
"Son da kike min ne ya hana ki tab'a lafiyar cikin jikinki?"
Kallon yadda ya had'ata da bango yana dauke da ita, asalima niman hanyar arcewa duniyar sama yake, ita kuma da bata da wayo ta sake.

"Ina miki magana kina murmushi ke daya" juyawa tayi fuskarta dauke da murmushin jin dadi,
"Am in love! Ina son shi! Mahaukaciyar so, na haukace akan son!"
"Amma ai ya miki girma Anum?"
Zaro idanu waje tayi tare da rike bakinta.
"Kan Uba! Aliyuna ne yayi min girma? Toh shekarun CM 51, Aliyu kuma 48, waye babba a cikin su? Ke nifa ina son abuna haka ko da kuwa ya tsufa tukuf ne balle

kuma mutumin da yasan hakkin mace, Toh bari na gaya miki wani abun da baki sani ba.

Lokacin da nake haukar gidan Ibrahim, gani nake dudduniya babu wanda ya kai shi kula da mace, sannan duk cikin mazajen da na aura shine me dan dama dama, sai Salmanu..sune ma zan iya cewa na auri yan dama dama.

Amma maude, a daren farko na fahimci sunan shi Asadullah ba banza aka kira shi da Zakin Allah ba, da akwai wani baiwa na musamman kingane ai!"

Kai mata duka Aunty Safiyya tayi tana rike bakinta tace.
"Anum haka kika zama, dama ina miki kallon Ustaziya."

"Hmm! Tab'jam Maude ya mai dani haka, idan ma ina da shi toh bai ta shi ba, sai bayan na hadu da Maude a karo na biyu ya fito min da asalima, Aunty Soffy zan koma ki gaida su Ilham." Ta bude kofar zata fita.
"Mrs Me shayi!"
Murmushi tayi sannan ta juya tace mata.
"Na'am!"

"Allah ya dawo miki da shi duk inda yake!"
"Amin Ya Allah, Nagode sosai!"
Ta fita daga motar ta nufi gurin Umma tana goge fuskarta, zama tayi suka shiga hira tare da tattaunawa, isowar CM Ibrahim ya sanya tayi shiru, tare da manta zancen gaiswa yayi da Umma sannan ya kalli Anum.
"Maman twins yaushe zaki zo duba su?"
"Bani da lokacin zuwa, nasan su Ya Binta zasu je." Idan akwai macen da ya tab'a haduwa da ita me aji toh Anum ce. Kome nata tana yin shine irin na wayayyun mata.
"Zamu fitar da Hishmah London ne!"
Kamar abin bai dame ta ba, ta share shi tana latsa wayarta, kurawa yan yatsunta ido yayi, wanda suke dauke da jan lalle.
Anum itace farin cikin shi, Amma Wancan bagidajen ya zarga mata igiyar auren shi ya fece abin shi, da yanzun suna zaune da yaran su.

"Alhaji Ibrahim, ciwon ta ya tashi ne." Kafin ya bada amsa tace mata.
"Umma ai tunda kika ji haka, an nakasa min yara ne,.kuma Ni da Ibrahim nace mishi ba zan bar musu yarana ba, yayi ruwa yayi tsaki ya sani na bar mishi, yaran yau ya barwa wacce bata bar Uwar da ta haifeta ba, balle y'ay'an kishiya.

Umma banje asibitin ba, amma na rantse da Allah, Abidah ta gama dani, domin ina da labarin irin uƙubar da take basu."

Wato idan kaga yadda Anum take fada kamar zata daki CM, sai ka zata D'anta ne, ita kanta Umma ta kasa magana domin da ya gaya mata irin abinda ya sami Hishmah. Mik'ewa Anum tayi tare da barin gurin.
"Gaskiya Labarin Nan bai min dadi ba, shi yasa naki dakatar da ita, Anum bata jin magana amma haka bai zama dole nuna hana ta fadar abinda yake ranta ba, hanata magana shine tashin hankalin mu, don Allah kayi ƙoƙarin kawo mata yaran."

Kasa yayi da kanshi tare da kallon kasa.
"Da ina son zamu tafi London da ita ne, sabida itace UWARSU zata fi basu kulawar da ta dace dasu, amma ki nazarci magabata da budaddiyar zuciya"

Shiru tayi na wani lokaci, kafin tace mishi.

"Zan yi magana da yayunta maza da mata, duk abinda suka ce zan maka magana, amma ka bani nan da kwana uku."

"Babu damuwa, Insha Allah zamu gama cuku cuku nan da sati daya sai mu tafi."
Ya faɗa tare da mik'ewa yace.
"Bari na duba Maman Anum."

"Toh babu damuwa!"
Yana barin gurin Shukrah tace.
"Umma! Wai ta ina AuntynAnum take haduwa da gayu haka ne? Kiga Kwamishina da kan shi fa, sannan kafin wannan matsayin yana aiki ne da babban bakin kasar nan idan ya gama abinda yake zai koma bakin aikin shi! Sannan na tuna Uncle Salmanu duk da shi din mutumin banza ne amma ya haɗu, ga Alhaji Hamisu Natsira, me shagon gwala-gwalai a Central market."

Dariya Umma tayi sannan tace mata.
"Kaddara kenan! Ita kanta bata tab'a kawo haka a ranta ba, aure aure sai gashi Allah ya jarabce ta dasu din."

"Gaskiya labarin ta, akwai fadakarwa gashi da alamu yau ba zata karasa mana ba, tunda ga Baban su twins yana maganar zata tafi London jinyar yarinya."

"Aikuwa dukkan su babu wanda ya kama kafar Aliyu. Domin ya fisu dacewa da ita, kawai al'amarin ne sai a hankali."

Haka suka ta hiran, fitowar Anum cikin b'acin rai ya sa Umma cewa.
"Allah ga baiwar ka! Ubangiji ka rage mata wannan zafin zuciyar nata,!"
"Amin Umma!" Inji Shukrah,
Tana isowa gurin sai haki take tace.
"Umma bari na koma gida, ba zan kuma zuwa ba Insha Allah."
"Bana son sakarcin banza."

Shiru tayi taki magana, abinda ya faru a cikin asibitin yana yawo a ranta, bata san me ta tsarewa Hafsat ba take tsanarta. Idan dan akan kayan ta da ta rike ne take tunanin zata mata magana ta bata hakkinta ne ita wannan bai dame ta ba.

..... Abinda ya faru lokacin da Hafsah ta shiga cikin ward ɗin, me ta gayawa Mama me ya faru, dan har take gaya mata babbar Yayar su tabi Aminu zuwa gida, zata huta. Toh lokacin da Anum ta shiga ne taga mood din Maman su ya sauya, dan haka ta zauna tare da Tambayarta.
"Mama jikin ne?"
Kallon juna suka yi da Hafsat, ta dauke kanta.
"Mama kinyi min shiru."
"Ko nima zaki dake ni ne kamar yadda kika daki Abidah? Kibi mace har gidan mijinta, tayi magana ki dake ta, har sai da ta suma! Anum me yasa kike son kashe ni ne? Idan dan laifin da nayi ne toh don Allah ki yafe min karki kuma zuwa nan inda nake domin ganinki masifa ce, da aurenki kike bin wani namijin."

Bata ce kome tak ba, amma yanayin yadda take sauke ajiyar zuciya zaka Fahimci, tana cikin damuwa da tashin hankali, dan haka ya juya abinta tare da kallon Hafsat murmushi suka sakewa junar su, domin ita burin Hafsat ta tinzira zuciyar Anum suyi abin kunya, ai kowa ya tabbatar da abinda take son su sani.

Ita kuma Abun taki kula Hafsat ne sabida abubuwa guda biyu, na farko suna cikin asibiti ne kuma akwai mutane da yawan da basu son hayaniya, na biyu ita kanta

Mahaifiyar su bata kaunar tashin hankali sabida jininta da yake hawa da sauka, ga ciwon suga da suke hawa da sauka. Wannan shine dalilin da ya hana bata kaftawa Hafsah rashin mutunci ba. Ta fito a fusace, har tana bangaje Ibrahim, shima dai bai wani samu fuska a gurin Mama ba, dan gaisuwar shi alatilas ta amsa mishi.
#Mai_Dambu

Ina Muku tallar sabon Book ɗina Me suna Daula biyu! Wanda zai zo insha Allah nan da wani lokaci! Duk wanda ya samu damar karanta masarautan Jordan toh tabbas zai so ayi tafiyar da shi!□□ Wato dai labarin Safinah da Ashraf! Yau gani ina nan sake zuwa muku da wani labarin da Ya shafi Islamic empires! Kafuwar daular Umayyad da Abbasid! Manyan Asahabbah Manzon Allah (S.A.W) kadan daga cikin abinda ya faru a daular Larabawa! Karku manta kudin shi 200₦ ne! Insha Allah zan sake FREE Pages Soon Soon Soon Insha Allah, karku manta Labarina ba sabo bane, ba kuma gama gari bane! Bani da salo! Amma ina da Chakwakiyya 😝😂 Naki na sauko na malake inda kana buƙatar zama na farko farko a paid grp tab'ani ta wannan Number +234 8130269641! Ba yawan kuɗin nake bukata ba, Dogon zangon a yayinda kowa yake fahimtar alfarma yakewa makarantan shi Ni nasan sune suke min alfarma duk wanda ya sayi book dina koda nera 5₦ ne alfarma yayi min Nagode sosai da alfarman da kuke min tare da soyayyar ku□□
[1/29, 7:33 PM] +234 706 153 2349: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN

Da zai fita ya ajiye mata kudi, kallon shi tayi sannan tace..
"Zo Ibrahim, dauki kudin ka Nagode"
Cike da mamaki yake kallonta, kafin yace.
"Mama ni kamar Aminu nake, don Allah ki mishi karamar Ihsan da nayi miki ba dan ni ba dan Allah."

"Allah Yasaka da Alkhairi, mun gode" inji Hafsat,
Haka yayi musu sallama ya bar asibitin, koda ya fito ya samu Anum bata nan.
"Uwar zuciya, sai ki cigaba da saka damuwar Hafsah a ranki, domin ba hankali ne da ita ba, tayi haka ne dan ta cusguna miki, kuma da baki bata amsa ba, shine abinda kika yi da zanyi alfahari da ke."

"Ya Usman, sharri ta kulla min fa!"
"Anumullah! Sunanki Kyautar Allah ce, ya malam ya kiraki da haka ne bayan yayi miki huduba da Khadijah, kin san me yasa ya kiraki da kyautar Allah, dan ke albarka ce lokacin da ya same ki, aka bashi babban sakataren kwamitin noma ta jahar Bauchi,malam ya samu kyaututtukan da matsayi dukda lokacin ya kusan ajiye aiki, amma suka rike shi ya kuma kara zama da ma'aikatan manoma na jahar Bauchi.

Anum, ke soyayyar malam ce, duk wanda zai ji haushin ki zai jine saboda kafin malam yayi kalmar shahadarsa ta karshe kece abinda ya fara magana a kai, yace zai tafi yabarki cikin damuwa da kuncin amma zai yi fatan kafofin Alkhairi da Nasara su bude a rayuwarki, zai miki fatan duk inda kika shiga ki zama kyauta ga Al'umma, Anum karki kuma kuka dan Hafsat tayi wani abu, zuba mata ido ga fili ga me doki sai suyi sukuwar su."

Goge kwallar tayi sannan ta kalli Aunty Binta.
"Na rasa gane kan Hafsat? Ban san me na tare mata ba, amma idan ta ganni kamar zata kashe ni, na bar.mata Maman sai ta cinye ta "

"Kash! Uwar mahaukata, waye ya tab'a barwa wani uwar shi? Kyaleta kamar yadda Usman ya fada Allah zai saka miki!"

Haka suka yi ta hira har Usman yayi musu sallama, da zai tafi yake gaya mata.
"Ya kamata ki duba Isma'il dasu Hishmah, shima bai. Da lafiya amma anyi na kai shi asibiti. Suma d'azun munje da su Ya Abubakar, mun duba su."

"INSHA Allah zuwa gobe zan je na duba su." Ta faɗa a sanyayye, duk da bata ga yaran ba, amma tana cikin tashin hankali.
Ace kowani lokaci yaranta sune fadawa matsalar rayuwa, Isma'il tasan ba mamaki canjin yanayi ne, da na ruwa, Amma Hishmah da take fama da cutar sikila wanda nata yayi tsanani ba kamar na Hisham, ba na shi bai kai nata tsanani ba.

-Xoxo bayan taci shegen duka da yasata suma, tana farkawa taga Beauty da Maman ta.
"Ke Abidah karo kika yi da mota haka?"inji Mahaifiyarta wato Adama wacce ta sami promotion daga Dama zuwa Hajiya tare da wasu beautiful hakoran gold dinta..

Tsaki Xoxo tayi tare da juya aya kai.
"Da jirgin sama nayi karo ba da mota ba, wancan yar Islam ce tayi min wannan dukar yar kutumar abukazan uban"

"Wa??" Suka tambaye ta bakin su a haɗe. Tsaki tayi tare da kauda kanta wasu kwallar bakin ciki suna sauko mata, musamman da taji fuskarta yayi mata nauyi!
"Don Allah ku bani madubi naga abinda Tsinanniyar yarinyar nan tayi min kai Allah ya kwashewa Anum albarka."

Ta faɗa tare da sake kuka, aikuwa jaka Beauty ta bude tare da dauko madubin kayan kwalliyarta ta mika mata, a hankali ta kai fuskarta tare da kallon kanta a madubin. Ganin yadda bakinta yayi kamar anyi babbaken fatar saniya. Ga bakinta da yayi kamar undurusun saniya,(😳)haka ta kalli kanta ta kuma fashe da kuka.

"Wallahi sai na kashe Anum!"
"Kiyi fatan Allah ya bawa Hishmah lafiya, domin Wallahi abinda Anum zata miki idan yarta ta mutu Allah kadai ya sani, ai cewa kika yi zaki musu wanka tun karfe shida na safe, kika tashe su.

Amma dake ke tsinanniya ce, laananninya kika kama yaran da basu ji kina azabtar dasu, bayan kin sani na mishi iyaka da Mahaifiyar su, Xoxo ke bakar kaddara ce, kin shigo rayuwar mu kin lalata min farin cikin d'ana, meye ribarki Alhamdulillahi Ibrahim ya san abinda kika aikata, kamar yadda kika zo min na shiga niman hanyar da zai aureki, toh gashi nan kije Allah ya baki sa'a amma ki sani matukar Hishmah ta sami matsala idan Anum bata daure ki ba, wallahi sai yadda karfina ya kare." Inji Hajiya Turai, ta fadi haka tare da ajiye mata Zungurerren takardan sakin da CM yayi mata.

Fashewa tayi da dariya, tace.
"Wallahi Ni annoba ce, da zarar na bayyana sai na kararr da kome, ki saka a ranki sai na ga bayanku har Anum din."

"Koda yake tunda kika zama rijiyar kowa! Uban waye ba zaki ja dashi ba, amma baki sani ba. Rayuwar Hishmah shi zaki fara fatan ya samu, idan ba haka ba hmm!" Ta juya ta fita.

"Bestie! Ina ganin d'aga hankali ba naki bane fa! Rayuwar yar Anum shine akan gaba, matukar wani abu ya same ta bazata yarda ba, dan Anum ba karamar mahaukaciya bace tunda ta iya dukarki babu abinda zata iya ba!"
Ajiyar zuciya ta sauke tare da, dauke kanta,

"Idan na tashi cin Ubanta sai ta manta da hanyar da zata bi," ta faɗa cikin kuri.
"Gaskiya kan shi yasa da ta tashi cin Ubanki ta sauya miki halittar da Allah yayi miki wannan shine karo na uku da Anum take jibgarki, amma kinyi asara duniya da lahira indai Anum ta zame miki dodo, dubeki fa, Anum tana dukarki kamar jaka yau nayi haihuwar asara!"

"Adama wallahi ki bar gaya min magana domin zan baki mamaki." Ta faɗa cikin fushi da kuka.
"Tafi can! Sakarya kawai." Aikuwa ranta ya b'aci ta sauko cikin rashin sanin abinda zata yi ta bangaje uwar ta fadi can kanta ya bugu da drower karfen da yake dakin, kara ta saka tare da shure shure.

"Beauty! Zaki amshi ragamar wannan al'amarin." Ta faɗa tana murmushi,.ihu Ta fasa, tare da niman dauki, koda Nurse suka zo .
Ido da ido Xoxo ta makalawa Beauty kazafin itace ta ture mata Uwa, baki sake Beauty take kallon ta,'.
"Karki damu zan dawo idan na gama da Anum tunda kuka sake min gwiwata, zan nuna muku yadda ake farauta."

"Abinda muka yiwa Anum shi yau kika min? Kamar yadda muka hada kai aka cutar da Anum shine kika cuce ni? Dama Anum ta gaya min, indai kece zaki cuci kowa sabida bukatar kanki, kin lalata min rayuwa? Yau kin jefa Ni a wani hali."

"Wayyo Allah na ta kashe min Uwa! Don Allah ku tafi da ita, wallahi ta kashe min Uwa ce." Aka suka fita da Beauty da ta kasa magana, a hankali ta koma kan Adama, ta kalle ta, tare da kallon likitan.
"Da fatan bata mutu ba?" Ta tambaya cikin kuka,
"Tana raye bata mutu ba, amma kuma zai yi wuya ta tashi domin gefenta ya shanye."

Wani ajiyar zuciya ta sauke sannan ta sake kuka, tana kallon uwar, a ranta tana fadin..
Na gama da ku, saura wancan yar iskar na saka a lalata min fuskarta

***
Tunda suka koma gida bata iya fahimtar kome ba, asalima d'akin ta koma ta zauna shiru. Cikin tsananin zafin abinda Hafsat tayi mata.
"Shin ko tana kallona a matsayin mazinaciya ne? Tunda ban taba tambayar wani ya bani wani abu ba? Kai haba dai! Toh kallon me take min? Da zata min Sharri, toh meye nayi mata?" Ga baki daya ta gama takura kanta da tunani har lokacin tafiyar Aunty Binta aiki yayi.

Wajen karfe shida na yamma, su Badi'ah da fa'iza, gabaki daya sun gama kaguwa suji yadda zata kaya tsakanin me shayi da Anum, malam da Maman Aminu. Ana sallar isha. Sai gasu duuuu. Kallon su tayi duk da bata cikin nutsuwa gyara zama tayi sanan tace musu.
"Yau kunzo da wuri, bari muga ko zan iya baku labarin kafin nan da sha biyu, dan gaskiya zuciyata babu dad'i."

-Back to story-

"Wallahi ba zata auri Me shayi ba, mara asali da dangi sannan me yaci me ya bata taci,"
"Hauwa! Don Allah ki bari ya tafi sai muyi maganar Arziki!"

"Eh lallai kan maganar Arziki, Mariyah na jima ina kallonki, na jima da fahimtar baki kaunar Anum, duk yarana a wulakance aka aurar dasu, baki wato sun huta nawa kuma su kare a galgalance,, ga sakarya sauna sha-sha-sha me kayan ashsha, toh wallahi baki isa ba, baku isa ba, yarinya da nake burin ta auri maitamakin gwamna ko d'an Gwamna sai a ta kare da wani me shayi, dan cira."

"Malam Maude! Tashi ka tafi zan sami shugaban ku nan, zan"
"Baka isa ba!" Inji Maman Aminu, duk yadda malam yaso dauke kanshi sai da ta tinzira shi ya mare ta, a gaban Maude sosai abin ya d'aga hankalin Umma, take ta sallami Maude, sannan ta kalli Malam.
" A gaban mijin da zai auri Yarka kuke abin kunya?"
"Anamimiya munafuka,, Insha Allah sai Kinga abinda kika mana akan jikokinki"
Murmushi Umma tayi sannan ta dauke kanta, tare da d'aga Anum da take zare idanu.
"Sake min Y'ata, algunguma. Allah ya isa tsakanina da ke, kuma in Allah ya yarda ba zaki tab'a ganin dai dai ba."

Idan kuka ga yadda umma take murmushi, sai ka rantse da Allah maganar Maman Aminu baya mata ciwo.
Mik'ewa malam yayi zai shiga dakin shi yace.
"Mariyah na saki Hauwa'u! Ta koma garin su ta bar min Y'ata nayi iko da ita."

"Hhhhh! Burinki ya cika abinda kike muradi ya tabbata, kin jima kina niman hanyar da malam zai sake ni bai sake ni ba, dake nafi karfin ki, shine kika zauna kika raba min hankalin mijina, toh sauki kwanta ki mikar da kafarki"

Ina irin ka mannawa mutum hauka, haka Umma ta sata keyar Anum dakin ta, ta rufe dan malam hana Anum bin Mamanta d'akinta ko ta koma d'akinta. A hankali Anum ta fashe da kuka.

Duk yadda aka so barci cikin salama, Maman Aminu taki barin su. Karshe a daren Malam ya kira Aminu ya fitar mishi da ita.
Dakyar da shudin goshi Anum ta iya barci, Umma kan kasa barci tayi tana sallah, tare da gayawa Allah kukanta akan abinda Maman Aminu tayi mata, wajen karfe biyu na dare ta fashe da kuka, zunzurutun zagin da Maman Aminu tayi mata sai lokacin yake dukarta, sai da ta dauki Alqur'ani domin umma tana da ilimin addini da na boko ba laifi, kuma wani abin burgewa tasan darajar kalaman bakinta. Shi yasa bata tofa kome ba da Maman Aminu ta gaya mata.
** Banda zuciyarta me kyau ne da safe haka ta tashi Anum tayi musu aiki amma yarinyan nan taki ko d'aga tsintsiya, da Umma tayi mata magana ta saka mata kuka. Murmushi tayi ta kama aikin gidanta, har ta gama na karyawa ta daura na rana, tana kallon Anum ta shirya ta fita daga gidan.

Bakin shagon Maude ta isa, ta shiga mishi b'arnan kunsan ta'asa, toh haka tayi mishi mutumin nan bai d'aga ido ya kalleta ba, yana zaune yayi Crossing leg din shi. Har ta gama fasa kwai tass ta ture table din na kayan tea din..
"How Are You da zaka ce zaka aure ni, matsiyaci da kai, wallahi idan baka rabu da ni ba, sai na saka ka kayi asarar kome naka, ban da rashin hankali irin..."

Wani irin wawan duka aka kaiwa keyarta sai da takifa. Dukarta yake tare da kwallo da ita, ran shi ya kai makura gurin.

"Kyaleta Rulwanu! Yaranta ke damunta, wata rana ba zata yi ba, aure kuwa tunda malam ya bani bar dukar min Mata na."

Ai kuwa ta fasa ihu, tana faɗin.
"Rulwanu kaci abu kazan Ubanka shege Azzalumin mutum, Kai kuma bakin algungumi sai na wulakanta aurenka wallahi sai na lalata maka farin cikin ka."

Asalin rashin mutunci da rashin kunya Anum take musu, sai da Maude yazo ya dauketa cak dan ya gaji da abin kunyar da take janyowa kanta.... Aure Babu fashi yar gatar gatan uwa! Wani zai gurji kwaila, Yarinya zaki tafi millions cloudy 😜
(A gaskiya zan shiga dunkule hannun tunda Na sauko daga sama! Karku manta ina tallar book dina me sunan Daula biyu 200₦ ta bank ko katin mtn)
#Mai_Dambuje😂
[1/30, 1:46 PM] +227 98 70 95 87: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN DA D'AYA.

TEAM Maude kuke zan makale fa

Cikin gidan ya nufa da ita bai direta a ko ina ba sai a tsakar gidan.
"Anum har yanzun ina kaunarki, shi yasa ba zan miki kome ba da b'arnan da kika min. Allah ya bamu yara kyawawa masu.."

Cak yayi shiru kamar wanda aka hana karasa abinda zai ce, ya kura mata ido. Zuciyarshi tana tuna mishi wani abu akan karan kanshi.
Karka manta waye kai? Sannan shekaru sha shida matan ka basu tab'a koda b'atar wata ba, adalci ne ka auri yarinya karama ka amfana da kuruciyarta? Kasan baka Haihuwa, sannan kuma ka nace zaka auri yarinya karama wacce nan gaba zata so haihuwa itama.

Tsintar kanshi yayi da juya tare da barin gidan, jikin shi yayi matukar sanyi, lokacin da ya koma shagon shi ya samu ila da jijjiya suna kwashe kayan sai fada suke, Rulwanu yana basu hakuri, murmushi yayi sannan ya tasawa Ila abinda yake damun shi kallon shi yayi sannan yace mishi.
"Amma ai ba hujja bane kace ba zaka aure ta ba, dan kana da matsala ta rayuwa, sannan kuma wannan haukar da take babu abinda zai bada sai sakamakon aurenta, wallahi Yallabai sai ka auri Yarinyar nan, ka nuna mata iya ikonka da karfin ka."

"Toh Allah yasa mu dace." Ya faɗa a sanyayye, yana kallon ta'asar da Anum tayi mishi.
-- A can gidan Aminu kuwa Mama ta zagi Umma ta tsinewa Umma,.tayi fadar tayi masifar karshe ta fashe da kuka, Yaran ta baki daya sun taru, suka yi ta bata hakuri amma bai hanata kuka ba.

Da ciwo ace aurenku a shekaru kusan arba'in da wani abu ka wayi gari ace mijin da kuka zauna dashi ya sake ka.

... Hafsat da Safiya suka fara zuwa bakin kura, suka sami Anum tana kuka, Umma ta sakata a gaba tana mata nasiha.
"Rayuwar duniya da kike gani hmm sauki ne da ita, idan ka nemi sauki amma idan kace zaka ci da zuci ba zaka kai labari ba.

Khadijah duk abinda kika ga ya sami bawa mukaddari ne, duk abinda ya tsara miki me kyau ne, Ni nasan kina son Maude, amma wasu dalilai naki yasa kina ganin baki dace da me karamin sana'a.

Anum masu manyan gidaje da manyan motocin nan, basu kai masu kananun karfi tattalin mace ba, shi me katon gida da katon mota yana ganin su kika biyo, dan haka yayi miki Alfarmar ki zauna da shi, kuma duk abinda yayi miki haka zaki hakura dashi ba tare da kin fadawa duniya ba.

Sannan baki da ikon nuna damuwarki akan shi, tunda rana tsaka kika aure shi da yatsunsa biyar kika same shi, shi kuma wancan shi zai zauna dake ne sabida kinyi mishi alfarman haka, kuma koda yaushe yana cikin niman hanyar da zai kyautatta miki,

Zai yi wuya ya cusguna miki da gayya, kullum kokari yake ya saya miki farin ciki kida kuwa iya abinda yake gare shi kenan.

Idan zaki shekara dari dashi kullum cikin ririta ki yake, sannan kullum tunanin shi taya zai inganta duniyar ku. Anum mijin mareniya kika samu, yayi wasa da samun shi akanki, kaf unguwar nan zuba ido aka yi ana jiran malam ya baki wani mijin ayi mishi dariya saboda an gaya mishi cewa ke ba matar talaka bace.

Kin san saunawa ana tare malam ana ce mishi kar ya nuna halin butulci ga wanda ya bautawa yar shi? Kin san yawan lokutan da aka bi ana gayawa Aminu magana akan ki.
"Kanwarku ta zama babban yarinya shi yasa take wulakanta me shayin kofar gidan ku, koda yake shima yayi karambani, waye ya aike shi auren matar da Sanata zai aura ko ministа." Ire-iren waɗannan kalaman da ake gaya miki, Anum Ni a nawa gani na, alkhairi ne ya kawo Maude rayuwarki, da babu Alkhairi ba zai nace ya aure ki ba. Ban san iya abinda zan gaya miki ba. Karki bijirewa mahaifinki, wallahi matukar kika yi biyayya Allah kaf yan uwa kin sai kin fisu daraja da farin ciki. Kiyi hakuri ki mishi biyayya. Allah zai baki abinda kika rasa, Anum maude nagartaccen Mutum ne. Yana da addini, kuma Manzon Allah yace idan mutumin kirki yazo niman auren dayan ku, kuka hana shi bayan kunsan mutumin kirki ne.

Allah sai ya jarabce ku da damuwa da tashin hankali, kina son jefa Mahaifinki cikin tashin hankali ne."
"Umma kifa bana son shi ne! Don Allah ki cewa Malam ya hakura da auren mutuwa zanyi."

Dariya Umma tayi lokacin da su Hafsah suka shigo a ranta so take tayiwa Umma rashin kunya dan wai ita ta saka malam ya saki uwar su, kallo daya umma tayi mata take ta shiga hankalinta, kyale su Umma tayi bata kuma mata magana ba, har suka gama kananun rashin kunyar su, a daki.

Lokacin da suka tafi Anum kasa fitowa tayi dan sun zugata, tayiwa Rashin kunya, amma ta kasa, ba zata iya ba. Sai tayi ta kuka a dakin. Sosai yadda take kukan har Umma tana jiyota. A cikin kananun maganar da Hafsat tayi akwai wanda ya tab'a ran Umma.

"Ko yau malam ya fadi ya mutu kowa yasan uwar mu ce da gidan nan, dan haka juya mishi hankali da aka yi Allah sai ya saka mata." Wani irin murmushi take, tare da kallon Anum bayan ta d'aga labulen dakin tana zaune ta cusa kanta tsakanin cinyoyin ta. Hannunta ta zagaye kafarta dashi. Zama tayi sannan ta janyota jikinta.

"Kiyi hakuri Umma! Ni ba zan iya miki rashin kirki ba."

Hawayen da take kokarin binne shine ya zuba akan dokin wuyar Anum, innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, zo kuga yadda ta birkice tana kuka tare da rike hannun Umma.
"Don Allah Karki zubda min hawaye, Umma ki rufa min asiri wallahi zan auri Maude, UMMA na ki bar kuka. Ba zan kuma ba, don Allah ko daina kuka, Umma daga yau ba zan kuma kuka ba. Na shiga uku na lalace Umma tana kuka aka ina."

Rungume ta tayi a jikinta, tana shafa bayanta.
"Kince zaki auri Maude ba dole aka miki ba?" Cikin kuka tace.
"Naji zan aure shi ba dole aka min ba."
"Anum idan kika san baki san shi yau Insha Allah zanyiwa malam magana."

"Umma Ni mallakar ki ce, ba zan tsallake bukatar ki ba" shafa kanta tayi, sannan tace mata.
"Daga yau kar na yarda na kuma jin wani ya zugaki akan Maude!"
Cikin wani irin shashekar kuka tayi ta gyada mata kai tana kukan.
"Wannan kukan yana fada min kamar dole aka miki?"
"A'a Umma!"
Haka ta kuma kara mata da nasiha.
"Duk wanda yayi wa iyayen shi biyayya da ɗa'a Allah ba zai tab'a wulakanta shi ba, Allah yana girmama al'amarin shi..duk wanda ya sab'awa iyayen shi. Allah yana fushi da fushin da iyayen shi, kuma sai ya wulankata shi a duniya, ya kuma je lahira. Anum kin sami mijin da yake kaunarki.

Tunda ya iya baki kyautar shaddar dubu hamsin, meye ba zaki baki ba, Anum maude ba zai tab'a wulakanta ki ba, wallahi zai girmama al'amarin ki. Anum ki nunawa duniya cewa, ba lallai me kudi bane yake samun kyakyawar mace ba, talaka irin maude yayi deserved dinki, sannan ki tuna rayuwar ki da kika yi waye zai iya jure zama dake ba tare da anyi uwar watsi dake ba. Wata rana zaki nazarci abinda nake son ki fahimta kuma bana son lokacin kome ya kure miki."

Duk yadda Umma take kokarin mamaye zuciyar Anum tayiwa Mahaifinta biyayya sai da su Hafsah suka hanata, Yaran Umma kan iyaka tayi musu, tare da gargad'in kar taji labarin wani ya Kuskura ya ce wani abu akan Anum da Mahaifin su indai ba zasu bata shawara tayi biyayya ba.

A bangaren Maude yan uwan su yan Nijar da kuma shugaban su, sun zo sun nima mishi auren Anum, malam ya karb'e su hannu bibbiyu, tare da mutumtaka, inda suka kawo har da sadakinta, nera dubu saba'in da takwas. Malam kan talatin ya dauka ya maida musu arba'in da takwas,.yace musu.
"Kowa yasa halin yar da zan baka, idan na amshi wannan kudin haka yana nufin na rufe ka ne, dan haka idan ta cancanci kari zaka iya bata."

Haka suka dawo da sauran kudin. Bayan an saka ranar nan da wata uku, sakamakon zai yi yan gyare-gyaren wuraren da zasu zauna.

***
"Anum me kike nufi? Ni zaki tozarta? Ki amince da auren matsiyaci nan sabida Mariyah!" Kashe wayar tayi tare da fashewa da kuka.

Umma da take bakin kofar, rike da abinci ta shigo dakin a hankali ta fara bata tana ci, tana kuka.

"Umma wai na gudu zamu tafi Edda!" Ta faɗa tana amsar abincin dan ita kanta ta manta rabon taci abinci da hannunta, wanka kawai da alola da saka kaya take,, sai maganin sanyin da Umma take ta bata.

Dan tace ita ba zata bata maganin mata ba, zata dai gyara mata jikinta yadda zai zauna cikin dumi.

Tana gama bata abinci, ta dauko zunguro, ta saka lalle a cikin shi ta saka mata. "Duk wanda zai baki shawaran ki gudu, zai b'ata miki martabar ki ne, kuma zai lalata miki alaƙar ki da Mahaifinki ne, Malam bai zab'a miki maude dan ya cutar dake ba, yaga yafi dacewa dake ne."

.tana gama kunsa mata lallen ta fita, wato irin kulawar gargajiya da ake yi zamanin da Umma takewa Anum, bayan awa biyu. Ta cire mata lallen sannan ta mika mata dafaffen madara, dama tayuwa malam magana yana kawo mata d'anyen madaran saniya daga gidan gona, karamin galan din manja. Shi take sakawa a randan kasa, idan ta diba ta faɗa, sauran kuma tana zuba kayan kamshi kanumfari, tazargaje, kurku lalle, ta kaiwa Anum ban daki tayi wanka dashi. Idan tafito kuma akwai asalin dafaffen siga da madaran turare, tana goge mata jikinta,. Tana gamawa zata kwab'a kwai da nesfe, ta zuba garin kurku a cikin shi, sannan ta goge mata jikin ta dashi, tas.

Takan so Anum tayi kuka, amma dake tana da taurin kai, sai dai kaga tana ajiyar zuciya, idan umma taga haka takan ce mata.
"Autar Malam!" Wannan sunan sakata kuka yake tuni zata sake kuka.

Ire-iren waɗannan abubuwan yana matukar damun Umma, dan haka ta sami Malam ya dawo da Maman Aminu.
"Ki fita ki bani guri bana son damuwa"

"Babu inda zani sai ka gaya min meye nufinka akan Maman Aminu? Kasa duniya tana zargina akan na rabata da uban Yaran ta, Malam ka rufa min asiri ka dawo da Maman Aminu, domin wallahi nima ina dab da barin gidan nan!" Ganin yadda take fada har da kuka yasa shi juya mata baya.

Idan ya cire munannan halayyar maman Aminu mace ce, me matukar biyayya da sanin darajar aurenta kawai Abu daya yake damunta son kanta da rashin adalci yasa shi sake ta daya. Kuma yasan idan ya dawo da ita ba zata bar Anum tayi mishi biyayya ba, zata cigaba da zugata ne. Don haka yayi mirsisi ya dauke kanshi daga batun komen Maman Aminu.

Ita kuma Umma sai da ya kai karar ta, gurin Usman da Aminu, tare da Aunty Binta. Saka umma suka yi a gaba suka kallonta kowa dariya yake an rasa wanda zai mata, magana. Dakyar Usman yace.
"Umma! Idan kika tafi kika bar malam waye zai tsaya mishi? Duk halin da yake ciki yasan kina tare dashi ne? Don Allah Umma ki duba Alamarin shi karki ce kema zaki juya mishi baya!"

"Umma! Idan muka yi yaji ke me zaki ce mana, Umma a halin yanzun ina niman shekaru arba'in, ban tab'a yaji ba sabida Ni din tarbiyyar ki ce, toh yau wacce ta bani tarbiyya tayi yaji Ni me zanyi gaba, ina budurwa sa'ar Anum, yau gashi kakar ta zata yi yaji." Inji Aunty Binta,

"Umma kiyi hakuri! Don Allah Ni dai ban san me ya faru ba, amma tabbas nasan ana b'ata miki rai. Don Allah kiyi hakuri! Insha kome zai"

Ba zaku sami na dare ba, Yau weekend ne lokacin iyalina ne da nawa kaina dan haka karku saka rai zaku sami na dare!
#Mai_Dambuje
[1/31, 10:55 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu
Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN DA BIYU

*_Salon d'an magori nake yawan amfani dashi a labaruna shi yasa da yawan mutane suke ganin kamar ba Nice nake rubutawa ba! Ku dunkule hannun toh a haura katanga dan ta rushe daku babu ruwana_*

"Babu kome Al Amin, ya wuce wallahi kawai ya dawo da matar shi, shine gaskiyar magana..idan kuma bai dawo da ita ba, zan bar mishi gidan shi. Na rantse da Allah ba zanyi kaffara ba." Daga haka ta wuce dakin ta, ta bar su a falon.

Allah sarki, idan ka ga yadda suke zauna sai sun baka tausayi, domin kuwa yanayin su ya nuna a tsorace suke da matakin da zata dauka basu san me zasu cewa Malam ba,dan haka suka nufi unguwar mahaukata akwai yayan Umma a can, a bayan dutsen unguwar, suka dame shi da maganar, shiru yayi sannan yace musu.
"Akwai abinda ake mata ne? Indai babu toh tabbas zata iya abinda tace, amma kuce mata inji ni Yahya nace ta zauna a d'akinta idan kuma bata mutuntani ba Allah ya bata sa'a."

Lokacin da suka dawo aka rasa wanda zai mata magana, sai zare ido suke tare da kallon juna, kafin Usman yayi kundum balar mata magana.
"Wato kun kai karana? Naji kun kyauta min Allah yayi muku albarka."
Daga haka ta juya ta koma cikin Kitchen tana hada tuwon dare.
"Anum!"
"Me zata muku? Bana son tana shan iska mara dalili ne, kuma nasan zata iya fitowa kamar gayan borodi ne."

Tashi Aunty Binta tayi tare da shiga dakin ta d'aga labulen dakin.
"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun! Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, Jama'a Ku taimake ni Ya Allah." A rud'e suka shigo dakin tare da sake salati.
"Hasbunallahu wa ni'imal wakeel
La'ilaha illa anta subhanaka innee kuntu minazzalimin" jin Umma, kallon Anum tayi ta ke kwance dafara yana fitowa daga bakinta. Tace,
"Usman dauko min mangyada a d'akina"
Da sauri ya juya, sai gashi da mangyadan "bude bakinta Binta, juye mata shi!

"Aminu ka nufi waje yanzun ka amso min madaran ruwa!" Kamar zai kifa haka ya fita, can sai gashi da tin din milk yana zuwa aka juye mata, aikuwa ta fara amai.
"Goge mata jikinta, ku nufi asibiti da ita," da sauri suka nufi da ita waje, kallon su Maude yayi tare da tambayar su.
"Lafiya?"
"Faduwa tayi ta buge kanta!" Inji Anunty Binta, haka suka sata a motar Usman aka nufi babban asibiti da ita.

Tunda aka shiga da ita, kasancewar sun san Aunty Binta basu sha wahala ba, aka fara kokarin mata karin ruwa, tare da tambayar abinda ya faru, wa likitan kawai suka wa bayani, suka yi shiru.

Duk yadda suka so Anum ta farka ranar, abin yaci tura domin maganin kwarin da taci yana ƙoƙarin tab'a kayan cikin ta, dan ma umma ta bada taimakon gaggawa. Haka suka gama kokarin su akanta. Har dare bata farka ba.

A gida kuwa, maude ne ya shiga cikin gidan, ya gaida Umma cikin nutsuwa. Sannan yace mata.
"Ban gamsu da abinda Hajiya Binta tace ba, ko dai akan auren ne?"
"A'a! Ba kai bane! Kawai faduwa tayi kuma."
"Umma, a uwa na dauke ki. Meye akayi da madara? Kenan Khadijah ta zab'i kashe kanta ne sabida aurena?" Ya faɗa a cikin sanyin murya.
"Kayi hakuri! Da abinda zan gaya maka, ka janye niman auren..."

"Wallahi ko mutuwa Anum take ta dawo, ba zan sauya tsarina ba. Ba zan fasa abinda na saka kaina ba, Mariyah kisaka a ranki auren anan dan da sati Uku, da yardan Ubangiji idan anyi ta kashe kanta, ba tasha piya piya sabida auren bane, toh wallahi idan Anum taki auren nan sai dai na zare ta a cikin yarana!"

Duk yadda aka so taushe shi amma fir malam yaki,asalima kara tunzura shi suke, dan haka ya hana Umma itama zuwa asibitin, yace zata dawo ta same shi.

Sannan ya umarci Maude da ya fara shiri babu kama hannun yaro,. Bayan fitar Maude ya dauke kanshi daga Umma da take kallon shi, tana bude bakin ta yace.
"Duk wanda yaga zai iya tsayawa KHADIJAH na yafe mishi ita."

Dan haka ta ja bakinta tayi shiru.
Tunda ta Fahimci ranshi babu dad'i ta kasa sakewa ta koma dakin shi, ta zauna a d'akinta.
Washi gari.
Da safe sai ga yaran d'akin Maman Aminu, suka saka malam a gaba, da cewa.
"Tunda tace bata son shi! Dole sai shine gashi zamu rasata a karon iska, gaskiya Baba Malam ka duba Al'amarin Yarinyar nan fa, karta shiga duniya bamu sani ba!"
"Allah ya bada sa'a, wanda bai zo ba ma duniya tana jiran shi balle wanda yazo ya same ta a cikin idan zata tafi kuyi min magana zan bata guzirin da zata rike a hannunta."

Shiru suka yi tare da jinjina al'amarin malam, duk borin da suka shirya banza yayi dasu, ya gama karyawa ya barsu a gidan bai saurare su ba. Bayan tafiyar shi, Safiya da Hafsat suka yi tawa Umma rashin kunya. Kasa hakuri tayi sannan tace musu.
"Duk wacce ta zage ni sai nasaka Abubakar ya mata shegen duka, kuma naga allon rashin kunyar ku, wallahi kubi duniya a sannu."

Simi simi suka bar gidan, ransu a b'ace, sam sun manta Alkhairin Umma, gani suke kamar itace take kuma rura wutan rikicin su, dan haka suka fito da niyyar warware Maude, kallo daya yayi musu, kawai sai ganin shi suka yi ya cika musu ido, babu hanyar da zasu mishi diban albarka.

Haka suka bar unguwar, suka nufi asibitin, inda suka sami Aunty Amina da Rabi sune a jikin Anum, sai rikici take musu, su kuma suna lallabata, yadda suke circcira bai fahimtar da su Aunty Aminatu ba, dauka suka yi akan auren suke masifa dan suma sunyi nasu, kalmar da Hafsat ta furta yasa Aunty rabi zuba mata ido.
"Wasu ai farin ciki suke dan sun san hankalin wasu a tashe shima malam dake an tofe shi, sai yadda aka yi dashi yasa ya kafe da.."
"Rashin kunyar da kikewa dangin mijinki, zaki mana? Ko ance miki bani da labarin rashin hankalin da kikewa Umma."

"Rabi, kiyi shiru karki tadda mana hankali a cikin asibitin, Allah ya kyautata karshen mu." Inji Aunty Aminatu.

Haka suka bar asibitin ransu babu dad'i, cikin kuka tace.
"Don Allah ku kira min Ummana, don Allah kuce Umma taxo, wallahi ba zan kuma ba."

"Wato kina son ki cigaba da janyowa Umma abin fada shi yasa kika sha piya piya, hankalinki ya tashi yan uwan ki suna zargin Baba ya kore Maman Aminu ne dan Umma, bayan kuma ba haka bane, kema kanki sheda ce, dan haka muma zamu barki a nan, kiyi jinyar ki ke daya a daina zagin mahaifiyar mu."

"Don Allah kuyi hakuri ba zan kuma ba, sako XOXO ta turo min wai idan nasha piya piya aka ga zan mutu a fasa aura min Maude don Allah ki cewa Umma ba da son raina nayi ba." Ga abin duka rashin sanda, dan haka suka share ta,basu mata magana ba.

..... A daren ranar Maude yazo dubata, ya samu jikin da sauki. Tana kwance a jikin Aunty Binta, da take bata ayaba,matar Aminu tana matsa mata kafarta, taki ta kalli inda yake duk maganar da suke mata. Asalima kifa kanta tayi tare da fara barcin karya.

Har ya mike zai fita, ya kalle ta, sai lokacin ta d'ago kanta, ta zuba mishi wani uwar kallon banza, ta dauke kanta, juyawa yayi zai fita suka bangaji juna da wani mutum.
"Sannu don Allah!"
"Yawwa babu kome!" Ya faɗa mishi,
har ya kai zai fita, yaji mutumin yana faɗin.
"Major General Asadullah Haidar Turab!" Cak ya tsaya,
"Hasbunallahu wa ni'imal wakeel! MG Asadullah! Kai ne?"
Juyawa yayi tare da girgiza kan shi yace.
"A'a sunana Maude, ban san wanda kake fada ba."

"Amma wallahi kayi min mugun kama da shi Babban sojan kasar Nijar, wallahi babu abinda ka bar mishi. Allah sarki!"

Bai ce kome ba, ya saka kan shi ya fita daga asibitin. Shi kuma mutumin sai jajjanta zancen yake da kamar ya koma gurin Maude ya karya shi.

.... Ajiyar zuciya yayi sannan ya shiga abin hawan shi. Yana nazarin mutumin da yayi mishi magana. Share maganar yayi tare da wurgata a kwandon shara.
Bayan kwana biyar aka sallami Anum, ta dawo gida. Tunda ta dawo umma kamar zata yi fushi da ita, sai kuma ta kasa, ta cigaba da kula da ita.
Satin ta daya da dawowa aka kawo kayan lefe. Wanda ya taimaka gurin d'aga mata hankali. Bayan kawo lefen dake har dasu Hafsat a karb'a. Bayan zasu koma gida ne ta dauko kudi har dubu uku ta mika mata.
"Ki tafi wani guri ki zauna idan kome yayi kyau sai ki dawo."

"Toh zan yi yadda kike ce" ta ajiye kudin, tana kallon shi har ta fita.
Kasa aiwatar da abinda Hafsat tasata tayi, karshe ta shiga dakin Umma tana sallah ta zauna har ta idar, ajiye mata kudin tayi..
"Umma gashi wai na gudu, don Allah karki gayawa Malam yayi musu faɗa."

"Wacece tace ki gudu?" Shiru tayi tana wasa da yatsunta.

"Toh ba zaki yi magana ba?"
Kuka tasaka mata.
"Umma kina fushi dani dayawa, bana jin dadin rayuwa na!"
"Toh idan banyi fushi dake ba, KHADIJAH wuka zan burwa cikina? Ke daya tal kin hana kowa sukuni, sabida ke kullum Mallam sai ya sha maganin hawan jini, sabida ke yan uwanki suke min kallon na raba auren mahaifanku, gaya min idan banyi fushi ba in zauna nayi ta dariya sabida kina aikin kwarai?

Wai har kin san kisha madarar piya piya, ki mutu? Toh sai me dan kin mutu? Wallahi nayi danasanin renon abinda zai kashe ni da bakin cikin rayuwa har na aurar da su Binta basu saka Ni damuwa ba, Rulwanu da yake namiji bai saka ni damuwa ba, sai ke Anum? Meye nayi miki da kike azabtar da ruhina?

Mahaifiyarki tana jin zafina! Yayana da na haifa suna jin zafina,.mijina yana jin zafina kinyi min adalci? Ai dana san XOXO ce ta baki shawaran shan piya piya, wallahi kinji na rantse da wanda rayuwata da mutuwata take hanun shi ba zan tab'a kawo miki ɗauki ba. Anum kiyi yadda kike so bani kuma dakatar dake idan na kuma ni shegiya ce ba yar halak ba.

Yadda kika iya daukar shawarar XOXO nayi imani da Allah idan aka yi auren haka zaki.dauko shawararsu su. Meye amfanin na zauna ina bata lokaci na akanki? Anci mutuncina akanki an zarge ni akanki ashe ban cancanci na samu nutsuwa, Anum idan Aminatu da Rulwanu haihuwa ta suka yi ta hanyar sunnah, ba zan kuma cewa ki gyara kayanki ba, idan kuwa a kasuwa suka samar dani zan miki magana, ki saka kai ki ficce min daga cikin d'akina kafin na sab'a miki, duniya ce tafi gabaruwa ji ma."

Kuka Anum take son yi amma fir yaki zuwa, haka ta makale jikin umma tana cewa.
"Wallahi mutuwa zanyi idan na saka kafa na fita daga dakinki." Aikuwa ran Umma ya kai iyakar b'aci, tana tashi ta yakinin ceta a jikinta ta wullar da ita waje ta datse kofar ta, gashi ana ruwan sama, ihu Anum take tana buga kofar Umma, itama a cikin dakin kuka take me mugun cin rai, tana jin ina zata iya daukar kasadar rabuwa da Anumullah ɗinta,

Yarinayr da take ji tun ranar da ta fado cikin uwarta itace ta fara daukarta tare da rungume ta, sabida an haifeta ta wahala ko numfashi bata yi, domin tayi kankanta lokacin a tunanin su ma bata cika wata tara ba, duk iya kokarin ganin yarinyar ta motsa Umma tayi ta daura ta a kirjin Maman Aminu amma ko gizau, sai da Maman Aminu tace mata.
"Ki sakata a jikinki mu gani, kamar bazata tashi ba."
"Anya zata tashi kuwa?"
"Gwada dai mu gani!"
"Toh Ya Allah, gamu gare ka mun gode maka"
A hankali ta saka Anum din cikin rigarta tare da mannata sosai a kirjinta, ta kuma dauko zani da bargon Maman Aminu, ta manna Anum din sosai.
*_Fatan Alkhairi Sister Maryam Badam Nagode sosai Allah ya saka da Alkhairi nagode sosai_*
#Mai_Dambu
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA...!!
Rayuwar Aure a Arewacin Najeriya

Mai_Dambu
Farga daji....
BABI NA UKU

Ina jin hayaniyar yan uwana, amma sabida kasancewa ta, mujiya a cikin su, ya sani kara lafewa a gadona, ina had'iye yawun, sakamakon kamshin soyar namar da ake na sunan Ikilima matar Ya Abubakar, wacce ta haifi d'a namiji aka sami shi sunan Baba Malam.

"Mama yar sarki me rigar mutum ba zata fito bane ayi aikin da ita? Wato ga bayinta su gama mata, ta zauna ta cinye?" Inji Aunty Hafsah, yayata ce da muke ciki ɗaya.

D'aga labulen Yaya Binta tayi dan ita ce ya ta farko a cikin gidan mu, ta kalle ni na tashi zubur ina zare idanuna da suke cike da kwalla. A hankali ta sake labulen sannan tace musu.
"Da bata yi aikin sai ya kashe ku? Hafsat da Safiya kuna bani mamaki. Da akace karta na yawan shiga damuwa shine bari kuyi ta sirka mata rashin mutunci?

Hmm! Zuciyarta yana tabuwa da abinda kuke mata, idan rayuwarta ce baku so! Shi kenan, zaku iya Cigaba da abinda kuke."
Daga haka ta wuce dakin Mahaifiyar su. Cikin jin haushi Safiya tace.
"Yarinya ta gama rashin kunyarta tare da mana sanadin mahaifin mu, amma ake ganin bata yi kome ba, har abada ba zan tab'a yafe mata ba, taji kunci da Baba Malam yaji lokacin da yake rokonta arzikin da bai mata ba, amma fir taki kula shi."

Haka suka yi ta mita, tare da jin haushin yar autar su. Wato Anum.

... Duk ina jin su, amma bani da ikon fitowa wajen domin ina fitowa zasu min caaa, dan haka na cigaba da zama a d'akina. Har zuwa azhar da na fito alola, naga yadda suke kallona, jikina ne ya dauki rawa, kamar zan kifa, dan har tsalleke abubuwan nake sakamakon tsawar da Aunty Hafsah ta daka min.
"Ke wata irin dabba ce? Kin zo kina niman zuba mana, ruwan butar a cikin abincin da muke banza akuya, karya k...."

"Hafsat!" Ya Aminu ya daka mata tsawa, cikin jin haushi ta ce mishi.
" Ba ajiyar bace? Ko ba karyar bace? Wallahi har kunyar nunawa kawayena wannan yar iskar cikin mu daya, sabida yadda ta zama taxi.."

"Kina da yaya mata, sannan kina zagin yar uwarki ciki ɗaya, sabida ajizanci." Take kowa yayi mata caaa, ni kam nasan haka zai faru, da bi bango na isa d'akina, na zauna tare da sake kuka me mugun ciwo, wanda su kansu yan wajen duk sai da suka ji yo ni.
Kallonta kowa yayi cikin jin haushin abinda ta aikata, sannan suka ce mata.
"Yayi miki kyau!"
Maman su da take jin abin a cikin ranta, share su tayi amma tasan duk abinda Khadijah Anum tayi ba laifinta kadai bane har da nata,a matsayin ta na Uwa ta gaza tsawa yar autarta ta zama abin alfahari.

Itace ta gina mata kome na rayuwar da tayi, ita ce ta nusar da ita abinda zata aikata, ita ta nuna mata kudi da kyau sune cikon muradinta,. Ba lallai sai ta zama mace ta gari ba, zata iya zama mace mafi daraja indai zata hadu da me daraja.

Haka ta share kukanta a cikin dakin ta, dan bata son yaranta su gani wutar k'iyayyar da take ruruwa a tsakaninsu ya kuma tashi.

--- bayan sun gama kome, suka shirya tare da barin gidan, suka nufi gidan da ake taron sunan wanda yake Makara huta, dake garin bauchi. Suna shiga aka shiga tambayar su.
"Ina Anum? Aunty Hafsah"
Inji wata budurwa wacce ba wuce shekaru ashirin da hudu ba, duk da bata girme Anum ba, amma kuma zasu iya zama kusan shekaru daya.

"Shukrah, yaushe kika zo daga Kano?" Murmushi sannan tace mata.
"Yau kwana biyu kenan, don Allah Aunty Anum zata zo ne?"
Tab'e baki Hafsat tayi sannan tace mata.
"Ban sani ba, ko zata zo ashe."

Ta wuce Shigowar Mahaifiyar yarinyar ta mike tare da amsar jakarta, tana faɗin.
"Ammih Aunty Khadijah Anum ba zata zo bane?"
Shiru tayi sannan tace mata.
"Kuma na manta da sakonki, Amma Insha Allah zata zo dan naji tana cewa idan kanta yayi mata sauki zata zo."

"Toh Ammih, Allah yasa kin san yanzun Aunty Anum ta zama wata iri ne tsoro ln shiga mutane take."
Kallon ta Uwar tayi sannan ta girgiza kai, ta wuce komawa gurin Kawayenta tayi tana gaya musu, bata zo ba amma Insha Allah idan ta kama suje bakin kura sai suje.

"Toh ishashiya, kowa ya tafi gidan sunan shine ba zaki tafi ba!" Inji Mamarta.
Sunkuyar da kai tayi sannan tace mata.
"Don Allah Mamah ba.."
"Ok shima Zumuncin so kike ki lakata min kashin kaza? So kike a Cigaba da cewa nice nake hanaki shiga yan uwanki."

"Don Allah Maman Aminu ki bar yarinyar ta samu kanta mana, wannan wacce irin rayuwa ne, tunda bata jin dadi ta hakura mana!"
"Umma zani Insha Allah. Bari na shirya."
A gurguje na shirya tare da saka wata shaddata, wacce aka mata aikin surfani, sai hijab me yashi.
Babu wani kwalliya na fito tare da daura niqab nayi musu sallama, ina fitowa daga cikin gidan na sami Abba K2 yana zaune a bakin shagon Oga Maude, kallona yayi sannan ya ajiye kofin shayin yana faɗin.
"Uwargida, ina zaki?"
"Zamu gidan Yayana ne ana suna." Na bashi amsa a takaice bai na kokarin barin gurin su,

Tashi yayi daga gaban shayin, ya shiga keke napep din shi, ya sha kaina da keken.
"Muje ko"
"A'a kaje kaci.."
"Karki damu sabida ke nake aikin da babu ke haka zan cigaba da sara suka, a kashe ni a banza,.dan haka ki shiga muje."

Ban musanta mishi ba, dan yaran suna bani wani irin girma ne na musamman, gani suke kamar nice ogan su ma. Har kofar gidan Ya Abubakar ya kawo ni, kuma abinda zai daure maka kai shine bai dauki kowa ba, sai ni yana ajiye ni yace min.
"Uwargida yaushe zan zo daukarki!"
"Karka damu zan sami motar da zata..."
A birkice ya kalle ni tare da tsuke fuskar shi yace.

"Ina nan ina jiranki duk lokacin da zaki koma sai na koma."
.sake bakina nayi domin kuwa ya bani mamaki, akan me zai zauna,
"Ka dawo bayan isha."

Na fada mishi haka, dan kar ya b'ata lokaci, a gurin zaman gadina, duk da nice na janyowa kai na, da ace hannun agogo zai dawo baya lashakka zan gyara kuskure na.

Labarina babu abin dauka a cikin shi, domin cike yake da ƙadarorin masu girma, kowani dan Adam da irin tashi ƙaddarar amma yawa ƙaddarar nice na zanata wanda har yau na kasa goge shi.
"Laa, Aunty Anum!" D'aga niqab dina ina kallon yar Yayar mu.
"Shuky yaushe a gari?"

Cikin farin ciki da gani na ta shiga rawan jiki tare, da bani amsa, yayuna mata uku musamman yan dakin mu, tsaki suka yi tare da dauke kan su, duk da yaran su, suna murnan ganina, isa nayi gaban su na dauki yaran tare da musu wasa.
"Ajiye min Y'ata! Da kin san zafin shi ba zaki sake a tafi da shi wata duniya ba."

Murmushi nayi a karo na farko da naso majin zafin kalamanta, nace mata.
"Zanen ƙaddara ta kenan! Amma haka bai hanani kaunarta ba, kome zaki gaya min ki min a cikin gidan mu, inda ba zan kulaki ba, nan kuma cikin jama'a ne, zuciya bata da kashi kina min zan rama." Daga haka na ajiye yarinyar na bar su tsaye cikin damuwa da mamaki, suna jin haushina, amma kuma halin da nake ciki, ba zai hana su min rashin mutunci ba.
Gurin mejego na shiga muka gaisa dasu Ya Amina, Ya Rabi, da Ya Bintu, zama nayi ina narkewa a jikin Ya Maryam.
"Kin san Allah Autar malam, ki rabani da son jiki. Kun hadu da shukrah."

"Eh!"
"Wai zata zo ki mata nasiha akan zaman aure ne. Tazo gurina nace mata bani da wannan tunanin, tayu ke asamu wani abu daga gare ki, idan mutum ya duba daga yanayin rayuwar da kika yi."

Tana maganar ne amma kasa kasa, da sauri na d'ago kai nace.
" Kuma kika ce Ni? Amma ai naga rayuwar auren da nayi babu kome cikin shi sai damuwa da son zuciya!" Na fada a raunane.

"Babu son zuciya cikin ƙaddara, duk da kina da laifi, sai dai ki sani ƙaddara itace igiyar da ya jaki zuwa ga wannan rayuwar, idan Allah bai zana miki haka cikin ƙaddarar ki ba, toh babu abinda zai sanya haka ya faru, zanen ƙaddara kenan, ki same ta naga har da Kawayenta suka zo, ita daya tana shirin aure nan da sati biyu, daya kuma tana fama da matsalar mijinta da baya iya ciyarwa sai dai iyayenta su kawo musu, yaci kuma ya kwashe musu albarka."

Kallonta nayi sannan na mike tare da cewa.
"Toh bari na gani."
"Yawwa yar albarka."
Fita nayi suka bini da kallo cikin tausayi da damuwa.
"Wallahi Yarinayr nan tausayi take bani, ga baki daya ta firgice da yan uwanta, ganin dodanni take musu, don Allah Aunty B kunyi musu wani abu su kyaleta ta huta, kiga duk fushin Baban Ayman haka ya hakura tunda yaji zuciyar ta zata iya bugawa sabida damuwa, ku wanda kuke akan shi yayi tafiyar shi ai sai ku kyaleta haka."

Tattaunawa suka yi tayi, har zuwa wani lokaci, kafin suka share batun.

Ina fita ta mike muka shiga wani falon da babu cunkoso mutane, zama muka yi suna kallona, nima kuma kallon su nayi kafin Shuky tace min.
"Aunty Khadijah, sunan ta, muna kiranta da Anum, kyautar Allah.!" Jan fasali tayi tare da nuna musu ita, sannan tace mata.
"Mu nan, Kawata ce zata yi aure shine muka je gun Aunty Salamatu, wai muzo gurin."

Shiru nayi tare da nazarin ta inda zan fara musu bayanin.
"Wato shi Al'amarin aure girma ne dashi tare da fadin gaske, duk yadda mutum zai gwada muku matukar bai tab'a shiga wannan bangaren ba, toh babu abinda zai gaya muku sai hakurin. Abu na farko da zaku fara shine kuyi auren ku da Kyakyawan niyya,karki yarda kiyi auren dan yana da kudi! Karki yarda kiyi auren da yana da kyau! Karki yarda kiyi auren da shi wani ne! Karki yarda kiyi auren dan zai miki lefen kece reni! Kuyi auren domin bautar Ubangiji, haka zai sanya ku rabauta, karki yarda ki aure shi dan samun Freedom! Babu yancin da yafi ki bautawa Allah a cikin zamantakewar aurenku!

Karki yarda ki aure domin ya cancanci haka ne, a'a ki aure shi domin Allah kuma kiji a ranki koda shi gwamna ne ko shugaban kasa, zaki zauna dashi ne a matsayin miji da mata, a karkashin kulawar Addininki!
Rayuwar Aure yayi ne! Domin babu rayuwar da yafi rayuwar aure dad'i, a rayuwar aure babu, abinda zaki yi bai zama lada da Alkhairi ba, amma a wannan lokacin rayuwar aure ya zama niyasu, sabida yadda muka sake addinin mu da Ibadar mu, da ace mutanen baya sun san da haka toh bazasu tab'a barin mu,. Haka ba sai sun mana addu'a akan zamani, sabida a lokacin su ana girmama auren fiye da kome a duniya, amma a wannan lokacin auren ma wulakanta shi ake, da zaka tambayi wani dan me zaka yi aure? Zai ce maka kawai zai yi ne sabida ya dace da haka, ko kuma zai yine sabida Yarinayr zata kawo mishi kayan daki da Gara, har hada suke da junan su.

Da zaran anyi auren sai kaga kwanaki ƙalilan an fara samun matsalolin rayuwa, ka rasa ta ina aka fara, bayan daga mune abin ya fara, karki yarda mutumin kirki ya subuce miki bayan kina sane da shine zai ririta alamarin ki, karki yarda da wanda zai zauna kullum yana gaya miki yayi mafarkin ki, bayan ba aurenki zayi ba.

Shukrah karki yarda wani ya baki damar da zaki ki auren Mutumin kirki, bayan kema kinyi imanin mutumin kirki ne, irin su ƙalilan ne muke dashi a cikin al'ummar mu. Toh Alhamdulillahi anzo fagen aure, kowa zai ce miki kiyi hakuri halin maza sai su, tun kafin ki isa gidan mun gama razana ki da mabanbanta Halayyar maza, da fadar wasu munanan halayen su.

Shin kin tab'a tambayar Mamanki wani irin halin Mahaifinki yake dashi? Toh ai idan halin shi mugun nufi ne, haka kuwa tayi hakuri da shi ta zauna a haka dashi, idan halin shi na kwarai ne, haka zaki zauna da naki, duk duniya babu wanda ya isa ya baki shaidan zuciyar mutum sai Allah, dan haka kiji a ranki zaki zauna dashi ne da zuciya daya. Anzo fagen aure!

Anyi aure, an haihu daya biyu uku, wai sai kiji matsala ya dame ki, kina kukan ya zaki yi,kece Posting a grp na Whatsp! Kece kaiwa IG, kece kaiwa Facebook. Kin tab'a zama kinyi nazarin zaki magance wannan matsalar? Wadannan Groups da kike Turawa 75% na cikin su Yan mata ne da suke niman mijin aure kin dauki damuwarki kin kai musu! Shin akwai wani bayan Allah ne? Babu tabbas babu, akwai me magance miki matsalar ki ce? Babu tabbas babu, Amma akwai Allah, Tabbas akwai shi. Kin tab'a yin azumi domin Allah ya yaye miki damuwa? Toh indai har kinyi wallahi zaki iya akan damuwar mijin, kin dauki Matsalarki kin gayawa mutane,

sannan sun ce miki gaskiya ki rabu da mijinki nan baya sonki da zuciya daya, shin kin tab'a ganin matar auren da ta shekara goma a gidan mijinta ta bawa wata mace shawarar ta kashe aurenta? Sabida duk lalacewar auren shine kimarta, bari na gaya muku wani abu, yan fashi da manyan masu laifi, wallahi suna da matan su na sunnah kun tab'a ganin matar su tafi toh tace mijinta dan fashi ne? A'a ba zata tab'a barin kowa yasan halin mijinta ba, sabida boye sirrin shi.

Amma zaka samu mijinki yana zuwa kasuwa, domin niman na kanshi daga karshe zata yi Posting don Allah ku boye sunana, mijina bayi da kirki. Mijina ya cika masifa, mijina kaza yaushe Hausa Fulani suka koma haka? Wallahi tunda nake yawon aure aure, ban tab'a kawo kara gida ba, sabida bana son Kowa yasan damuwata, sai dai idan kunje kuga halin da nake ciki. Ban tab'a ganin zamani ne cike da mamaki kamar wannan zamanin ba.

Kun mai da rayuwar Freedom kamar yadda kuka tsarawa kanku. Kun mai da aure kamar takalmi, wai har budurwa zata baki shawara bayan ita bata zauna da namijin ba, kunsan falalar da Allah yayi mana, toh ku barshi a haka karku what man can do, Woman can also do it, wannan kamar kunyi fito na fito da yar Allah ce, kina da uwa kina da Uba, kina da yan uwa, ki zaɓi abokin shawarar ki karki kaiwa kowa kukanki sabida Akwai Allah.. rayuwar mu da ban mamaki take, wai sai kaji ana ce maka maganin mallaka, Yes kiyi maganin gyara, amma duk Wanda yace miki, zai baki maganin mallakar miji, karya yake miki domin ko kin same shi kwana biyu, zai lalace kuma zai ci Ubanki, karki yarda kawarki ta kawo miki wani abu dan mallakar mijinki, domin cutar dake zata yi babu wani mallakar shi da zaki yi.

Idan baki mallake shi ba, ita zata mallake shi ta aure miki shi. Kuma a zauna lafiya, babu yadda kika iya.

Kince baki son kishiya ba laifi amma ki sani dole yayi aure, domin idan bai yi ba, zai bi matan layi, kuma zai kwaso miki damuwa, babu yadda kika iya.

Uwar mijinki, Allah sarki uwar miji. Har ulcer ake ce miki, zunzurutun rashin kunya da mutunci, kin mai da mahaifiyar mijinki da yan uwan shi abokan adawarki, toh my Sister karki manta kema uwace, iya haka ma ya ishe ki, kamar yadda kika hana shi kyautatta mata, haka d'anki zai auri yarinyar da zata miki, kuma baki da abinda zaki iya, sabida rashin adalcin da kika nuna mata.

Na rasa gane wani irin kyashi da Hassadar da take damun mu, bamu kaunar muji mazajen mu zasu kyautata yan uwansu, take kishi da bakin ciki zai motsa kin tab'a tunanin kema kina da dan uwan namiji abinda kika yiwa wasu shi za a miki, mata muji tsoron Allah, zamu mutu mu tarar da Ubangiji, mu girmama auren mu, mu cire cutar kai da hassada mu rike auren mu da kima.

Maza kuma kuji tsoron Allah, baka auri mace dan ta rike kanta ba, wallahi muji tsoron ganuwar mu da Allah, domin duk wanda ya auri mace yasan ci da shan ta yana wuyar shi, amma sabida rashin amana ka sauke ƙana jiran danginta su kawo maka ka cinye kuma kabi yarsu da zagi da cin mutuncin, shin idan aka yiwa Yarka haka zaka ji dadi? Zaka yi farin ciki? A'a kawai dai ka auro mace kayi ta gana mata azaba, daga karshe kace kai ba zaka zauna da ita ba, sai ta biyaka kudin da ka kashe, anya kana tuna bayanka kuwa? Toh idan barci kake ka farka, tuni. Domin kuwa idan ka sake Allah ya kamaka da hakkin wulakanta aure, sai kayi DANASANI mara amfani.!

Karku manta da wasiyyar Manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama, idan yace yafita hakkin mu, ya zo mana da addinin musulunci, ya kuma isar da sakon shi, sannan yabaku amanar matayenku, ku zauna dasu da amana, karka yarda Manzon

Allah ya kamaka da hujjar shiga hakkin aure.! Da wannan nake kawo karshen yar ƙaramar nasihar da na kawo muku da fatan zaku karu dashi"
[1/31, 11:27 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA...!!
Rayuwar Aure a Arewacin Najeriya

Mai_Dambu

Kowa ya tuna bara..
BABI NA HUDU
Wani banzan shewa Ya Hafsah ta saka, cike da izgilanci sannan ta taki gabana, zata ci zarafina.
"Akaramakiya, Hamshaqiya, Sayyida, Ustaziya Khadijah, Eyye Ashe Anum ta iya wa'azin zaman aure bamu sani ba?

Matar da ta gaza zama a d'akinta, yarinyar da tunda kuruciyarta take dauko magana, karewa har cikin..."

"Ke wacce irin sakarya ce? Ke wacce irin mahaukaciya ce? Yo Allah na tuba, me zaki gaya min? Me zaki fada a gaban jama'a? Wai naka ke yake shirin tozarta ka a gaban mutane, gaya musu wacece Khadijah! Tayu ba zasu sake gani na ba, ke kuma ga kishiyar ki nan ta sami abin goranta miki gara ni, wallahi duk inda na shiga bana boranta Ni mowar miji ne, tun daga cikin gidan mu ya kamata ki fahimci Ni autar Yaya ce , bana tab'a zama bora ko a gida ko a dawa. Idan kece da wuta da aljanna don Allah Hafsah idan nazo ki rufe aljanna ki wurgani cikin wuta. Jahila kawai."

Daga haka na mike tare da ɗaukar jakata, na fara ƙoƙarin barin gidan sunan, ban ma kira wanda ya kawo ni ba, zunzurutun raina ya b'aci, kuma a yanzun bana son tuna bayana ne. Idan na tuna yadda na b'ata tambarin gidan mu sai naji na gaji da kome na rayuwa. Tunda na fita na sami napep na shiga, goge kwallar da take fuskana nayi, tare da kallon gefen hanya.

Beauty na gani, sanye da wata swiss gefenta Alhaji Dan Azumi ne, dauke kaina nayi tare da cewa a raina.
"Allah nagode da ka cire ni a wannan kazamar rayuwar, Allah Nagode da ka barni da Imani na, Allah ko makiyi na, karka wurga shi cikin wannan yanayin shi yasa Bala'i tayi mana Yawwa."

A hankali napep din ya sauke ni a kofar shagon Oga Maude, haka kawai yau nake matukar jin kewar shi, yana cikin raina wanda ban san lokacin da haka ya min diran mikiya ba. A hankali na sauka tare da saka hannu a jakata zan ciro kuɗi.
"Jeka malam."

D'ago kai nayi naga Rulwani ne, dauke kai nayi, tare da nufar cikin gidan.
"Shegen rashin mutunci, ai kyace kin gode ko?"

Tab'e baki nayi tare da cewa,
"Daka biya na saka ne? Ko kuma nace maka ba zan iya biya bane? Kai kaji gurin!"
Daga haka nayi wuccewa ta cikin gidan mu, ina jin shi yana bolokoko, ina ruwan ayagi me fada ko daga zaune a tab'a.

... Ina shiga na sami fadar Mama,.kamar zata cinye ni wai na ci mutuncin Hafsah a cikin jama'a me yasa ba zanyi hakuri ba, dan tayi min fada har ina mata gori, shiru nayi tare da wuccewa d'akina, ina jinta tana kuka.
"Bayan b'ata min suna da kika yi haka ma bai ishe ki ba, sai kin tozarta yar uwanki a cikin gidan suna a gaban jama'a kika zage ta."

"Mama, wallahi ba haka bane, kawai ta gaya miki son ranta ne, amma wallahi ban zage ta ba."

"Ki min shiru! Karki kuma gaya min maganar banza, taya zaki ci mutuncin yar uwarki a gaban jama'a? Daga gaya miki gaskiya, ke wacece da ba a gaya miki gaskiya ba. Ni zaki kawowa karya!

Wallahi zan saka Bashir yayi miki mugun duka, sakarya kawai mara hankali ba gwara ita ba, tana zaune a dakin mijinta, kuma tana min duk wani abinda ya dace ke ince rashin rabonki ne ya hanaki Fahimtar Arzikin da Allah yayiwa mijinki."

Kallon ta nayi baki sake, hawaye na zuba daga idanuna, lekowa Umma da Goggo Hamah, tare da kallon Mama ta sani a gaba zata dake ni.

"Toh ai sai ki kyaleta, lokacin da ta kika lalata abinki ai babu wanda ya sani, yanzun da kuma duniya tayi muku juyin masa shine bari ki goranta mata, ai duk abinda Khadija tayi bata da laifin ki ne, kwaɗayin duniya ya kai ku ya baro ku. Yanzun kin wani zo zaki dame mu da Hausar ki da bata ishe ki ba, don Allah ki kyale jama'a su huta haba don Allah."

Juyawa tayi tare da fita, Mama ta zuba min ido, cikin tsannanin b'acin rai, yau akai na ake gaya mata magana, kafin na ankara sai ganinta nayi tana zubda kwalla. Jikina ne ya dauki rawa tare da girgiza mata kai nima ina kuka.

"Don Allah!"
"Ya isa haka! Kije na cire hannuna daka kanki, kije duniya ta ishe ki riga da wando, Anum Ni ake gayawa magana sabida ke? Idan dan soyayyar da na nuna miki ne kije na barki da duniyar." Tana kaiwa aya ta ficce, ina tsaye a inda ta barni wani irin kuka ne yazo min tare da nadama mara amfani, zama nayi cikin mutuwar jiki. Duk da kiran sallah da ake bai sanya na tsayar da kuka ba.

Na kai minti goma sha biyar, har aka fito masalaci ina kuka, kafin na mike na bar gurin, fitowa nayi na yi alola na koma cikin dakin, tunda na zauna nake kuka, ina taryo abubuwan da suka gabata na rayuwata, da ace a lokacin ta bata fahimci kallon tausayin da Baba Malam yake mata ba, me yasa bata fahimci kallon tausayin da Maude yake mata ba.

Idan ta tuna lokacin da yake Maude yake cewa.
"Khadijah! Wannan rayuwar da kika dauka karya ce, Khadijah ni me kaunarki ne, kuma ina kaunar farin cikin ki ne, KHADIJAH zan iya samun matar da suka fiki, Khadijah ina da su, amma zuciyata bata kansu, sai ke don Allah ki taimake ni ki haifa min cikin jikin ki lafiya Wallahi zan baki mamaki a rayuwarki!"

Dariya ta saka tare da gyara kwanciyarta bayan ta matsa daga inda yake, ta juya mishi baya tace.
"Cikin ƙaddara ko? Toh zan haifa maka shi meye a ciki daga duniya sai Abuja, zan haifa maka abinka amma wallahi ka sani babu rabon sharyawa a jikina, na gaya maka. Duk abinda zaka yi kayi daga yanzun amma ba zan shayar maka da abinda zan haifa ba. Me kake dashi? A cikin su Hishmah Dubai aka kai ni sayayya kayan haihu,a can na haihu kai me ka tara? Me kake bukatar nayi da Kaddararren auren ka, banda cin Amana taya zamu shirya abu da kai ka dawo kace baka san zance ba.

Sake ka daura aniyar sai ka tozartani shine ka dawo da cewa ba zaka sake ni ba, wallahi zaka rabu dani domin tun fil azale bana kaunarka, kuma bana sonka ka gane mana..."

Jikin shi na rawa ya matso kusa da ita, tare da janyo ta jikin shi.
"Karki ce haka! Naga soyayyar gaskiya a idanunki don Allah karki ce baki kaunata, ni ana sonki zan cigaba da sonki, KHADIJAH Dubai fa, haba sai dai England kayan haihuwar abin cikinki, wallahi na shirya baku farin ciki, zan d'aga ki daga cikin gidan na mai dake gidan da kike bukatar rayuwa, Khadijah zan baki motar da tafi wanda na amsa, don Allah ki amince dani. Mu rayu lokacin da na gayawa Dattijo kina da ciki, cewa yayi na kai ki nijar ki haihu, amma nasan ba zaki tab'a amincewa ba, don Allah ki taimake ni, ki kula da lafiyar abin cikin ki da kuma ni. Kaddarar ki ce ta kawo ni, da kuma kaddarar cikin jikinki ya kawo ni tsawon shekaru a garin bauchi.

Ina da rayuwa da dangina, don Allah karki juya min baya, ina sonki zan baki kome kece matar da nafi so da kaunarta, don Allah karki ce zaki juya.."

"Maude! Wallahi kaji na rantse maka billahil azim, ba zan shayar da wannan wulakantattacen cikin jikina ba, ai kaci iya kudinka, kuma ka sami abinda kake bukata, ba dai jikina bane damuwarka ai samu.

Kuma nasan har abada ba zaka kuma sami mace irina ba, dan haka matsa min na sauka daga hanya na sauka zan kwanta a kasa ka rike katifar, tunda dashi kazo yawon cira ko? Toh indai zai kara maka jarin shayi da burodi ka dauka kara, dan na san fatara da talauci ya kawo ka najeriya ko? Gashi daga zuwa ka auri Sumayyah, gashi nan kazo ka kara dani."

Lumshe manyan idanun shi yayi cikin damuwa lashe bakin shi yayi, tare da zuba mata ido, zata sauka ya dawo da ita, hannu d'aya ya saka ya zare rigar jikinta, bai barta ba sai da ya sami dukkan nutsuwar da yake bukata, sannan ya janye daga gareta ya sauka zuwa ban daki ya barta tana shashekar kuka, cike da bakin ciki.

..... "Anum!!!" Kiran da Umma tayi mata ya katse mata tunanin da take yi ta mike a hankali ta fita, tare da mik'ewa tsaye ta fito waje.
"Kina ina Mamarku ta fadi innalillahi wa'inna ilaihi rajioun." Ji tayi kamar zuciyarta zata fado daga kirjinta maza tayi ta rike kirjin ta, jikinta na rawa, numfashinta yana sama da kasa.
"Ke kan kiyi asara rayuwa! Uwarki ma ba zaki barta ta rayu cikin salama ba, sai kin kashe ta kamar yadda kika kashe mun d'an uwa, wannan wani irin masifa ce.

Anya babu hannun a jikinki, yarinya sai kace yar Allah bani."

Had'iye yawu tayi tare da kai hannu zata tab'a Maman su, aka buge hannunta, aka yi tare da nuna ta da yatsa.
"Ke kan! Wallahi bamu san wani irin zunubi muka yi aka bamu ke ba, kin kashe mana mahaifi yanzun ma mahaifiyar mu baki barta ba Anya Anum kina niman lahira kuwa? Toh kar na kusku..."

"Bashir! Anya kuna yiwa kanku adalci kuwa? Meye laifin Anum, ai tayi kyan kai."

"Zainabu ki barshi yayi magana! Me aka yi da yarinyar da ta kashe Ubanta da bakin cikin! Wallahi ka mata shegen duka, me zayi da ita." Inji Goggo Hamah,

"Dakata Hamah,ke baki kashe wutar rikicin gidan kiba, ba zaki zo kice zaki kashe na wasu ba, dan haka ki ja bakin ki, babu ruwan ki a wannan karon, domin ba zaki tadda husuma ki tafi ki bar mu cikin Jalala ba. Sai mai kuna meye tayi muku?
Wannan yarinyar bata muku kome ba kuke tsana da tsangwama? Meye laifinta? Anan Hafsat Da Safiya jikin su na rawa suka kira uwarku, suna gaya mata abinda ya faru! Kai Jama'a? Anum ce baku son gani a raye ko Uwarku? Tunda nake da Anum aurenta biyar bata tab'a zuwa gidan nan da sunan kawo kara ba. Kai kana ihun ka karta tab'a ta akan me? Uwarta ce yarinyar nan tunda mutumin nan ya tafi da tarehi bata kuma barci ba wai kasheta kuke so zaku yi ne? Toh idan Anum bakin cikinku bai kasheta ba toh uwarku zaku kashe tunda ba zaku tab'a dauka maganar matsalar ku da Anum kuna gaya mata ba, wallahi ita bata kashe ta ba, toh ku hankalin ku ya kwanta."

Daga haka ta koma d'akinta ta dauko hijab ɗinta, ta saka, tare da cewa.
"Ka riketa mu kaita bakas!"

Jikin shi ne yayi masifar sanyi, duk masifar da yake ji zai yiwa Anum sai gashi Umma ta dakatar dashi tare da gaya mishi gaskiya, nima na basu zuwa asibitin,muna zuwa aka karb'eta, cikin lokaci ƙalilan suna fara bata kulawa na musamman, ina kallon kome kamar kiftawa da bismillah, kome ya lalace.

Dakyar na dawo gida, na kwanta, can cikin dare. Garin yayi sanyi kasancewar muna cikin lokacin damina ne, dan muna dawowa daga asibiti aka fara ruwan sama, wani irin feelings naji kamar me, tun bayan tafiyar Maude ban kuma jin wani abu a kan shi ba, sai yau. Dan haka ina kwance har barci yayi nasarar tafiya dani.

Wani irin mafarki nayi da Maude kafin kace me, har naji Ni cikin wani duniya na daban, tsawar da aka buga wanda yayi sanadiyar farkawa na daga mafarki mafarkin da nake, tashi nayi zaune, sannan naji gaba daya bana cikin nutsuwa, tashi nayi na tab'a flask dina na ji da ruwan zafi, dan haka na juye a babban butana. Na fito tsakar gida, a hankali na nufi ban daki nayi wankan tsarki, sannan na fito a hankali ina rawan sanyi, walkiyar da aka yi ya sani ja da baya, sakamakon kicibis da nayi da...[2/2, 9:41 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN DA HUDU

Godiya da fatan Alkhairi! Masoyan Zanen Qaddara ta Me akayi da maza karuwa taga mace da ciki Ku biyo Ni dan ba a san maci tuwo ba sai miya ya kare! MOM SAYEED how market naga kinyi shiru Eyyeeeee 😉 My Hafsat mom Khairat

_____

"Alaji baka auri yar mutane domin ka kashe musu ita ba, asalima an baka ne sabida ganin ka cancanci haka! Idan kace zaka biyewa halin mace wata rana sai ka fita layi kana sumbatu, ita mace duk girmanta duk shekarun ta, yanzun dan sha tara zai iya tsarata kuma ta tsaru!

Karka yi tunanin dan ka rabata da gidan su akan sadakin dubu hamsin kace zaka maida da baiwa, ita ba baiwa bace Y'a ce. Karka ga dan tsaya ta nace sai kai kayi tunanin bata da wasu masoyan ne! Idan da maza zasu yi tunanin cewa ina da Uwar da ta haife ni mace ce! Ina da kane mata, kuma ba zan iya d'aga hannu na dake su ba, tabbas da babu wanda zai wulakanta mace.

Amma kai ne baka da aiki ke Jummai, ina butata Jummai takalmi na, jummai tazoje na. Haba bawan Allah, Manzon Allah Sallallahu alaihi Wasallama. Gidan shi har dashi ake girki. Matan na aiki shima yana aiki, gidan Manzon Allah zunzurutun soyayya idan yayi alola zai tafi masallaci duk macen da ya gamu da ita sai ya sumbace ta.

Me yasa mu ba zamu iya wa wannan tausayin ba, a'a tun daga lokacin da aka aura mishi ita dan karta rena shi sai ya tsiro da wani halin banzan na fushi. Ka dauko yar mutane ka ajiyeta a gida shin ita ba mutum bace, da zaka na b'ata rai dan karta rena ka, sai dare yayi kace Laraba bude min zani, anya kayi adalci. Idan ka dauki mace ta wannan sigar har abada zata na jin haushin ka, tayi ta addu'ar Allah ya raba ku tunda bata da amfani a gurin ka sai na jima'i. Maza kuji tsoron Allah, maza ku mu'amalanci matar ku da adalci.

Karka yarda matar ka ta maka kallon mara adalci, ka rike matar ka kamar yadda Manzon Allah yace.

Wallahi karka yarda Allah ya kamaka da laifin ka zalince ta, mace ba a mikar da ita da karfin tsiya, da hikima zaka mikar da ita, a duniya kowa yasan babu shu'uma sama da mace, amma kuma kowa yasan babu halitta mafi raunin zuciya irin mace, matar da kawai da layin baiti daya ka sace zuciyarta, ka gwada mai da gidan ka wani yanayi na daban sai zaman gidan ya isheka. Dan haka nake baku shawara da mu rike abokan zaman mu da amana,. musamman matan mu haka suma matan su rike mazan su da amana wani tsabar rashin tsoron Allah, shi gashi nan dan dukununu. Amma matar shi kullum burin shi ya ganta fess bayan shi bai gyara ta gani ba, idan ayi magana yace feee. Kai kana son gyara amma ba zaka gyara ba, sai kaje waje ka dawo kana zare ido. Wallahi sai ka ga sani namijin ya sami mace kamar jaka, bayan yana da kanwar shi da Yar shi idan kaga anyiwa kanwarka ko Uwarka zaka ji dadi wannan abun fa Simple And easy ne kana tab'awa ko kaho ne a kanka sai an rama,mafi alkhairi karka cutar da yar wasu kai ma Allah sai ya tsare naka,karka yarda ka tab'a domin za a rama mata, kai ko zina ce sai ka biya shi, balle cin zali me sauki ne a rama mata."

Yayi nasiha sosai ga ma'aurata, sannan aka tashi taron Anum tayi laushi kamar ba ita ba, burinta ta isa gidan ta gaji, da wannan tsayuwar.

"XOXO baki ga kayanta bane yayi kaya da" tsuka tayi, sannan tace.
"Ba kayan bane matsala ta, auren ne bana son tayi, asali ma Ni bana son Anum ta sami cigaba da nutsuwa a rayuwarta, gani nake zata wuce ni. Duk inda nake tsammani samun damar nasara sai na ga Wancan tinkiyar ta wuce Ni.

. Waye ya tab'a kawowa Wancan me shayin zai yi abinda yayi mata,walimar nan da abinda za a raba shi ya dauki nauyin shi.

Gaskiya iyayen ta, ba karamin shige shige sai da suka sa shi mata b'arnan kudi, ya kika ga idan na lalata kome auren ya dawo kaina?"

Cikin tsoro da ruwan ciki, tace.
"Eh mana haka yayi, aure me shayin."
"Ke na aure me shayin zaki ce, ba mu aure ba, ki gane, tarawa da ragewa indai ba so kike nace anyi asarar tara ba."

..... Ana gurin Walima su Aunty Binta da matan kanenta suka nufi gidan da Anum zata zauna, matan abokan maude suka bude musu, mamaki ne ya kashe su, sakamakon ganin yadda ka tsara cikin gidan kamar a g.r.a ko wani unguwar bauchi.

A hankali suka shiga cikin gidan suka yi, cikin uku daya na gefen shi wanda aka raba da kofar glass, har kana iya hango falon wanda aka zuba mishi kayan alatu, domin wata babban cinema tv ne a falon. Sai wasu irin kujerun alfarma wanda ya watsa su a falon tare da labulen da zaka gani kasan cewa ma mallakin kayan gurin yasan meke damun shi.

"Toh kenan ai da ya gaya mana falo biyu ne da..."
"A'a kin ya shigo gari cirani dole ya nunawa duniya shi din yana son auren yar kasa." Inji matar Musa, wato Zeenatu.

Kallon ta Aunty Binta tayi sannan tace mata.
"Bana son rashin hankali!"
Sannan suka nufi kitchen, inda shima aka mishi tsarin shi irin na yan gayu, kai gidan ya tafi da Zuciyar Aunty Binta har take gaya musu idan.

A hankali suka shiga gyara gidan, dama an kawo kayan tun shekaranjiya, dan haka aka shiga kimtsa ko ina, tare da shirya kayan, masu saka labule suka zo aka saka dasu.

Sosai suka kintsa ko ina, kitchen biyu yayi mata, akwai wani a tsakar gidan wanda ya kasance ma daidaici ne.

Sai bayan gidan tsakar gida yadda ba za a dame su a cikin gidan ba, akwai daki ma a tsakar gidan, cikin kuma dakuna uku ne daya na shi daya nata, daya kuma an zuba kayan da ba zasu yi amfani akan lokaci ne, dan haka bayan sun gama wajen karfe bakwai suka rufe gidan, sun kashe kudi na fitar hankali domin gas ɗinta babba ne, har zata iya gasa Cake.

Sannan suka fito zuwa gida, suna shiga suka same Baba Hama tazo, tana ta faɗa.
"Wato Bello dan bani da kudi shine ba zaka gaya min zaka aurar da yar ka ba, sai dai naji labarin a wata uwa duniya."

Nan tayi ta fad'a, Malam da Baba Hama, y'ay'an maza ne, dan dakin su malam shi daya aka haifa, amma yana da yan uwan kuma suma sun zo wanda suke Uba daya. Dake mutum ne me zumunci take gidan ya cika da yan uwan da abokan arziki.

Anum tana kwance akan cinye shi, ta daura kanta akan cinyar shi. Sai kuka take, tab'e baki Baba Haka tayi sannan tace mishi.
"Toh Bello idan bata sabon auren sai ta zauna kujika ta kamar kanwa."

Shafa kanta yake, cikin murmushi.
"Anumullah! Kukan ba zai kare bane? Idan kina kukan sai naga kamar akwai abinda na tauye miki! Kiyi shiru kinji, kije Allah ya tsare gabanki da Bayanki, Insha Allah babu namijin da zai wulakanta min ke da Izinin Ubangiji.
Ki zauna dashi da zuciya d'aya Allah zai albarkaci zaman ku. Bana son kawo ƙara, bana son rashin kunya, ba sa'anki bane ki girmama shi kamar yadda Ummanki take girmama al'amarina." Yadda yake mata nasihar sai jikinka ya mutu. Bayan ya gama aka kaita dakin Umma, da take ciki uwar daki.

Kallonta Umma tayi jikinta yayi mugun sanyi, musamman da ta fahimci halin da yarinyar ake ciki, shafa kanta tayi sannan tace mata.
"Zauna ku kuma, ku bani guri."
Fita suka yi, umma ta kawo mata, ruwan addu'o'in sannan ta d'iga zuma, ta bata tasha kafin ta kuma dauko wani ruwan rubutu, ta bata tashanye. Sannan a lokacin ta dauko kunun tsamiya ta mika mata, tana sha tana kuka.
"Kina son kullum ana kawo miki kunun tsamiya da na gyada ne?"
"Eh Umma na,"
"Dumame fa?"
"Duk abinda zai fito hannunki ina son shi!"
Shafa kanta tayi sannan tace.
"Malam ya shirya miki bazata, amma kuma yace sai kin zauna lafiya a gidan mijinki, idan kuma kika ki zama toh ni dai ban san me zance ba, amma zaman da zaki yi a dakin mijinki shi zai baki damar samun wannan abun.

Karki yarda kiyi abinda zai fasa miki kyautar, babban kyauta ce kuma, Allah yana kallonki idan kika zalinci mijinki, ba zai barki." Umma tayi mata nasiha me matukar shiga jiki, kuma dama malam aikin hajji ya biya mata, shine abinda yayi mata na aure domin kome yayunta sun mata, babu abinda zai mata sai dinkunan ne da ya sayo atamfofi ya zuba mata su..yasa Rulwanu ya kai gurin telanta basu sani ba.

A yanzun ma lace din jikinta na shine wanda yayi mata a cikin kayan, bayan ta fito dakin Umma, hannunta dauke da wani zoben gwal din Umma.
"Anum me kike so a dakin?".ta tambaye ta, tare da danne kukarta. Dan itama tun Anum bata tafi ba ta fara kewarta.
"Umma na, babu"
"Duba dai ba zaki rasa ba"
Haka ta tashi ta duba nan ta duba can bata sami kome ba, sai sauka da idanunta yayi akan zoben gwal din, a hankali ta kalle ta tana zubda kwalla tace.
"Ba zaki bani ba, umma Na!".
"Me kike so?"
"Zoben hannun.."
Zare shi tayi tare da saka mata, dama Aunty Rabi ce ta saya mata, dan dukkan su, sun saya mata, haka ta saka mata, wai ita Umma a nata tunanin idan tayi haka yarinyar hankalinta zai kwanta da gidan mijinta, kuma haka take fatan samu.

Bayan sun gama, aka mikata dakin Maman Aminu.
"Ni bani da Abinda zan gaya mata, kome ba, tasan abinda na umarceta idan ta kiyayye ni da ita zamu zauna lafiya, idan bata kiyaye ba. Toh ai tasan sharadi na."

Daga haka ta koma d'akinta, kallon bayanta Anum tayi, tare da sauke kanta kasa, da idanunta da suka yi jajjur. Allah ya bata Umma ne domin ta tayata kuka, haka kuma ya bata Maman ta domin tasata kuka, ta zab'i muradun zuci sama da ita kanta, ta nuna mata ba lallai bane dai.kayi abinda zai faranta ran kowa, matukar zaka faranta ran ka.

A zuwa yanzun ta Fahimci wacece Umma Mariyah, wacce Mama Hauwa, jin hannun Abubakar a kafad'arta ya sata sake kuka. Haka yayunta mazan wannan ya rike ta, wannan ya kamo hannunta, koda aka fita kis ta, basu wuce da ita gidan ta ba.
. Sai da suka zaga da ita ta tashan babaye tare da zagayowa ta titin baba sidi primary school, suka fito ta kofan ran sannan suka nufi unguwar su, aka kaita gidanta, da kansu..suka sakata a tsakiyar su. Har cikin d'akinta. Tare da zaunar da ita a bakin gadon.

Rike Hannun Aminu tayi tare da sauko ajiyar zuciya a kai a kai.

"Autar malam! Ki zauna lafiya da mijinki kinji, duk abinda kike bukata kiyi min text zan turo miki ko na zo da kaina,."

Haka yayunta maza kowa yake mata alkawarin zai mata kaza idan ta zauna, tayi kuka tayi kuka. Tana ji tana gani suka tafi abinsu, su kansu kukan tausayin ta suke domin sun san baya ga dole da aka mata, tana bukatar rarrashi.(wai nace Anum din yar wofi 😉

Bayan sun watse aka barta da daga ita sai Shukrah da Jidda yar Aunty Rabi,sai Ummita yar Abubakar ta fari me sunan Umma. Fatimah yar Aunty Aminatu. Haka suka cika dakin cass, ana ta hira.

Suna zaune Ila ya kawo musu,abin tab'awa tare da katon leda cike da nama, sai jug me dauke da tea, sannan yace.
"Don Allah Anum tazo Maude nadin ganinta."
Shiru tayi sannan...
[2/2, 9:41 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN DA BIYAR

"Aunty Anum, tashi kije."
"Babu inda zani"
"Toh aikuwa bari na kira Umma na gaya mata" inji Ummita.
Da sauri ta mike har tana tuntube. Kamar zata fadi.
Dariya suka saka mata, yada suka ce zasu gayawa Umma ta mike a tsorace.

Fitowa tayi ta hango kofar glass din tagan shi zaune yana kallon tashar kwallon kafa, tsaki tayi ƙasa ƙasa, sannan ta shiga cikin. D'ago kan shi yayi tare da kallon ta.

Ban tab'a ganin abinda ya hanani sukuni ba kamar ki ba! Alhamdulillahi da na same ki a matar aurena
Dauke kai tayi tare da zama a nesa da shi. Tasowa yayi tare da rufe kofar glass din sannan yayi jifa da key din, Allah ya gani ya jima rabon shi da mace. Dan haka ya yake jin zai rage zafin shi yau koda kuwa zata hana shi buga wasan farko ne.

Dawowa yayi ya zauna a kujeran da take zaune me cin mutum daya, toh ba wani auki ne da ita ba, dan haka ya zauna tare da matseta. D'ago kai tayi yaja mayafin da aka rufe kanta dashi, kallon juna suka yi sai ta ga yayi mata wani gandarere, bakin shi taji a goshinta, kafin ta Fahimci me yake nufi tuni ya sauko kumatunta, ya shiga bata wani erect kiss, wanda yayi mata shigan ba zata.

Rike shi tayi cikin kuka, domin yadda yake bata hotters kiss gaba daya yana niman daukewa duniyarta alfarma ce. Kallon shi a matsayin bakauye dab cirani ya tsayar mata da kome domin wani makahon rarumar da yake mata, ita kanta ko a bakin Xoxo bata tab'a jin wannan abun ba, domin wuta wuta yake gabatar mata da kanshi. Kukan da take yi ne ya dauke cak domin ba zata ce ga asalin abinda take ji ba na wasa bane.

Ji take kamar ba a duniyar mutane take ba, rike hannun shi tayi cikin kuka da bori tace mishi..
" Ya isheka! Wallahi ka tab'a ni kaji na rantse da Allah ka bani lasisin shiga bariki kenan, Kuma da igiyar aurenka."

Hade bakin su yayi tare da nuna mata ba bariki ba, ta shiga duniyar a guje, ya bata damar haka, kafin kace me maude ya(😂😉😂) ya haura katangar yar gidan Malam, sai dai ganin yadda take kokarin kwace kanta tare da fashewa da dariya tace mishi.
"Wallahi ka kuskura ka tab'a min budurci na, sai na fita nabi wasu mazan da aurenka, idan kuma kana ganin karya ne ka tab'a min shi"

Ganin yadda take maganar tana kallon cikin idanun shi yasa shi gasgata zata aikata,
"Dama nasan jikina ne abinda yasa ka nace me yasa baka gaya min tun a waje na baka shi ba, idan ka cika d'an halak ba shege ba, karka kuma kallona da sunan wani abu. Anga yarinya karama zaka kwanta da ita ko kunya baka ji ba, geme geme da kai, kaci zamanin ka,.kuma kaci na wani."

Tashi tayi ta saka kayanta, shi ba ma ta ita yake ba, kawai yana nazarin abinda malam yace mishi ne, lokacin da aka kai sadakinta, kenan duk rashin hankalin da take babu namijin da ya tab'a kusntarta lallai Anum taci saba'in har da kari.

Dan haka yana kallonta take kara gyara zaman kayanta da yashashen kamfenta da ya wular can gefe guda, ta dauka tare da sakawa akan idanun shi. Irin zan saka a gaban ka duk abinda zaki yi kayi, nice dai kwalelenka.

Shi kuma abinda ya bashi mamaki lokacin da tace mishi zata shiga bariki, shine ya nuna mata shi din namijin duniya ne ta shiga duniyar.

Kawai ya shiga rabata da kayanta, tare da isa(Kutmelesi 😉 inji me leke) dan haka yana zuwa kawai ya fahimci kome dai dai yake zamzam () tunda ya fahimci koda ya haura katangar akwai nisa tsakanin ƙasa da katangar, idan ya nace sai ya haura tabbas katangar zata fado dashi.

Dan haka ya zuba mata ido, har ta bar falon shi, yana kuma jin kaunarta a ranshi, tare da jin zai iya zama da ita a hankali zata hakura da kome suyi zaman auren su.

--- tana komawa dakin taga duk sunyi barci ban dakin da yake manne da d'akinta ta shiga taga babu wani ruwan kirki dan haka tayi hikima ta yi wanka domin a saninta dai abu ya fita a jikinta kuma tana jin ciwon yadda ya nemi tab'a lafiyar katangar, ( ) haka ta gama tare da fitowa daga ban dakin ta nufi gurin da zata kwanta, tana jin babu dad'i a.
....
Washi gari.
Da sassafe sai ga Hafsat, ta shigo kallon Anum tayi wacce take ta barci tashin yan matan tayi tare da tura su gida, suna fita ta zubawa Anum ido.

"Kin san me ya kawo ni? D'azun nake jin wai maude ya kai karin Sadakinki tare da wasu kyautatta, kina nufin kin bashi kanki kenan har yasa haka? Toh Mama ce ta turo ni, tace na gaya miki kika sake wani abu ya shiga tsakanin ku dashi bata yafe miki ba, kuma zata bar garin nan domin ba zata iya daukar abin kunya ba, duk tattalin da take miki saboda ki auri mutumin kirki ne(lolz su da mutanen mu me kudi shine mutumin kirki, talaka kuwa mutumin banza ne😒) dan haka tana jin zafin

abinda kika yi tace dai kika sake kika dauko cikin shi sai dai ki zauna babu ita babu ke"

Nan suka kuma rud'ar da ita, suka yi ta rudar da ita tare da gaya mata manyan maganganun da zai sakata tsoron karta fada cikin fushin Allah.

---- Kafin yamma gidan ya cika makil da mutane, aka yi wuni da wasu al'adun da ake na aure a kasar Hausa, har yamma ana hidimar. Aka ɗauki kayan Gara aka bawa mutanen shi na nan, har bayan magbri ba a watse ba sai da aka yi sanyan baki sannan suka watse.

Sayan bakin da ya baawa kowa mamaki, dan haka da suka dawo gida suka yi ta raba abinda suka samu.

.... Ana watsawa ta tabbatar babu wanda zai kuma shigo mata ta rufe d'akinta, tayi kuka ta kuma yin kuka, dakyar ta sauke sallolin da suke kanta, sannan ta kwanta.

Yadda yayi tsammanin ba haka ya samu ba, dan haka shima ya share ya wuce shashinsa,

Washi gari da safe, Rulwanu ya mikawa Ila kayan karyawa akan ya kai gidan dan shi kan ba zai shiga gidan ba, domin bayan maude ya kai akwati karami dauke da kuɗi tare da sisin gwal sai wasu shadduna guda biyu, Super vlisco lokacin yana matakin holland biyu English biyu, Super wax biyu, kai tsayar ya ce.
"Malam ga shi karin sadakin Khadijah ce, da yan kunnen, sai kayan shaddar naka ne, sauran kayan na Uwa ma bada Mama ce wato Umma."

Murmushi malam yayi domin bai tab'a kawowa Anum zata amshi wannan kyautar karammawa ba.
"Allah ya baku zaman lafiya. Sannan kayan sunyi yawa."

Murmushi maude yayi sannan yace..
"Da a ce ina cikin dangina ne, sai abin yafi haka, domin ta cancanci dattijo ya bata kyautar rakumai."

Duk sai Malam ya rikice, tare da zuba addu'o'in, ya kai kayan cikin gidan ba tare da ya d'aga hankalin shi ba, ya kira Umma ya gaya mata, ai kuwa ta sake murmushi tace mishi.
"Wallahi Allah shine Sarkin da wani bayan shi, na san Khadijah ciki da wajen ta, ba zata tab'a wasa da kimarta ba."

Nan ta baza kayan kowa yazo yana gani, a take ta raba kome tace a bawa Maman Aminu. Matar nan bata da kunya, tana kallon kayan tace musu..
"Ba zan karb'i kayan da sai da yaji dandanon gi.... Y'ata zai ce zai kawo min kayan tsiyar shi ba, idan kuka amsa sai na tsine muku."

"Auuu! Maman Aminu ai duk abin bai kai haka ba, shikenan ba zan baki ba, bari na rike kayana. Yar Arziki irin albarka yar da aka haifa tsiya tana barci!"
Baba Hama ta rangad'a guɗa abinta, kunga yadda suka mannawa Maman Aminu hauka, sosai anan malam yake kuma tabbatar musu da cewa.
"Aikin hajji Bana da za ayi da Anum za ayi Insha Allah,"

Wai duk kawai ta zauna a d'akinta ne, ai Maman Aminu ta Cigaba da cin alwashin sai ta kashe auren shine ta tura Hafsat tayi mata barazana, tare da kwashe mata albasa me lawashi.
Karshe Kafin a watse daga bikin Maman Aminu tayiwa Umma rashin mutuncin da yaran Umma sai da suka kasa hakuri suka tankawa Maman Aminu.

Musamman Aunty Binta da zuciyarta yake kusa, umma tana sallaman wasu baki taji zagiin Maman Aminu.
"Banda rashin tsoron Allah, a rabaka da d'anka ai rashin imanin yakai karshe, Allah zai bi min hakkina kuma zaki gani!"

"Umma ba zata ga kome ba, ai abinda Umma tai miki idan ke me hankali ne ba zaki ce ta cutar dake ba, amma dake butul..."

Umma bata ga girman Binta da take da manyan yara ba, ta kifa mata mari a gaban jama'a, tana faɗin.
"Zagin abokiyar zamana kika yi? Zagin matar da tayi dawainiyya dake kika yi?

Kin manta lokacin da kika yi ciwo bayan haihuwar Yarki kina zubda jini guda guda, itace take wankewa? Ita ce ta cancanci zagi? Lallai na yarda inda ranka ka sha kallo.

Binta Maman Aminu kika zaga? Toh ba makawa wata rana zaki zage ni, zagi mara iya ka ma, Nagode Binta na gode sosai na gode da kika zage ni, duk abinda ake a cikin gidan nan Aminu da Usman basu tab'a kwana basu kirani since Umma kiyi hakuri musan kina fama da Maman mu, ki kara hakuri akan na da, jiya nan Kafin Khadijah ta bar gidan nan sai da ta kara ce min Umma kiyi hakuri da Maman mu, amma ke da kanki kika zagi Maman Aminu, Toh na haramta miki shigowa d'akina, ba zan cire ki a cikin yarana ba, amma na haramta miki taka inda nake."

Wannan abinda Umma tayi ta kashe jikin Maman Aminu, domin ita kanta bata tab'a ganin mace me karamci irin Umma ba, duk abinda take mata da ita dasu Hafsat bata tab'a da'ga ido ta kalla ba, yau yarta na cikinta ta rama mata, amma taki yarda akan haka me yasa halinta ya fita daban?

Sanadin abinda ya faru, yasa sauran kanen Binta fushi suma suka tattara suka bar gidan. Asalima irin haushin Maman Aminu suke ji, amma shakkar Umma yasa kowa ya b'oye yanayin a ranshi, shi yasa koda ya dauko kayan karyawaan ya bawa Ila duk da ila ya girme shi.

..... Da sallama ya buga kofar falon maude ya bude mishi, mika mishi abin karyawan yayi sannan yace.
"Gashi Inji Umma, gaskiya auren nan naka ya bar baya da kura, kuma ya raba zumunta, wani irin abu ne haka a cikin auren nan da ba za a ayi shi cikin nutsuwa ba. Yallabai gaskiya ka rike yarinyar nan da amana."

"Nagode Ila Insha Allah zanyi yadda kace, Ni kaina bana jin dadin yadda kome ya lalace, amma zan gyara kome, tunda Allah ya Hadani da su, kuma naji dadin wannan haɗin. Sai dai kuma ina tsoron kar Ni ne da matsalar rashin.."

"Kai haba Yallabai bana tunanin haka, Allah zai baka masu albarka, karka yarda ka jingina auren ka da wannan ƙaddarar, sabida shi wannan mizanin shi daban wannan kuma shima haka, Allah ya baku zaman lafiya da zuri'a dayyiba."

"Amin Ya Allah, Nagode sosai Ila kayi min kome a rayuwa, k tsaya min ka bar naka rayuwar ka tayani duba tawa rayuwar, Ila ban san dame zan saka maka ba"

"Allah ya bani damar kyautatta maka, Yallabai ban biyaka abinda ka min ba, ba dan kai ba da Yanzun na zama wani iri a cikin al'umma. Nagode sosai"

Daga haka ya juya ya bar gidan, rike basket din yayi tare da nufar part dinta, yana zuwa ya buga mata, sai da ya buga kofar sau uku kafin ta bude.

Sanye take da wani shegen wando ya matseta sai rigar haf vest, wanda ya kara fito da dukiyar fulaninta. Mika tayi tare da kallon shi tana hamma.

"Lafiya ka zuba min ido kamar tsohon mayye?" Ta tambaye shi tana murguda mishi baki.
"Tare da ke tsuhuwar mayya, naga kayan hutu ai dole na sake baki, yarinya ki barni na huta dake kiga yadda zaki kara girma da cikowa, kiga yadda wannan abun kirjinki zasu cika famm"
"Har duniya ta tashi ba zaka tab'a samun abu daga jikina ba."
"Wai, ina da matan da suka fiki fa....
□□□ ku dunkule hannun, ki dale katanga..
#Mai_Dambu
#Mai_Dambu...v[2/2, 9:50 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN DA SHIDA.

Murmushi yayi sannan yace mata.
"Ni nake da rabo a jikin ki, sai dai idan kaddarar mu bata hade matukar tana hade ba makawa sai na tsaya akanki!"

Ya fadi haka yana tab'o kumatunta, buge hannun shi tayi kasa kasa tace mishi.
"Mayyen mata!"

"Mayyar maza!"
Ware idanu tayi tare da dalla mishi harara, murmushi yayi a karo na biyu, ya juya ya barta a gurin sai lokacin ta lura kusan shiga d'aya iri daya suka yi, shima kayan kananun ne a jikin shi, ga muscle din shi ya firi sosai, yana tafiya irin na giant men irin kosassun mazan nan ne Maude.

Dan tasha ganin shi yana d'aga karfe me nauyin buhun siminti. Dauke kai tayi tare da tsaki, juyawa yayi yana kallonta, bai ce kome ba, sai dai kawai ranshi ya tab'o da tsakin ta dan haka ya dawo bakin kofar dan har ta koma cikin dakin, buga kofar yayi tare da tsayawa.

Tsigai kuwa ta bude kofar cike da masifa zata balbale shi ya fincikota, tare da had'ata da bango, ya hade bakin su guri guda, ta dake shi ta yakushe shi, ta ture amma bai sake mata bakinta ba, ba tare da tasani ba, mutumin har ya kwab'e mata dan boxes ɗin ta, sai da taji Yaren toh toh bance ba amma kuyi nazarin abinda yake shirin aikatawa.

Kokuwa ta fara yi dashi tana dukar, ɗaukar ta yayi cikin nutsuwa ya wuce da ita d'akinta. Duk yadda taso kwatar kanta, ihun da take tare da buge buge yasa maude ya zuba mata ido yana kallon yadda kirjinta yake rawa, wani irin desire yake

ji akanta tare da bijirowar al'amura masu matukar girma..dan haka ya shiga lallabata ko zai sami kanta,. amma fir taki..

Haka ya kyaleta, ya dawo dakin shi tare da bude wata karamar jakar shi, ya dauko magani a gwangwani, ya zuba a bakin shi tare da ruwa ya sha, sannan ya koma ya zauna a bakin gadon shi.

.....
"Kar naji kar na gani wani ya taka gidan Khadijah! Idan na sami labarin zan sabawa mutum" inji Malam yana bugawa mutane kashedi. Dan haka kowa ya kama gaban shi, masu tafiya garin su na tafiya masu nufar gidajen su na tafiya.

Yaji aka kawowa Umma ta gyara zaman shi a cikin wani katon langa tsirara, sai dambun da Hajiya hashiya ta kawo mata, na kasa, shima ta juye shi ta shiga hada kayan kamshi na shayi, tana sallaman bakinta tana faman hada kayan kamshin da za a kaiwa Anum.

Tana gama juyewa a cikin langunar, ta kuma koma d'akinta ta dauko yajin daddawa yar asali, ta juye shi sannan ta nufi kitchen ta dauko maganin sanyin da take daga mata ta zuba mata a cikin robobin. Abubuwan da suke cikin bokatayen har da ma shanu.

Garin kukar miya, garin bushashen kubewa, sai bushashen kifin da aka kawo mata daga biyu kanwarta Innah Saroh, lekowa malam yayi sannan yace.
"Umman Anum! Akwai zuma naga kina bata ko na kawo mata ne da kwan zabi, malam buba daga birshin Fulani ya kawo min wai bai ji labarin auren ba sai yanzun."

"Eh kawo malam ai na hada mata kome, zuwa jibi sai a mika mata." Inji Umma, "Nagode sosai Mariyah."

Murmushi tayi sannan ta cigaba da aikinta.
"Assalamun Alaikum! Umman Anum ina wuni!"
"Waalaikumun Salam, Mahidah ya Mamanki?"
"Lafiyan ta lau, wai ga turaren bai iso bane sai d'azun wai don Allah kiyi hakuri, bata san cewa haka abin zai dauki lokaci ba."

Murmushi Umma tayi sannan tace mata.
"Kice matarta damu ai ba yau muka fara ba, sannan kice mata nagode sosai." Ta dauko ledar kulli kulli(kusan anan Bauchi haka muke cewa cin cin, kulli kulli)

Bayan ta bata sannan ta amshi turarukan wutar, dake Yarinayr tare da yara uku tazo, mahaifiyar Yarinayr Hajiya Yanah yar Yobe ce, toh suna islamiyya daya ce da Umma, har tana kawo musu tallar kayan kamshi daga yobe.

Shi yasa umma tabata dubu talatin tayi mata turaruka da humra, sai matar ta tura aka mata a Yobe sabida hadin su nacan zai fi nata dadin kamshi.

Dan haka ta dauko kwalin kwalaben turarrukar wutan ta ajiye sannan ta koma dakin ta Cigaba da aikinta, dake ranar akwai sauran bakin yan biki sune suka taimaka mata ta karasa zuba turarukan a cikin kwalbar su. Ta kuma saka a kwalin yadda za a kai mata.

Ga turarukan tsinke da na sugar, ga irin na Dubai din nan, wai duk sabida Anum din.

.....
Wunin ranar maude da Anum kamar wuta da ruwa, idan ya ganta dauke kai yake, gashi yan cikin gidan kowa yaji ihunta, asalima sai abin ya zama gulma, wasu na tir da ita, wasu na zama su gulmatawa junan su.

Can yamma matan gidan suka shigo mata, lokacin ta sha kwalliya cikin riga da zani na diamond, tai kyau da ita kamar wata yar babyn roba, haka ta amshe su, tare da basu cincin tare da ruwa, suna zaune ya shigo. Ganin ta shantake tana kara sake baki ana hira da ita.

Yasa Atika tace mata.
"Amarya ango ya shigo!"
Murmushi tayi sannan tace.
"Eh na ganshi idan yana. Bukatar abu zai magana."

Haka suka bude sabon hira anayi ana cewa.
"Amma cincin din nan yayi dadi baran ma dubulan din kai, alkakin ma yayi dad'i."

"Toh ko na karo muku ne?"
"A'a.. ai abin ba yar haka bane."

Ganin suna so suna kaiwa kasuwa yasa ta kuma kawo musu, ta ajiye musu ya fito kallo daya yayi musu fuskar shi babu walwala, take suka mike tare da cewa.
"Amarya bari mu barki haka, tunda muna tare"
"Toh babu damuwa muje na rana ku?"
Dake sunyi gaba, zata saka kai ya fincikota tare da watsa mata kallon banza.
"Zanji dad'in kiyi mu'amala da mutane cikin salama, amma matan gidan nan bana fatan kiyi mu'amala kota kwana ɗaya tsakanin ki dasu, gaisuwa Barka, jejjeto da wasu abu idan ya faru bayan nan ki zauna a idan na ajiye ki"

"Toh Ubana ba zan yi yadda kake so ba, yadda nake so zanyi, a idan Ubana ba a takura min ba banga uban da ya isa takura Ni ba, babu shegen da zai takura min."
Ta faɗa cikin rashin kunya tare a nufar d'akinta.

Bai kulata ba har zuwa lokacin da ya kuma shigowa bayan sallah isha, yana kallonta sai zare idanu take, ta cinye abincin da Umma ta kawo musu na rana, dan tsabar mugunta da taci ya koshi ta juyewa yaran da suka shigo mata, bata san wa kanta tayiwa ba.

Mik'ewa yayi ta nufi kitchen, ya shiga duba abinda zai iya samar masu a daren, tana makale a falo har ya gama ya dauko sanan ya kawo falon ta ya ajiye mata. Yawun kwaɗayi ta had'iye, tare da dauke kai irin me zanyi dashi. Tana game da wayar ta.

Komawa yayi ya gama abinda zai yi ya dawo zai Wuce ya samu bata falon da abincin. murmushi yayi sannan ya haɗa tea din shi ya sha sannan ya had'iye maganin shi, ya jima a zaune a falon kafin ya tattara ya koma dakin shi ya kwanta. Tare da rubda ciki yana nazarin abinda yake ganin zai ficce shi.

. Bayanta gama cinye abincin ta fito da plat din ta ai kitchen, ta samu ya wanke nashi ya kifa, ajiyewa tayi abinta tare da shan ruwa ta koma d'akinta.

Tana zuwa ta kwanta tare da kashe wutar dakin.

--- A kwana biyu kacal da yayi da Anum ran shi yayi masifar b'aci domin ganganci iya ka tayi mishi rashin mutunci kuwa, ko Jikar maguzawa sai haka, Amma cikin ikon Allah bai tab'a bin takanta ba, asalima dauke kai yake da abinda take mishi.

A ranar da ta cika kwana uku, umma ta kawo mata kayanta. Inda ta aiko Jidda da Ummi suka kawo mata. Tayi murna nan suka shiga kitchen suka dafa taliya da mai da yaji, aka baje a falon ana ci ana hira. Lokacin da ya fito daga dakin shi yaji muryan su, da kanshi ya tawo har gurin su, ya fito suka gaisa.

"Madam babu ni ne a cikin abincin." Watsa mishi kallon banza tayi sannan ta mike dan lokacin da zata girka sai da suka yi takaddama da Jidda tace mata.
"Aunty Anum ki fada leda biyu! Sabida Uncle maude!"

"Ke Ni bana son kinibibi." Haka ta dafa dashi, sannan ya zuba mishi kamar nasu, dauko mishi tayi dake su Jidda sun bar falon, dangwala mishi tayi zata mike ya riko ta, hannun shi ya kai kirjinta.

Ta buge hannun cikin tsiwa, sumbatar wuyarta yayi ta ture shi tare da barin gurin shi. Ganin irin yajin da ta zuba mishi yasa shi kowa kitchen ya kuma hada sabon abincin maggi ya zuba tare da mai dashi kan wuta ya yanka albasa ya kuma nutsuwa akan abincin.
"Uncle Maude zamu tafi!"

"A'a da wuri haka, toh ku jirani mana," ya fada tare da fita daga kitchen ɗin. Tsabar mugunta tana shigowa ta zuba mishi gishiri na fitar hankali, haka ya basu kudin dan yasan ai ba a unguwar suke ba, iyakarta bakin kofar, bayan tafiyar su ya koma kan abincin shi. Shigowa tayi tana dariya.

Kamar wanda aka ce ya duba abincin yana sakawa a bakin shi ya lumshe idanun shi, sannan ya zubda, ya nutsu tare da dauko kwan zabin ya shiga aiki sosai, bread ya fita ta amso tare da kifin gwangwani ya zauna yayi wani irin hadi na musamman sannan ya juye a plat.

Ya fito abun shi, a bakin kofar shiga ya ganta, bai ce mata ta tafasa ba balle ta kone, kamshin girkin shine ya hanata zama dake kwaɗayi yayi mata katutu.

Cikin rashin kunya ya nufi falon shi, yana zaune ya hada tea, daukar kofin tayi ta fara kurb'a, sannan ta kai hannunta kan abincin ya fara ci. Kallon shi tayi cike da mamaki.
"Waye ya koya maka girki haka?"
"Kauyen mu na koya!"
"Hmm! Amma kuma ka iya yi yayi dadi hakan? Hmm! Yayi kyau."

"Ke baki iya girki bane? Ki girka baki mana ki bar min bawa!" Dariya tayi sannan tace mishi.
"Wani kazamin abincinka mara daɗi, dan na taimaka ina cin abincin ka zaka min wulakancin banza."

Bai ce kome ba, dan ya fahimci duk masufarta ba bazata iya bar mishi abincin shi ba, haka suka cinye tare sannan ya mike yabarta a gurin, ta fara kallo kafin barci yayi gaba da ita. Gudun karta zarge shi yasa shi ya barta a gurin, ya koma d'akinta ya sami kayan da Umma ta kawo mata a wargaje.

Daukan shi ya bude kwallayen ya jerasu akan show glass, sannan ya nufi sauran tarkacen ya kai kitchen ya jera su, sannan ya dawo gurinta ya durkusa kadan sannan

ya sumbaci goshin ta, tare da daukarta cak zuwa d'akinta ya ajiyeta sannan ya fita abinshi bayan ya rufe kofar ta.

.....
Duk yadda yaso su zauna lafiya Abun yaci tura, Umma tana bakin kokarinta ita da Malm Maman Aminu da Hafsat suna kara haukata Anum, a hankali rashin mutuncin da take yi ya fara fita yawo, idan tana mishi har waje Ana jin su, wani lokacin fita yake ya bar gidan sai tayi barci yake dawowa gashi ta hana shi hakkin shi.

Haka yake hakuri da ita,.har aka fara shirin azumi, a lokacin watan su biyu da aure amma babu canji, domin Mama na zugata Hafsat ma haka, ga XOXO a gefe.

.. a cikin wannan yanayin malam yazo ganinta, da kanshi domin ta kai mutanen da suke haya a gidan sun fara gulmar anum din, gefe daya mazan suka sami Malam da maganar shiru yayi sannan yayi musu godiya shine yayi zuwan bazata yaji yadda take sheka mishi rashin mutunci. Bai ce kome ba ya juya dan dama bai shiga gidan ba iya karshe tsakar gida. Har sun gaisa da mutanen gidan ya juya ya fita.

Anan Maman Tasnim take buga mata kofa zata yi magana sai ga sallamar Umma.
"Kizo muje."

Hijab ta dauka tabi Umma...
#Mai_Dambu..
[2/2, 5:35 PM] +234 806 041 0931: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN DA BAKWA.

Cikin rashin hankalin taja hijab tabi Umma, tunda suka fita taga wajen yayi mata fadi da girma, suna shiga Malam ya rufeta da duka, irin wanda bai tab'a yiwa wani daga cikin yaran shi ba, duka ne irin na cire haushin da kika bani.

"Wallahi ba zaka kashe min yarinya ba, haka kawai zaka samun yarinya a gaba bayan auren da aka mata na dole, toh wallahi ba zan yarda."

Ko kulata bai yi ba, ya cigaba da dukar Anum, ran malam ya b'aci dan haka dakyar Umma ta dakatar da shi, tana gaya mishi.
"Malam karka yi abun kunya idan akwai lalura a jikinta idan ya tabo me zaka gaya mishi don Allah barta haka bata da laifi."

Wurga da bulalar yayi tare da juyawa ya shiga dakin shi, ita Kuma Maman Aminu ta shige da ita d'akinta.
"Ai karki damu, haka zai gama jarabar shi ya kyalki. Nagode yar albarka, ki cigaba da abinda kike yi babu wanda ya isa miki dole shi kuma wancan munafikin zan same shi har gidan."

. Cire kai tayi tana kallon su Badi'ah, kwalla na zubo mata, ta gyara zaman sannan tace musu.
"Ban san yadda zan gaya muku ba, amma tabbas zanen kaddarata tayi mugun shatamin abubuwa da dama, wanda akan maude ya sauka, da ace ban dauki shawaran mutane ba, da har yanzu ƙaddarar tana nan tare da juna, dan haka ku cigaba da sauraren yadda na fatattaki masoyi na, na kama masoyan bogi"

Sannan ta cigaba da basu labarin kamar haka.
Haka Maman Aminu ta cigaba da nunawa Anum hanyar da ba zai bulle da ita ba, sannan ta haɗa mata ruwan zafi ta shiga wanka, tana fitowa ta sami Umma a bakin rijiya tana diban ruwan aiki.
Sake bokitin tayi tare da matsawa kusa da Umman, zata mata magana.
"Nana KHADIJAH! Jeki don Allah bana son damuwa"

Sake matsawa tayi zata kama gugar ta maza ta sake a rijiya, ya faɗa gaba daya har da igiyar da sauri ta d'ago kanta tana kallon Umma. Zata mata magana.
"Karki damu, Rulwanu zai cire min..kawai ina Son ki cire Ni a cikin rayuwarki ne kamar yadda gugan nan ya fada da igiyar shi!

Bana son na kuma jin kin kira Ni da Ummanki, Nana KHADIJAH kije kiyi rayuwar ki yadda yayi miki, matukar Ubangiji yana sane da abinda kike Allah sai ya fidda kowa hakkin shi, idan na rike ki da Amana sai Allah ya fidda ni idan kuwa kece kika zalince tarbiyyar da na miki Anum nasan baki na ba zai kama ki ba, Amma gamu ga duniya da abinda yake cikin ta."

"Ikon Allah! Maman Sadeeq baki kike sarawa yarinya na, toh Insha Allah ya sauka akan ku keda Yaranki." Tazo ta ja hannun Anum suka kamo dakin su.

Ranar da dare Maude yazo ya dauke ta, bai ji dadin dukar da malam yayi mata ba, asalima rarrashinta yake, tsabar damuwa yayi mata yawa, nan take gaya mishi abinda Umma ta gaya mata, tana kuka.
"Maude ni ba wai bana son ka bane, kawai as my husban ne ban karb'e ka ba, kana da abubuwan da duk macen da ta gani zata bukata, amma bana son haka, kawai ka barni na tafi nayiwa Mahaifiyata biyayya."

Kallonta yake kawai ya rasa me zai mata, har suka kwanta kowa da abinda yake damun shi, Umma ranar kwana tayi idanunta biyu, tana mamakin yadda Maman Aminu take son kashe auren yar karama yarinyan irin Anum,

Bata kuma tsinkewa ba, sai da taji tana waya akan akaawo mata abinda zata rufe bakin mutane akan Anum, nan ne ta yarda da duk wanda Allah ya fitar daga ragamar shi karka ji mamaki.

Bayan kwana biyu, Umma ta zama yar kallo, domin tunda taji labarin abinda zata yi ta daina cin abincin duk ranar girkin Maman Aminu, asalima tsiro da azumi tayi, haka ya taimaka mata ainun. Wasa wasa malam ya zama hoto akan sha'anin Anum.

Dan tun bayan komawar ta, suka fito da wani mugun abu, shine daukar Anum zuwa unguwa, ko taje gidan yayunta tayi kwana biyu, musamman wanda suke uwa daya Uba daya,

Maude bai hana su ba,.dan da farko yayi yunkurin dakatar dasu. Amma Maman Aminu tayi mishi iyaka bayan ta hada shi da shugaban yan Nijar na garin bauchi. Tunda suka fara magana bai d'aga kan shi ya kalleta ba. Sai ma zubawa kasa ido da yayi, goldrn eyes din shi sunyi jajjur, har wani oily. D'ago kai yayi lokacin da shugaban su ya kira sunan shi.
"Kaji abinda surukarka tace."

"Naji babu damuwa."
Yana fadar haka ya mike zai fita.

"Da sake min Y'ata yayi hankalina zai kwanta."
"Ba zan sake Khadijah ba, idan kun matsu ku kai maganar da mahaifinta idan yayi magana zan san abinyi."

Daga haka ya bar musu gurin, ya koma shagon shi. Tun lokacin ya zuba musu ido.
-
"Anum ki bani set din aurenki Insha Allah zan baki daga baya baban Annur ne kasuwa ta juya mishi baya, Insha Allah idan kome ya mishi kyau zan dawo miki dashi." Da sauri ta mike tana cewa.
"Ayya babu kome, wallahi."
Ta dauko tare da bata, tun daga ranar da ta fita suka shiga, mutunci a nutse ana cin zarafin Maude..
Ajiyar zuciya ta sauke tare da kallon su, hawaye na zuba mata tace musu.
"Mun zalince maude fiye da yadda baku tsammanin, mun cutar da shi."

Sai da ta kai hatta ruwan shan gidan shi ya fi karfin shi zunzurutun tashin hankali da rashin zaman lafiya, gashi a cikin gidan gulmar suke.

Umma da kanta ta kira shi suka yi magana, tare da bashi hakuri. Sannan ta sami Malam yace shi babu abinda zai iya yi akan sha'anin Anum, su je suyi kome ma yayi musu.

Musa da Bashir suka fara nasu rashin mutuncin, ta hanyar bawa maude notes ya tashi musu a kofar gidan su, shi kuma basu suka bashi damar zama a kofar gidan ba, Abubakar ne dan haka ya same shi da maganar, shima ya sami Malam da abinda yake faruwa.

Malam bai ce kome ba, sannan ya tara su a kofar dakin shi.
"Kun ce maude ya tashi akan wani dalili? Kawai dalilin nake bukata idan kuka fada nima zan baku goyan bayan ya tashi!".

Shiru suka yi tare da sunkuyar da kan su..
"Idan dan mahaifiyar ku ce, toh idan na yanke sauran igiyar da ya rage zaku sami me saka ku kare shi? Toh zan kore maude a bisa sharadin zan sake mahaifiyar ku har abada."

"A'a malam haka duk bai taso ba, Allah ya huci zuciyar ka. Ya sha zaman shi."
Aikuwa ya kafe sai ya kore maude, suka shiga bashi hakuri. Duk yadda suke tsammanin abu ya ci tura sun nemi Umma tace babu ruwanta suyi duk abinda ya dace..ta kuma umarci Abubakar ya fita cikin maganar su idan ba haka ba, zata saba'a mishi.

Umma da yaran ta sun zubawa Mman Aminu da yaranta ido idan ka cire Usman da Aminu, da suka zare hannun su akan sha'anin Anum da Maman su.
A irin wannan yawon banzan suka tafi wani gidan suna aka saci gwal din me jego aka wurga a jakar Anum, da aka zo dubawa aka samu, karshe sai da aka dangana da police Station na , hankalin Hafsah yayi mugun tashi dan haka ta nufi gidan ta gayawa Maman ta.

Dake bata da hankali sai gashi tana ihu, tare da fadar Abinda ya faru, Umma tana jin su bata ko tofa ba, har suka tafi..bayan awa daya, suka kuma dawowa wai an tura su kotu.

Da Malam yaji haka, koran Maman Aminu yayi tabar mishi gidan shi, wasa wasa ana ta boye abin dan kar Maude yaji,.a hankali maganar ta kai dare wajen karfe tara na dare malam ta gaya mishi abinda ya faru. Bai ce kome ba, ya koma gida ya kwanta, sannan ya tashi ya buga mashin din shi sai police Station. Nan ya shiga ya samu wasu yan sanda biyu, maza a bakin table din sukayi magana.
"Wayyo Allah na, don Allah ku kyale ni wallahi Ni ba yar iska bace, kuma ban dauki abin wuyarta ba."
Cakume wuyar yan sanda yayi cikin fusata ya daka musu tsawa.
"Waye a tare da mata ta?"
"Yallabai, d.p.o ne kayi hakuri." Wular dasu yayi tare da nufar cikin da gudu. Ya samu jibgegen ya mata rumfa zai hake mata, ai kuwa ya shiga mishi lugude, sannan ya d'ago matar shi suka fito. Ganin yadda suka kasa tabuka kome har maude ya bar Office din, yana fitowa ya haura babur din shi ta dafa kafad'arshi. Dauke kai yayi dan ji yaƙe kamar yayi ta dukarta, bai san ya zai yi da Anum ba.

Lokacin da suka tawo gida, ya wuce dakin shi, a ranar da dare ya shigar da karar cin zarafin matar da akayi tare da tura dokokin kasa da ƙasa, karewa har da dokar yan sanda da na sojojin kasar, a take aka dakatar da yan sanda, dama bawai za a tura su kotu bane, tunda d.p.o yaga Anum yaji abin ya zo mishi.

Toh bai sami Anum ba,an dakatar dashi..
--- kwana biyu da faruwar haka ya fita zai shiga kitchen, ya same ta tana kallon fim a falon ta, dan tunda abin ya faru ta rage yawo, kallon gefen fuskarta yayi wanda yake kwance da jini. Sannan ya dauke kan shi.

Ya shiga tare da hada abubuwan da zai tafita ta kalle shi.
"Wai da gaske Malam bai da lafiya?"
"Eh yana can rimee Clinic!" Ya bata amsa a takaice,
"Toh don Allah meke damun shi?"
"Wai sunce hawan jini"
"Toh, yaushe zan je!"
"Keda kike auren kanki ai zaki iya zuwa ko ina."
"Ban gane ba!"
"Ok wancan lokacin da dan sandan ya kwanta dake babu abinda ya dame ki ba?"

Shiru tayi tare da sunkuyar da kanta, tana wasa da hannunta.

"Amma maude wannan bawani abu bane da zaka saka ranka akan shi" ta faɗa mishi tare da tsare shi da idanunta..
"Eh ba wani abu bane a gurinki, Ni kuma igiyar aurena fa? Me zaki ce min idan aka tab'a min kimar shi! Koda yake aikin ce zaki shiga bariki idan na tab'a fatar da kike ajiyewa me kudi ko?"

Daga haka ya barta tsaye tana bin bayan shi da ido, kitchen ta shiga ta fara niman abinda zata saka a cikin ta, domin bata san yadda zata iya sarrafa wani abincin bayan taliya ba, kai ta dauka ta shiga soyawa, tana gamawa ta haɗa tea sannan ta fito falon, tun zuwanta gashi an kusan shiga azumi bata tab'a girki dan ta ciyar da maude ba, amma idan yayunta mata zasu zo.
Tare da Nafisa suke aikin abincin, Nafisa yar makotar su ce a cikin gidan take zaune ta iya girki dake tayi aiki a Abuja...

Haka ta gama karyawa ta zauna tana jiran ko zai ce ta shirya bai fito ba, sai da ya gama abinda yake zai tafi shago tace mishi.
"Maude jiranka nake fa!"
" Toh maza ina jikin ki, sauri nake!"

"Zuwa asibitin!"
"Baki na da iko da kanki ba, ko ke baki san cewa kina da damar yin yadda kike so bane?"
Daga haka ya juya yi fitar shi.

--- yana fita, ya gamu da wata mata tana jan yaron ta zuwa makarantar rariya primary school, sai ihu yake yana tirjewa..
"A'a barshi zan tafi a hankali."
.cike da b'acin rai ta juya, kamar zata yi kuka.
"Idan na sake shi guduwa zai yi!"
"Toh ina baban shi."
"Allah yayi mishi rasuwa shekara daya kenan."

Shiru yayi yana ganin zata cigaba da jan yaron yace mata..
"Bar shi zan kai shi."
Riko hannun Yaron yayi tare da nufar makarantar da shi, ya saya mishi sweet da cheese,.ya saka akwandon makaranta yaron.

"Idan ka taso zan zo daukar ka, kuma zan saya maka kayan daɗi amma sai kayi karatu fa"
"Zanyi!"yaron ya faɗa a sanyayye, sannan ya sauke shi....
#Mai_Dambu
[2/3, 8:57 PM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA ASHIRIN DA TARA

Tun farko na gaya muku labarin nan True life story ne! Dan haka a cigaba da bibiyar Labarin □□□□

Bai damu da yadda zai tarar da hajjo ba, haka ya dauke ta suka fita rungume da ita, zai kaita dakin shi tace mishi.
"A'a barni na koma d'akina."

Shigar da ita d'akinta yayi, tare da ajiyeta.
Har zuwa lokacin idanunta rufe tana kuka.
Dakyar ya samu ya tayi shiru, sannan ya fita, bata kuma ganin shi ba, sai jin muryan shi yana hira da Hajjo, shima a bangaren shi duk yadda yaso zuwa ya dubata abin ya ci tura.

Dan haka ya ajiye batunta ya shiga kula da Amaryan shi. Wajen karfe biyu na rana tayi wanka ta shirya tsaf, sannan ta fito dan ta kasa jefa wani abu a cikin ta, tana fitowa ta samu an mata kaca-kaca da falo, bata damu ba, ta dauki tsintsiya da parka ta share falon tass, domin akwai wani abu da yake karawa Maude son Anum tana da tsafta,

Duk da bata iya girki ba, saidai tana da tsafta me ban sha'awa,domin ko shigowa kai d'akinta ka fita zata bika da sharan ka.

Hango su Hajjo a falon shi yasa ta sauke kanta, dan baya nan. Ita da mutanen gidan, da gayya suke d'aga murya suna cewa.
"Wasu matan ai gantalallu ne, sun gama raba kansu a waje."

"Maman mansurah Kinga yadda ya hauka ce jiya, kai namijin da ya iya da mace karshe ne"

Shiru tayi tare da dauke kanta, tana abinda yake gabanta.
"Ai wasu iyayen su, jahilai ne. Ko a tarihi ban tab'a ganin uwar da zata raba yarta da mijin da take aure ba, koda yake an ci kudin shi gudun kar a zargi tsohon da son kai," inji Hajjo.

"Tsohon banza ba!"
Wani irin duhu ne ya lullube mata idanu. Da gudu ta koma d'akinta tare da zuɓewa a kasa tana kuka.

..... Da farkon Auren Anum ta fara watsar da al'amarin Mamanta, domin kwanakin da ta gama al'adarta zata koma gare shi su fahimci juna, sai dai me?

A cikin abinda bai fi awa daya ba, zuwan HAFSAT da fadar da suka yi da matar Maude, har ya kai Maude da kanshi ya hana Hafsat zuwa gidan shi dan tace.

"Ke masifa ce a rayuwar Khadijah, babu Alkhairi a tare da zuwaki gare ta, kar na kuma ganinki domin zan dauki mataki akan haka!"
"Maude yaya ta ce fa, kake gayawa magana son ranka?"
"Anum ba zaki gane wacece ita ba, cutarki take, kuma wallahi daga ranar da ta ga baki da amfani zata gudu ta barki."

"Haka muka fita da Hafsat duk da ya hanani fita, akan kar na bita, amma haka na saka kai na bita" kallon su tayi ganin yadda suke kuka wiwi, kamar wanda aka gaya musu anyi mutuwa.
"Aunty Anum, me yasa?"
"It's about Destiny, it's my Destination, babu abinda zan iya fahimta ina shekaru sha shida hauka da rashin hankali yayi min yawa, i luv my husban fiye da kome amma na kasa fahimtar kome akan shi, yayi kokarin shi iya kokarin shi amma ban fahimta ba, kunga Ni na gaji gobe zamu daura."

"Don Allah kiyi hakuri karfe sha biyu ne na dare ko zuwa biyu zamu tafi!"

Suka fada kamar zasu yi kuka.
"Toh naji amma kunsan me? Shin duk abinda yake faruwa laifin waye?"
" Da farko akwai laifin Malam! Na biyu Laifin Maman Aminu! Na uku Laifin Yayunki! Na hudu toh gaskiya ban gama hango laifinki ba."

Dauke kai nayi hawaye na zuba, daga idanuna,
"Tabbas sun taka rawan gani a rayuwa ta, amma ku biyo Ni kuji abinda na aikata."

--- tunda ga ranar da tabi Hafsat bai kuma magana ba, asalima ya zuba musu ido ne dan saura kwana ki ƙalilan a fara azumi.

Wasa wasa, har aka fara azumi Anum bata dawo ba, sai ranar da Malam ya turo da kaji da danyen nama kayan tea da garin gero, da gyadar kunu tsamiya, yaji na musamman Umma ta haɗa mata, ga miya na garari da Aunty Rabi ta aiko mata, wai tana sahoor dashi, sai kayan tea na Aunty Binta, dan tunda ta taso a hannun mahaifiyar su basu banbanta da su, asalima kamar sunfi yan uwnta ciki daya kula da ita, sai an Aunty Aminatu, da ta mata kamu aka kulla a laida da surfeffen wake an wanke shi an gyara tass ya bushe. , a kawo mata Allah yasa yana gida Rulwanu ya zo,

Bayan sun gaisa ya saka almajirai su shiga da kayan.

"Gashi inji Malam da Umma sai su Aunty Binta, nasu kenan wannan tarkacen Allah Maude yan uwana suna da son kai, dubi shara na Arziki da suka mata"

"Toh ai renon Umma ce!" Inji Maude,
"Ina gaya maka akwai mangyada rabin galan, da manja tare da kudi inji Ya Abubakar, Ni kuma ko oho." (😏😂 Shifa Rulwanu gani yake Anum ta kwace mishi nashi fadar ne,)

Nan maude ya gaya mishi gaskiyar abinda ya faru, tare da nuna mishi kar ya gayawa Umma da Malam, yayi alƙawarin haka.

Sannan yana fita ya kira Ya Usman ya gaya mishi tare da Ya Aminu, daga nan ya zuba ido ya ga wani irin Action zasu dauka.

Bayan awa daya, Aminu da Usman, suka dira gidan Hafsat sun same su, su huɗu har da Maman su, wacce tasan da cewa Anum bata gidanta. Babu fada babu zagi suka riko hannunta, zuwa gidan Usman.

"Kina da ciki?"
"A'a bani da kome?"
"Ok zaki ci Ubanki yau din nan ba an jima ba, domin ba zaki kashe mana mahaifi ba."

Birkin mota Aminu ta rufe ta dashi, dake Usman mutum ne me rauni bai iya zama a gidan ba, Matar Aminu ce ta kira Umma tana gaya mata Baban Amir zai kashe Anum tazo,

Duk inda za a sami mace bayan Umma ce, dan haka wallahi babu nutsuwa dan ko takalmin kafarta daban daban ta saka, ta saka Rulwanu ya kawo ta. Tana shiga gidan ta nuna mata dakin shi, tana zuwa ta buga.
"Bude min kafin na sab'a maka."
Wurga da bulalar yayi tare da budewa Umma ta zuba mishi ido, kafin ta wuce tare da d'aga Anum da take yashe a sume.

"Bani ruwa Maman me gida!" Umma ta ce mata, da sauri ta kawo ruwan, ta shafa mata, a gajiye da wahala ta bude idanunta.
"Umma na! Wayyo Allah na wayyo cikina? Zan yi amai!"
Ai kuwa ta fara sheka amai, "idan kuma ka tab'a cikin me zaka gaya masa?"
"Wannan munafukar bata da kome Umma wai ashe Maman mu tasan ta gidan ta, yau kwana goma kenan? Ba dan an kira Ni an gaya min ba."

"Duka ba zai gyara kome ba, Mahaifiyarku da su Hafsat sune suke lalata min tarbiyyar Anum, wallahi tana son mijinta, don Allah mu bar wannan batun tsakanin mu, dan yace matukar yaji wani abu ya biyo baya, ba zai bata kujeran hajjin ba."

Lumshe idanu tai, Umma tasa Maman Amer ta haɗa mata ruwan zafi tana tambayarta ko tana da ciki ne? Tace a'a.

Bayan tayi wanka Maman Amir ta bata wata doguwar riga, wanda Aminu ya bata sabo, a cikin kayan da zasu bata na sallah. Ta saka sannan Umma tasa Aminu ya dauke su, a motar shi ya dawo dasu gidan ta.

Har suka shiga, kuka take kasa kasa, tana gayawa Umma Hajji gori take mata tare da zagin iyayen ta, dan haka da ta dawo da ita, dama ya gansu yana tawowa Aminu ya tare shi suka yi magana na Fahimtar juna, sannan yace saka ido akan gidan shi, bayan na da ya shigo ya sami Umma a dakin Anum, kallon falon Anum da kujerun ta da aka saka reza aka yaga rigar su. Sai kitchen ɗinta da aka mata barna na fitan hankalin.

Shima sai yanzun ya fahimci haka, kallon ko ina yayi yaji ran shi ya b'aci,
"Maude ga Anum! Amma kasan ban tab'a maka magana akan Anum ba ko?"'

Ya gyad'a kai, mik'ewa tayi zata fita tace mu yi magana a waje.
Tunda suka fita ta kalle shi kansa a ƙasa ya rasa yadda zai yi.

Allah ya gani kofa biyu ne a gidan bai cika bin ta kofar Anum ba, sai ta kofar falon shi za zai fitar da kai waje, kofar Anum yasan ya rufe, sai dai yana bawa Hajjo key tana share mishi falon shi da. Dakin shi, akan me zata lalata mata kayan ta?

"Ban san me zance ba! A matsayina na Uwar Anum! Idan nayi magana zaka dauka ina tayata kishi ne!"
Da sauri ya d'ago kan shi, yana kallon umma sannan yace.
"Ina haka ma ya kinyi magana Umma nasan ba zaki tab'a taya Anum kishi ba, tunda kece kashin bayan aurena da Hajjon, don Allah kiyi hakuri"

Sai taga no matter how, ta tsaya tana fada da surukinsa, mutum min da ya kasa tsayuwa ya daidaita kan shi da ita, haka ya bata girmanta na Uwa, murmushi tai sannan tace.
"Ayi ta hakuri wata rana sai labari!"
Daga haka tayi mishi sallama, tana komawa gida ta kira Abubakar tace maza ya nimo mata masu furniture azo a gyara na Anum.

Yace to suna zuwa..
Tunda ya shiga cikin gidan, da kan shi ya fara gyara falonta wanda zaka rantse ya shekara dari babu gyara, tana share kwalla tana gyara cikin d'akinta, zuwa ban d'akinta, babu inda ba a shiga ba a cikin dakin, bata kuma kuka ba sai da ta ga an mata wulakancin na fitar hankali kayan akwantinta na aure da na fadar kishiya an watsa mata ruwan b3t cikin shi ta zuba gwiwar ta a kasa tana kuka.. har yana jin muryanta.
Shigowa yayi kowa wani zani ya d'aga ya sai ya rididige.

Haka ya maida ya rufe yana bata hakuri, sallamar ya Abubakar yasa shi fita, suka shigo aka duba kujerun, tare da kayan kallonta da aka kona, anan Ya Abubakar yayi fada sosai, da sassarfa ta fito daga dakin ta,

Da sauri ta isa gare shi tana kuka, tare da gaya mishi abinda aka mata, hatta kayan sawarta sai da aka lalata su. Anan Abubakar ya fara fada, wallahi karku ga yadda hankalin maude ya tashi.

Nan ya shiga bashi hakuri, dukda maude kusan sa'an Aunty Binta ne, amma haka ya saukar da kanshi yana bawa Abubakar hakuri, bayan tafiyar su, ya tattara lalatattun kayan ya kai dakin shi, sannan ya fito.

Dakin hajjo ya shiga..tana barci bata san ma Anum ta dawo ba, dan a tunaninta ta tafi kenan..
Jan kafarta yayi take ta bude idanunta.

Ganin yadda fuskar shi a tanke, tashi tayi zaune.
"Hon...."
"Daga Ni sai ke a gidan nan, waye ya lalatawa KHADIJAH kayanta?"

"Ni....Ni...Ni.."
"Tambayar ki nake?" Ya daka mata tsawa,
"Wallahi sharrin shaidan ne!"
"Toh tattara ki koma gidan ku, zan nime ki. Iyayen Khadijah sune suka tsaya min na aure ki, yau kayan Khadijah kika lalata, hatta frij ɗinta, meye yayi zafi shi ba wuta ba?

Mijin ta kika aura zaki nuna mata kishinki yafi nata, ban da dalilin me ƙarfi ce miki aka yi ina sonki ne? Itace macen da na fara so? Ko wadanda na bari babu wacce na aureta da sunan kaunarta kawai na auri kowacce ne da sunan zab'in iyayena. Ita kuma zab'in raina ce, zoki fita min a gida."

Kuka ta saka tana bashi hakuri ya fita, dawowa dakin Anum yayi, ya same ta tana kuka sosai, shi yana zaune a cikin gidan bai tab'a sanin anyi wani mugun abu ba, asalima hankalin shi baya kan kome. Dan haka ya yi ta bata hakuri ko zata wuce. D'ago kanta tayi tare da zuba mishi ido. Sun jima kafin ta dauke kanta bata yi mishi magana ba, ta mike tare da cire kayan jikinta, yaga yadda bulala suka kwanta a jikinta, tasowa yayi tare da rike hannun ta, kukan da ta saka ne ya sashi sassauta rikon da yayi mata, yana kallon hannunta, wanda ya kumbura sosai. Rike wuyar hannunta yayi....
□□ Anya ba zamu saka a gurguje ba? Dan na gaji wallahi....
#Mai_Dambuje
[2/4, 10:23 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN

"Ka rabu dani, tunda aka iya zuba min ruwan b3t a kayana gaba Ni ce za a nemi kashewa,"

Tana fadar hakan ta mike zuwa ban daki, ta sake fashewa da kuka ganin yadda aka lalata mata kome nata, babu abun amfani.

Tunda ta shiga ban dakin yake kallon kofar, ya rasa yadda kome ya lalace haka, mik'ewa yayi tare da shafa kanshi ya nufi waje ya sami Hajjo a tsaye tana kuka, ita a tunanin ta wani farraku aka musu, ita da shi. Bayan tabargazar da suka yiwa Anum hatta firj ɗinta babban su da aka fasa silindar gas din, anyi mata barna ga satar da aka mata.

Bayan ta fito ta kuma gyara d'akin, tsaf sannan ta shiga store ta ga kayan da aka kawo mata, durkusawa tayi ta fara kokarin ajiye kome a muhallin shi, sannan ta dibo dankalin turawa, ta fere. Tare da doya tayi aikin su.

Namar da malam ya kawo mata, ta yanyanka a choping bot, tana gamawa ta wanke kamar yadda taga umma ta dibo kayan kmshi da albasa ta gyara sanan ta zuba bayan ta kunna gas din.

Ta daura miyar ta, bayan ta duba taga akwai kayan miya, idan ya sayowa hajjo yana kawo mata na, tana aikin amma kuka take sosai, domin ban da rigar jikinta babu kayan da zata saka.

Haka hada miyar ganye kuma babu ganyen, komawa d'akinta tayi tare da niman wayarta ta kira Rulwanu ta gaya mishi tana son ganyen miya, alayahu. Bayan minti goma sha biyar sai ga Maude da kanshi ya kawo mata, koda ya mika mata kin amsa tayi tare da dauke kanta, kamar ba zai ajiye ba. Kuma sai ya ajiye mata, ya saka kai ya fita. Bin bayan shi tayi da kallo, wasu fitinannun kwalla suna kuma sauka mata.

Bata san me zata yi ba dan maude ya rabu da ita ba, amma tabbas tana cikin damuwa da tashin hankali. Dan haka bayan ta gama hada miyar ta kuma daura tuwon shinkafa, tayi kome dan dai-dai, sannan ta yi kunun gyada, tayi abubuwa da yawa, da jera tare da kaiwa d'akinta ta ajiye. Dan tana gudun kar a sake mata wani abu.

Wanka sallah tayi tana kallon kayan jikinta, bayan ta zuba ta gumi, wani kaya zata saka. Kwalla ne ya zubo mata, tana jin kamar tayi ta kurma ihu.

Dan haka ta cusa kanta a tsakanin cinyoyin ta, tana kuka kamar ana mata mutuwa, yana shigowa yaji sautin muryanta. Jikin shine yayi matukar sanyi.

Tsayawa yayi a bakin kofar ta,. Har ya kai hannun shi handle din kofar kamar wanda aka ce ya juya ya fasa, shiga dakin ya koma falon shi yana me dafe goshin sa bayan ya kwantar da kan shi a kujeran.

*ANUMULLAH!"
Ya faɗa da dan karfi, ji yaƙe kamar son zuciyar shine ya sanya shi ta faɗa cikin wannan yanayin. Ajiyar zuciya yayi sannan ya juya yana kallon kofar falonta.. kitchen yana kallon yadda take tafiya a hankali kamar wacce kwai ya fashe mata a cikin ta.

Nan kuwa zunzurutun zazzaɓi ne da yake damunta, sabida tsamin da jikinta yayi sakamakon dukar da aka mata, a gurguje tayi gyaran kitchen ɗin sannan ta fito, hango shi tayi har ya shiga dakinta. Ban daki ya shiga ya sami koma fashe wankar da da tayi ma da buta tayi, fita yayi tare da kallon agogon d'akinta. Sannan ya fita.

..... Dab za a sha ruwan sai gashi dauke da babban baho wanka da kayan bukata dai na banɗaki ya ajiye mata, sannan ya kalleta tana kwance, sallamar almajiri yayi, ya amsa mishi sannan ya fita.

Mika mishi wani katon leda yayi sannan yace.
"Oga maude daga gidan su Anum aka bani na kawo mata."

"Toh kace mun gode." Ya faɗa tare da shafa kan yaron, ya koma cikin gidan, bude ladar yayi, kayan shan ruwa ne da aka zuba shi a wani katon roba, dan haka ya shigar mata dashi cikin ɗakin.

Tayi laushe kamar ba zata kai azumin ba, ya isa gurinta. Sannan ya d'aga ta tare da saka mata pillow ta jingina.
"Anum! Waye yayi miji duka haka?"
"Wanda ka kai ƙara na gurin shi mana"
"A'a Anum ban kai karan ki gurin kowa ba;" dauke kai tayi tare da gyara zaman ta.

Ya bude baki zai magana aka kira sallah, ruwan zafi ya zuba mata a kunun gyadar kamar ba zata amsa ba, kuma sai ta kai hannun ta zata masa, rike hannunta yayi suna kallon juna.
Ofco's yaga soyayyar shi d'anye a cikin idanun ta. Amma me yasa take iya boye soyayyar shi.

Bayan ya ganshi ƙarar a cikin idanunta, sake mata hannunta yayi ta fara sha, kwarewa tayi yayi maza ya rike hannunta, yana murza yatsun hannunta. Cikin kulawa har ta daina tarin. Sai da yaga tasha ruwan kafin ta samu ya sha nashi.
"Ina Matarka?"
"Ta tafi gidan su."
"But Why?"
"She deserve."
"Maude! Kasan me kace?"
"Ai nayi English ko?"
"Kwarai kuwa!"
Ta faɗa tana cizon lips dinta, murmushi yayi sannan yace.
"Toh nayi yaki da jahilci, har na kasa karasawa amma ina iya rubutu da tsintar wasu kalmomin Faransanci da turancin nayi ƙoƙari ko?"
Ya tambaye ta tare da mata alamar da idanun shi,
Murmushi tayi tare da gyada mishi kai. A hankali ya haɗa kunun suna sha suna hira, cike da kewar juna, duk da tana tsoron abinda haka zai kuma haifar wa, haka suka gama sannan ya nufi masalacin Sheikh Aminu bakin kura.

Bayan ya idar ya saka kai zai dawo, suka gamu da yayan Hajjo. Gaisawa suka yi sannan yace mishi.
"Don Allah kayi hakuri, nasan abin da aka yi bai maka dadi bane, tunda har ka iya zama da yarinyar da kowa yasan bata sonka, aka zauna lafiya. Ita wannan kuma da ka iya."

"Malam Adam, da ace abinda tai shi Anum take yi min wallahi zan sake ta! Ko ban sake ta ba, zan turata gidan su. Malam Adam b'arnan da Hajjo tayi min ko Anum da bata kaunata ba ta min ba, haba jama'a kayan amfanin Kishiyarta ta lalata kasan asarar da tayi sanadiyar shi kuwa,bayan kayan auren Anum da ta b'ata.

Hatta kayan da iyayen ta suka mata sai da ta lalata su me tayi mata? Kishi hauka ne? Don Allah kayi hakuri ta zauna zan nime ta da kaina."

Daga haka ya wuce abin shi. Ya bar yayan hajjo cikin damuwa, koda ya koma gida ya same ta kwance jikinta yayi zafi rau, riko hannunta yayi zuwa falon shi. Suka zauna duk da ba wani hira suke ba, abinci ya zubo musu, tace ta koshi dan dankalin da tasoya ta kasa ci. Haka yayi ya mata hira, har barci ya dauke ta,

Shafa kanta yake, yana kallon yadda take barci, kamar wata yar mage.
Yana zaune tare da kallon tafsir din Malam Haifan har aka kira sallah, kafin ya tashe ta. Shi kuma ya nufi masalacin.

A d'akinta tayi sallar isha da tarawee, tana idarwa a gurin ta bingire da barci, yana Shigowa ya same ta a kasa rufe kofar gidan yayi sannan ya dawo d'akinta ya ci abinci, ya koma dakin shi yayi wanka tare da shiryawa cikin kananun kayan barci, ya dawo falon ya zauna.

--- Ya jima yana kallon tashar gidan tv har karfe sha biyu lokacin yaji wani irin yanayi na kewar Hajjo, tashi yayi ya nufi dakin shi har ya kwanta ya tuna bai kuma

leka Anum ba, shine ya koma dakin, ya duba ta ya samu tana nishi zazzafar zazzabi ya tirmushe ta.

Gyara mata kwanciya yayi, sannan ya haura gadon, taimaka mata yayi ya cire mata kayanta, sannan ya dawo kitchen ya debi ruwan zafi ya je ya goge mata jikinta, ya kai bahon ban daki.

Gyara kwanciyar ta yayi tare da kwanciya a bayan, yana matsa mata jikinta, a hankali take mika saboda yadda jikinta yake matsanancin ciki, tausa yake mata har ta daina, sannan ya cigaba da taimaka mata, bayan awa daya zuwa biyu. Barci yayi gaba da ita, karon farko tare da Anum suna kwance jiki da jiki.

Shafa kanta yake zuwa bayanta, tare hura mata iskar bakin shi. Gyara kwanciya tayi a jikin shi har da wani rungume shi tana kara mannewa a jikin shi. Wani irin nutsuwa ce ta shige shi. Tare da da jin zai iya manta kome da kowa idan har Anum zata bashi dama sun shimfid'a soyayya me tsafta.

Wanda duk inda ka zaka sai ka magantu akan su,. Da zata bashi damar haka da sai an tambaye ta wani boka da malam ne yake mata aiki haka, domin zai manta da past Future's din shi ya zauna da ita, ya manta da duniyar shi ya rungume duniyarta..

Da ace zata bashi dama, da ya maida Ila cikin ahalin shi ita kuma ya rungume ta, su boya daga iyayenta babu wanda zai kuma ganin su. Me yasa yake raye?

Saboda kaddarar shi da Anum, sake k'amk'ameta Turai yana ji kamar wani zai amsa mishi ita, d'ago kanta yayi tare da d'ago kanta.
"Anum! Ina ta gudu! Ina gudun ceton rayuwata, Ina ta boye gobe na, Anum ki bani damar na gaya miki waye ni. Ki bani dama na shimfid'a kaunar mu, mara iyaka.

Amma, nasan duk yadda naso na kasance dake haka bai zai samu ba, sabida."
"Maudeeeee!" Tsigar jikin shi ne ya mike wanda ya haifar da mikewar gargasar jikin shi, a hankali yaji yanayin halittar jikinsa ta motsa, a hankali yake biyar da ita, tare da gaya mata irin kaunar da yake mata, a nutse yake kokarin gudanar da sha'anin rayuwar auren su.

"Maudeeeee! Mama tace idan na sake wani abu ya shiga tsakanin mu, Allah ya tsine min Albarka!" Ta faɗa muryanta na rawa, tare da kifa kanta a kirjin shi tana rizgan kuka.
"Tabbas babu amfanin zaman mu! Ba zan iya zama dake ba, Kaunar da nake miki gaskiya ce amma ba zan iya rabaki da Mahaifiyarki ba, Anum"

Rike kanta yayi, yana jin zafin zuciyarshi, itama hannunta ya kai tare da rungume shi tana kuka, yau gata ga Maude. A sanyayye ya janye tare da saka kayan shi ya bar mata d'akin, tun daga ranar bai kuma mata magana ba, asalima tana lura da yawan mishi aikan da Umma take, karshe ta tsare Rulwanu da tambaya.
"Matar shi zai dawo da ita"
Ita a tunaninta ai Hajjo ta tafi kenan, ji tayi cikin ta ya cure guri guda, da sauri ta juya ban daki. Kuka take irin na zafin kishi, amma sam bata tab'a tunawa shi ma Ɗan Adam ne kuma yana bukatar nutsuwa da rayuwar shi.

Sunyi haka da kwana biyu, Hajjo ta dawo, lokacin har an gyarawa Anum kayan falonta, na wutan kuma Maude ya sake mata wasu, deep freezan kuma aka gyara tare da kawo mata abinta,

Zaman su da Hajjo kadaran kadahar, babu me shiga harkan kowa, maude ya hana Hajjo shiga falon Anum, shi yake Bin ta d'akinta.

Zaman su babu wani abinda zaka iya gani kace ai ana karuwa, har aka gama azumi akayi sallah, yan uwan Anum da malam sun mata kaya wanda ya ci Uban na da, shima maude ya maida mata da kayanta, har yafi nada, a hirar da suke ne ya tambaye ta gold dinta dan ya gani a wuyar Hafsat. Ta shiga kame kame, karshe yace mata.
"Kin bawa yar uwarki ba! Kinsan me? Ba zaki gane yadda take cutar ki ba, idanun ki a rufe suke."

Shiru tayi bata kuma ce mishi kala ba, haka ta fara zuwa inda ake bitar darasin aikin hajji. Shi yake kaita ya dawo da ita, wani abun da yake bawa kowa mamaki, idan ya kaita aka tambaye ta mijinki ne? Sai ta ce a'a ya rage mata hanya ne.

Asalima bata kaunar ta gaya musu waye mijinta, ko maude ne mijinta, ranar wata talata. Wata yarinya itama an biya mata tana zuwa bita, kawai ta haɗu da Maude yazo daukar Anum.

"Don Allah ki cewa Khadijah mijinta yazo daukarta!"

Da sauri yarinyar ta shiga cikin jama'a tace.
"Khadijah mijinki yazo daukarki wanda yake kawo ki a mashin"

A kunyace ta mike tare da musu sallama, tana zuwa bata kalle shi ta juya bayan mashin din ta haura yaja suka fita. Kuka take a bayan mashin din. Kamar wacce aka zagi uwarta. Har suka isa gidan tana gaya mishi.
"Uban waye yace ta gaya musu, kaine mijina."
Ran shi ya b'aci sosai, kawai ya tsinka mata mari, tare da matse bakinta jikin shi yana rawa.
"Idan zaki min rashin kunyar ki yarinya ki tsaya a kaina, karki yarda ki tab'a min iyaye, lusarai sha-sha-sha, wallahi ban da girman Mahaifinki da na Umman ku, da yau sai na nuna miki yadda nake, Ni ba sakarai bane. Nayi hakuri nayi hakuri, Khadijah ba dai Arziki kuke nima ba, kije aikin hajjin ki dawo .

Ko kece autar matan duniya na gaji dake, bani da nutsuwa bani da kwanciyar hankali. Khadijah duk wanda zai miki fatan Alkhairi da na Arziki bayan na wanda ya jibanci soyayyarki ce, wallahi na rantse, ba zaki tab'a samun irina ba, ba zaki samu wanda yayi hakuri na ba, Idan ina raye da kafar ki zaki zo niman Alfarma ta, a lokacin zaki san waye *BANIJARE*" ya tureta tare da tsallakata ya bar gurin.

Cire kai tayi tana kallon su, yadda suka zuba mata ido.
"Karfe uku, kaina na ciwo sosai don Allah kuje zan kwanta gobe Ku zo zan baku labarin da safe, karfe goma sha biyu, karku tashe ni, dan barci nake ji sosai"

"Kiyi hakuri Aunty Anum, hakkin Maude ba zai tab'a Barinki ki rayu cikin salama da nutsuwa ba, kai ko da bai sake ki ba, wallahi baki ga kome ba. Yo wannan rashin Imanin har ina? Mutum da lafiyar shi a hana shi kwanciyar da matar shi, wallahi ji nake kamar nayi ta dukarki!"

Inji Fa'izah,
"Karki damu, zaki dake ni idan lokacin dukar yayi." Na fada ina dariya, domin gani nake har yanzun ban zo inda ya dace su fahimci laifina ba.....

Walle nepa sun kumdume mana wuta 😂llah Nagode maka da kasa suka dauke wutar 31 Insha Allah gobe ko
#Mai_Dambu....ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA ƊAYA

Fita suka yi tare da cewa.
"Allah zamu tashe ki, dan jiya kman nayi hauka,. Ina ji kamar gari ba zai waye ba."

"Ai kunga gobe idan Allah ya kai mu sai ku zo da hantsi, zuwa karfe 10 na dare Insha Allah na gama baki labarin ko?"

Na gaya musu, fita suka yi. Nima na shiga ban daki nayi alola tare da gabatar da sallar nafilla. Har kusan minti talatin da biyar, sannan na kwanta. Ina kwanciya na kasa samun nutsuwa, wani irin yanayi nake ji, me cike da faduwar gaba. A hankali nake jin bugun zuciyata tana kara tsannanin ta, tashi nayi zaune kwalla na zubo min.

"Wacce ƙaddara ce take kusanto Ni? Ya Allah na tuba, na kuma na tuba, Ubangiji bani da kowa bani da kome sai wanda ka arzurtani dashi idan ka kuma amsar sauran Ya Allah niyi laifi, ya Allah ka yafe min, Ni baiwarka ce me wanka cikin zunubai. Ya Allah na tuba, ya Allah na tuba ya Allah tuba."

Shigowar Shukrah, bai hanani kuka na da tashin hankali, ji nake. Rungume ni tayi tana kuka nima kukan nake, muna a gurin har aka kira sallah farko. Sannan muka mike tare da gabatar da sallar raka'atun fijr, kafin muka zauna a gurin har aka yi sallah asuba. Wani irin zazzaɓi ne ya rufe ni bayan nayi Sallah asuba.

---- karfe goma sha daya dai dai na farka sakamakon saka alerm da nayi, a hankali na bude idanuna na zuba su a kan su, sun jeru kamar wasu masu niman gafara, murmusa musu nayi tare da mik'ewa na nufi ban daki nayi wanka da alola, tare da brush. Koda na fito same su har abin karyawa aka kawo min, bana jin dadin rayuwa ta, a hankali na zauna tare da ɗaukar mai na shiga shafawa a jikina, ina yi ina ka musu rai.. My Asadullah ne ya fado min a rai, murmushi na sake. Ina tuna ranar da yazo ya same ni ina shafa mai, cikin rashin kunyar da ya saba min wai yazo ganin ajiyar shi. Sauke kaina nayi Ni daya na. Sai dariya nake me hade da kuka.
"Am sorry! Ka yafe min Zakina! Ba zan kuma ba. Aliyu na, na tuba wallahi na bar duniya da abinda yake cikin ta, ko a daji kake zaune zan zauna da kai, domin kaine cikon mafarkina."

Badi'ah da tafi kowa ruwan hawaye, kuka take tare da cewa.
"Don Allah, Sadiya jeki dauko min wayana. Zan kira baban Khalid."
Da gaske fa take kuka, tare da kiran a Nimo mata wayarta, Yau tuba ya tashi (😂😹)

Tashi tayi tare da fita, daga d'akin. Ta sami sadiya a waje, ta amshi wayar, ina jin yadda take kuka bayan ya dauki kiran, murmushi nayi, kai na a kasa, na share kwalla da yake bin fuskana, tare da ɗaukar kofin tea na sha, har yanzun ruwa tana maganin daudda, sabida surar nan da take birkita yan maza da gigita duniyar wasu Mazajen yana nan, hip da Beautiful sexy body dina da yake ruda mutanen da suka jefa ni cikin damuwa yana nan, kallon Cutie da dina nayi.

Murmushi nayi amma fa inside me, ina jin zafi da ciwon zuciya akan abinda a jikina yaja min, lumshe idanuna nayi tare da tuna abubuwan da suka faru.

Dawowa nayi ka zauna akan gadon tare da nad'e kafana, sannan nace musu.
"Kun tashi lafiya?"
"Lafiya Aunty Anum."
"Toh mu Cigaba ko"

Son Zuciya...
Bahaushe yace son zuciya b'acin zuciya, lokacin da ya fita daga falona, ina jin shewar Matar shi. Kuka ne ya kwace min tare da kifa kaina, akan babban kujeran falon, ina kuka.
"Ba dama an kaiwa dodon igala wanda yake tsafi." Tare da fadar wasu maganar banza akan iyaye na.

Da gudu na ficce daga falon, ta nufi tsakar gidan, na shake yar iska, na fara dukarta ko nace muka fara dambe, na bura uban bala'i, dukarta nake ina juya ta, kafin kace me ihunta ya cika ko ina tare da kiran niman taimako.

Babu shiri aka kira Maude, yana shigowa ya ga yadda nake gwara kan matar shi, zuwa yayi ya raba mu da karfin tsiya, tare da dauke ni da sabon mari, ya ingiza kai na cikin falona, a wulakance.

Tun daga ranar Maude ya bude babin wulakanta ni, a tunani na da kenan. Amma a bangaren shi, wulakancin ya buɗewa Matar shi, domin yace mata tunda na iya kamata da dambe, tabbas akwai abinda tayi min, dake sokuwa ce, fada mishi tai.

Ga baki daya mun hada mishi zafin kai, tsakanina da shi babu wani abu dad'i, har zuwa lokacin tafiyar su aikin hajji. Allah sarki haka ya dauko U.S dollas. Ana jibi zasu tashi dan yace matar shi ba zata bi motar da maza suke ja ba. Da kansa shi ya dauke ta zuwa kano,.bata san me yasa ya nacewa wani irin riga me hula, sai face mask domin lokacin a kano ake tashin alhazzain jahar Bauchi.

Tunda suka isa, yaki kai ta tashan jirgin saman, kasa hakura yayi, domin kamar wani maganaɗisu, haka ya makale mata. Wani irin abu yake ji ya cika mishi mara, dan haka ya matseta yana jin daga wannan yanayin shikenan, ya rasata kenan.

Haka yayi ta kokarin ya shiga duniyar,(□□□□) amma ina ta kasa nutsuwa ta bashi wannan damar, domin ta firgice ta gigice daga abinda yake kokarin kai mata, (Inji Noorh tace Uncle bindinka ne □) da ya fahimci idan ya saka karfi sai dai ta fasa zuwa aikin hajji nan, ya sashi hakura tare da wasu dabarbaru irinta manyan maza, ya samu ya rage nauyin da yake damun shi. Taimaka mata yayi tare da kai ta tayi wanka, sannan ya bata kayanta ya saka, yana kallon yadda take jan kafarta, rungume ta yayi tare da sumbatar wuyarta, ya saka mata hijab ɗinta. Suka fita kasa kallon shi tai sabida yayi mata wani abun da ya kasa barin jikinta da zuciyar ta, wani irin shauki take ji akan shi,. Kamar zata fadi dan haka ya daura kan ta a kafad'ar shi.
. Idan ka ga Anum da maude dem luk perfect couples, sunyi wani irin kyau wanda duk hassadar ka sai sun baka sha'awa, koda suka isa airport din inda ake screening, kuka take tare da rike hannun y, sumbatar goshinta yayi.
"Anum ina kaunarki! Amma rabuwar mu ita ce mafi alkhairi, Anum na yafe miki,.Anum Nagode da zaman da kika yi dani.

Anum don Allah ki sani a matsayin masoyanki na har abada, ina sonki Anum ba so da yake tashi ba, a'a kaunarki nake da zuciya ta, indai kaunar da na miki don

Allah ne, Ubangiji zai bani ladar shi. Idan kuma sabida wani abu ne Allah zai bani akasin haka."

Shafa kanta yayi zuwa fuskarta gurin su Umma da su Aminu suka nufa suka gaisa sannan ya kai ta inda za'a yi mata screening, har aka gama mata, zata wucce. Juyawa yayi zai bar cikin airport din yana jin zafi da damuwa a ranshi, ya rasa yadda zai yi da ran shi lallai so masifa ce. So Bala'i ce, duk wanda yace so ya hadu toh bai san so bane, kasa tafiya tayi tana wani irin kuka, a hankali ta juye taga shima tafiya yake amma babu kuzari a cikin Ni, watsar da passport dinta tayi tare da juyowa da gudu, tana kwala mishi kira,.wanda ya sanya gabaki daya hall din ya dauki muryanta, hawayen da yake shirin sauka daga cikin idanun shi ya maida a hankali, tare da juyawa yayi yana kallon yadda take gudu, koda ta iso. Tsayawa tayi kamar wacce zata fadi wani abu, tsalle tayi tare da rungume shi.

Hawayen da yake tarewa ne ya fara kokarin sauka, waye shi? A wata duniya ya rayu? Kuka ba na shi bane, domin idan yayi kuka akan so meye sunan shi? Ya kamata ya tuna gumurzun da ya faɗa da wanda ya tsallake, da irin al'ummar da ya jagoranta! Dole ya cigaba da amsa sunan shi koda kuwa ba zai samu lambar yabo ba, dole yayi alfahari da kasancewar shi daya daga cikin hafsshin hafsoshi kasar shi. Ya zame mishi tilas ya amince da ƙaddarar shi, kuka ko zubda hawayen bakin ciki ba na shi bane.

"Ina kaunarki Anum, kiyi min Addu'a Allah ya rage min kaunarki!"
Kuka take tare da kara rungumo shi, dakyar ya sauke ta, taje tayiwa su Umma sallama, Rulwanu yana Tsokanar ta.
"Layla majnon kiyi hakuri irin wannan lokacin zaki iya."

Make bakin shi Umma tayi tana kallon shi.
"Ubangiji ya yaye mata."

Tura bakin shi yayi.
"Allah Umma Rulwanu sai Du'a'i."
Haka suka yi ta hira, a gaban yayunta da Umma, bai hana Maude nuna mata wasu abin da ya burge shi, ba tana juyawa zai sumbaci kumatunta.
"Wai meye haka baka ganin Umma ne,"
Hannun shi da nata ya haɗa, tare da sumbatar bayan hannunta, yana kallon fuskarta.
"Babu ruwanta, domin ba zata hana d'anta abinda yake so ba," shiru tayi tana kallon shi, sannan ta dauke kanta, har aka fara kiranta, haka take zuwa jikin yayunta, suna mata fatan alkhairi. Tana zuwa gaban shi. Ya bude mata hannun, cikin jin kunyar su Umma ta shiga tare da sauke ajiyar zuciya, kwalla na zuba mata.

A hankali yake buga bayanta, har ta yi shiru, da kanshi ya rakata har cikin jirgin, kafin ya fito yana jin anya ba zai fasa kudirin shi ba, toh ai dan ita zai yi dan tayi farin ciki, domin tayi rayuwar da ya tauye mata.

Haka ya dawo, gurin su Umma suka tsaya sai da jirgin su Anum ya tashi, kasancewar Malam yasan Agent din da zai tafi ta tafiyar su Anum, Sannan Maude yayi mata bayani, tare da nuna mata yadda zata yi amfani da kuɗin ta, domin lokacin ba a shigo da tsarin lallai sai da muhrammin ba a tafiyar aikin hajji.

Tunda ya dawo ya kasa samun nutsuwa, kullum yana cikin damuwa, tare da karanta wasikar jaki. Yana son ya rabu da Anum kafin ta dawo amma abin da yake hana shi

kunyar malam, ga Musa da Bashir da suka matsa mishi lallai ya sake musu Kanwar su, tunda mahaifiyar su bata son shi.

Suma kamar ba mutane ba, sai Abinda Mama da Hafsa suka ce musu. Wasa wasa suka uzura mishi, kuma baya son ya kai ga rashin mutunci, sai yace musu toh babu damuwa zai sauta idan ta dawo, domin lokacin da suke damun shi idan ya sake ta, wallahi bazata aikin hajjin ba, domin malam ba zai bata kujeran ba, shi yasa ya zab'i idan ta dawo da kanshi zai rabu da ita.

Bawai dan yayunta da iyayen ta ba, sai dan ra'ayin kan shi. Dan haka ya zauna da shirin sa.

Hajjo kuwa ba laifi zaman su ya mike tunda Anum ta mata duka, maude yace mata shi bai ji dadin da Anum bata karya ta ba, tunda bata da hankali. Wannan abun ya bata haushi, dan haka tare da shawarar su XOXO suka fara shige shige. Mutumin ya fara ganin shi, shi ya fara gaya musu.

"Ko kuyi sanadin auren ko karku yi, Sanadin kenan dan haka al'amarin Ubangiji akan Yarinyar nan da ban mamaki yaƙe ba Ku tab'a tare mata Arzikinta ba, domin Allah yana tare da wadanda suke mata kuka. Ko da nayi muku wani abu akan shi zai karye domin shi ba gama garin mutane bane marasa sanin addini. Dan haka idan zaki more shi, ki yarda a gurin shi ita yarinyar tafiki. Amma kika ce sai kin nemi karfin da ta samu a ranshi! Hmmm zaki iya rasa aurenki da shi kanshi har abada.

Na sha raba tsakanin ma'aurata, amma ban tab'a ganin ma'auratan da suke tare da juna ba sai ita da shi. Dan haka kuje akwai sauran lokaci."

Haka suka dawo jikin su a mace.
**
Yau sauka isa Madina sakamakon basu sauka a can ba, sabida aikin hajjin da ya matso dan sun iso ana saura kwana uku za ayi afrah dan haka suka yi aikin hajjin , yanzun ziyara suka zo yi.

Bata rude ba, asalima kamar ta iya duk abinda aka koya musu, kullum zasu tafi ziyara tare da zuwa guraren da aka yi wasu abubuwan musulinci a gurin, sai da suka shafe sati a Madinah sannan suka dawo, suka dawowa , bata kwanta ta huta ba ta yi wanka tare da ɗaukar kwalbar turaren da maude yaƙe zuba mata idan ya sayo, digawa tayi a cikin man shafawa, tayi amfani dashi. Sannan ta shirya cikin doguwar riga ta nufi ka'aba zata yi dauwafi.

"Ya Allah ka dawo min da Aliyu na! Ubangiji duk ina yake ka jibanci al'amaruran shi, Ubangiji ka taimaki bawan ka, ka rage mishi zafin zuciya." Tausayi ta bawa Anum tare da kallon ta tace mata.
"Amin! Iya" juyawa matar tayi kamar zata fadi Anum ta riko hannun ta, suka fito daga cikin mutane, suka nemi guri suka zauna.
"Allah yayi miki Albarka. Rabona da na sami me taimaka min nayi aikin hajji cikin nutsuwa shekara takwas kenan, tunda Suka min sanadin da na rasa Zakina sh..."

"Amma Dijama baki da damuwa, muna can ana rikici tsakanin Charifah da Nana Aicha, akan sun barki kin fita."

"Ke tafi can, mara kunya waye zai zauna kuyi ta juya shi kamar dan kamfe, ki lokacin da muke zuwa anan da Namijin duniya,.ai ko ke ba a haifa ba yar banza da idanunta a tsakar ka, gwara Idrisuu da Ghali su miki aure da wancan mara ta idon."

Isowar wasu tawaga guda, yasa Anum kallon su. Kallon da wata cikin su take mata irin kallon kurilla nan ne, duk da ransu a b'ace yake, amma haka bai hana su tambayar tsuhuwar.
"Dijamah, wacece wannan da take tsaye a kusa dake."

"Ubanki Zakariya ne, Charifah ki fita idanuna." Kallon Anum tayi gabanta na faduwar. Itama Anum kallonta take,
"Ke ba a koya miki gaida na sama dake bane kika kallon kwayar idanun jama'a?"

Inji Charifah, dauke kai Anum tayi sannan ta kalli tsohuwar tace mata.
"Iya zan tafi, Allah ya bayyana miki jikankin nan."

"Amin Yar nan ai wallahi da ace zai bayyana sai na zo har gidan iyayenki sun bashi aurenki."

"Aure kuma? Wai me yasa da zaran kin ji haushin mu kike kiran mishi aure, wallahi duk matar da ta kuskura ta kuma rab'an Ya Asad sai ta gwammace kida da karatu, dan sai na lahira ya fita jin dadi." Inji Charifah,

"Kwantar da hankalinki baiwar Allah, nima matar aure ce, da mijina. Dan haka babu wani tashin hankali ko damuwa da zai kawo ni inda kike, bana fatan kaddarar da zata kawo ni inda kike." Inji Anum,
Wani banzan tsaki taja tare da kallon Anum irin kallon k'iyayyar nan ne, na lokaci guda na tsane ka.

Dauke kai Anum tayi tare da kallon wasu mata hudu da suka gurin Fara cikin su me tsananin kwarjini da haiba, ta kalla babu yabo babu fallasa, ta gaishe su tare da musu sallama tabar gurin, bin ta da ido matar tayi tare da kiranta.
"Baiwar Allah!"
Abin ya basu mamaki, Innar Ya Asad da bata magana itace yau da magana,. Cikin jin muryan matar tare da nima inda ta tab'a jin makamancin shi, ya sata juyawa.
Wani irin girma da cika ido matar tayi mata, tare da mika mata hannu, suka gaisa. Daga haka bata ce kome ba, itama Anum cikin jin kunya da wani irin dad'i yasa ta sake musu sallama tabar gurin.

.... Bayan tafiyar ta, mazan suka zo.
"Kai Jama'a! Naji kamshi Asad? Ina yaƙe."
"Kai bana son wargi kaniyar kanin ubanka, yaushe muka fara wasar haka da kai, Anya Malik kana da imani kuwa? Wato dan na mutu kuyi iya shegen da kuke so shine zaka ce kaji kamshin turaren shi. Uwaka gata can Gaje dan banza makirin wofi. Matsa min can!"

Hak tayi ya masifa, kafin daga baya tace musu.
"Dan salon munafunci, kusan ina mura shine bari ku ce kun ji kamshin turaren shi. Na kuma jin wannan maganar sai na muku shegen duka."

Da haka suka bar gurin.
"Nana Aicha! Baki yarda da abinda Malik yace bane? Ni ina ganin yarinyar da ta taimakawa Hajja itace take kamshin Turaren shi."

Juya mata baya Nana Aicha tayi tare da cewa.
"Nima nayi zargin haka? Amma ai ba yar kasar mu bace baki ji kalar hausarta ba, sannan Allah daya gari banban..."

Long page □□□
#Mai_DambuZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA BIYU.

*_Naga jarabawar rayuwa dayawa, naga kaddarorrin rayuwa masu girma da banbanci, na koyi darasin rayuwa domin amfanin da rayuwar gaba! zanen ƙaddara ta ba kamar na kowa bane, Zanen ƙaddara ta, tayi daban da na kowa nayi kuka nayi bakin cikin nayi danasanin mara iyaka, Har yau ina nan da tabon zanen ƙaddara ta_*

Shiru tayi sannan ta koma gadonta ta kwanta, tana jin ciwon rashin mutuncin da ba tayiwa Anum ba, domin taso ta kuma samun dama ta kafta mata tijara, dan haka kawai ta tsani Anum. Gashi kuma Hajja Dijamah ta kuma cewa zata hadata da Asad. Tsaki tayi ta sakewa har wani lokaci kafin barci ya dauke ta.

** A bangaren Anum itama haushin matar take duk da kalla zata mai sa'ar Matar Ya Sadeeq, wato Aunty Aunty Zaituna, dauke kai tayi da zata kuma haduwa da ita sai ta zabga mata rashin mutunci, dan ta tsani irin kallon da take mata..

A haka itama ta kwanta, washi gari ta shiga gari tayi sayayyar dan an sauya tsarin dawowarnsu.. kasancewar sune jirgin karshe a zuwa sai akace zu zasu Fara dawowa,
Lokacin da taje dauwafi, zama tayi tana kallon dakin ka'aba..a hankali ta isa maqama Ibrahim, ta kifa kanta akan tafin hannun ta, wani irin kuka take, tana gayawa Allah damuwar ta, ta jima tana kuka..sannan ta ji an dafa kafad'ar ta, juyawa tayi a hankali matar ta sake mata murmushi.

"Kina son mijinki?" Gyada mata kai tayi,
"Meye matsalar ki dashi?".ta tambaye ta, bayan sun fito daga cikin mutanen, suka zauna..wani irin girma matar tai mata, sunkuyar da idanunta tayi tare da cewa.
"Mama na bata son shi, har ta shinga min iyaka a tsakanin mu."

"Kina son shi amma?" Ta kuma tambayarta,
"Eh amma na hakura da shi, domin matar shi tana min gori idan nayi magana sai ya mare ni yace ina da zafin kishi."

Riko hannunta matar tayi, sannan tace mata.
"Duk wata mace da kika gani a duniya da nata ƙaddara, karki yarda mutane su hanaki Fahimtar mijinki, ki yarda akan yana raye ne sabida ke? Ban cika magana ba, amma sabida ke naji kin kwanta min a rai, ki nutsu ba ayin tarayya a sabawa Allah, karki yarda Mahaifiyarki ta rabaki da Ni'imar da Ubangiji yayi miki, Ubangiji ya baku zaman lafiya."
Daga haka ta mike bata kuma mata magana ba, har ta b'acewa ganin Anum.

Dakyar ta koma masaukin ta, sanan ta shiga tunanin yadda zata fuskanci Mamanta, da batun tana son zama da Maude, dan ko jiya da suka yi waya sai da ta kuma cewa.
"Ina nan akan baka na, idan ba zaki rabu da shi ba, zaki koma gurin Maman Sadeeq, amma ki sani ba zata tab'a Barinki kiyi farin ciki a rayuwata ki ba, domin duk wani farin ciki akan yaranta da jikokinta zai kare.

Idan baki manta ba,ai nasha gaya miki ke arzikina ce, na haife ku amma kece yarinyar da zata cire min kitse a wuta, idan baki cire min ba,.ai bazaki cilla ni cikin wuta ba.

Anum wato kina bin na sharrin duniya kina son sana'a min, amma babu kome."

Bayan sun yi waya da ita be ta kira MAUDE, asalin kiran ya shiga amma kuma bai dauka ba, kamar ta hakura sai taji ba zata iya hakuri ba, kuma kusan karfe ɗaya na can ne, dan haka tana kuma kira. Aka dauka.
"Hmm! Nagode me shayi maza yi min yadda Zanji dad'i. Abu kazanka zai kashe ni, me shayi"
.sake wayar tayi ya fadi tare da tarwatsewa, tari ta fara wanda bata san ta kware ba, dakyar ya tsaya, sannan ta koma gefe ta sha kuka kamar me.

..... Bayan wasu kwanaki ta shiga kasuwa tayi sayayyar tsaraba, jaka guda tasaya mishi. cikin damuwa da kishin da yake dawainiyya da ita, ta suka gama aikin hajjin suka dawo, bai je daukarta ba, amma suna sauka a jirgi Abinda ta fara tambaya.
"Ina Maude?"
Kallon ta yayunta maza suka yi sannan suka ce.
"Yana can, amma"
"Amma me? Don Allah karku gaya min abinda zai saka na mutu" ta faɗa tana zare musu ido,
"Yana nan lafiya!"
Haka tabi motar alhazzai, su kuma suka bi motar su, lokacin da suka iso, aka kuma tarkattaa zuwa gidanta.

Gidan ya samu kulawar shi, tsaf ko ina, haka akayi ta shigo mata amma bai shigo ba, bai ta samu ganin shi ba, sai da isha ya shigo lokacin bata fito wanka, wurgi tayi da towel ɗin hannunta, ta iso da gudu ta rungume shi. Tana ihu. Jikin shi a mace, haka yasa shi rungume bayanta, "shi kenan ta faru ta kare"
Ya fada a kasan makoshinsa, murnan da take ya sa shi boye Damuwar shi, haka suka zube a gadon, tana dariya tare da nuna mishi hakorinta, cire karamin towel ɗin tayi tare da balle aninin rigar shi, tana wasa da giant body din shi. Murmushi, lokacin da yaji tana mishi wasu abubuwan. Rike hannunta yayi ta kai fuskarta.
"Na dawo domin kai! Na kuma ajiye kome domin kai, a yanzun na shirya baka rayuwata domin ka..."
"Na sani! Amma rayuwar mu da banbanci, ke iskace abar bukatar rayuwar wasu, Ni kuma ruwa ne haka zalika babu wanda zai fahimci ainihin abinda yake damuna. Anum Alhamdulillah burina ya cika, kinyi aikin da Mahaifinki yayi miki alƙawari, Anum naso mu gina."

"Zamu iya gina rayuwar mu,! Insha zamu iya, kaji a ranka zamu iya."

Duk wani abinda tasan zata yi tayi amma Maude ya kasa amsar wannan tayin kusan a jikin shi tayi barci.

Jikin shi ya mutu ainun, tausayin Anum ya kama shi, ya kuma ji a ranshi, dole ya rabu da Maman Aminu, amma kuma yadda suka kai shi kotun tashan babaye yayi mugun sanya shi tashin hankali, idan ya tuna wa'adin da aka bashi na ya sake ta, ko kuma ayi mishi abinda zai damu da kan shi, kasancewar shi bako. Abubuwan da suka Mishi na cin zarafi yayi yawa, amma sabida Malam da Umma ya barsu da Allah, yana son matar shi suka raba su, sannan suka kuma bashi kudin da ya kashe. A hankali ya kuma rungume ta, tare da shafa bayan ta.
*_Qaddarar Ubangiji rubutacciya ce_*

**Washi gari da bayan sallah asuba suka haɗu da malam,gefe suka tsaya da maude sun tattauna sosai, bai gaya mishi ga abinda yake faruwa ba, amma yayiwa Malam Hannunka me sanda, sannan ya fidda takardan da ya kasa mika mishi, ji yaƙe kamar kar ya mika nishi, jikin shi wani irin rawa yaƙe.

Dafa shi malam yayi zai magana yace mishi.
"A'a malam kar kayi magana, na kasa rike amanar da ka bani, na gaza fahimtar Meye banbancin kawaici da Yakana, Malam duk kawaicinka yau gani nazo gaban ka da takardan sakin yarda kafi kauna.

Ni ba magartaccen mutum bane. na kasa rikon ta, na kasa hakuri da ita, malam don Allah ka gafarce"

"Ni kuma mace maka me akan mutanen da suka kai ka kotu? Ko ka zata ban sani ba ne? Iyalina sun maka rashin adalci, Maude ko baka saki KHADIJAH ba ni zan ce maka ka rabu da ita ka huta, kasan me yasa naki magana tun farko, na zuba ido naga ne ko zasu maka tijarar da mahaifiyar su ta saka su maka, amma Nagode domin kayi min abinda yaran da na haifa suka kasa min, Maude wallahi ban kullace ka ba, domin kayi hakuri da Anum. Nagode sosai Ubangiji ya baka yaran da zasu maka Biyayyar da kai min."

Daga haka malam ya mishi sallama ya shiga cikin gidan,zama yayi a bakin kofar shi, tare da kiran Umma,
Sanye da hijab ta fito tare da cewa.
"Malam Barka da safiya"
"Barka dai Mariyah, gashi ki duba wannan sakon, Ni kam ba zan iya dubawa ba!"

Jin haka Maman Aminu ta fito, dan tana ji a ranta sakin Anum ce.
"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun Ubangiji Nagode maka da ka bani ikon ganin mugun sako. Alhamdulillahi Hauwa ga sakon Yarki!" Ta mikawa Maman Aminu,dake bata da kunya sai gata tana salati.
"Dama na san ba zama da ita zai yi ba, kawai ya aure ta ne domin ya lalata rayuwa da lokacin ta, ai musan irin su." Magana marasa dad'i da kan gado, haka tayi ta sakewa, sannan ya ja hijab ɗinta. Ta fice.
"Mariyah sune suka kashe mata aure, kuma tazo tana wani irin magana kuma" cikin wani irin murya me ban tausayi malam yayi Maganar, wallahi sai ka zubda kwalla,
"Kayi hakuri!"
"Toh Mariyah idan ban yi ba me zanyi? Ko zan cigaba da koran Hauwa ne daga cikin gidana, na Barsu da Allah, Ubangiji yana madakata, Allah sai ya wargaza duk wani tarayyar da badan Allah aka yi ta ba."

"Malam karka yi musu baki domin!" Inji Umma tana share kwallar ta,
"Ba baki bane! Mariyah rayuwar Anum zaki duba, mutumin nan boyayyen mutum ne, tun ranar da Fatimah ta gaya min cewa , wani mutum ya kira shi da wani suna yace ba shi bane, bayan tafiyar shi mutumin yake bata labarin shi yasan cewa Maude ne Major, amma yaki amsa mishi. Na saka ayar tambaya,dan haka da kaina na fara binciken wasu abubuwan akan shi. Sai dai ban yi nisa ba, yace min.

"Malam kai Ubana ne, don Allah ka dakatar da binciken da kake, ka barni cikin rigar aron da nayi don Allah karka tsananinta bincinke hadisin Manzon Allah ne, don Allah."
Tun daga lokacin, na daina tare da watsar da abinda nake yi. Amma babu kome, idan ma ɗan Arziki suke sunyiwa kansu biyu babu."

Daga haka ya mike zai shiga dakin shi, jiri ya kwashe shi zai fadi Umma ta rike shi, da kanta ta kai shi dakin sannan ta kira Binta ta gaya mata maza tazo, jikin Baban su ya motsa.

A gidan Maude kuwa, tunda ya shiga, bai kuma bin ta kan matan shi ba, dakin shi ya wuce, ya rufe kofar d'akin, tunda yake da Nana Aicha bai tab'a jin yasake ba, dukda kuwa bata haihu ba, aka kuma bashi Auren Charifah. Wacce itama sun jima da ita har ƙaddara ta ta basu, basu haihu ba. Amma dai dai da rana daya bai tab'a jin zai sake su ba. Amma lokaci guda dangin Anum sun saka shi yin abinda bai yi niyya ba, har Alkalin yana cewa. Ya bar musu Unguwar su da kofar gidan su. Anan ne yacewa Alkalin.
"Naji duk abinda kace, amma baka da hurumin d'aga ni a cikin Unguwar su, domin ina da abin yi a cikin Unguwar, Auren Kanwar su na ji zan rabu da ita, dan tunda nake ban tab'a taka kotu kowacce iri ba, amma yau sabida Khadijah na tako ta, dan haka zan baku lafiya unguwar kuma babu yadda kuka iya dani!"

Daga haka ya juya ya ficce daga Office din,yana jin kamar zuciyar yi zata fado.
Muryan Maman Aminu yaji, dan haka ya lumshe idanun shi yana jin tana cewa Anum..
"Fito muje, Allah ya rabaki da kangin talauci, maza zo muje ai kwarya tabi kwarya, ke sai dai a girka a baki kici ba sai ki girka ki ciyar ba, domin ke matar shiga mota ne."

Ajiyar zuciya ya sauke, da a ce sun gaya mishi Anum mota take bukata ai da ya saya mata,

Kallon Mamaki takewa Maman ta.
"Ban gane ba? Ina zan tafi? Bayan".

"Toh sakarya sake ki yayi!"
Wani irin faduwar gaba tare da jin kamar zuciyarta zai diro daga kirjinta, haka ta rike kirjinta tana jin wani abu yana taso mata har wuyarta, zuɓewa tayi a kasa, tare da kokarin niman numfashinta da yake kokarin Barin gangan jikin ta, sai bude baki take. Da sauri Maman Aminu ta shiga dakinta ta dauko goran zam-zam ta saka mata a bakinta sai da ta shanye tas, kafin ta sake wani irin kuka tana cewa.
"A'a wallahi ba zai sake ba, wallahi ban mishi kome ba."

Da gudu ta nufi dakin shi, dai dai...
□☹□
Wallahi ba zan iya baku ta firabet ba! Masu Niman grp kuma bani da Grp domin duk sun cika, a saka ku a grp ku kasa yin motsi □ nan kuma kun hana wasu shigowa, tunda ai a grp din da na fita ba wani abu kuke ba, sai aukin stickers, da ba zan turo page ba, a dame Ni da nima, Allah na fara gajiya□□□
#Mai_Dambu[2/5, 8:16 PM] +234 806 035 9614: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA UKU.

_Tun farko na gaya muku! Zanen Qaddara ta ba labarin SOYAYYA bace! Labarin ce da aka gina shi a tafarkin Kauna! Labari ne da yake wanzuwa a cikin wannan zamanin Labari ne da yake tafiya dai dai da zamani riga! Dan haka ku biyo zanen ƙaddara ta ku dauki na dauka ku yarda na yarwa domin tamkar hanjin jimina ne

akwai naci akwai na zubdawa □□□□□□ karku manta da dannewa katanga tare da dunkule hannun □□_

Mik'ewa yayi domin ya rufe kofar d'akin shi ta shiga da gudu . Tana ture shi, fadawa kirjin shi tayi tana kuka tare da dukar shi. Tana tambayar shi.
"Meye nayi maka? Me yasa zaka min haka! Na baka hakuri jiya na gaya maka zan zauna da kai me yasa ba zaka gane haka ba, me yasa ba zaka gane abinda nake fada ba.
Maude kayi yadda kake so dani ba zan hana ka ba, amma karka kace ka sake ni, don Allah ka rufa min asiri."

Jingina yayi da bango, yana kuma jin wani tashin hankali a ran shi. "Maude kace ka fasa!" Ta faɗa cikin kuka.
"Kiyi hakuri! Kije gurin Mahaifiyar ki!"

Yana gama fadar haka ya cireta a jikin shi tare da fidda ita waje, ihu take tana kiran shi. Ai kuwa ran Maman Aminu ya b'aci ta rufeta da duka, tana janta har waje.
"Wayyo Maude kazo kace ka fasa, Maude kazo ka ɗauke ni, don Allah kace ka fasa sake ni, don Allah Maude."

Haka Maman Aminu taja ta har gida, suna shiga ta wuce dakin Umma da gudu ta faɗa jikinta, tana kuka da ihu.
"UMMA na maude ya sake ni"
"Toh Anum amma naga abinda kuke bukata ya baku meye na kuka a ciki? Ba sakin kuke nima ba tsawon wata biyar? Alhamdulillahi ya huta kema kin huta, amma ki sani idan kece kika zalince shi Allah ba zai barki ba, idan kuma shi ya zalince ki Allah ba zai bar shi ba."
Daga haka ta nuna mata hanyar waje, tunda ta fita ta zauna a bakin kofar a hankali ta shiga dakin Malam, ta same shi kwance yayi rigingine, zama tayi tare da rike hannun shi.. yadda ta kifa kanta a jikin gadon shi tana kuka, yayi duk sai yaji babu dad'i.
"Karki damu! Ba shi ya zabi rabuwa dake ba, tilasta mishi aka yi, dan haka kiyi hakuri. Ai nasan Uwata zata iya daukar haka a matsayin ƙaddarar ta ko?"

"Malam! Amma kuma yana da kirki, kuma ya zauna da ni bai taba min dole ba, malam."
"Ya Isa Anumullah."
.dan baya son jin yabo ko gwarzanta maude daga bakinta, duk wanda ya tozarta maude bayanta ne, duk wanda ya wulakanta maude bayanta ne,

Itace ta bawa Mahaifiyar su damar ayi hakan. Suna cikin wannan yanayin Aunty Binta bata iso, suka gama duba malam sanan dan ita da abokiyar aikinta ce.

Kallon Anum tayi, bayan ta dawo daga raka kasarta,
"Anum, me ya faru?"
"Mmmm! Wancan dan ciranin ya sake ta mana, dama ai ba zai iya ba malam ya saka bashi ita toh ga sakamakon nan!"

Kuka Anum take tare da cewa.
"Saka shi aka yi ya sake ni, shi ba zai sake ni akan kan shi ba, Allah sai ya saka min, an raba Ni da mutumin kirki."

Haushi ya kama Maman Aminu, ta dauko mucen tuwo. Ta shiga kwala mata. Tare da gaya mata wasu kalaman da dole idan mutum ya nutsu zai fahimci inda Maman

Aminu ta dosa, daga cikin su kuwa har da cewa an asirce mata yarta da tsafin buza ne, magana wasu marasa dad'i,

Daga Umma har Binta babu wanda ya ce mata ta tafasa balle ta kone, har Binta ta bar gidan, bayan umma ta gargade ta, akan karta ji ta gayawa yan uwanta mutuwar Auren Anum.

Wannan karon Umma zuba musu ido tayi, domin da dare Anum tafiya take gurin Maude, ta saka shi a gaba tana kuka, inda take baya duba har ya tashi ta shigo gida, nan ma da Maman Aminu ta Fahimci ta kashe maciji ne bata sare kai ba, sai ta kuma saka Anum a gaba suka bar Bauchi..

Wannan shi ne mafarin fadawa ta hanyar da ban bulle ba
Na kalle su, naga suna kuka. Kallon agogon dakin nayi sannan na cigaba da basu labarin kamar haka.
.... Tunda muka isa, ba a ce min kome ba, sai dai daga kulawar da ake bani ya sani fara jin kamar ana danne min kewar maude, a hankali naso Mantawa da wasu maude, watan mu uku. Na manta da rayuwar shi, sannan muka dawo da Mama.

Lokacin da napep din mu ya tsaya a kofar gidan mu, sauka nayi tare da fidda jakar mu, kudin napep din zan mika, naga an bawa me napep ɗin kudi juyawa nayi muka kalli juna. Dauke kai nayi sabida kamar ana watsa min ruwan zafi, yana mikawa ya wuce abin shi.

Dauke kai Anum tayi tare da kallon Mamanta zata yi magana ta nuna mata kofar gidan, da gudu ta juya tana dariya umma ce tsaye tana murmushi, rungume juna suka yi dan tayi kewar yar nata.

"Autana sannu da dawowa! Yawwa Umma na, na same ku lafiya"
"Alhamdulillahi, mu shiga cikin gidan." Haka Almajirai suka shigo mana da kayan mu, tare da Mama. Tunda na shiga cikin gidan,nake raba idanu ga Baba Hama tazo gidan, dakin da nake da shi aka bata.

"Toh yar gwal har an dawo daga ga lakwajan ne?"
"Eh Baba mun same ku lafiya?"
"Hmm! Lau,"
"Umma na ina Malam dina nayi kewar shi."
"Yana nan d'azun yazo dubawa ko kin dawo,"
Wai irin murmushi take tare da gyada mata kai, haka suka shiga dakin Maman Aminu suka gyara ita da Maman ta, bayan tasha katon kashedi, tare da rike mata kunne.

Da karta ji karta gani wani dogon sabo ya shiga tsakanin su da Umma.. gyada mata kai tayi, ita Maman Aminu tana tsoron kar Umma ta dan karya mata abinda tayiwa Anum na Mantawa da Maude, shi yasa take gargad'in ta. Sai dai kuma tsakanin su babu wanda ya isa ya shiga.

--- bayan dawowarnsu yan uwan ta, da malam sun ji dadin ganinta, gefe guda Xoxo da Beauty har gida suka zo mata jajjen mutuwar aurenta, kallon su take tana son tunowa ita ta taɓa aure ne, karshe dai haka ta amsa musu.

Tun daga lokacin suka kuma dinkewa kamar da can baya, sake kulla alaƙar su ya sanya Anum ta kuma sanin wasu abubuwan akan rashin kunya, fitsara wanda yaci Uban nada, kiriniya kan ba a cewa kome.

Ga shegen yawon tafiya bikin ko yar uban waye, tsakanin ta da Maude harara da hantara, ta tsane shi sama da kome a duniya, bata kaunar ta kalle shi. Asalima idan aka ce mata ta zabi mutuwar shi zata zab'a.

Haka ta zama wata karamar Side chicks, wannan na sauke ta wannan zai dauke ta, Anum ko kasuwa ta shiga sai ta fito da zawarawa.. wannan gaga din da take yasa ta kuma fallewa..su kansu zawarawan kashe mata kudi suke na bala'i, Anum ta zama wata big beby, ga Maman Aminu har maganin gyaran jiki take saya mata, Umma da Malam nasu ido. Uwar kwaɗayi Baba Hama, ana bata tana gulma dan ma Umma bata daukar iskanci, tsefeta take tare da nuna mata illar haka.

Dan ita Umma da zuciya daya take tare da Maman Aminu.

Zaune take tana waya, Rulwanu ya shigo, kallonta yayi sabida ta canza daga yadda ya santa abaya, tana shafa man bleaching. Ta kuma fari sama da nada, yadda take wayar zaka rantse da Allah, bakinta ciwo yake saboda baka jin me take cewa.
Bayan ta gama yace mata.
"Akwai wani yana miki magana a waje."

Hijab ta saka tare da cewa.
"Toh kace mishi ganin nan zuwa."
Tsaki yayi sannan ya zauna abin shi, dariya tayi sannan ta fita,

Sauke glass din motar shi yayi yana murmushi.
Dafe goshinta tayi sannan ta shiga kusa da shi.
"Sorry alhaji, na rashin maka kwantancen gidan mu!"

"Toh Anumullah! Baki gaya min sunanki ba, sabida kina ganin na tsofa ko? Toh ga Alhaji Mudi wuntin dada nan yazo baran soyayyar ki ya sani zuwa gare ki ta hanyar Aminiyarki XOXO."

Dauke kai tayi tana kallon waje, ita duk rashin hankalin ta, bata iya sake jiki na miji ya more ta ba.
Hannun shi taji a saman gwiwarta, ba wani sabon abu bane a gurinta, duk da tasan shi abu zasu nima ba, iya su sanyi shafe shafe da dai soyayyar shan mintin nan da ake tana sakewa ayi da ita, amma bayan shi bata jin zata iya sakewa wani namijin ya lalata mata rayuwa.

"Alhaji Ni ban ki maka ba, kawai irin soyayyar da kuke dasu Xoxo baya tsarina."
Daga haka ta juya zata fita yace mata.
"Toh meye Matsalar ki?"
"Ba ma zai yiwu bane kana tare dani kuma kana tare da kawaye na, sannan kuma ka zago gurina taya haka zai yiwu?"
Ta kafe shi da idanu, murmushi irinta yan duniya yayi mata sannan yace mata.
"Karki damu sai na rabu dasu.".
Girgiza kai tayi sannan ta fita daga cikin motar.

Bata ko mishi magana ba, tana zuwa dab shagon Maude suka zubawa juna ido na wasu dakikai, kafin ta dauke kanta daga gare shi ta nufi cikin gidan, gabanta yana faduwa.

Kallon shi Xoxo tayi ai tasan za ayi haka, ita da take burin ya aureta shine zai zo mata da maganar banza. Mik'ewa tayi sannan tace mishi.

"Ka cigaba da nace mata, sai dai fa bazawara ce, kuma kaga zata fi sanin wasu abubuwan wanda da ace budurwa ce zata baka wahala. Dan haka kayi ƙoƙarin nace mata. Tana son kyauta da kuma son rayuwar hutu, idan ka shiga mata haka zata iya baka hadin kai.

Dauke kai tayi sannan ta sake kayanta tana kuma jin tsanar Anum a ranta, idan ta fahimci wani abu Anum ta zame mata karfen kafa, sannan a duk lokacin da ta taso domin gyara GOBEN TA, wargaza mata take.

"Ai ina miki addu'a Allah ya kawo miki miji nagari, wanda zaki huta na huta, ina dalilin kasayar da akuyarka ta dawo tana ci maka katanga." Inji Maman Aminu,
"Kwarai! Ai Anum yarinyar nan ba karamin farin jini ne da ita ba, Ni ina ganin a manemanta har da attajiran aljanu, kiga idan ta fita sai ta shigo mana da kayan Arziki."(😂 Chaiii if you no die you go neva see wandaful pipul shaa naji ance wani abu)

Wani irin murmusa mata Maman Aminu tayi, tare da wurga mata robon vanilla ice cream, tana lasa.
"Ai yarinyar tasan darajar kanta, gashi kaf unguwar nan da gidan nan babu wanda yayi farin jininta, Yar Arziki irin albarka yar da aka haifa tsiya na barci."

Murmushi Umma tayi tana lazumi, domin duk abinda Anum take ƙawowa bata taɓa amsar shi ba. Wani lokaci a dakin Umma Anum take boye abubuwan da taxo dashi, domin Maman Aminu da Baba Hama idanun su idanun abinda tazo dashi.

Haka wani lokaci Baba Hama zata na yadawa Umma magana, basu isheta ba balle tayi kokarin biye masu..

***
"Khadijah!" Ya kira sunan ta dai dai zata shiga cikin gidan "Malam me shayi! Da wani abu ne?"
Ta tambaye shi, murmushi yayi sannan yace mata.
"Kawai rayuwar da kike ne sam babu wani Cigaba a cikin shi, babu dad'i yau ace kina hawa wanan motar kina sauka a wancan motar"

"Toh kace kai ma ka fara sana'ar banza sa'ido sana'ar banza, wato kana jin haushin dan ban kula ka ba shine bari ka fake da guzuma ka harbi karsana. Idan ka cika d'an halak karka kuma min magana, banza dan kauye kawai."
Kura mata ido yayi sannan ya dauke kanshi, tare da cigaba da jinjina kalmar banza dan kauye da tace mishi. Komawa shagon shi yayi yana kuma rokon Allah ya bashi dama ko wacce iri ce ya nuna mata shi dan banzan dan kauye ne.
#Mai_Dambu
[2/6, 9:18 AM] +234 813 026 9641: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA HUDU.

*_Fatan Alkhairi Sadnaf □□□□□ Nagode sosai_*

□□□Na gaya muku bani da salo da□ amma akwai Chakwakiyya zalla□ irin sa zuciya tsalle□□□

Shiga tayi cikin gida tana kananun rashin kunyar ta, sabida ta tsani renin hankali, ji fa sai kace Ubanta yana wani irin magana sai ka ya ajiye ta, irin ga yar shi.

Nan Mama da Baba Hama suma suka shiga maganar suna gaya mata idan ya kuma mata magana karta raga mishi tayi mishi tijara taya za ayi dan cirani da kazamin rayuwar shi zai sakawa yarinya me tsada idanu.

Tun daga nan, bai kuma mata magana ba, amma ya zuba mata idanu.
--- Tare da Alhaji Mudi wuntin dada, suka fito daga hawala hotel. Daga nesa Rulwanu ya hangota. Cikin b'acin rai ya sauka akan mashin din da yake tafiya ya nufi inda take, bai yi wata wata ba, ya finciko hannunta yana janta. Duk da ta razana amma yarinyar nan cewa take.
"Malam lafiya? Waye kai da zaka rike hannuna Jama'a ku taimake ni wallahi ban san shi ba, dan iska ne"

Lokaci guda yaji kamar an daure shi da jijjiyar shi, a hankali ya juya ga mutane da suka Mishi kawanya, ji yayi zuciyar shi zata kwace daga kirjin shi. Bakin shi na rawa, ya juya zai mata magana. Aka rufe Rulwanu da duka, sosai da sauri ta nufi gurin Alhaji suka bar gurin.
Khadijah amma yayanki ne fa? Idan suka kashe shi fa?"
Tab'e baki tayi tare da dauke kanta tana kallon waje.

"Ni Wallahi ban tab'a cin abinci me dad'i irin na hawalan nan ba, kome nasu yayi babu laifi"
"Haba gobe ma ai zamu iya dawowa idan kin yarda"

Dariya tayi tana kallon shi, bude asusun motar shi yayi ya ciro mata wata kwali, sabuwar waya ce dall, juya wayar take cikin wani irin yanayi me cike da jin dadi da mamaki.

"Ya hajj, duk Ni daya?"
"Haba Baby ai kinfi haka ma," wani fashewa kanta yayi tana murmushi har suka isa unguwar su. Murmushi yayi tare da riko hannun ta ya sumbata,

"Mun iso gida, me zan kawo miki da daddre?"
"Alhaji ka kawo min Habib yorgot da duk wani abin makulashe."
"Baki da case!"
Suka yi sallama zata fita yace mata.
"Baki ji ba" tsayawa tayi tana kallon shi, ganin yadda yan shagon Maude suka zuba mata ido.
"Gashi nayi typing so jiya na dawo, na manta ga tsarabarki" mika mata jaka yayi ta amsa bayan wayar da ya saya mata har da wani kayan, k'arara ta fidda halinta nason abin duniya, tana murmushi ta amsa tare da mishi godiya, dake tsohon banza ne, muna mata yayi. Ta sumbaci kumatun shi.

Babu b'ata lokaci ta kai bakinta, tare da sumbatar shi, sannan ta fita tana mishi godiya.

Tun da ta fito, sau daya ta kalli Maude, sannan ta dauke kanta gabanta yana faduwa. Tana tsaye Alhaji yabar kofar gidan su..ya tafi sanan ta nufi hanyar cikin gidan.
"Kasan yanzun zawarawa sun zama ƙaruwai! Basu maida bin maza a bakin kome ba"

Cak ta tsaya tana kallon su, murmushi tayi sannan tace mishi.
"Dayyabu! Da tsohonka muke karuwanci, shi yake biyana kudin karuwanci. Kai ma munafukin da kake ajiye su sai na zagi danginka mara zuciya, wanda tsiya da talauci ya hana shi zaman kasar shi ya shigo cin Arziki."

Magana marasa dad'i da muni take gayawa Maude..
"Ke dan Uwarki!"
"Ka gayawa Babar Asabe"

"Jɨjjiya!"
"Wallahi wannan yarinyar, shikenan Oga."
Ya faɗa cikin jagaliyanci, tare da cin magani, bata fasa zagin maude ba,.har da cewa.

"Idan kayi zuciya kabar min kofar gidan Ubana, tunda anan aka makale ake zagina Annamimai munafukai."

Wallahi zaku sha mamaki, babu wanda ya kuma kulata manna mata hauka suka yi abinsu.
Da wannan bakin cikin ta shiga gida, ko zama bata yi ana aka yi sallama da Umma, lekowa tayi tare da cewa.
"Anum leka ki gani wake sallama"

Zuba kayan tayi sanan ta koma kofar gidan, Ila ta gani..kallon rashin imani yayi mata sannan ya dauke kai yana faɗin.
"Ki min sallama da mahaifiyar Rulwanu"
"Mtsew banzan dan ƙauye!"
Aikuwa ya bita zai mare ta, tace.
"Mare ni ka gani, wallahi zaman Bauchi cirani sai yafi karfinka."

Sake sallama yayi bai kulata ba, fitowa Umma tai dan tana jin rashin mutuncin da Anum take mishi, kallon ta tai tare da girgiza kai tai sannan tace mishi.
"Lafiya malam Iliya?"
"Toh Rulwanu ne ya gamu da hatsari. Yana asibitin badan Allah ya kawo ni ba, toh da sai dai kuyi hakuri"

Shiru tayi sannan tace mishi.
"Wani Asibitin?"
"Nan bakas!"
"Toh bari na kira yayun shi. Nagode sosai Allah ya saka da Alkhairi."

Sannan ta koma cikin gidan, ta kira Sadeeq ta gaya mishi, ko awa daya ba ayi ba sai ga yaran Umma dukkansu suka nufi asibitin da Rulwanu yake.

"Me ya faru haka?"
Murmushi me ciwo yayi, maganar Maude yana dake yawo a kanshi.

Khadijah yar Uwarka ce! Idan ka gayawa Umma har abada ba zata daina ganinta da tabon ba, kayi ƙoƙarin shiru ka mata addu'ar shiriya, sannan idan ka yi magana ma zai iya zama rikicin cikin gida, don Allah ka kyaleta muyi ta mata addu'o'in shiriya

Idanun shi ne ya cika da kwalla, badan Allah ya kawo ila akan lokaci ba, da shi kan yasan ya tashi aiki. Share kwalla yayi.

Bayan tafiyar Anum da Alhaji mudi, aka rufe Shi da mugun duka, har suka cewa zasu saka mishi taya, kokarin ya gaya musu Kanwar shi ce amma suka ki, sauraron shi. Shi kuma ila ya fito amso kwai ne yaga taron mutane har zai wuce ya tsaya tare da tambayar me ya faru, nan ake gaya mishi ai wani ne yazo sace wata budurwa, ta yi ihu shine aka rufe shi da duka.

Gyada kai yayi zai wuce, sai suka d'aga shi sama, shine ya hango rigar kamar na Rulwanu dan har yana mishi tsiya da cewa yayi zuciya ya canza yar gado, ajiye kwan yayi tare da tsallakawa.

Ya ciro wayar shi ya kira MAUDE, ya gaya mishi don Allah yazo akan lokaci. Shi kuma taje ya leka yaga Rulwanu ne.
"Subhanallahi! Malam Rulwanu,"

Dakyar ya bude idanun shi da suka kumbura.
"Kunga d'an uwan shi abokin satar mutane!"
Juyawa suka yi tare da nufar Ila, suka mishi caaa.
"Kasan shi ne? Wato tare kuke sana'ar sace mutane? Toh zamu kona ku."

"Kuna da hujjar da sace ta yazo yi?" Maude ya tambaye su, lokacin da yake karasowa gurin, ya cika musu ido sosai, kwarjinin da yayi musu yasa suka kasa bashi amsa.
"Rulwanu me ya faru?" Ga baki daya ya fita hayacinshi ya fara mishi bayani,
"Yarinyar da kuka dake shi akanta kanwar shi ce. Ko baku ga kama bane?"

Riko shi suka yi tare da saka shi a napep, suka nufi Asibiti da shi..anan yake rokwanshi ya rufa mata asiri.
"Mara kirkin mutum! Kaje ka lakato rigima sun maka rotsi, toh bani zaman jinyarka."

Umma ta shiga mishi fada, kwallar bakin ciki, da tsanar Anum yasa shi kuka(😂😹 shegiyar yarinya kowa sai yayi kuka da ita) yana yi yana kwashe mata albarka, tare da jan Allah ya isa yafi kwando dubu.(😂😹)
.... Lokacin da Umma ta dawo gida tana faɗa abinda ya faru, dariya Anum tayi tare da gayawa Maman Aminu abinda ya faru, tace.
"Allah ya kara duk wanda ya nufe mu da mugun nufi sai yaga karshen abun shi."

Suka ci-gaba da hidimar su, dakyar Anum tayiwa Umma jajje.

..... Da dare, zata fita dake babu wuta sai a shagon Maude, zauren gidan da akwai duhu Sosai. Tun a bakin kofar cikin gida ta hango mutum a tsaye, saka kanta da tayi zauren kamshin turaren shi ya daki hancinta.. sassanyar ajiyar zuciya ta sauke, yana tsaye tana zuwa zata gitta ta gefen shi ya fincikota. Tsoron shi ne ya cika zucuyarta. Ta kasa magana.
"Akan wancan dan iskan kika wulakanta yaron da uwar shi da yayun shi suke miki hidima? Anum wacce irin lalacewa kika yi ne? Maza sun bude miki idanu baki ganin kowa da gashi. Kyamar ki nake ji! Tunda kin zama abinda kika zama, wawuya jahila wacce gata bai mata rana ba."

Daga haka ya ture ta, ta fadi shiru tayi domin tsoron kar yayi mata wani abu, haka ya fita ya barta kafin ta sami damar mik'ewa ta fita, a gurguje suka gaisa da Alhaji ya bata kyautar shi da ita. Sannan ya bar kofar gidan su.

"Alhajin Allah, ai ko uwar Khadijah kasani na dauko maka zan dauko maka ita balle ita kanta, yanzun ka cigaba da jan ra'ayinta da kyaututtuka wanda zai saka ta bika ko ina!"

'"Yawwa Xoxo, haka yayi min.kuma zan baki kyauta na musamman. Amma yaushe ne zaki kawo min ita?"

Shiru tayi sannan tace.
"Ka bari nan da sati Uku."
"Kai ina wallahi a matse nake da ita, kuma idan ban yi yadda nake so ba, kai har sati Uku!"

"Toh shi kenan kayi yadda kake so?" Ta faɗa tare da bude motar zata fita.
"A'a bai kai haka ba, na amince."

"Akwai bikin yar Shehu, zamu yi anko ka bata kudin zan kai mata ankon ta gani sai ka saya mata. Idan yaso sai ka kaita gidan ka na bayan airport ba."

"Nawa ne zan baki?" Kallon shi tayi sannan tace.
"Yadda idanunta ya bude da me shayi bani hamsin, da ace a budurwan ta ce zan iya amsar dari ma,"

Dariya yayi tare da shafa fuskar ta, ya ciro kudin sannan ya ce mata.
"Karki ji kome idan tayi min zan kara miki sama da haka"
Tab'e baki tayi sanan tace mishi.
"Karka damu ai wani ya tsotsa abinda zaka samu dan haka wani abu da zaka samu!"

Haka dai suka yi ta jayayya har ta gaji tare da fita daga cikin motar.

..... Bayan kwana biyu, aka sallami Rulwanu, tsakanin shi da Anum ido, domin Allah ya gani tsoron sharrinta yaƙe, yarinya karama ta zama bom, dan haka baya mata magana. Sau dari idan zai shigo gidan ya same ta ita daya baya tab'a kallon inda take, zunzurutun sharrin ta. Ita kuma tsabar niman tsokana idan ta ganshi dariya take mishi, bai tab'a damuwa ba.

... Matar Aminu da ta haihu, kullum zata fita zuwa gidan nan kuwa yawo take fita da Alhajin Allah, wanda yanzun take mishi lakabi da suna baby, idan yace mishi baby.(soko 😂 Chaiii)
Abin haushin haka zai ta yawo da ita, ana gobe suna ya dauke ta zuwa Zaranda hotel,. Anan suka yi kicibis da Ya Abubakar, ranshi ya kai kololuwar ɓaci. Har inda take ya nufa sannan ya nuna mata motar shi, babu musu ta juya, ba tare da ta cewa Alhaji Mudi wani abu ba.
"Alhaji mudi, kai babban mutum ne. Kuma kana da wasu abubuwan na girmamawa. Don Allah ka rabu da kanwata."
"Toh amma ai ni sonta nake"
"Ba soyayya bace, Muradin rai da zuci ne don Allah ka bar mana ita!"

Bai kuma magana ba, yana kallon su, suka bar hotel din. Tunda ya saka ido akanta sai da yayi abinda yake so da ita zai kyaleta.

.... Bai mata magana ba, suna isa gida, ta fita, bai iya hakuri ba dan ya zuciya sosai..dan an sha kawo mishi karar ta, da abinda take aikatawa. Yana shiga kawai cikin gidan ya shiga rufeta da duka. Aikuwa Hafsat da Safiyya suka fito.

Tare da tambayar me ya faru, ranshi ya b'aci.

"Zaka kashe ta ne? Wannan rashin imanin na me?" Inji Hafsat.

Bai fasa dukarta ba, sai da Umma tace mishi.
"Ban sanka da wannan halin ba, ka kyaleta idan ka kuma d'aga bulalan a jikinta lallai furucin da zai fito bakina zai tab'a har bayan bayanka!" Wurga da bulalar yayi, cikin bakin ciki ya kalli Umma da jajjayen idanun shi,
"A hotel na same ta ita da wani mutum wanda kowa yasan mutumin dan iska ne da tsofar shi yake bin Kananun Yara."

"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, sharrin da ake bin mu dashi kenan? Toh Allah zai gwada maka me zuwa hotel ba dai ANUM KHADIJAH ba, sharrin da kayi mata sai ta koma kanka da y'ayanka."

#Mai_Dambu..ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA BIYAR

Bawa baya wuccewa ƙaddarar shi, tun ran gini tun ran zane! Dukda naso zuciyata! Haka ba zai hanani kiran abubuwan da suka faru dani a matsayin ƙaddara ta ba! Zanen Qaddara ta ce ban isa tsalleke shi ba

"Kai Maman Aminu, kai Maman Aminu Maman Aminu kina kuskure, Maman Aminu duniya tana kawo miki yadda kike so, Insha Allah ni mariyah da yaran da na haifa da cikina babu wanda zai kuma d'aga ido yayi miki magana ke da yaranki gamu ga Duniya!"

Tankar saukar aradu Anum ta ji saukar muryan umma, wani irin kuka ne ya kwace mata, tana niman rike kafar Umma, ta nunawa Abubakar hanya tare da kakkausar kashedi akan Anum, haka ya fice tare da alƙawarin ba zai kuma shiga harkan su ba.

.... Kukan da Anum take kamar ana yage namar Jikinta, ba daukar ne yake damunta ba, banzatar da ita da Umma tai yafi kome mata ciwo, dan haka ta shiga tashin hankali. Kafin wunin ranar ta manta da kome, har zuwa dare.
Ai tunda Umma tace babu ruwanta ita da Yaran ta, Maman Aminu ta kuma buɗe idanunta suna zuba iskanci, duk yadda suka so su tinzira ta, bata tab'a d'aga ido ta dube su ba.

Asalima nunawa tayi bata san suna yi ba.

---- kamar dama jiran Umma suke ta daina saka musu ido, Anum ta tsiro da wani sabon iskanci, idan ta fita hira bata dawowa har sai malam ya rufe kofar gidan, mamanta ta bude mata. Wanda ba kome bane yaja haka sai banzan hirar da suke.

Maude da ya saka ranshi a wahala, kasa komawa gidan shi yake sai ta shiga gidan shi, abin na matukar mishi ciwo. Musamman yadda ake cewa a unguwar yana kallon tsohuwar matar shi ta zama kason dankali, sai yadda aka yi da ita. Bai tab'a cewa kome ba,yana dai kallon kowa da abinda yake ranshi.

Tsakanin shi da matar shi,suna zaune zama na rufin asiri, babu wanda yake jin kansu. Asalima tana ƙoƙarin kyautatta mishi ta kowani ßangare, abin da ya fahimta

akan ta,tana da mugun kishi. Idan zai fita shafi tayi ta fushi kenan, har sai ya dawo cin abincin rana.

Akwai ranar da ya dawo ya samu tayi parking kayanta zuwa part din Anum, Maude babu kunya yace mata, ta koma inda ya ajiyeta inda rai da rabo matar shi zata dawo gare shi, dan haka babu wanda zai zauna a part din ta,. Dole ta koma nata babu shiri.

Akwai abubuwan da idan Anum ce, zai iya mata amma Matar shi ta gida yana kai zuciyar shi nesa akan ta.

"Assalamun Alaikum!" Umma da take tsince shinkafa ta amsa musu da.
"Waalaikumun Salam!"
Dake tasan su Xoxo ne kuma sun kulla Abotar su da Anum yanzun bata kuma kallon su ba.
"Ina wuni Umma?"
"Lafiya!"
Daga haka bata kuma kallon su ba, asalima dauke kai tayi..tana aikinta.
"Abidah ku shigo mana!" Inji Anum da ta leko, kallon shashin da Umma take aiki tayi,.sannan tace.
"Ku shigo Mana bata nan!"
"Toh sauri muke, ankon yar shehu kuka kawo miki, ko zaki samu yi?"
"Toh ku shigo mana!"
Babu musu, suka shiga. Mika musu sabuwar wayarta tayi sai kayan kyaututtuka da Alhaji yake bata, tare da basu labarin tana dariya.
Murmushi Xoxo tayi sannan tace mata.
"Ai kuwa bikin da zamu yi abokin su ne zai auri yar Shehu, Kinga wannan material din dinner ce, sai wannan atamfar ranar wuni,"

"Toh aikuwa zanyi amma zan tambayi alhaji idan na samu zan kiraki."

Ta faɗa tana kallon kayan da suka dauki hankalinta, mik'ewa tayi tare da cewa.
"Ban baku ruwa ba!"
"A'a ajiye abinki, muma tafiya za muyi."
Inji Beauty, haka ta rako su waje suna hiran batsa tare da maganar banza, dariya take tana kallon su har suka fita kofar gidan.

Kamar ance ta d'aga kanta ta hango su, kamar abun bai dame ta ba, amma kuma tana dauke kai ta ji lallai dole sai ta kuma kallon su. Maude da matar shi, suka kan mashin yana magana da ila. Bugawa kirjin ta ya fara kamar zuciyarta zai diro, kallon juna suke da matar Maude tana mata dariya, dauke kai tayi abinta, sannan ta kuma kallon Maude wanda shima fuskar shi babu walwala, hararar shi tayi sannan ta ja tsaki tare da murguda mishi baki.

Ta juya zuwa cikin gidan, tana kananun magana.
"Ko ina sai sun nunawa duniya su ma'aurata ne tsabar Iskanci."

Umma tana jin ta,ta tafasa bata ce ba balle ta sauke, sallamar maude da matar shi wacce tayi mishi magana akan ya dace su gaida Umma ai.

"Waalaikumun Salam, ku shigo mana! Anum dauko min taburma" tana tura baki ta fito daga dakinsu, tare da shiga dakin Umma ta dauko taburma ta shimfid'a musu, sannan ta juya zata koma.

"Idan dan basu ruwa mana. Barkan ku, Hajjo ya kwana biyu."
"Alhamdulillahi! Umma muna lafiya, ya sanyi da zafi."

Anan sukayi ta gaisawa, wato fitowar da Anum tayi sanye da wata doguwar rigar English wear, ya saka maude kura mata ido, ajiye musu ruwan tayi sannan ta juya abinta, ai kuwa haka ya bita da ido, kasa magana yayi amma Anum ta gama dashi.

Daukar ruwan hajji tayi tare da fara sha, Anum ta kuma fitowa,.zata nufi kitchen. Umma tana halkance dasu, wato Anum bata son maude amma tana kishin sa.

Kamar yadda take lura da Anum ɗin, yanzun ma zani ta daura tare da wata shimi, ta daura top akan shi. Tana tafiya tana girgiza kirjinta. Kusan duk rabin maganar da suke da Umma ba fahimta yake ba, asalima ji yaƙe kamar ya dauke matar shi ya gudu da ita a maida musu auren su, ya fasa hajjo da tazo ta kular da Anum maude ya zama nata, sai gashi kamar zata fashe da kuka.dakyar ta matsa mishi suka bar gidan.

Tun fitar su take masifa tare da cewa ta fasa zuwa gidan su ma. Ita kasuwa zata ta sayo English wear, bai hana ta ba.. amma suna shiga gidan su, sai da ya tirmushe ta, domin Anum ta yadda mishi hankali.

Ban daki ya shiga yayi wanka ya kuma saka kayan shi ya bar gidan, yana fita itama ta shirya ta nufi cikin kasuwar muda lawan, layin yan gwanjo..anan ta sayo Kananun kaya, tare da jidar riguna da wanduna.

"Haba baby! Wallahi ba haka bane kawai Ni bana son irin wannan abun ne, idan kana buƙatar haka kazo gidan mu, ayi magana."

Ta faɗa mishi a sanyayye, murmushi yayi mata, tare da gaya mata ai zai zo. Kawai akwai abinda yake bukata ne.

Dauka tayi da gaske dan haka ta shiga narke mishi da shagwab'a.

Satin da ta zagayo da kan shi ya kawowa Xoxo kuɗin ankon Anum ta kawo mata nata har gida, sannan ya kuma zuwa daddare ya kawo mata kudin dinki da kayan kwalliya masu shegen kyau da tsada, bayan ya d'an matseta a cikin motar shi. Kawai burin shi ta bashi hadin kai.

.... Irin b'arnan kudin da yake mata sai ka rantse da Allah, da aure yazo nimanta ba da wani abu ba, kuma munafuki yaki yarda su yi magana da malam, tsakanin shi da Maude kallon banza.

Har ranar ya gaji ya tambayi Anum waye Maude? Tab'e baki tayi sannan tace mishi.
"Wahalalle ne bai da aiki sai saka ido, mara zuciya ya tashi a kofar gidan mu yaƙi!"
Fita yayi daga motar tare da takowa har kofar shagon Maude.
"Kai d'an nijar?"
"Na'am Tsohon banza, Uban yara ashirin da biyar, ka saki mata biyu, dabi'ar ka auri saki, idan ka gama da na gidan kana ganin wata zaka sake daya ka auri wata.

Mafi munin a cikin halayyarka baka da kirki, baka da adalci mace kome tsufar cikin jikinta kana ina lakad'a mata duka! Mafi kazamtar halinka shine lalata kananun yara marasa hankali da nutsuwa ko?"

Kurawa juna ido suka yi, Allah yasa babu mutane a shagon ila da Rulwanu ne a shagon dan shima yanzun ya nace sana'ar shayin yana a.t.b.u a fannin agriculture.

"Kai waye da kake bincike a kaina?" Alhaji Mudi ya tambaye shi a fusace,

"A matsayin wanda ya auri yarinyar da kake yawo da ita, kasan dai ya cancanci yasan waye zai nemi tsohuwar matar shi?" Inji Rulwanu,

"Au kace kishi ne yake damun ka?" Ya tambayi maude wanda yake kurb'an shayi a hankali,
"Ni idan zanyi kishin matar da nake so? Kai baka isa ka d'aga ido ka kalle ta ba, balle kazamin mutum irinka ya sami damar fita da ita, kai kana Sonta ne sabida bukatar kanka Ni kuma sabida Muradin rayuwa ta ce, ko tayi kyau ko ta lalace ba zai hanani kaunarta ba."

Bai kuma ce mishi kome ba, ai kuwa cikin kumfar baki Alhaji Mudi yace mishi.
"Wallahi sai ka san damu ake Damawa a gwamnatin nan! Sai ka san kayi min rashin kunya, kuma akan idanun ka zan yi yadda nake so da Anum! Kai banza d'an cirani..wanda talauci da tsiya suka hana shi zaman kasar shi."

Rike kofin hannun shi yayi wanda rikon da yayiwa kofin sai da ta fara tsagewa, ji yaƙe kamar ya dauki bindiga yayi ta sake mishi harbi kamar me! Dauke kanshi yayi daga kallon shi idanun shi sunyi wani irin jajjur da yayi zagin bai bar shagon ba, ya cigaba da maganar banza tare da gori. Abinda ya fusata Ila da Rulwanu kenan suka mike tare da mishi rashin mutunci.

Asakature! Uwar yan kankanba, ganin ana ture shi ta fito a motar zata musu rashin kunya Rulwanu ya zaro belt din shi, tuni ya koma da baya, ya shiga gida tana gayawa Mamanta, tunda ta fito ta shiga surfawa Maude da Rulwanu zagi da miyagun kalamai, shi kanshi Alhaji tafiya yayi, bayan minti goma da aka samu Maman Aminu ta shiga cikin gida.. sai ga Alhaji Mudi da hilux din yan sanda.

Abin mamaki, take yan Unguwar da matasa suka yiwa yan sandan caaa, dan sun ce babu wanda ya isa ya fitar da maude a cikin Unguwar matukar suka raye, rigimar da ta janyo hankalin manyan mutanen unguwar kenan suka yi maza suka kashe case din, tare da sanin malam suka mishi magana.
"A gaskiya Malam ka aurar da Yarka! Idan ba haka ba gaskiya zamu dauki mataki akanta, kwanaki d'an uwan ta, Rulwanu anan titin awala hotel tasaka za a kona shi sabida ya ganta da wancan mutumin, wallahi ba zamu cigaba da kallonta tana ja mana magana ba,duk cikin Yaranka maza da mata, kuma sun girma a cikin unguwar nan basu ja maka Magana ba, amma ita wannan gaskiya kayi wani abu akai domin zata kai ku ta baro ku!"

Haka suka gama gayawa Malam magana, godiya yayi musu sannan ya dawo gida, bai cewa kowa cikin ka ba, balle kace ga abinda aka gaya mishi. Umma kuwa shiga dakinta tayi tare da kunna radio dinta ta kamo Ba.R.C bauchi..tana sauraren tarihin magabata na Dr Zubairu madaki, hankalinta a rabe, bata jin dadin rayuwar da Anum take..shi yasa tunda ta rabu da sha'anin su, bata daina gayawa Allah matsalar Anum ba.

Kwanakin baya har azumi ta fara, Alhamis da Litinin. Ulcer ce ta hanata yi sai ta amaida shi sadaka tana girka abinci ana kaiwa makarantan almajirai da yake bayan rariya primary school..yanzun ma duk abinda yake faruwa tana jin shi ta kura Radio ta.

Haka dai aka yi ta ririta alamrin Maman Aminu da Baba Hama, suna kara gayawa Anum karta kyale Rulwanu, Umma kan bata san me suke ciki ba, dan haka ta zuba musu ido. Dan lokacin da Rulwanu ya kawo mata karar abun fada tayi mishi.

__ bayan kwanaki kome ya wuce kamar babu abinda ya faru, malam kuma bai mata magana ba, iya kai dai ya shirya mata tsiya ganin idanunta. Duk abinda zasu yi ita da uwarta nan da wata biyu ya kammala.

Yau suka fara hidimar bikin Yar shehu, dan haka bata zama sune Kawayen amarya.

Ranar farko sunyi duk wani abinda ake bukata, irinsu ajo, washi gari suka yi tea party, tun safe da ta fita bata dawo ba sai dare, ranar juma'a, aka daura auren aka wuni ana casu a gidan su yarinyar, bayan sallar isha suka shirya zuwa dinner.
Da sauri ta fito tana kallon agogon wayarta,
"Anum ba hollandia milk!" Inji XOXO.
Amsa tayi cikin jin dadi tace,
"Amma wannan y'a Allah shi tofa miki albarka cikin babban masaki, kamar kinsan yunwa nake ji"
Ta amsa babu bismillah ta d'aga goran yayi sanyi sai da ta sha rabi sannan ta kalli XOXO tace mata.
"Aminiya Nagode muje"
"A'a ai ga motar Alhajin ki can, shi zai kai mu Zindaba hotel!"
"Toh" tace mata tana kuma shan madaran sai da ta shanye tass lokacin har sun kusan isa gurin motar dan tana bakin titin Unguwar ne.

Isa ta shiga gaba, XOXO tana baya, anan suka shiga hira bayan tadda motar.

.... Ga baki daya nutsuwar zuciya Umma ta rasa, meke damunta ga faduwar gaba, alola tayi tare da sallar shafa'i da witiri, kafin wani lokaci zazzaɓi yana niman rufeta.

Maude shima wani irin kunci ya tsinci kanshi da ita, wanda ya rasa gane dalilin haka, kawai ya barshi akan ko dan yaga Anum ta fita ne cikin kazamin shiga.

---- Kasala ne ya fara rufeta tare da kwantar da kanta a jikin kujeran, kafin nan wani irin sanyi me hade da barci.....

Bai zama dole gobe nayi update da safe ba□□□ amma Insha Allah na gama Uzuri na zan muku
#Mai_Dambu...[2/7, 9:04 PM] +234 815 770 3430: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA SHIDA

_Kusan me? Comments dinku na matukar ban sha'awa! Musamman yadda kuka kasu bangare uku! Masu goyan bayan maude! Masu goyan bayan Anum! Da masu goyan bayan Alaƙar su 😂😹 Wallahi idan naga kwamens din Teams din nan

musamman team MAUDE! Maman Hajiya da da sauran su! Team Anum! Auntyn Safiya Jos da sauran su! Dariya yake bani 😂😹_

Bayan awa biyu.

A hankali take bude idanunta, motsin ruwa taji a ban dakin, sake komawa yayi jikin matashin ta kumshe idanunta,tana ƙoƙarin tuno abinda nake da yakinin ya faru da ita, wani irin kuka ne ya kwace mata, lokacin da hoton abin ya shiga yawo a kanta, dakyar ya tattaro sauran kuzarinta ta sauka a gadon, jini na bin kafarta, a hankali ta tsince kayan ta, ta saka takalmin ta da posed dinta a hannun ta rike su, sannan ta fita a hankali tana jan kafarta, da take jin sun mata nauyi. Har ta bar dakin tana fitowa waje taga gurin ya mata irin gurin ban tsoro a haka, da sauri ta yi ta zaga bata samu hanya ba.

Kuka ne ya kuma kwace mata,.tare da dafe goshin ta, tana tir da XOXO itace ta jefata cikin wannan tashin hankalin, dan haka ta ciro wayarta tare da haska wayar tana bin labin tayar mota.

Haka ta tattare skirt ɗinta, ta fita da gudu, tana niman hanyar, dake dare yayi sosai kuma babu farin wata, dan haka duk inda ta kama bi take, bata tab'a ganin irin wannan tashin hankalin ba.

Kuka take kamar ranta zai fita, ga wani irin ciwon da take ji a gabanta kamar an watsa mata barkono, tana jin yadda abu ke bin kafarta dan haka ta cigaba da gudu har Allah ya kawo ta bakin get din gidan, bata yi wata wata ba, ta bude da sauri ta fita.

Sannan ta shiga gudu domin burinta ta fito daga Unguwar.

Ga baki daya ta rasa inda take, dan haka ta cigaba da gudu. Dakyar ta fito daga bayan airport, sannan ta iso bakin titin karfe sha biyu saura minti goma sha biyar, tafiya take da kafa, har ta wuce wani gidan mai a nan ta sami wani me mashin, ta gaya mishi inda zai kaita.

Yace dari biyu, tace ita ya kai ma haka, amma yayi sauri. Dakyar ta iya d'aga Kafarta ta hau bayan mashin din.

** Cikin mugun nishadi yake wanka tare da jin lallai zai tafi da Anum, domin awa biyu da suka wuce ya sami kiran sanata Na'ibi Giwa, akan yazo zasu yi wani tafiya kuma ba zasu wuce wata ɗaya ba, sabida wani kwangilar da suke nima Gwamna yasa musu hannu.

Abinda ya faru kuwa, lokacin sa suka tabbatar Anum barci ya dauke ta.
"XOXO aikinki ya gama, sai dai kar na yarda naji wani abu yana yawo a cikin gari da bakin mutane. Zan iya kome dan na kare mutuncina." Wurga mata kudi yayi, sannan ya ajiyeta a wunti market.

Ta fita daga motar, tana murmushi tace mishi.
"Alhaji! Kasan abinda na zuba mata a cikin milk din nan kai ma ya Kamata ka..."

"Shaidaniya ai tun karfe shida na yamma na had'iye maganin kuzari," ya fadi haka yana dariya. Haka suka yi ta dariya tare da yin sallama, tana jin ciwon abinda Anum take mata, banda Beauty bata kaunar hada wani abu da Anum dan tasan zata iya rabata da shi.

Gurin da zasu yi taron su ta wuce, kamar zata yi kuka.
..... Lokacin da ya isa gidan da ita, bai damu da yadda take ba, ya dauke ni zuwa cikin dakin shi.

Tunda ya baje ta a gadon, ya kunna tv kaset din batsa ya saka, da wannan abun da yake gani ya taso mishi da nashi bukatar dan ya gayawa Xoxo karya ne babu maganin da ya sha, dan haka da yasan ba wani daukar lokaci yake ba, yana hawa kanta bai mata irin dan abun nan na irin shafe shafe dan dama ya gama kwashe shi.

Kawai abinda ya bashi mamaki da yazo,(😹)yaji gurin toh sai a hankali, dan haka ya saka mata karfi baki daya. Yadda ya samu ya shiga ko minti biyu me kyau bai dauka ba, ya shiga sauke ajiyar zuciya. (□□□) Amma maganar gaskiya yadda yayi mata ne sai a hankali, dan sai yayi ya sauka ya kuma cigaba da kallon tv yana ganin yadda ke abun zai kuma ji ya sake bukatar ta, a lalace a lalace sai da yayi yadda yake so da ita, kafin yaji yayi satisfy. Sannan ya barta, dan yaga ta fara motsawa alamar zata farka, shine ya kashe tvn ya shiga wanka, kafin ta farka.

Koda ya fito, ya samu bata nan bai wani damu ba, kawai abinda ya sani dole ya nimo ta, domin irinta yake so, dan haka tafiyar da yake gaban shi gobe da safe ya sashi bai bi bayanta ba, gidan shi ya nufa.

--
"Yawwa malam ya isa" ta faɗa a sanyayye, tana hango yadda Unguwar yayi shiru, sauka tayi tare da mika mishi kudin da bata san nawa bane, kwalla na zuba daga idanun ta.

Saka dan mayafin ta tayi tare da goge bayan mashin din, sannan ta juya da sauri, amma sabida yadda take jin jikinta, dakyar take haɗa kafarta har ta kusan isa kofar gidan, hango shi tsaye hannun shi cikin aljuhun wando shi yana sanye da wata farin shirt da wando blue kaftani, ya zuba mata ido. Ganin yadda take tafiya tare da kame jikinta ya sashi ji kamar ya had'iye zuciyar shi ya huta da wurga yarinya karama cikin musifar rayuwa, dole sai ya matsa mata zata wuce.
"A nawa kika basu kanki? Nawa ya biya kika bashi ta kazamar hanyar. Anum da sadakina da kome, kuka hanani hakkina. Hmm Alhamdulillahi Ubangiji ya fara nuna muku ayoyin rayuwa, wata rana sai wajen nan ya fi karfin ki"

Kukan da take dannewa ne ya fito, tare da jingina da motar ALHAJI NUHU fawa, kuka take tare da rike jikinta.
"Da na gaya miki Xoxo bala'i ce a rayuwar ki baki yarda ba, gani kike kamar da gayya ake hana ki, rayuwa da su, da XOXO da Hafsat Yayarki d'an jumma ne da dan Jummai, Mahaifiyarki kuwa! Ban san wani aji zan sakata ba.

Khadijah kin san me? Zuciyata bata tab'a kinki ba, asalima yanzun nake kuma jin kaunarki, ki bani dama ta biyu na, adanaki a."
"Don Allah ka bani hanya na wuce, domin babu kome a tare dani."
"Kece kika dauke shi wani abu, ba shi bane a gaba na, babban damuwa na, ki amince min!"

Girgiza kai tayi tare da niman rab'ewa gefen shi zata wuce, a hankali ya kai hannun shi kwaib'in ta, da sauri ta d'ago kanta. Hawaye na zuba a idanun ta, a lokacin kuka ya kwace mata sama da na da, tana niman abokin da zata gaya mishi matsalar ta, dan haka ta kifa kanta a kirjin shi tana kuka, sun jima a gurin sannan ta fara sauke ajiyar zuciya. Zafin da jikinta ya fara yi ne ya sashi ce mata.

"Ko zaki shiga gida ne domin,.na hana Rulwanu rufe miki gida, Anum don Allah ki rabu da su Xoxo. Mu gyara zaman auren mu. Kinji ko? Mu hada kanku mu zauna lafiya, zan saya miki mota, zan biya miki makaranta, a duk inda kike bukata, don Allah ki bani dama mu koma rayuwar auren mu, idan ma baki son zama da Hajjo zan rabu da ita sai mu koma mu biyun mu!"
"Toh Maude!"
Ta faɗa mishi haka a sanyayye, sannan ta nufi cikin gidan, kamar zata fadi yayi saurin bin bayanta, ya bude mata kofar gidan, har cikin gidan su ya rakata, adaddafe ta nufi hanyar dakin Mamanta, Umma ta gani ta fito daga ban dakin. Kallon ta tayi sabida akwai hasken lantarki a tsakar gidan, zuba mata ido tayi.
Sannan ta nuna mata d'akinta.
Babu musu, ta nufi hanyar dakin Umma, kasa nutsuwa Umma tayi kawai ta ajiye butar, ta biyo bayanta, ta tirketa tayi da barazana sosai, inda ta dauko Muciyar ta, kamar zata rutseta.
" Ciki kika zubda?"
"A'a wallahi ba ciki na zubar ba, fyade aka min" toshe bakinta tayi tare da dafe kumatunta, hawaye na zuba mata, bakin ciki yasa Umma rufeta da duka, kamar Allah ya aikota, tana yi tana kuka, tare Da cewa.
"Kin cuce Ni! Nasan zaki bawa wani kanki ne da bazan baki kulawa na Musamman ba, Anum meye malam yayi miki kika shafa mishi bakin fente, eyye Anum meye muka tsare miki? Me yasa zaki saka mana"

Zama Umma tayi tana kuka, tare da kallon Anum ji take kamar ta shaketa, ta huta.

Fita tayi tare da hada mata ruwan zafi, a cikin baho tashiga.
"Zoki wuce ki gasa kanki kizo ina jiranki, kuma kiyi wankar tsarki "
Gyada kai tayi sannan ta fita, daga dakin, haka tayi wankan sannan ta fito daga ban dakin, bayan ta gama ta shiga d'akin ta zauna Kamar mayya, huci umma take kamar ta had'iye ranta, idanun ta sun cika da kwalla, har suna zuba.

Fita tayi tare da yin alola, ta gabatar da sallar dare yadda ta saba sakata a cikin addu'o'in ta na kullum haka ma yau tayi.

Barcin da taga take yi ne yasata had'iye kukan da take yi tare da alwadar halin Maman Aminu.

***Washi Gari.
Da asuba bayan kowa ya gama fita, ita da kanta ta kuma haɗawa Anum ruwan zafi ta taimaka mata zuwa ban daki tayi wanka, sanan ta haɗa mata kunun tsamiya,
Ta zuba mata sugar me yawa, sannan ta nufi dakin Rulwanu da yake zaure ta bashi kudi ya nimo mata kaza, tasan duk abinda zata yi ba zai dawo mata da abinda Anum ta rasa ba, tunda tayi wasa da damar ta.

... A d'akin Umma kuwa kwance take tana jin ciwon abinda suka yi ta aikatawa Umma, kuka take tare da tsinewa Xoxo, tare da Alhaji Mudi tayi musu Allah ya isa yafi kwando dubu.

A hankali har barci yayi gaba da ita,
Fitowa Maman Aminu tayi tare da kallon takalmin Anum wanda ya b'aci da jini, dauka tayi ta wanke mata, sannan ta leka d'akin Umma har uwar dakin ta same ta kwance. Kallon yadda fuskarta ya faɗa ne yasata jin haushi, me yasa Meta?
Ta tambaya a ranta, kad'ai kai tayi tare da jin takaicin Umma.

***

Duk wani kulawar da ake bukata Umma tayi mata, bata tab'a nunawa Maman Aminu abinda yake damun Anum ba, abubuwa dayawa ta dauke ba tare da ta damu da Maman Aminu ba.

A hankali Anum ta sami lafiya, tare da samun sauki. Anan aka yi wani irin rigima har malam sai da ya kwanta asibitin, sabida Maman Aminu ta nuna akan me Umma zata rike mata ar ta.

Umma bata yi magana ba, kuma bata ce kome ba, ita Anum tsoron kar Umma ta fadi abinda ya faru da ita yasata tayi ta kuka, kuma duk wannan masifar da ake Anum taki rabuwa da Umma, dan tace.

"Wallahi bani kuma zama da Mama kawai ku bar ni da Umma na, idan kuka matsamin zan gudu nabar gidan nan."

Haka ya sa kowa ya kyale ta, ta cigaba da zama da Umma, wani irin nutsuwa ne ya shige ta, tana yawan cewa Umma.

"Umma na, hakkin Maude ne ya kamani, ban bashi hakkin shi na aure ba, Abidah ta yaudare ni, wallahi ban tab'a aikata zina ba."

"Amma ai kina barin maza su tab'a lafiyar jikin ki ba? Kuma Allah yana nan domin baki gama fita a hakkin Maude ba."

A duk lokacin da tayi mata haka, kunyar Umma take ji. tayi ta kuka.

... Satin malam daya aka sallame shi, Anum da Mamanta suna son kashe malam, bakin ciki ya ishe shi, dan haka ya zuba musu ido yana kallon su. Domin yawan maganar ma an hana shi.

Maude ya sha turo mata Rulwanu, ya gaishe ta. A cikin yan kwanaki ƙalilan alaƙar da tayi rauni ce ta kuma dawowa sabuwa, domin dai ya kuma dawowa hidimar da yake mata har yana shirin fin nada, har fada suka yi da Ila akan yace mishi bai dace ba abinda yake yi taya yarinyar da ta wulakanta shi, yanzun kuma ya dawo yana nimanta, sai kace ba cikakken Zuri'ar Sheikh Abu Turab ba.

Murmushi yayi sannan yace mishi.

"Idan akwai abinda aka jarabce ni dashi, toh bayan Qaddarar da ta baro ni cikin ahalina sai Soyayyar Anum! Zanen Qaddara ta ce ta shatamin har da Anum bayan haka babu dalilin da zai kuma mai dani soyayyarta! Ina Kaunarta wanda ban tab'a yiwa wani irin shi ba, Nana Aicha zab'in Hajja Dijamah ce da Abbina, Ita kuma Charifah Zab'in tsoho ce da Gaje.

Babu wacce naganta ina sonta dan kaina Sai Khadijah, Ila wallahi ban tab'a ganin abinda Zuciyata ke muradi irin Anum ba, kasan cewa da ina da wani zabi da na zabe shi na bar Anum. Kuma Alhamdulillahi yanzun niman mu zai tafi yadda yake ganin ko da bamu yi ba."

Duk yadda yaso nunawa Maude illar komawa rayuwar Anum bai fahimta ba, asalima sai gani yake kamar ila baya son shi da ita ne kuma Allah ya gani yana matuƙar son Cigaba Maude sosai, domin zai iya cewa, duk cikin yaran Maude shine kawai yayi kasadar rabuwa da dangin shi, duk da lokacin yasan darajar iyalin shi.

Amma haka ya zabi bin maude da ya zauna dasu, ya rabu dasu ya biyo shi duniya, wanda sunyi hakan ne dan tsira da rayuwar Mauden ne yasa suka fito, suka bar kome nasu da farin cikin su da jin dadin su..akan mace da idan maude yace yana buƙatar irinta goma zai samu a dangin su, shine wannan yarinyar da bata wuce yar shi ta fari ba take juya mishi hankali.

-- Tana tsaye a tsakar gida, tana wanke kayan ta.
"Assalamun Alaikum!" Gabanta ne ya fadi domin rabonta da XOXO yau sati biyu kenan, bata ganta ba kuma bata zo ba, tunawa da tayi itace silar rasa mutuncinta yasa ta juya tare da kallonta.

"Anum baki ganni bane!"
"Na ganki mana, shigo daga ciki." Ta fadi haka tana karamin murmushi, kallonta Xoxo tayi tana murmushin mugunta. Suka shige d'akin Umma, bata ce musu kome ba bayan nan, dan Umma tana ban daki, Maman Aminu tana kitchen, Baba Hama tana kwance a bakin kofar d'akinta.

Wato da Anum ta shiga kitchen tare da dauko Muciyar tuwo, ita Maman Aminu ta zata zata gyara kayan ta ne da take shanyawa. Dan haka bata mata magana ba, dan fushi take da Anum da taji labarin sun koma SOYAYYA da Maude, har yaci Uban na da, a cikin sati biyu,

Dan haka take fushi da yarta akan tana niman hanyar da zasu sami matsala tunda taki.ta bar abinda zata tsine mata, abin dariya ido da ido Anum tace.
"Karki damu, da karin shayin zamu kai ki Makka Insha Allah, sai sai kiji ana kiranki Hajiya Maman Aminu."
Abin na mugu bata haushi sai ta daina mara magana... Wannan kenan.
Tana shiga dakin su, wato da ta shiga dukar Xoxo da Beauty, dan sai da ta rufe kofar dakin. Tana dukar su tana kuka da ja musu Allah ya isa....
Kun gane ina busy ne kwana biyu nan, idan na sami lokaci zaku samu koda page 1 ne, Insha Allah
#Mai_Dambu....
[2/8, 12:47 PM] +234 814 541 5831: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA BAKWAI.

Ihu suke tana kara maka musu, dukar su take kamar Allah ya aikota, buga kofar ake, kamar za a balla amma Anum bata bude ba.

Asalima kamar wata me cutar hauka haka take jibgar su, kafin Umma takira Rulwanu da ya dawo daga makaranta kenan, yana zuwa ya daki kofar amma Kyam yaki buɗewa, karshe haka ya fita ya kira Maude da kan shi ya mata magana, taki buɗewa sai ma cewa da tayi.
"Wallahi ba zan bude ba kashe su zanyi!"
Karshe dai fasa kofar aka yi sun cure guri guda, suna ihu. Ana bude su, suna fita da mugun gudu.

Kifa mata mari Maman Aminu tayi tana kuma kokarin dukarta tace.
"Me zaki ce min? Me zaki min bayan lalata min rayuwa da kuka yi! Kin san me tayi min? Amma kike dukana, daga yanzun ba zan kuma bin ra'ayin ku ba, abinda yayi min zan bi an jima ba a tsine min ba." Ta koma Uwar dakin Umma ta zauna, budar bakin Maman Aminu tace.
"Wato dan anga bani da dangi anan shine bari a mallake min yarinyana a hanani sukuni!"

Ta shiga habaice habaice, tare da maganar banza babu wanda umma ta biye mata, dan haka ta gama masifarta tayi hakuri,

Abin haushi kayi abu kana niman me tayaka babu shine abinda yake faruwa da Maman Aminu, ita kuma Anum kamar mayya taki barin d'akin Umma,.

Suna zaune da Umma, ta kalleta bayan fitar su Xoxo.
"Me yasa?"
D'ago large eyes din tayi, tana kallon Umma,
"Cuta ta suka yi, bayan nima na cuci kaina, na hana shi hakkin shi, sabida Mama tace zata tsine min" ta karshe da kuka, sosai hannu ta saka a goshinta da yake sara mata kamar zai tsage.

"Toh yanzun kina son maude ne?" Cikin azama ta d'ago kanta, tare da kura mata ido.
"Umma ina son shi, amma kuma ba zan iya zama dashi ba. Sabida nayi wasa da dama ta. Kuma da wani ido zan kalle shi."

Jikin Umma ne yayi sanyi, musamman yadda Anum take magana cikin kuka da damuwa, da alamu ta watsar da kome. Amma kuma uwarta zata iya maida ta cikin halin baya.

"Toh ina sarkarki na Aure? Har da Zoben ki yanzun bana ganin su?" Umma ta tambayeta,

Kame kame ta fara, tare da kallon Umma, sai da ta kuma tambayarta, sannan ta gaya mata inda abin wuyar yake,
"Me yasa kika b'ata baki gaya min ba! Sabida bakin ciki shine zata rabaki da dukiyar aurenki?"

.... Cikin tsoron kar wani abu ya dawo tacewa umma.
"Na hakura!"
Buge mata baki tayi, sannan ta hararar ta.

Cikin wannan yanayin yaran Maman Aminu, suka zo gidan duk Yadda suka so Anum ta sake dasu taki, sai dai ta gaishe su ta koma dakin Umma, Safiya da Hafsat, suka zauna a dakin Maman su. Suna gama kulla sharrin su.

Abun tausayi, bayan sun gama Anum ta sami Hafsat da maganar abin wuyarta, dan ko Maman Aminu bata sani ba, da tana sakawa, amma ganin yadda maude yaƙe mata kallon kaskanci yasa ta kai aka sauya mata, mata.

Cikin tashin hankali mara iyaka tace.
"Wani gold kuma?"
"Na kayan aurena mana, kafin mutuwar aurena maude dai da yayi min fada akan ya gani a wuyar ki, bayan mutuwar aurena baki dawo min da Abuna ba, ai cewa kika yi zaki dawo min dashi, amma kika kuma karb'an zoben da Umma ta bani. Toh ki bani abina"

Tass ta wanke ta da mari, kallonta Anum tayi cikin mamaki da kukan da yazo mata.
"Ni zakiwa Sharri? Yaushe na.."
"Amma ai Khadijah ba mahaukaciya bace ko? Da hankalinta ba zata miki sharri ba? Dan haka bani zoben shine a hannunki, halinki kuma Allah ya shirya miki shi. Karki kuma dukarta domin bata kai matsayin duka ba, idan dukar ne na mutanen da suka mata fin karfi ne, ita da dukiyar aurenta kuma a dake ta,.kinyi mata adalci.? Toh bani"

Haka ta zare zoben hannun ta, ta wurgawa Anum, zata dauka Umma ta dakatar da ita.
"Zo nan Hafsat!"
Tana zuwa umma ta bada mari me kyau, sannan ta cigaba da cewa.
"Bani zoben da hannunki!"
Durkusawa tayi sannan ta mikawa Umma, taki karb'a ta nuna mata Anum,
A sanyayye ta sakawa Anum zoben a hannun ta.
"Insha Allah yadda kika karb'e mata hakkin Aurenta, Ubangiji sai ya ciyar dake arzikinta, kamar yadda kika tozarta ta, Allah sai ya rufa miki asiri ta jikinta.

Bani na haifeta ba, sai dai bani jin ko uwar da ta haife ta,ta fini kaunar Anum, idan da abin zuciya ne da na daina ko kallon inda take, amma sabida kaunar da nake mata na kasa hakuri da na rabu da ita."

Umma ta wanke Hafsat tass, kuma tace wallahi ta nimo mata sarkan ta kawo ko kuma ta bata mamaki. Wannan abin yayi matukar tinzira Maman Aminu, tace za a raba mata kan yaran, Umma tana da lissafi, duk abinda zata yi bata tab'a yarda tayi malam yana gida ko ta gaya mishi, sabida tasan yana fama da hawan jini.

Amma Maman Aminu kan sai da Usman da Aminu suka taka mata birki, amma bai da yar banzan nan ta hakura ba, Malam yana dawowa daga aiki, ta gaya mishi.

Dama ya zauna zai ci Abinci ne, haka bawan Allah nan ya kasa kai koda loma daya ne, ya kurawa Abincin ido.
"Mama wallahi Allah sai ya sakawa Baba Malam, sabida son kanki yasa ba zaki Fahimci halin da yake ciki ba, Mama idan dan nice zaki kashe malam mama naji zan bar dakin Umma, kuma na yafe sarkan don Allah ki bar mana shi, ya rayu cikin salama!"

Sai lokacin ya d'ago kanshi ya kalli Anum da take kuka wiwi ana dukarta, mika mata hannu yayi tazo ta zauna kusa dashi Baba Hama tana zunbura baki. Haushin kowa take ji, Malam da ya kasa fahimtar Iskancin Maman Aminu, Umma da ta kasa hakura da Anum, ita kuma Anum da ta kanennaye mata dan uwa!

(Kai duniya ina zaki damu?😂😹)
Duk yadda kake tsammanin abin ya wuce haka, shi yasa ta daina goyon bayan kowa, ita kanta kawai take so a yanzun.
Daura kanta tayi akan gwiwar malam tana kuka.
"Ki godewa Allah da ya baki damar samun Ummarku! Domin ita din macen rufin asiri ce, dan haka ban amince miki, ki rabu da ita ba, kina rabuwa da ita kin rasa uwa ta gari."
."Insha Allah Malam ba zan rabu da ita ba."

Murmushi yayi Umma da take jin shi, itama murmushi tayi. Domin har ga Allah Anum tausayi bata,kuma ko da tayi magana haushinta Maman Aminu take ji.

Tare da Anum Malam yaci abinci sosai, sannan ta kawo mishi ruwa ya wanke hannun shi.
Tun daga ranar Malam da Anum suke cin abincin dare.

A hankali kwanaki suke tafiya, cikin wannan yanayin Anum ta fara wasu abubuwan tashin hankali. Domin Umma tayi tafiya zuwa Dewu amma ranar zata dawo, ita kuma Baba Hama tana gidan Muttaka matar shi ta haihu.

Amai da yawan zubda yawu, sai barci da kasala. Tun Maman Aminu bata damu ba, har ta fara damuwa, ritsta tayi ta tambaye ta, ta gaya mata abinda ya faru, suna cikin wannan yanayin suka ji sallamar Umma, da sauri Anum ta fita ta bude mata daki tare da mata Barka da zuwa.

Sam bata dauko wani abu yana damun Anum ba, dan haka tai mata dariya ce mata.
"Auta na dawo, idan zan koma dake zan koma!"

"Barka da dawowa, Maman Sadeeq, dan bani aron autarki muje nan gurin yar garin mu!"
"Toh Maman Aminu, sai kun dawo!"
Suna fita zauren gidan Maman Aminu ta kifa mata mari, cikin fada tace mata.
"Uban waye yayi miki ciki?"karab a kunnen Maude, bude window yayi yana kallon su, da suka yi tsili tsili, jikin Anum yana rawa.
"Don Allah ka rufa mata asiri! Don Allah karka bari wani ya sani"

Komawa cikin gidan Maman Aminu tayi.
"Idan na rufa miki asiri, kaina na rufawa, idan na tona miki asiri wa kaina na tonawa, amma maganar gaskiya, kiyi hakuri karki fidda cikin."

Karshen Maganar maman Aminu taji, tana fitowa ta yayi mi hannun Yarta, sai can bayan kasuwar muda lawan, akwai wani inyamuri, zuba mishi kudi tayi tare da cewa.
"Oga maza ka cire min cikin da yake cikin mahaifarta."

Dariya yayi sannan yace mata.
"Madam karka damu zamu cire aikin mu ne!"
Dan haka ya mike tare da nunawa Anum tabi bayan shi.
Koda suka je wani dakin, dan iska nunawa yayi ba zai cire ba sai ta bashi kanta, wani kazamin kallo tayi mishi sannan ta juya zata fita, ya dawo da ita yana dariya.
"Karka damu za cire."

Tsaki tayi mishi tare da cewa.
"Wallahi ka kuskura kayi min wani abu, sai nasaka an rushe wannan asibitin kasan waye yayi min cikin nan kuwa? Toh wallahi sai yasa an rufe asibitin nan. kuma a kore ka a Bauchi baki daya."
Tsoron Allah da Abinda ta faɗa yasa shi nutsuwa, ya mata Allura tare da tsayawa na wani lokaci, sannan ya tura mata abin wanke cikin..tass ya kwashe cikin wata gidan jikinta, sannan ya kira Nurse suka fitar da ita daga cikin ɗakin, kai ta wani daki aka yi, sai da tayi barci awa daya. Sannan ta farka. Murmushi Maman Aminu tayi sannan tace mata.
"Gaskiya ya kamata yanzun ki nime miji kafin lokaci ya kure mana, idan ya kama ma muyi na farin jini ne sai muyi."

Shiru Anum tayi kafin suna bar asibitin, zuwa gida. Koda suka dawo, umma bata sani ba, sai bayan da Anum ta shiga wanka ciwon ciki ya turnike ta, ga jikin da take zubdawa kamar zata mutu. Hankalin Maman Aminu ya tashi, cikin kuka take gayawa Umma.

Ita kuma takira Aunty Binta ta gaya mata tazo don Allah. Kamar ca zata zo ba, haka ta zo ta duba Anum, a take ta fita haduwa suka yi da Rulwanu, ta mika mishi kudi ya karo mata allurai da wasu Abubuwan.

Dan wanda tazo dashi bai isa ba, haka tayi ta fama har Rulwanu yazo, aka saka mata ruwa da allurai, kasanta kuwa saka mata wani katon ƙwayar magani tayi, bayan kamar minti goma sha biyar kacal, jinin ya tsaya cak.

Sai magunguna da ta Rubuta mata, sannan ta koma dakin Umma, tana sauke ajiyar zuciya..
"Umma wallahi bata jin magana, zuwa tayi aka cire cikin da karfin tsiya."
"Kaddara ce babu wanda ya fi karfin fadawa, ki mata addu'a kina da baya"

Daga haka tayi shiru, karshe dai ta ji haushi zata fita. Umma tayi mata kashedin kar ta ji maganar a kunnen Aminatu da Rabi, gyada kai tayi, duk da tasan yaranta amma yana da kyau ka kuma jajjircrwa.

Ko Malam Umma bata barshi ya sani ba, sai dai da yazo cin abinci aka ce mishi bata da lafiya har karin ruwa aka mata, ya shiga dakin ya bata abincin, a baki tana ci tana kuka. Tare da tambayar kanta meye Umma da Malam suka mata da ba zata musu adalci ba?

Haka ya gama bata, sannan ya fita. Wannan abin da ya faru,.ya ɗan kunyata Maman Aminu, ta dan nutsuwa sosai..ta daina yiwa Umma wasu abubuwan.

Idan kaga irin hidimar da Maude yake zaka rantse da Allah, shi yayi Abun, da kanshi yake kawo abu har cikin gidan ya mikawa Umma, sai dai tayi murmushin jin dadi..domin kuwa a wannan jinyar da tayi kowa yasan yadda yake kaunarta.
Itama bata da abokin hira da ya wuce shi, domin idan ya shigo gidan, takan saka babban hijab ta fito suyi ta hira, duk da ran Umma bai so ba, amma bata da zab'in da ya wuce hakan.

Har Anum ta sami lafiya, tass sanan malam ya kuma gabatar mata dashi a matsayin wanda zai aura mata, anyi haka washi gari. Sai ga Alhaji Mudi wuntin dada.

Yana zuwa ya samu malam baya gida, nan yayi sallama da Anum, ta tura akan cewa ba zata zo ba.
Maude da kan shi ya shiga tare da fito da ita, murmushi tayi..sannan tace mishi.
"Ni na sami mutumin da ya dace da rayuwa ta, dan haka kaje da kazamar rayuwar ka, Ni bana bukatar ka!"
Dariya yayi sannan yace mata.
"Ba zaki tab'a rabuwa dani ba, sabida nasan kaina, duk kananun yan matan da nake nima, Kece macen da banyi tarayya da ita da kariya ba, saboda Samunki da nayi cikakkiyar mace, kuma ni mutum ne mai baiwar haihuwa, nasan kina dauke da cikina.....
😈😁 How Market MAUDE?
#Mai_Dambu
[2/8, 7:03 PM] +234 803 835 1003: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
BABI NA TALATIN DA TAKWAS

Kallon juna suka yi da maude damm gabanta ya fad'i, bakinta yana rawa tace mishi.
"Babu cikin da nayi, kuma ai fyade kai min tunda ba nice na baka kaina da kai na ba, wallahi Maude!"

"Anum! Karki damu, nasan da cikina a tare dake, ba wani abu bane sai mu zubda shi a matsayin wanda yazo mana bazata, idan yaso mu kuma gina rayuwar mu."

"A'a wallahi bana sonka, kuma cikinka na zubda shi!" Zaro idanu yayi cikin nutsuwa sannan yace.
"Tabbas zaki aure ni ko kuma kotu ta rabani da ke."

Maude kan shiru yayi, yaso ya wanke Anum, da tace babu cikin, amma cewa da tayi ta zubda sai ya sare mishi gwiwar shi.
"Amma malam katon banza, tace bata sonka dole ne?"
Inji MAUDE.
"Kai kana jin haushina ne dan ta hana ka kwasar kayan daɗi, ni kuma a banza na kwashe shi, na ci na kuma ci, na kuma harba mata kunamar cikin jikinta, yadda zan kafa shaida, dan haka ka ha bakin ka, kayi min shiru."

Kukan da Anum take yi ne tare da juyawa gidan da sauri, ta faɗa jikin Umma, tana gaya mata abinda ya faru, fitowa Maman Aminu tayi, ganin shi Alhajin birni da shi, nan ta shigo da shi zauren gidan, tare da tattaunawa kamar yadda take tsammanin, Alhaji Mudi ya bude mata aljuhun shi, bayan sun gama magana ya bata kuɗi. Masu yawan gaske,

Bayan tafiyar shi, ta shigo gidan suka fara magana da Umma, tace mata.
"Me yasa kika saurare shi? Ai tace bata san shi an tab'a so dole ne?"
"Toh ai yace tunda ta zubda mishi cikin shi sai ya kai Ubanta kotu dan haka babu abinda ya dame ni ku hadu a kotu," (□)

Haka Anum ta wuni tana kuka, kafin zuwa yamma malam ya dawo, Maman Aminu ta gaya mishi abinda ya faru, kallon Anum yayi tare da tambayar ta.
"Dama kin hada jini dashi ne?" Dan tambayar da zai mata yayi mishi nauyi.
"Wallahi malam fyade yayi min?"
Kifa mata mari yayi, sai da ta kusan shiɗewa,

Sannan ya kuma tambayar ta,
"Eh malam!" Ta bashi amsa a tsorace.
Dauke kan shi yayi tare da cewa.
"Shi kenan, ai ya same ni a gurin aikina, sabida ke ake tozartani Khadijah, Allah ya shirya min ke, Ubangiji ya kyautata rayuwar ki."

"Don Allah malam ka rufa min asiri, bana son shi, wallahi Maude nake s..." Buge mata baki Maman Aminu tayi tare da zabga mata harara.

Jinjina kai yayi sannan yace Mata.
"Dama maude nake miki fatar ki koma hannun shi, amma tunda kin dibo kayan da yafi karfin ki shikenan. Allah ya bada zaman lafiya. Domin ba zan rasa mutuncina sabida ke ba, Anum Allah yayi miki albarka, iya abinda zance kenan da fusatar da nake ciki, Allah ya shirya rayuwarki."

Aikuwa Anum tayi ta kuka tana cewa.
"Malam kana bani dama a rayuwata, me yasa ba zaka bani wannan damar ba, don Allah ka rufa min asiri karka bani abinda bana so?"
Dukda tausayin ta da yake ji, bai hana shi yanke hukuncin da yaga dacewar shi ba.

** Duk da Umma tayi ƙoƙarin ganin Malam bai yanke hukuncin aura mata wancan mutumin banzan ba, amma ya ke kashe kasa, ya kuma kafe. Cikin kwanaki

ƙalilan Alhaji ya shiga musu barin nera, haka bai dami Anum ba, domin duk hanyar da zata bi domin kin amincewa da auren abun yaci tura.

Karshe sai da takai ta kawo, ta kira Maude ya shiga maganar, abinda yace mata yasata fashewa da kuka.
"Anum! Bani da abinda zan iya, domin mutumin nan ya shirya tozarta Mahaifinki, me yasa kika ce mishi kin zubda cikin? Da baki yi magana ba, dole na tsaya miki, amma meye ya faru ko jiya sai da yazo da wani lauya akan a gabana kina fada mishi kinyi cikin, abinda na sani Allah yana tare da masu hakuri."

Rikici ta saka musu, ita ba zata auri Mudi ba, idan yazo ta yi mishi rashin mutunci da rashin kunya, haka bai hana shi kuma dawowa ba, karshe Haka mutumin nan ya ci mutuncin Malam.

Babu shiri aka ranar juma'a aka daura auren Alhaji Mudi da Anum, haka Umma tayi ta gyarata, tare da kulawa domin ansaka tarewan sabon wata.

Duk wanda ya kalli Anum sai ya tausaya mata, domin ta fita hayacinta, burinta ta kashe auren, tun da Maman Aminu ta fahimci haka, wani tudu wani ganganre aka wani Anum tana son aurenta, kamar tayi hauka. A wannan tsakanin mijin yayi ta koda musu kudi, yana fita da ita.

Duk tafiyar da zai yi da ita yake tafiya, kafin ta tare ta zama side chick din Alhaji. Kuma kome dare tace mishi ga abinda take so zai kawo mata. Hmmm.

"Hajiya Hafsat Kanwar ki nan wata rana ba zata cigaba da biye muku ba, kin rufe mata baki bayan kin san cewa tafiki gaskiya. Sannan maganar gaskiya idan kika cigaba da haka wata rana zata bijire muku, wanda ku kanku ba zaku tab'a jin dadinta ba, ku daina tankwarata dole tayi abu."

Jikinta ne yaso yin sanyi, amma ta kudira a ranta sai ta hanata sakat yadda babu wanda zai fahimci meye a kasa, domin ba zata iya maida mata gwal ɗinta ba.

Yadda yake kawowa malam Uzuri, yasa shi tsayawa sosai suka fahimci juna.
"Alhaji idan ba zaka zauna da ita ba, toh kawai asan abin yi, na gaji da ganinta da aurenka tana yawo." Inji Mlm,

"Toh babu damuwa wata sati sai ta tare ba, ai ba wani abu bane."
Ya fadi haka, amma a kasan ran shi bai so haka ba, dan haka ya koma gida ya shiga gyaran shashin da Anum zata zauna. Umma ta cigaba da gyarata, duk da sai tayi zuciya amma ta Cigaba. Dan gani take kamar itace tafi dacewa da amsa sunan mahaifiyar Anum, amma sakamakon Maman Aminu ce ta haifeta bai hanata kaunar ta kamar yadda take kaunar Yaranta, sama da Yaranta ma.

Ita kanta tasan tana son yarinyar da rayuwarta ya inganta, amma bata jin uwar ta nan zata barta ta zama abin zata yi kyau gobenta.

"MAUDE!"
Ta kira sunan shi a hankali, tana kallon yadda yake aikin shi.
"Kayi hakuri!"
Bai tanka mata ba, asalima abinda yake gaban shi yake, irin wannan kuma matsalar kice,
"Don Allah!"

"Khadijah! Ke matar aure ce, kuma matar wani, me zai hana ki daina min magana, saboda kar mu saba'awa Ubangiji."

"Amma san kai mutumin kirki ne, baka tab'a min maganar Asha ba. Maude bana barci, idan dare yayi sai nayi ta juyi, Bana jin dadin rayuwata, Mutumin nan ina matuƙar tsanar shi, amma kasan me? Haka kawai sai naji ina son zama dashi, amma a raina bana son shi."

"Anum kina wasa da ibada, shi yasa kowani kare da doki yake iya cutar dake, shawarar da zan baki ki hana idanun ki barci kina kiyamul laili, yana taimakawa gurin maidawa masu sharri sharrin su. Kina yawan karatun Alkur'ani, magani ne na kowani irin lallura.

Anum rayuwar duniya idan babu addini ba zai yiwu ba, ki rike Allah. Duk inda kika shiga Allah yana tare dake,kasan me? Idan wancan tsohon banzan yayi miki Iskanci. Ki Kur'ani wallahi sai na gyara mishi gurin zama!"

Murmushi tayi tare da dauke kanta, tana dariya.
Murmushi yayi sannan yace mata.
"Koma kafin ace ina magana da matar aure!"
A hankali ta juya, duk sai take jin babu dadi, ta cutar dashi dayawa, kuma yana ƙoƙarin sataka farin ciki. Juyowa tayi tana kallon har ya rufe window, a hankali ta juya tare da shigewa cikin gidan.

Maganarta ne yake yawo a kunnen shi.
"Ila! Yarinyar nan tana cikin damuwa da?"
"Ai ba Kanwar gyatumata bace da zan hana kaina sakat akanta, ba damuwa ba, tashin duniya take ciki."

Rike baki yayi yana kallon Ila da ya matse fuskar shi, alamar yana cike da maude, kuma kiris yake jira Mauden ya tinzira shi ya kwashewa Anum albarka daidaigwargwado.

"Ila maganar gaskiya nake gaya maka fa?"
"Lallai kuwa, maude kana nufin duk Iskancin da akan ta, wai Ni kam yarinyar nan tafi sauran mata ne? Meye take dashi da ka damu da ita? Gaskiya karka dame ni akan ta, Allah yasa ta mutu kowa ya huta."
."amma da ka saurare ni, kaji abinda zance maka, kawai ka hau fada kamar wanda na gaya maka wani abu na daban."

"Eh kai, ai abu na daban ka gaya min, me aka yi da halin Yarinyar da bata da kamun kai,kafi kowa sanin halin gidan ku, wallahi faduwar daraja ce ka nime wannan Yarinyar da bata mai da kanta Mutum me kima ba, a duk lokacin da ka girmama kanka Allah sai ya kawo maka masu girmama ka, Yallabai gidan ku manyan malamai ne, manyan mutanen ne da suka san ma'anar daraja, taya zaka dauko musu kara da kiyashi daukar mara sani?

Yallabai ka rabu da yarinyar nan. Karka manta Nana Aicha mahaifinta shine sarki a maradi, kuma mahaifiyarta Kanwar mahaifiyarka ce, me yasa ba zaka gane mugun irin da zaka kai muku cikin zuri'a ku!"

Shiru yayi sannan, ya dauki ruwa ya sha, tare fita yayi daga shagon ya nufi gidan shi. Ya sami gidan cike da matar gidan da suke haya, ana gulmar da aka saba.. suna jin sallamar shi suka shiga, mik'ewa kowacce bata gama gulmarta ba, zata fita amma babu karya sun ji haushin dawowar shi.

Yana shiga ya sami, Hajjo tana kallon wani Hausa Film, tashi tayi tare cewa.
"Barka da dawowa, kayi hakuri sun zo kallo ne!"

"Karki damu," ya gaya mata tare da niman guri ya zauna, a dame yake, amma baya jin damuwar shi ta kai wanda Anum take ciki, tabbas yana jajjantawa halin da Anum take ciki, ji yaƙe kamar ya cireta a cikin matsalar ya wurga kanshi, yasan Allah zai fidda shi da Insha Allah, ita kuma fa?

Yadda ya lura da Maman Aminu, bata da cikakken hankali, yasan bai zama dole tasaka ta a cikin addu'o'in ta ba, yasan dai in akwai addu'ar da zata mata, bai wuce na niman kudi ba. Kai matar nan bai tab'a ganin mutum me shegen masifar son abun duniya irin Maman aminu ba.

Tsakanin da Allah idanunta yafi raja'a akan kuɗi, idanunta idanun nera, har tausayin ta yake ji, irin su ne ake saka musu abu a cikin kudi.

Murmushi yayi, tare da shafa kanshi. Yadda take son kudin nan, ka tula mata miliyan goma nata na kanta, zunzurutun tashin hankalin da zata shiga sai takwana bata rintsa ba, dariya ya sake yana girgiza kan shi.

Yana jin a ran shi, tabbas dole ya taimakawa Anum domin.. wani tunani ne yazo mishi yace.
"Toh ita da zata yi aurenta, ina ruwana?"

Haka yayi ta magana shi daya yana kuma ganin rashin dacewar, saka mata baki akan rayuwar da zata yi gidan mijinta...

--- Rana bata karya.
Ranar juma'a da dare aka kai a gidan mijinta, wanda yake wuntin dada, a can baraya Quarts. Babu laifi inda aka sakata, plat ne me kyau.

Inda Safiya suka mata jere kome nata, A daren kuwa Alhaji Mudi ya gurji amarcin shi son ranshi, babu wani katabus, sai tsabar jaraba. Bayan minti goma zai sauka. Kuma ba zai fasa matseta ba, har asuba idan yayi barci ya tashi zai tab'ata.

Karfe biyar tayi wanka, maranta na mata mugun ciwo, har bayan ta. So gari na wayewa. Aka shiga kawo mata abin karyawa,.kafin karfe goma gidan ya cika da baki yan uwan ta, da matan yayunta.

Tayi kyau cikin buba na lace, an mata dauri me kyau. yaran Alhaji Mudi suka shigo. Sun kai rai goma, kana ganin su kamar yaran dan wake, kuma kowani yaro kamar shi daban, gashi kamar wanda aka kwato su daga fari. Gasu da katon ciki da katon kai.

Sai zare idanu suke, lokacin da aka kawo abinci daga bakin kura. Kamar zata yi kuka tace musu.
"Daga ina kuke? Kun shigo kuna kare mana kallo"

Kallon abincin da suke ci har da namar kaza, Hafsat na ajiye filet din suna saka super! A guje Anum ta koma saman kujera a tsorace.
"Na shiga uku!"
Shigowar daya daga cikin matan Alhaji yasa su d'ago kansu.

"Kuyi hakuri! Kai kuzo muje, sha'anin yaro bai saba ganin haka ba, shi yasa suke muku halin su. Gaki da kyau me yasa kika zab'i kare rayuwarki a cikin gidan nan? Amma ba zaki gane ba, sai nan gaba."

"Malama dakata mana, ki fita ki bamu guri." Inji Hafsat,
Murmushi matar tayi sannan ta kalli Anum, kafin ta kori yaran waje.

Kallon juna suka yi, sannan wasu suka fara cewa, kishi ne da rashin godiyar Ubangiji, amma kamar Alhaji ai ba zai wulakanta su ba.
Dan haka suka shiga zuga Anum ana gaya mata kar ta sake su rena ta, dan yanzun miji yana hannunta....
□□ Kuma dai!
#Mai_Dambu
[2/10, 9:50 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai..
*Dubun gaisuwa gareki Mrs J Moon! Ga shafin ki nan😘

```Ga masu bukatar littattafan Marubuciyar da aka kammala zasu iya tuntubar Marubuciyar +2348132166848 an kammala Dr Laylah```

BABI NA TALATIN DA TARA.

Kallon su Anum tayi tare da sunkuyar da kanta, tana jin wani abu ya tokare mata, kirjinta bata kuma d'ago kanta ba, sai da tayi kusan minti talatin a haka, sannan ta d'ago kanta, tana kallon matan makotan su, suna shigowa.

Haka suka gama gulmar su, suka fita,Yayunta mata suka shiga mata ingiza me kantu ruwa, har yamma suka watse dan daga unguwar zuwa bakin titin akwai tafia, bayan tafiyar su. Ta shiga kimtsa cikin gidan, tana gamawa ta nufi cikin dakinta, domin sun rage mata aiki sun tafi da kayan da suka zo dashi, sauran abincin sun bar mata a cikin kitchen ɗin ta.

Wanka ta kuma tare da sheka kwalliya, sannan ta fito falo, sai lokacin ta sauke sallah da yake kanta, tana kan Abin sallah ta tsinkayo Muryan mace tana ihu, lekawa tayi ta window. Da sauri ta mai da labulen ta rufe kirjinta na dukar tara tara, zunzurutun tsoron yaran Alhaji Mudi.

Sake d'aga labulen tayi taga sun zuba mata ido, kamar wasu zombia, zunzurutun yunwa da suke ji, dage kanta tayi taga Alhaji da kanshi yake zane matar nan da ta musu magana, murmushi tayi sannan ta isa bakin kofar ta, ta bude kofar juyowa yayi tare da sake mata murmushi. Itama murmushin tayi Mishi, taja kofar ta ta rufe. Dan lokacin karfe shida da minti hamsin ne, ana kiran sallah a ko ina.

"Baby, ya isa haka kazo muje kayi alola ka tafi masalaci, zan baka labari." Sake belt din injin din yayi, tare da juyawa suna murmushi. Sanan suka bar gurin, tunda daga ranar Alhaji yake riga Anum, abin karyawan su special. Haka abincin ranar su ma, na dare kuwa fita suke su tafi saya a waje, idan tafiya ta kama shi zai dauke ta su tafi tare, idan zasu dawo haka zata yi sayayyan kayan abinci domin yana masifar jin dadi mu'amala da ita.
```

Wato bari kuji yadda gidan Mudi yake, babban gidane me dauke da mata uku da kananun yara kusan rai goma sha biyu, banda cikin da sauran mata biyu suke dashi, aka'idar gidan.

Abinci sau daya ake girkawa, idan aka saka ƙatuwar lamva talatin na tuwo,(□□□) ƙatuwar lamba sha biyar na miya, asalin tuwon za ayi talgen shi(mu nan muna kiran shi da Ruɗe) ne da tsakin garin tuwon, sai a dauren wancan talgen da garin tuwo, miyar kuwa TOH yaddiko tana iya nata ƙoƙarin.

Dukda bata da d'a a cikin gidan, amma wallahi duk wani wahala itace take Mishi, ya aureta a bazawara ce, lokacin mijinta ya rasu, tana da manyan yara a wani gurin, da taimakon su take iya daukar dawainiyar gidan Alhaji, domin tana sana'o'in hausawa, kukar miya, garin kubaiwa, kayan miya Daddawa da kanta take yi domin yawan gidan su tasa take hada daddwan waken soya, dashi ake miyar gidan.

Dan haka idan za'ayi miyar,akan zuba yaji daddawa, da kuma ajina moto, yadda miyar zata yi zaƙin Bala'i.

Idan aka gama tuwon, akwai wani kular da Yadiko ta sayo, a gurin tani dilalliya, shi ake kwashe abincin dukkan a juya shi, sai miyar wanda zunzurutun rashin manja.

Zaka dauka barin garin kuka aka yi a cikin miyar haka suke ci,har suna kashe hannu.

Matan shi da yake aurowa daga ƙauyukan bauchi, a yanzun wanda suke gidan Akwai.

Barirah, daga kayarda sai Mairo, daga Nasaru, sai Karime daga can maina maji, anan ya auro su. Dake yan kauye ne kuma yara ne suna bin Yadiko sosai, kafin shigowar Anum akwai wata yar bununu me suna Sakina, dake ita tana da ciki shine aka sake ta, tare da hankadata can garin su da yake geendi.

Duk yaran da suke cikin gidan Mudi babu wanda suke su biyu, sai Hassan da Hussaini, sune UWARSU daya. Domin amma kaf yaran uwaren su daban, kuma suna shirin dosar talatin, domin itama Barirah ana kyautata zaton cikin ne da ita.

Yadiko dai itace turmin tsakar gida, sha daka, wani banzan halin Alhaji shi ba zai ci abincin gidan shi ba, sai dai ya sayo daga waje, nama, tukunya, balangu ko tsire, doya da kai ko kuma taje Banilla yasayo abinda zai ci, yana da kayan abinci a cikin dakin shi.

Idan kaga an girka shinkafa a gidan,(😂😹😂 Marori)
Toh sallah ce, ko sadaka. Dake mutum ne me mugun bin malamai, haka zaka ga yaran shi suna buga sowa, (wallahi abin da mugun ban tausayi, maza kuji tsoron Allah, wallahi Allah ba zai barku ba, nasan maza dayawa da suke karanta book dina, kuma nasan zaku gani)

Sannan yadda ya rena Yadiko zaka sha mamaki, dukarta yake a gaban uban kowa, dayawa matan da ya aura bawai sun aure shi dan kasu bane, a'a yana sake kudi idan yarinya zata mishi gardama ya saka malamin shi ya rufewa iyayenta baki yadda zai aureta ya kuma kawo ta yaci Uban ta.

Sannan akidar shi idan mace tayi ciki, zai fara cin Ubanta, ko ta fita da kafarta ko kuma ya wulankata ta, da kanshi, baya son haihuwa yace hayaniyaar yaran ta ishe shi, na farko dai basu zuwa boko balle islamiyya, na biyu basu da tarbiyya, balle su

sami nutsuwa. Na uku basu koshi ba, balle su zama masu cikakken lafiya da kuzari babu wannan abun a tare dasu..idan gansu zaka rantse irin yaran nan ne da aka yi yaki da baƙin talauci ya cinye su. Ga rashin sutura wanda ya taka rawan gani domin wallahi yaran almajirai sunfi su gata, tunda suna fita bara, su kuma wannan basu fita ko ina, ga sata idan ka ajiye abunka kafin ya dawo sun dauke kuma a rasa waye ya dauka a cikin su.

Idan suka fara fada da junar su, wallahi sai Yadiko ta dauki Muciyar suke rabuwa dan yi suke kamar zasu kashe junan su, idan kuma aka zuba musu abinci, sai kayi kuka da idanunka, domin baya wadatar su, karshe wanda yafi wani ƙarfi shine zai dauko tiren abincin, wannan yanayin sam Yadiko bata fatan wata ta auri Alhaji, domin mara mutunci kamar wanda yake da ciki a hannu yana d'aga bujen mace, toh magana ya kare, shi yasa da taga Anum taji ciwon auran Alhaji da tayi har ta mata magana, karshe bayan an watse suka fara sa'in'sa da Alhaji take gaya mishi magana. "Kaje ka auro yarinya karama, me dauke da danyen kuruciya bayan wanda ka tara a gida, idan ta sami ciki ka sake ta ka sauko wata, wallahi Baka kyauta min, meye na rage dashi, ina laifin ka barta tayi rayuwarta amma ka aurota, sannan ka ajiye ta nan da wani lokaci, ka sake ta bayan ka gama gina mata wulakancin, sannan ka na sane kake barinta take abinda ta dagama, wallahi Allah sai yabi mana hakkin mu," shine ya kamata da duka fa,

Abubuwan fada akan Mudi dayawa suke, idan zaka fada sai ranka ya b'aci a banza.

Ko lokacin da ya gayawa Malamin shi batun Anum, sai da yace mishi akwai aure a tsakanin su, amma kuma ba me nisan kwana ba, shi yasa lokacin da akayi auren yaso su rabu, dan malamin ya gaya mishi matsalar da zai iya samu da kasuwancin sa, sanan yake gaya mishi abubuwa biyu ya bashi damar auren Anum, uwarta da yar uwarta basu barta ba, dan tana da kashin Arziki, shi yasa suke gudun ta auri mutumin da bai da wani arziki, sai kuma cikin jikinta da shi kadai zai yake ta ta aure shi.

Amma kar ya kuskureta, domin yin haka dai dai yake da lalacewar wasu abubuwan shi, sannan ya kara mishi da cewa, tana da kwaɗayi da hangen dala,

Ya gaya mishi abubuwa dayawa akanta, sannan kafin auren ya kuma ce yayi bincike akan me ya rabata da mijinta, koda ya gaya mishi abin da ya faru, da wannan abun da abinda Maman Aminu suka mata, suka daure tunaninta guri guda.

Shine lokacin da take gayawa Maude cewa, ai bata jin dadin rayuwarta, bata iya barci. A duk lokacin da ake nufarka da sharri matukar baka tsaya da ibada ba, toh haka zaka ji, ka kwana kana jin damuwa da faduwar gaba, ciwon kai da na jiki, barci ya kaurace maka, sannan zaka naji kamar ana kiranka, ki wani abu na daban, toh idan kana yawan sallar dare, abun yakan komawa masu aiken.

Abincin da ya rage shi aka ta hada musu, sannan ta jera musu. Bayan ya dawo masalaci, dan ba wai sallar yake ba, ya fita ya zauna a gurin motar shi ne, sai da aka fito masalaci ya koma cikin gidan, inda ya samu ta Baje musu abinci suka ci tare da hira, daga gurin aka fara, (😂yana hawa ko minti biyar mekyau bai rufa ba, mutumin ku ya sauka.

Haka yayi ta janta da wannan shirmen, dakyar ta dakatar dashi tai wanka, marar ta yana ciwo.

... Haka suke ta amarcin su, yayinda ta budewa mutanen gidan rashin mutunci, shima kuma Alhajin bai fasa ba, haka sukewa mutanen gidan tijara. Idan ka ga yadda take tsiyar ba zaka tab'a dauka zai zo karshe ba.

*** Maman Aminu, baki har kunne yarta ta auri me kudi, sai hura hanci take, babu abinda ya dame ta, gashi tana dai samu a jikin sauran yaran amma dake Allah ya cire albarkan a cikin rayuwar sai taga abin baya jimawa.

Haka malam yake haɗa duk wani abun da samu zai bawa Umma ta ajiye a Anum, hidima sosai suke mata ana ajiye mata, ko bata zo ba za a kai mata. A cikin irin wannan lokacin kayan miya yayi araha, Umma tasa Malam ya saya musu kwando da aka markade, ta daure wasu a laida, ta saka a cikin freeza. Sauran kuma ta juye a langa tsirara.

Sannan ta ajiywa Anum, duk wani tattalin duniyar nan daga malam har Umma wa Anum ce, dan babu karya yaji labarin waye Alhaji Mudi, amma dan Anum ta janyo mishi rikicin da ba zai iya tarewa ba, ya amince ya bada aurenta.

"Malam yau sati biyu da auren Anum baka tab'a mana mijinta ba, dan ita Bama samunta" inji Maman Aminu,
"Tana lafiya, tafiya suka yi!"
Daga haka bai kuma cewa kome ba, sabida Allah ya gani ta ficce mishi a kai, kawai sabida Albarkacin Yaranta yake zaune da ita, bacin haka da ya hakura da ita baki daya .

"Beauty! Kinga tunda Alhaji ya auri Anum ya daina hulda da mu? Sai ma sakamu da yayi a blacklist." Inji XOXO,
Shiru Beauty tayi tana wasa za wayarta, kafin tace mata.
"Toh ni dai ban san me zance ba, amma kuma ki hakura da dashi mana"
"Wallahi ba zan iya ba, shine yake kashe min kudin da sauran basu bani, shi yasa na hanaki mu'amala dashi wata banziya daga mu'amala sau saya ta kwace min shi, Allah sai na dawo da da shi."

Ta faɗa tare da ihu, tana kuka. Kallon ta Beauty take, sabida bata san me zata iya cewa ba.
Kuma tasan halin Xoxo ba mutunci ne da ita ba, yanzun tace da ita aka kulla mata wulakancin duniya, shi yasa take Binta duk yadda ya dace.
"Toh kiyi hakuri, ai babu wani abu da zaki d'aga hankalinki, Alhaji na mune! Kuma Insha Allah zai dawo gare mu, muyi yadda muke so dashi, kinji My Bestie!"

Da wannan maganar ta gyada kai kawai, domin tasan Beauty zata...
Kuyi hakuri, idan na sami lokaci zan kara muku
#Mai_Dambu...
[2/10, 9:50 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN.

Bayan Amarci....

Kwanaki suna tafiya, amarci nan dai gurjanta ake, sanabe da iyayin Anum kara yawa yake, kokarin ta na ganin ta sami damar juyar da kan Alhaji ya faskara, a hankali suka shiga jikin juna. Inda Anum ta fara fuskartan Allah Alh baya son ibada, sannan mugu ne na fitar hankali.

Idan zai samu nutsuwa a jikinta, baya damuwa da ita. Abinda ya fara damunta, ba kome bane, ana cikin haka gas din ta ya kare. Dan haka ta nufi dakin shi ta same shi yana barci.

"Baby bamu da gas din da zamu yi abin karyawa"

Budar bakin shi yace mata,
"Amma naga a gidan uban ki uwarki itace take amfani dashi bana son jakanci, ki fita ki hura wutar itacce."

Kallon shi tayi tare da sake baki hawaye na zuba mata.
"Ni dai ba Ubana da Uwata ba."
Ta faɗa cikin kuka, aikuwa tsalle yayi ya dirko daga gadon, ya rufeta da duka. Tare da kwallo da ita, dukar kawo wuka yayi mata, tare da mata wulakancin, aikuwa yaran gidan kowa ya shiga cikin nutsuwar shi. Yana gama dukarta ya fito.
"Idan kuka ganta zata fita kuyi mata haushi kamar kare, karku barta tafita ko kofar gida."

Bayan tafiyar shi, kuwa ta sab'i hijab zata buga yaji, tana isowa tsakar gidan, yaran suka fara mata gurnani kamar wasu karnuka, tare da mata caa zasu mata diban albarka, da gudu ta koma d'akinta. Ta rufe kofar ta.

Kuka take tare da niman wayarta, ta manta inda yake ma, tayi niman duniyar nan bata gani ba.
Haka ta wuni ranar bata saka kome a cikin bakinta ba, sai dare da aka gama kirb'a tuwon datsa, aka kawo mata. Shi taci dakyar ya wuce wuyarta. Ranar tayi kuka har ta godewa Allah.

Tun daga ranar kuma, ya bude mata wulakancin da cin mutuncin, ga cin fuskar Bala'i. Ya kira Maman Aminu mayyar kudi. Malam kuma ɗan maula.

Ita kuma karuwa, gashi kamar ya dauke hankali kowa a kanta, wani salon cikin Ubanta yake yadda ta kasa motsi.

Ana cikin wannan yanayin, sai ga ciki. Babu imani ya saka aka mata allura cikin ya fita, domin da ddare ya shigo da Nurse din, tayi mata alluran, kafin karfe hudu na asuba cikin ya fita, dukka dukka satinta biyar da kome ya lalace, da gari ya waye.. farkawa tayi cikin jini.

Dakyar ta mike ta kuma zuɓewa cikin jinin tayi tare da lumshe idanunta, kafin ta kuma yunkurawa.

Dakyar ta tashi ta rarrafa zuwa d'akinta, katon butar da take cikawa ta ajiye shi idan aka kawo wuta ta tafasa ruwan zafi, ta nufa tare da kunawa butar, Allah ya taimaka akwai wuta, kwanciya tayi a gurin, tana fidda numfashi. Ruwan na fara tafasa, ta ja dakyar ta kashe, sannan ta ja butar ta kashe wutar.

Tunda ta shiga ban dakin ta sirka ruwan zafin, ta fara wanka da shi, sai da ta gasa jikinta sosai. Sannan ta koma ta saka wani ruwan tana ganin jiri haka ta fito ta gyara falonta domin anan aka mata alluran tayi ta birgima har cikin ya zube.

Mopping ta goge falon, tana kwashe jinin tana kuka, tare da zuba gwiwar ta, a kasa sai da ta gama wanke gurin ta goge ta saka turarukan wuta, ta rum frsh. Ta koma dakin ta tana haki.

Bai shigo ba sai karfe biyu na rana, ya kawo mata bread naira hamsin da wata ruwan bunu, ya ajiye mata, gashi ta zubda jini. Tana bukatar kulawa amma babu.

A daddafe ta ci bread din da ruwan tea din, tana gamawa wani irin zufa ya karyo mata, kwanciya tayi a gurin, dungurawa tayi a gurin, tana jin Alhaji ya raba tsakanin cinyoyin ta, ya kwanta da ita, sanan ya fita yabar a cikin mugun yanayi.

.... Kallon su nayi naga duk sun rud'e, tare da lumshe idanuna nayi tare da sauke wasu irin kwalla masu zafi, murmushi nayi, sannan na ce musu.
"Kunsan hakki masifa ce, karki yarda wani yabarku da Allah, na zalinci Aliyu, ya kuma gaya min Ubangiji yana madakata. Har yau ina ganin sakayyar Allah. Mu Cigaba"
...
Kwana biyu, Anum ta warware. Kamar ba ita ba, kuma a cikin wannan jinin da tai na kwana goma, sai da Alhaji yayi ta tarayya da ita, ga azabtar da yunwa, ga hantara da masifa. Idan kuma ya zage ta ta rama, ya mata shegen duka..tare da rashin mutunci.

A cikin wannan yanayin wata rana ta samu ta kwace daga gidan, bata tsaya niman kudin abin hawa ba, ta nufi hanyar gida. Kamar wata kuncen hauka. Haka ya sauka a mashin tare da zare idanu, Allah ya takaita Muttaka da Abdul Hakim, suna kofar gidan, sune suka biya mata kudin mashin din, tunda ta shiga cikin gidan.
Da gudu ta nufi dakin Malam, yana kwance dake da daddare ne ta fita.

Ganinta yayi ta shigo mishi tana zare idanu, kamar dai irin ta firgita, rike hannunta yayi tare da zauna da ita, yana kallon yadda tayi zuru zuru, kamar wacce ta tashi cutar hauka.

Kiran Umma yayi, tana shigowa tare da sallama, kallon Anum tayi cikin mamaki da al'ajabi.
"Alhamdulillahi, Ayya yau nake batunki a raina, ashe kina hanya ne? Tare kuk..."

Murmushi malam yayi sannan ya bude baki zai Magana Abdul Hakim yayi musu sallama, tare da tambayar.
"Malam lafiya me yasa mu Anum?"
"Abdul nima ban sani ba, gata nan dai kamar wacce aka korota, Mariya duba cikin d'akina zaki ga ruwan zam-zam da zuma!"

"Toh malam." Inji Umma, tana daukowa ya janyo allon karfen shi ya fara mata Rubutu yana murmushi, zama yayi tare da mata mata rubutu, sannan ya bawa Umma Addu'a, yana kallon yadda Anum take zare idanu. Bayan ya gama ne aka wanke mata, tare da bata dabino, taci da bismillah.

Umartan Umma yayi ta haɗa mata tea me kauri, tana bata ko tsayawa bata yi ba, ta shanye tass. Sannan ya mika mata kular tuwon shinkafa miyar taushe wanda yaji tantakwashi.

Ga manshanu, ba karamin dad'i taji ba, hannu baka hannu karya ta cinye abinci tana zare idanu, mik'ewa Umma tayi ta kuma hada mata tea, tare da kiran Rulwanu ya karbo mata soyayen kwai, a shagon Maude.

Aka tura mata da bread, kamar mahaukaciya, ta nad'e shi. Tana gamawa Umma ta mika mata ruwa, tana sha tayi gatsa. Me shegen ƙarfi. Sannan ta fashe da kuka, zunzurutun tashin hankali. Tana son gaya musu halin da take ciki, amma bakinta yayi nauyi. Haka ta gama kukanta sannan ta tattara tare da nufar dakin Umma, ko dakin Mamanta bata nufa ba.

" Oga Maude! Kasan Anum tazo kamar mahaukaciya, wallahi tana dakin Malam sai kuka take, ina jin Malam yana cewa kamar bata da lafiya an tambaye ta meke damunta tace babu kome." Inji Rulwanu.

Cikin tashin hankali, yake kallon Rulwanu, kafin ya tashi daga shagon, gidan shi ya nufa. Abincin da Hajjo ta ajiye mishi bai duba ba, ya nufi dakin shi. Haka ya jima yana zaune kafin yayi alola tare da gabatar da sallar. Goran faro ya dauka tare da karanto ayatul shifa, sannan ya ajiye, tare da gabatar da wani sallah. Kafin ya dauki goran ya fita dashi wajen karfe goma saura, ya isa shagon ya mikawa Rulwanu yace.
"Ka bawa Umma ta bata tasha. Insha ALLAH zata yi magana."

Kamar da wasa, ya amsa..tare da mishi sai da safe. Cikin jin haushi ila yayi ta surutu, da ya gaji barin shagon yayi, tare da nufar gida.

Har su Umma sun kwanta Rulwanu ya buga mata kofa, amsa tayi tare da cewa.
"Toh amma!"
"Ki bata!"
Tana shiga dakin ta same ta, a zaune ta takura kanta, kuka take yi babu kakkautawa, sai da tayi ta isheta, sannan Umma ta mika mata ruwan tasha da bismillah. Sannan suka kwanta.

Wasu irin mafarkai take Alhaji yana Binta da wuka zai soka mata, bata san me ya tare ta ba, ta fadi sai dai mik'ewar da zata yi wani maciji ya fado kanta, tayi tayi ya wurgar dashi ta kasa, ihu take a cikin mafarkin wanda ya sanya ta farka da ihun, sai da Umma ta rike ta. Tana tofa mata addu'o'in. Wanda yazo bakinta, kuka take tare da gayawa Umma halin da take ciki, da yadda yake dukarta kamar jaka, ga wulakanci kamar me.

Ga yunwa, duk wannan maganar da take bata ce zata rabu dashi ba, dukda kuwa zuciyarta tana jin me yasa ba zata rabu dashi ba, amma akan harshen ta, ta kasa fadar haka. Alola suka yi da Umma tare da gabatar da sallah nafilla. Har karfe biyar suna gurin sai da suka gama azkar, sanan umma tace ta koma ta kwanta. Kallon yadda ta rame, yasa Umma tace mata.
"Amma kina da ciki ne ko?"
"A'a bari nayi."
"Shine kika lalace haka."
Yake tayi, kawai sannan ta lumshe idanunta.
"Ina kayan garanki bai ci ace ya kare ba."

Gabatan ne ya fara dukar tara tara.
"Umma Ni ban gansu ba, wallahi ban san inda suke ba,"
Ta faɗa cikin kuka, sannan ta sunkuyar da kanta.
"Toh Allah ya kyauta"
Tunda ta fadi haka ta fita, tana jiyo muryan Maman Aminu, da malam suna musayar kalamai masu zafi, akan lallai za a kashewa Anum aure ne, shi yasa malam yaki kiran mijinta, shima kuma yace bai ga shegen da ya isa ya maida mishi Anum gidan Azzalumin mutum ba..

Abun yayi tsamari wanda har ya sanya Anum din fitowa daga cikin dakin Umma, kallonta Mamanta tayi tare da sake baki. Ita a tunanin ta yarta ta kai ƙatuwar ban mamaki, sai ga Anum kamar a hureta ta fad'i.
"Ciwo kika yi Khadijah?"
Yake tayi tare da shafa fuskar ta, tace.
"Ban yi ciwo ba, kawai halin rayuwa ce."
"kamar ya?"
Shiru tayi, tare da komawa dakin Umma, haka maganar ta mutu. Tace lallai sai dai Khadijah ta dawo d'akinta, ita kuwa kamar wacce ka gaya mata wani abu, tace bafa zata koma d'akinta ba.

Wasa wasa sai da Anum ta kwashi kwana goma sha biyar, sannan Alhaji ya dibo jiki yazo, kallon juna suka yi, da Maude ajiye yanke bread din da yake hannun shi yayi sannan ya nufi inda yake.

Shiga motar shi yayi, shima alhajin ya shiga motar, kallon juna suka yi. Sannan Maude ya dauke kanshi yana faɗin.
"Kasan sai duk wani makirci da sanin darajar surkulle ba za'a gayawa Buzun mutum ba, domin shi yana rayuwa ne sak da bafulatanin mutum, ba zan hanaka shiga da sharrin da ka dibo dan su baka ita ba, sai dai wannan karon, wallahi zan baka kyautar da ba zaka iya min godiya ba, ka tsayar da fajurcinka iya kanka, ka rabu da ita, kai da kake nima a gurin wanin Allah, ina kuma ni da na tashi na rayu a yadda za a karyawa mutum sharrin da aka tura mishi. Idan ka kuskura ka kuma tab'ata, kai ma kasan abinda kake nima ba zaka samu ba, dan haka ka fita idanu na,.na rufe idan na rufe da kai, wallahi sai kayi hauka tuburan. Ka kuma gayawa Jahilin da yake maka shirka, Ni kuma zan ji daku da Yardan Ubangiji."

Daga haka ya ficce daga cikin su yabar Alhaji cikin motar alhaji, shakkar maude ne ya shige shi, wani irin mugun tsoron shi yake ji, dan haka ya kasa yin abinda ya kawo shi. Da sauri ya bar unguwar. Zuciyar shi kamar zata buga...
#Mai_Dambu....
[2/10, 9:50 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA ƊAYA.

GAISUWA TEAM MAUDE ANA MUGUN TARE□□□□

Yana barin unguwar ya kira Maman Aminu ya gaya mata shi akwai mutumin da yake shiga tsakanin shi da Anum, dan haka kawai zata kiran shi, waye ya mutu waye ya dawo, shi wallahi badan yana ganin mutuncinta da ya rabu da Anum.

Nan tayi ta bashi hakuri, tare da mishi alkawarin yazo ya dauke ta bayan sun gama waya ta fito tayi ta ruwan bala'i tare da sakata a gaba zata dake ta, wai ta tana biyewa Maude zai kashe mata aure, kuka Anum tasaka tare da nuna mata ita fa, babu wanda take kira sannan bata da waya dan bata san inda yake ba.

Mutumin nan haka ya kullawa Anum sharri, koda malam ya dawo,Maman Aminu tayi ta barbad'anci tare da kananun magana. Ai Anum da Maude kaza kaza, bai ce mata kome ba, sai bayan isha da Alhaji yazo Nan malam ya cire kome ya mishi magana akan rashin Abinci. kuma yar shi ba baiwa bace,kar ya kuma dukarta domin wallahi zai kai abin gaban Kwamishinan shara'a.

Sake maude ya mishi kashedi kafin ya shigo gidan haka dai yayi ta bada hakuri da sannan malam yace ba zata koma yau ba, sai bayan ta huta dan yaga bata da ishshen lafiya.babu yadda ya iya haka ya hakura tare da dauke kanshi, lokacin da ya samu ganin Maman Aminu, ya ajiye mata kudi, take ta fara cara a bar Anum ta koma. Dake munafiki ne yace ai ya barta ta huta tukun.

Sannan yayi sallama zai fita, ta kira Anum, bata son zuwa haka ta fita har zauren gidan ta same shi. Ta kowa gaban ta yayi tare da zuba mata ido.
"Kin kawo karana ko? Kin gaya musu na miki abubuwa, me yasa Bazaki nemi saki ba?"

"Saboda ni nasan illar haka ne, aure rai ne dashi, dan haka Ni ba zan kashe abu me rai ba!" Ta gaya mishi a hankali,
"Ok shi wannan banijaren fa? Shi yasa kayi mishi Sharri? Allah ya fika duk mugun nufinka zai dawo kanka Insha Allah."

"Yaushe kika sami bakin magana?" Murmushi tayi sannan tace mishi.
"Tun ranar da na raggon maza ya fara dukana."

Hannun shi da ya gama tab'e tab'e da wani layyar shi,a cikin aljuhun wandon shi ya kai zai tab'a ta,tayi maza ta dakatar da shi..
"Nagode, Mr ten minute. Ba sai ka tab'a ni ba,"

Shiru yayi sannan yace mata.
"Ok! Zaki dawo."
"Insha Allah zan dawo da Alkhairi idan ba zama ba, gamawa."

Daga haka ta shige cikin gidan, ba tare da ta kalle shi ba. Aikuwa yaji haushi. Yana barin gidan ya kira malamin shi ya gaya mishi. Bai boye mishi ba, ya mishi ai da yabi sai yafi kowa moranta, amma fir yaki fahimtar haka dan haka yaje yayi fama da matsalar shi.

--- Washi gari.
Tare da Malam suka karya shi ya bata kuɗi taje tayi lalle da kitso. Haka kuwa ta tafi gidan lallen aka mata, bayan ta dawo Aunty Binta tazo ta kaita asibiti, aka duba lafiyar ta, aka samu jini ne bata dashi da yinwa sosai, magungunan jini aka bata, suna dawowa gida, suka fadawa Malam,

Haka yasa Ya Sadeeq ya kuma sayo mata magani, Umma ta mata miya, dan Malam yazo da nama daga gidan gona, me shegen yawa, aka kuma soya mata wani. Yadda ake ta shirya mata kayan kome zaka rantse da Allah wani garin zata koma, Umma ta saka aka mata garin kunun tsamiya, wanda ake haɗawa da tsamiyar a nika, ga kullun gyada wanda yasha kayan kamshi.

Sai dambun Naman, da garin tsari da kuma shinkafar tuwo da ta wara. Malam ya kuma bata kuɗi yace ta rike saboda wani abu, hidimar da malam da Umma suka mata babu iyaka, Ita Maman Aminu burinta ta koma gidan kamar wanda ake yakushinta.

Maude bai samu damar ganinta na, sai ana gobe zata koma, ta tsaya a shagon shi suka gaisa, mika mata wani roban butter yayi sannan yace mata.
"Gashi ki bawa Malam, kice mishi yajin mu na buzaye ne, naga yana fama da Mura."

Dariya tayi sannan tace mishi.

"Allah yasa da dad'i nima ya samin domin ina mura,"

"Me kwaɗayi!"
"Nagode, Amma Maude ina cikin damuwa"
Kallonta yayi sannan yace mata.
"Allah ya kawo miki dauki, kuma ita rayuwa da kika ganta ba dukka mutane bane suka san hakkinta, dan haka kiyi hakuri. Duk abinda aka miki ki bar mutum da Allah zai bi miki hakkinki."

Ajiyar zuciya ta sauke sannan tace mishi.
"Maude har dukana yake! Sannan bai."
"Anum me yasa kike son zama daya daga cikin matan da bazasu iya boye sirrin su ba? Kiyi hakuri ki boye wannan lamari, Allah yana tare dake, idan naji labarin abinda yake damunki hakan zan ta kallon Alhajinki"
Ya faɗa yana mata dariya, sam bata ga abin dariya ba, murmushi tayi sannan tace mishi.
"Aifa, Alhajina mmm!"

Yayi mata nasiha, sannan ya bude wani drowa a shagon ya dauko mata karamin Alkur'ani me dauke da Yasin! Da wasu addu'o'in. Ya mika mata, insha Allah kika rike Alkur'ani Allah zai tayaki yaki, amma kema fa baki da dad'i!"

Gyada kai tayi sannan tace mishi.
"Eh bani da shi, amma toh ba damuwa."

Ta faɗa, ya fahimci taji haushi yasa shi, ya sashi dafa mata indomie tare da kifin gwangwani, suna tsaye tana mishi mita, yana jinta sannan ta mika mata.
"Jeki ci, nasan kinyi kewar shi."

Hawaye ne ya zubo mata daga idanunta, tana kallon shi. Dauke kai yayi tare da rufe window, a hankali ta koma cikin gidan, ta zauna tana wani irin kuka. Ga abincin amma ta kasa kai loma daya. Tana ji a ranta tayi rashi na har abada, me yasa bata rike shi na lokacin da yake tare da ita, tana kuka ne da duk zuciyarta.

Kallonta Umma tayi,
"Toh ya isa haka kar malam yazo yaga kina kuka."

Bata daina kukan ba sai da Umma ta zauna a jikinta, ta fara ajiyar zuciya. Shafa kanta tayi sannan tace mata.
"Ci!"
"Umma"
"Bana son magana!"
Haka ta kwantar da kanta, tana ajiyar zuciya, daga baya ta cinye indomie (😂😂😹😹) tunda ta cinye ta kasa maida mishi plat da cup din, karewa sakawa tai cikin kayanta ta boye.

Haka umma tayi ta bata maganin gyaran jiki, tasha a daren washi gari ma ta wuni sha, kafin yamma. Aunty Binta da Yan uwanta suka rakata, har gidan ta, sun sami Alhaji yana korawa Barirah Ashari'a, ganin su Anum ysa shi yin Fuska. Ya karbe su hannu bibbiyu, ya kuma kai su part dinta, da ta samu a gare.

Sai lokacin maganar Malam ya dawo mata,.tare da turaren da ya bata, wanda Maude ne ya hada yabawa Malam, sai wannan yajin, bai bata abun dan ya kashe mata aure ba, asalima ya bada ne dan taci yakin duk surkullen da. Alhaji zai mata Insha Allah ba zai kamata ba.

Sai wasu na karya sihiri ko tsafi,.wanda ya haɗa mata a cikin turaren wuta, ya bawa Malam dan ya gaya mishi kome akanta, ya kuma ce mishi Insha Allah, ba zata kuma fita hayacinta ba.

.... Tana shiga abinda ya fara yi, shine dauko burning, ta zuba turaren tare da zama tana cewa.
Aunty B! Ina kewar Umma Na!"
"Ai baki isa ba, muma haka muke kewarta, kuma muka yi hakuri."
Inji Aunty Aminatu,
Tura baki tayi, tare da cewa.
"Sai na gayawa Umma abinda kuke min!"
"Ke Anum bamu ciki da gulma me muka miki"
Inji Aunty Rabi.
"Oho ina nasani, kawai dai naga kuna min dariya."
Dariyar suna saka sannan suka nufi kitchen ɗin ta,.suka saka mata kome a cikin freeza musamman garin kunun tsamiya, da miyarta sai soyayyen nama,.kula shi aka yi a laida.

Suka bata tare da cewa.
"Saura ki ajiye mishi."

Murmushi tayi, sannan tace.
"Toh"
Make keyarta Aunty Binta tayi tana dariya, haka suka taimaka mata ta shirya kome cikin tausayin rayuwar da take, da zasu tafi haka Suka bata dubu biyar biyar su Uku, dan Aunty Rabi bata zo ba, Ya Abubakar ne da Rulwanu, shima sabida gobe zai kawo mata taliya yar murji ne, da su tafi har kofar gida ta bisu, tare da cewa Rulwanu.
"Rulwanu don Allah kace Umma, barshi ungo ka saya min Masa a kawo min"

Ta faɗa idanunta na kawo ruwa,
Murmushi yayi sannan yace mata.
"Ni zan saya miki, Insha Allah zan kawo miki kinji ko!"

Hawaye ne ya sauko sharrrr, tsayawa suka yi suka rarrashe ta, sannan suka bar gidan, tana shiga cikin part dinta, ta sami Alhaji yana zaro idanu.
"Wannan turaren babu dad'i."

Bata kula shi ba, ta wuce kitchen ta daura abinci a saman reshon da tazo dashi, tare da katon galan din kananzir. Haka ta shiga abinci cikin sauri ta dafa shinkafa da waye, sannan ta juye a wani kularta, ta kuma kai d'akinta miyarta ta zuba a kan wanda taci, sannan ta dawo falo,.ta ajiye yayi sanyi dan bata son cin abincin da sanyi d'akinta ta shiga tayi Alola, kamar ance ta d'aga labulen d'akinta bayan tafito daga alolan hango Alhaji tayi yana saka wani irin halitta yana hura mata abincin da zata ci, cikin tsoro ta sake labulen.

Shi yasa Maude yace barci ba nata bane, bata cancanci barci ba. Tana rayuwa idanunta a rufe, had'iye kukan da yazo mata tayi, sannan ta gabatar da sallah, tana idarwa ta fito. Yana gurin sai sashe baki yake, daukar plat din tayi tare da fitowa waje, ta kira yaran shi kafin ya dakatar da ita, ai kuwa yaran sun fauce abincin tare da daka sowa. Tuni suka cinye abincin.

"Wannan wani irin Iskanci ne da zaki basu abincin." Kallon shi tayi cikin mamaki sannan tace.

"Ai Yaranka yarana ne, kuma banga laifin dan na basu abincin na ba, so idan ba wani abu bane a ranka manta kawai."

Daga haka ta ajiye Plat din, ta shiga cikin d'akinta ta koma kitchen ta sake zuba miyar asalima tsoron kar ya zuba mata abinda ta gani tasa a ranar ta maida freezan ta d'akinta dake akwai sarari, shima firjie din ta mai da cikin ɗakin.

Ta bar kitchen ɗin domin girki, kayan abincin ta kuwa a cikin wardrob ta zuba kayan sawanta ta maida cikin akwatinta.

Duk bai Fahimci abinda take ba, sai da da.ddare da ya shigo. Yaga freeza a d'akinta ya tambaye ta hujja.
"Kawai naga zai fi min sauki ne na ajiye kome a d'akina, dan wancan lokacin ban san ya akayi kayan ya watse ba. Shi yasa yanzun na tattaro kayana ka ajiye kusadani. Ban sani ba ko nayi laifin da za a zagi iyayena da dukana ba."

"Haba Autar malam, babu wannan keda kike da masu tare miki fada ai ko tsohon mijinki ba zai bar mutum."

"Don Allah, barci nake ji!"
Ta faɗa mishi a sanyayye, domin ta ji ya fara lallubar ta, duk yadda taso bijire mishi, haka ta bar shi ya mori gajiyar Umma, iya hanata barci yayi tare da masifar naci. Sai karfe biyu na dare ya mike ya fita, da sauri ta sauka tayi wanka, tare da alola tazo ta fara sallah, tasan idan ya dawo zai kuma koma mata, dan haka ta shiga sallar dare babu wasa.

Koda ya shigo ya same ta, tana sallah, ƙarara ya razana da wannan sabon lamarin da tazo dashi. Dan haka ya zauna tun yana jiranta har ya kwanta. Haka ya bingire da barci, tana idarwa ta dauko Alkur'anin da maude ya bata, ta iya karatu toh meye ya shagaltar da ita, dan haka ta shiga karatu tare addu'a.

Karfe uku da rabi ta kwanta, dake akwai, masalatai a cikin Unguwar, tashi tai daga abin sallah ta nufi ban daki, tayi tsarki da alola, sannan ta kuma gabatar da sallar asuba. Tana zaune a gurin har rana ta fito, Alhaji yana barci, bata tashe shi ba, dan tasan yanzun sai ta fara masifa. Tana idar da azkar, ta kwanta a gurin....
Tsugunne Ba kare ba.....
#Mai_Dambu.
[2/10, 9:50 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA BIYU.

Wannan Shafin na kune masoyan Zanen Qaddara ta! Nagode Nagode na kuma Cewa Nagode sosai! Ga Anum a gidan Mudi wunti

*** Washi Gari
Sai ga Rulwanu da katon kwalin taliya, da kular masa, na gidan Dahiru me sugar. Sai farfesun kayan cikin rago, yayi kyau sai kanshi yake, ta zauna tana ci tana kuka.
"Rulwanu kayi hakuri!"
"Babu kome Little princess! Ci abincin ki, Insha Allah duk ranar Juma'a zan na zuwa duba ki!"

Haka kwalla ya shiga zuba mata, shi kanshi Rulwanu tausayin Anum ya kama shi, dan haka ya fita da sauri ya barta karta karya mishi zuciya....

Tunda ya lura da sabon salon da ta bijiro dashi, sai ya shiga mata rashin mutunci.

Idan tayi mishi abu zai kama masifa kamar zai dake ta, ita kuma bata tab'a damuwa ba, dan tasan haka zai ganta ya barta.
Suna cikin wannan yanayin, ta kuma samun ciki, irin me shegen laulayin nan, bata son wanka. Kai duk wani dabi'ar kazamta, duk da Rulwanu yana zuwa dubata.

Amma bayan jin dadin yadda take rayuwa, akwai lokacin da yazo ya samu ta tara wanki, haka ya sakata ta hada kayan, ya tafi dashi gidan, Umma da kanta tayi mata wanki. Aka mata goga, sannan da zai kawo suka zo tare da Umma da Maman Aminu.

Duk yadda take tsammanin zata ga gidan sai da ta karaya, dan haka babu yadda ta iya, koda suka shiga part din Anum, suka ga tana kwance a kasa, ga dan roban yawunta, sai da suka rasa yadda za suyi da ita, take Umma ta shiga gyara mata gidan,
Jikin Maman Aminu yayi sanyi. Kamar me duk yadda take ganin Alhaji yana mata b'arnan kudi, ashe cin Uban yarta.

Shiga dakin Anum tayi tare wanke ban dakin ta fidda sauran kayan da ta b'ata, Sannan ta haɗa mata ruwan zafi, ta kai Anum ban daki tayi wanka, tana fitowa suka bata wani kaya.

Niman Alhajin suka yi, akan zasu kai Anum Asibiti, yaki zuwa. Dole suka kira Binta. Tazo har gidan ta saka mata ruwa, suka duba akwai sauran kayan abincin da aka dawo da ita. Yana nan.

Girki Umma tayi mata faten wake, da ta tura Rulwanu ya sayo mata ganyen alayahu a kasuwar Wuntin dada, suna cikin haka Aunty Binta tazo ta saka mata ruwa da allurai, da Magani,
"Maman Sadeeq, gaskiya auren Anum da wannan mutumin akwai matsala, gaskiya ba zan iya ba."
"Ni kam a bar min aurena, ina son zama da shi. Lokacin da nace bana son shi ai cewa kika yi zaki tsine min yanzun kuma kice zaki raba bar min aurena ina son shi haka. Duk wani rayuwar aure juriya da hakuri yake tafiyar dashi, Ibada da niman dacewar Ubangiji yake zaunar dashi lafiya, ba za a kuma kashe min aure ba."

Ta faɗa a sanyayye, tare da lumshe idanunta, aikuwa ran Maman Aminu ya b'aci, wallahi sai ta kashe auren ko da kuwa zata rasa nata auren ne. Haka suka zauna har ruwan ya kare, sai da zasu tafi Alhaji yazo, kallon juna suka yi da Umma, kwarjinin da tayi mishi yasa shi sunkuyar da kai.

"Sannun ku! Ayya wallahi ina ta sauri naje ganawa da Me girma gwamna n.." cikin jin haushi Maman Aminu ta kalle shi zata yi magana, Umma ta rike mata hannu.
"Toh Alhaji, Ga Anum can mun gama abinda zamu yi, idan Allah ya kai mu ko zuwa dare zamu zo mu duba lafiyar ta, da abin cikin ta."
"Ciki ne da ita?" Ya tambaye su a rikice.
"Eh Muna fatan haka!" Inji Aunty Binta,
Shiru yayi sannan yayi fatan Alkhairi, ya raka su har suka fita, dawowa yayi wani irin bakin ciki yake ji.
Yana shigowa ya same ta akan abin sallah, tana addu'a. Dauke kai yayi tare da cewa.
"Ashe ciki ne dake?"

"Nima haka naji!"
"TOH gaskiya a zubda!"
"Ba zan iya wannan kasadar ba"
"Lokacin da kika zubda wancan me yasa baki gane kasada ce"
"Saboda ban ji a raina na haifi dan gaba da fatiha ba,"
" Ni kikewa rashin mutunci?" Shiru tayi bata kuma kula shi ba, haka ya fice, tun daga ranar ya tsiro da rigima, tayi magana yace zai hadata da yaran shi, bata kula shi.

Sai dai wani barazanar da take fuskanta da yaran shi haka kawa zasu shigo mata suyi ta mata wani abu kamar marasa hankali, duk abinda suka gani naci saukewa suke su fita dashi su cinye, Nan ma bata kyale su ba. Ta cigaba da addu'a, tana saka turaren ta,
Idan ta saka da gudu suke fita, kawai sai taji tana shakku akan haka, dan hakan ta fita gurin yadiko yaran suna ganinta suka taso mata, cikin wani irin tsoro take kallon su, kamar ta zura d'akinta. Daka musu tsawa Yadiko tayi tare da kallon ta, ta dauke kanta.
"Nace ba"
D'aga mata hannu tayi, sannan tace mata.
"Ba zaki samu abun da kike son sani ba, ku matan waje kuna rayuwa ce ta wata irin hanya mara bullewa, kuna ganin mazan da suke shiga manyan mota kamar sune yan Gatan Allah, idan da zaka bincika dukiyar su bata halal bace, amma burinku ku aure shi ko ba haka ba?

Idan ya sauke wasu matan daga kauye, ke fa a cikin gari ya ganki ya auroki. Toh gashi an wayi gari iyayenki suke ciyar dake, meye amfanin bad'i ba rai? Ka sayar da Akuyarka ta dawo tana ci maka danga, abinda naso sanar dake kenan ranar, baki dace da nan gidan ba, Allah yana sonki da rahama ne yasanya iyayen ki sukar tsaye akanki, bai kai da ya miki kome ba."

Daga haka ta juya abin ta, shiru nayi ina kallon bayanta, ina jin tashin hankali a kasan raina, ina na kawo kaina? A hankali ya juya tare da komawa dakina, idan na fahimci yanayin gidan nan, akwai wani abun da Alhaji yake aikatawa. Amma Allah ya fishi. Tunda na shiga naji sabon zazzabi ya rufe ni.

Karfe tara na dare, muna zaune a falo, tsautsayi ya sani kunna BATV, na samu sun saka labarai. Ina zaune ina kallo har suka gama, wani horror fim suka saka. Wai The rings.

Tashi nayi na shiga ban daki nayi alola, sanan na gabatar da sallar isha tare da shafa'i da witiri. Ina fitowa falo na sami Alhaji yana zaune. Zama ina nayi ina kallon fim din.

A hankali aka fara yadda yaron yake ganin fatalwar, Film din baki dayan shi abin tsoro ne, dan haka da naga zan razana zuciyata, na tashi tare da mishi sai da safe, ina shiga dakina. Nayi sabon alola. Sannan ta kwanta.

Ko minti biyar banyi ba barci ya dauke ni, ba zan iya cewa ido biyu nake ko mafarki nake, karar tvn naji hakan yasa na mike domin kashewa ina mamakin me yasa Alhaji bai kashe tvn ba.
Ina fita falon, naji Ni cikin ruwa, dubawa nayi naga ashe daga tvn jini yake zuba, daga wani rijiyar jini, ga wannan yar fatalwar cikin jini tana mika min hannu.

A firgice ta fara karanto ayatul kursiyu, kafin na farka. Addu'ar wanda yayi mugun mafarki.

Wanda Ya yi Mafarki mara kyau.

أَعُوذُ بِاللهِ مِنَ الشَّيْطَانِ الرَّجِيمِ ثَلاَثٍ مَرَّاتٍ.
a'uzu bi-l-lahi mina shaytani r-rajeem (3)
Wanda ya ga abu mummuna a mafarki, to sai ya yi wadannan abubuwan:-
-Ya yi tofi ta gefen hagunsa sau uku.
-Ya nemi tsarin Allah daga shaidan da kuma sharrin abin da ya gani, sau uku.
-Kada ya gaya wa kowa wannan mafarkin.
-Ya juya daga kwibin da ya kasance yana kwance a kansa.
Sannan na kara da addu'ar farkawa da nayi a firgice.

Addu'ar wanda ya Razana a cikin barci, Da wanda Ya Kasa Barci.

أَعُوذُ بِكَلِمَاتِ اللَّهِ التَّامَّاتِ مِنْ غَضَبِهِ وَعِقَابِهِ، وَشَرِّ عِبَادِهِ وَمِنْ هَمَزَاتِ الشَّيَاطِينِ وَأَنْ يَحْضُرُونَ.
A'oozu bikalimatil-lahit-tammat min ghadabih,wa'iqabih, washarri 'ibadih, wamin hamazatish-shayateen, wa-an yahduroon.

Ina neman tsari da kalmomin Allah cikakku daga fushinsa, da ukubarsa, da sharrin bayinsa, da kuma wasuwasin shaidanu, da kuma kada su zo mini (a cikin al'amurana).
Kullewa mara na, yayi na tashi zuwa ban daki nayi tsarki da Alola, nazo na fara nafilla, ina cikin sallar naji abu na sauka daga tsakanin kafana, sallame sallar nayi na nufi ban daki, na tsuguna a kasa, hawaye na zuba daga idanuna.

Ina jin yadda gudan jini ta, yake zuba. Kuka take kamar wacce ta rasa uwarta da Ubanta. Tun karfe sha biyu na dare, take wannan yanayin, bata samu saukin al'amarin cikin ba, sai karfe hudu na asuba, sannan taji saukar shi, sannan ta shiga rarrafa zuwa d'akinta, ta haɗa ruwan zafi, a hankali take sauke ajiyar zuciya, jin kanta take kamar ana mata ihu akai. Dan haka ta shiga karanto addu'o'in niman tsari.

لاَ إِلَهَ إِلاَّ اللهُ الوَاحِدُ القَهَّارُ، رَبُّ السَّمَوَاتِ وَالْأَرْضِ وَمَا بَيْنَهُمَا، الْعَزِيزُ الْغَفَّارُ.
La ilaha illal-lahul-wahidul-qahhar, rabbus-samawati wama baynahuma, al'azeezul-ghaffar".

Babu abin bautawa da gaskiya sai Allah, makadaici, marinjaye, ubangijin sammai da kasa da abin da ke tsakaninsu, mabuwayi, mai yawan gafara.

Da sauki ta samu, sakamakon kuwwar da kaita yake. A hankali ta janyo ruwan zafin ta shiga da shi ban dakin, tayi wanka da shi. Ta wanke gidan jininta, ta nade shi da tsuma, sannan ta wanken jinin d'akinta, tare da abin sallah.

Tunda ta samun ta gyara jikinta ta fito, rub da ciki tayi ta kwanta.

A hankali barci yayi gaba da ita, me cike da mugayen mafarkai. Sakamakon ganin Alhaji yana Binta da wuka, wannan karon ma macijin nan sai da ya fado kanta ya makale, akan cikinta, kanshi a kirjin ta. Haka ta farka daga barci.

Ganin Alhaji tai a kanta, addu'a tayi tare da, wanda ya ji tsoron wasu mutane zai fada:

اَللَّهُمَّ اكْفِنِيهِمْ بِمَا شِئْتَ.
Allahummak finihim bima shi'ita.

Ya Allah! Ka isar mini su da abin da Ka so.

Birkicewa yayi, tare da kallon ta. Yana ƙoƙarin boye abinda yake hannun shi.
"Meke damun ki?".
Dakyar ya bude baki tace mishi,
"Bari nayi!"
"A garin sakarcin ki, kika zubda shi? Don Allah yanzun me zan gayawa iyayenki, ko kina son ki koma gurin mijinki nan ne kika zubda min cikina?"

Kwanciya ta gyara,tayi sannan ta cigaba da addu'a, har barcin ya dauke ta, murmushi yayi sannan ya fice daga d'akin.

A hankali ta farka daga barcin tayi addu'o'in farkawa daga barci, sannan ta lallabatawa tayi cikin nutsawa ta kwashi abin miya, da soyayyen nama, taje tayi dan farfesun wanda yaji attarubu, tana zaune a gurin jiri na diban shi.

** Koda ta gama miyar, taliya ta dafa, tare da juye abincin zuwa d'akinta, tayi wanka tare da gyara Jikinta, sannan ta ci abinci, ta shiga Niman maganin ta na wancan barin.
Shi tasha, sannan ta kuma kwanciya. Karfe biyar na yamma Umma suka kuma zuwa, anan take gaya musu cikin ya ficce.

Shiru Umma tayi sanan tace Mata.
"Babu kome, Allah ya baki wani me amfani."

Ta mata nasiha sosai, sannan suka bar gidan, washi gari sai ga Rulwanu da katon bokitin anyi miyar kafar saniya, da bindin shi aka kawo mata, sai kamu da kayan yaji, Dakyar Maman Aminu ta bada dubu uku aka kawo mata, malam kuma ya sake hada mata kayan gara.

Sannan Suka zo da Maman Aminu, ta kawo mata har da Ganyen auduga aka tafasa mata, ta sha madara, kafin wani lokaci ta daina jin jiri. Sun mata hira kafin suka bar gidan.

Tukun nan....Inji me mugun labari
#Mai_Dambu
[2/11, 9:05 AM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA UKU

Bata sake zani ba, dan zaman ba wani dadi bane, take ji daga kan wannan b'arin bata kuma samun ciki ba, sai bayan wata biyu cif ya samu ciki.

Dan haka tayi ta b'oyewa, duk da ya fahimci tana da ciki, sai ya zuba mata ido yaga iya gudun ruwan ta, abu kamar wasa cikin yana zaune kyam.

Wani rikici suka yi, ta gudu gida Malam ya dawo da ita da kan shi, suka yi magana sosai. Bayan Nan Muttaka da Abdul Hakim, suka je har gurin aikin shi suka mishi rashin mutunci, kamar zasu sake shi, Muttaka kam ma sai da ya mari Alhaji.

....Abinda ya fusata shi shi kenan ya dawo gida, tare da saka yaran shi, suka rufe Anum da duka, Suna cikin wannan yanayin Allah ya wurgo safiya da Hafsat, sune suka kira yan uwan su, suka gaya musu. Ko minti talatin basu yi ba, suka iso aka kaita asibitin.

Dakyar aka tsayar da cikin jikinta, shi kuma Alhaji aka kama shi, domin Yadiko ta gayawa yan sanda abinda ya faru.

Koda aka kai shi Office din yan sanda, nuna musu yayi yana da kudi aka juya case din tare da tuhumar Anum, tana kawo mishi maza gida, kuma ba kowa bane sai MAUDE.

Lokacin da aka zo kama maude bai d'aga hankalin shi ba, bin su yayi.tunda ya shiga office din D.P.O, wani tudu wani ganganre aka juya case da cewa. Alhaji yana tsafi da cikin Anum, abubuwan da yake aikatawa da wulakancin da yake mata, karshe dama yana koran matan shi da ciki ne, sai gashi ita kuma bokan shi ya ce ya barta ta samu cikin yana bukatar shi domin Arzikin shi yana jikin cikin ne, shi yasa tana samun cikin yake sanin yadda yake zubda shi.

Sannan idan tayi b'arin baya barinta ta samu hutu yake koma mata, wanda haka cin zarafi ne, gashi baya ciyar da ita,abubuwan da ake yi ta lissafowa basu fadi.

Dan haka suka tura su kotu. Tun daga nan maude bai kuma bin case din ba, sai ranar da za a zauna ne, aka nuna musu iyakar su,kuma ace babu saki sai ma ta bada miliyan daya da rabi, kudin wanke muni.

Maude da kanshi ya kuma niman Alkalin a sirrince, bayan sun gama magana, aka kuma d'aga kara.

Ranar da za a kuma komawa, cikin shirin shi na buzaye ya isa kotun, inda ka gabatar da wani case kafin nasu Anum, cikin takaici da bakin ciki, Alhaji yayi ta ihu yana zagin maude da Anum sannan alkali ya raba auren. Tare da zaman gidan kaso ko zab'in biyan tara miliyan uku da wani abu, sakamakon yayi yunkurin kashe mace da ciki.

Wannan shine dalilin da ya kashe auren Anum da wancan jahiliin.

A can asibitin kuwa, Anum sauki ya samu sosai domin ba zaka ce tayi jinya ba, ta mai da jikinta kamar ba ita ba, sabida kulawar da take samu a gurin Umma.
Idan ta Maman Aminu ce, bata ki a zubda cikin ba, amma Malam ya hana kowa, dan haka da aka sallame ta, suka dawo gida, nan suka shiga lallabata tare da ririta cikin jikinta, ana bata kulawa.

Cikin da kamar jira yake, a san da zaman shi, Alhaji ya kawo kudin baki daya, Maude ya bawa Malam shawara ya sayawa Anum fili wata rana zata amfana dashi.

*** A gurin kwashe kayan ta, ne suka shiga tsoro wasu mugayen abubuwan da aka saka a cikin dakin, basu tab'a ba,suka tattara aka kawo wa malam, shi kuma ya duba ya kona tass, sannan ya bada addu'o'in aka kawo mata tana sha tare da yin sallah dare.

A hankali rayuwa take juya musu, tare da abubuwan ban mamaki, a yanzun Anum ta shiga nutsuwarta babu ita babu su Xoxo, gashi Malam yana ƙoƙarin inganta mata lafiyarta, da abinda zata ci, Maude ma kullum yana bashi ƙoƙarin, koda zata fara awo. A kofar ram tayi awonta.

Rulwanu yake kawo ta a mashin din Maude, bayan ya ajiye ta, tana gama abinda zata yi zata kira shi.

Wani irin jituwa da mutunta juna, ya kuma samun mazauni a zuciyar su. Idan ka gansu da juna zaka fahimci cikin jikinta shi yayi musu iyaka da juna, dan haka take ala ala ta haihu, domin su koma rayuwar su ta baya.

**

Bayan wata uku.

Indomie da kwai ta cinye tare da sake katon gatsa, sannan ta jingina da bango, tana lumshe.
"Umma na nagaji wallahi ko ina na na jikina ciwo yake!"

"Toh ai sai ki kwanta kiyi barci tunda barci kike ji, umma bata rufe baki ba, ta dungura a gurin, tayi barci ya har da munshari,

Tunda ta dawo bata wasa da ibada, kuma bata tab'a barin sallah ya wuce ta, ga shi Umma ta bata addu'o'in sosai tana yawan karantawa tana sha, musamman ba kambun baka da idanu, haka take kullum, malam yana mara Rubutu, ga wanda ake kawowa daga shagon Maude,

Cikinta yana shiga wata bakwai, kawai maude idan ya fita yaga kayan yara wanda mace da namiji zasu iya sakawa yake kwasowa. Duk wanda ya gani sai yayi maganar kayan.

Dan haka ya tattara soyayyar duniyar manya daurawa cikin Anum,matar shi kuwa fada suke har da yaji akan zai dawo da anum murmusa mata yake kawai tare da manna mata Hauka, Kuma ta zata da da gaske yake shi yasa take birninta, bai tab'a damuwa ba.

--idan ka kalli Anum sai ta baka dariya cikin ya sata tayi muni, tare da zama rushsshiya hancinta yayi wani katon, cikin ya buda ta sosai kamar ba ita, ba,.
Shi yasa wani zuwan da Malam yayi Badara, yayi mata sayayya kayan kamshi da Umma ta bashi aikan,
Aikuwa ya tawo mata da uban lodin kaya,kamar wanda bai san ciwon kudin ba, tun haka bai damun Hafsat da take zuwa lokaci zuwa lokaci har ya fara samunta.
Haka maude da daurawa kai dawainiyya,ya shiga mata sayayya kayan baby, duk lokacin da ya shiga kasuwa sayan kayan shagon shi yana ganin abinda yayi mishi zai sayo mata,

Tun Umma bata magana har ta kare tayi mishi magana,sai dai abin da ya gaya mata ya kashe mata jiki ainun kasa magana tayi tare da cewa.
"Toh mun gode, Allah yasa ka da alkhairi!"

Haka ta koma cikin gidan tana jinjina qarfin hakurin shi tare da yarda da ƙaddara. Abinda yace mata ya tsaya mata a rai. Da tace mishi.
"Malam Maude, kana hidima da yawa, don Allah ko zaka hakura da wani abun ne?"

Murmushi yayi sannan yace mata.
" Ba Anum nakewa hidima ba, abinda zata haifa nakewa hidima, rabon su ya hanani zama da ita, ashe kuwa idan na yarda da ƙaddara toh yaran da zata haifa tankar nawa ne, ni ki dauke ni a matsayin d'an ku, karku duke Ni a matsayin surikinku,

kuma da ace ban rabu da ita ba,. ƙarshe mutuwa zan yi sabida rabo, kuma yarda da ƙaddara wajibi ne ga musulmin kwarai."

Wannan maganar ya tsaya mata a rai, sosai. har take gayawa Malam yadda suka yi dashi. Murmushi yayi sannan yace mata.
"Dan babban gida ne, ya fito daga gidan da aka san darajar mutane da kan shi ne!"

Bayan rabuwar Alhaji da Anum a kotu, kamar zai yi hauka. Dan Yadiko ma ta bar gidan, yaran ta sun zo sun dauketa. Barirah ma ta gudu garin su. Sai gidan ya zama wani irin gida, yana shiga yaran shi zasu nime kamar zasu kashe shi. Karshe guduwa yayi ya bar gidan, ya koma gidan gonar shi ya zauna.

** A gidan Maude ma, Hajjo masifar take kamar zata cinye kanta, sakamakon yadda Maude yake b'arnan kudin shi akan Anum, idan tayi mishi korafi yace bata da hakuri, ko ta cika kishi.

Anum da take da ciki me zanyi mata ko me zata mishi. Wannan dalilin yasa take hakuri, dan ráshin kunya har gida tazo tayiwa Anum kashedi ta rabu mata da miji, murmushi Anum tayi sannan tace mata.
"Idan ina son na kasance da shi, wallahi sai kin rabu dashi, ko yayi pushing dinki out, dan haka karki sake na haihu, domin me guri yazo, mai taburma ya nad'e."

Ta gaya mata haka, sannan ta cigaba da abinda take yi, wai ita tazo gaida Anum ne take gaya mata magana, kuma Alhamdulillahi taji amsa daidai da wanda bata zata ba.

"Umma! Don Allah kice Rulwanu ya bar kallona." Ta faɗa da karfi, tare da tura baƙi.

"Rulwanu tashi a gabanta" inji Malam.
Tsaki Maman Aminu tayi, babu wanda yabi ta kan tsakinta.

"Wallahi Umma yarinyar nan ta koma kamar matan sayawa!" Ya faɗa yana Dariya.
"Umma kinji shi ko, wai kice basaya"
"Shi kuma sai mu kirashi da bahangashe. Ko shi da kare mutu kara ba!" Inji Umma.
"Malam kana jin Umma ko? Wai ni ne hangas!"
"Toh Rulwanu, kai kace mata Basaya, kai kuma bahangashe" inji Malam,
Hiransu gwanin ban sha'awa, har malam ya fita aiki. ya rage daga Umma sai Anum da Rulwanu, wanda yake mata tsiya.
"Umma nikam!"
"Ya dai Anum? Ke kam me?"
"Wallahi abin nan ne yake tsaya min a cikin Kinga yadda yayi ranga ranga!"
Ta kuwa bude cikin, tana kallon Umma.
"Yaushe ya fara miki haka?"
Shiru tayi na wani mintinan tana son tuno lokacin da ta fara jin haka.
"Umma ba zance miki ga lokacin ba, amma bana jin dadin yadda yake min, sai naji na gaji. Sanan nayi ta hakki"
Kura mata ido Umma tayi, sannan ta kira Maman Aminu,
"Toh Ni da aka kira ni wata uwar zan mata?"
"Babu abinda zaki min, kije abinki, kudi yana iya fin d'a! Miji! Da wasu abubuwan, Amma soyayyar gaskiya bata tab'a karewa, ban san me yasa Ubangiji ya sani fitowa ta jikinki ba."

Aikuwa ta rufe ta da duka, sai da Umma ta shiga tsakanin su.
"Wannan wani irin shirme ne? Zaki daki yarinya da ciki. Meye Matsalarki da rayuwa Anum, ai gaskiya ta faɗa, ince nan kike kuna baki son ta, da abin cikin ta. Har kina cewa ta zubda cikin. Tsakani da Allah, kike nunawa yan uwanta sun fita daraja a gurin ki, Maman Aminu kowa rai ya amfani yafi ga me shi. Anum Yarki ce, amma yadda kika juya mata baya bata cancanci haka daga gare ki ba."

Juyawa Umma tayi ga Anum da take kuka wiwi,
"Ke kin san darajar Uwa? Toh karki yarda ki sab'a mata, karki yarda ki rabuwa da ita cikin bakin ciki da damuwa, Uwa ba abar wasa bace!"

Cikin kuka tace.
"Umma me take so na mata wanda ban yi ba, Umma nayi mata biyayya, ta rabani da mutumin kirki, ta amshi kudi a hannun Alhaji Mudi, duk lokacin da muka sami saba'ni sai ya gaya min, cewa Uwata makwadaiciya ce. Me take so? Na zubda cikin na kuma fadawa zawarci me hatsari? Sakacinta ya sani na fada sharrin kawaye da Alhji mudi, wallahi Maman Mu, ki tanaji amsar da zaki bawa Ubangiji, domin ni dake zamu tsaya a gaban shi yayi mana shara'a. Kuma daga yau mijin da yayi min zan aura, inda kika ga Ban Auri Maude ba, wallahi tsananin rabo ne ya kuma shiga tsakanina dashi."

Daga haka ya yinkura da karfi, zata mike Aikuwa bayanta ya amsa, komawa tayi ta zauna, kwalla na zuba mata, kallon Umma tayi sannan tace mata.
"Umma bayana kamar zai b'alle!"

Umma kan kasa magana tayi, domin abin ya fara damunta. Dan haka ta taimakawa Anum zuwa d'akinta, Maman Aminu kuwa bakin ciki kamar ya kasheta, domin tana ganin Anum tana shirin fin karfinta.

Duk da cikin bai cika watan Haihuwar shi ba, amma Umma ta Fahimci irin silent labour take yi, dan haka basu B'ata lokaci ba aka wuce da ita asibitin. Suna zuwa kofar ram aka tura su Babban Asibitin.

Suna zuwa, aka ce musu aiki ne. Dan haka Umma ta kira Abubakar, shi kuma ya gayawa Yan uwan shi, jinin da za a saka mata, aka rasa wanda yayi dai-dai da nata, dole aka shiga nima. Na malam kuma yana fama da rashin sinadarin glucose. Dan haka suka ce a'a. Na Rulwanu aka diba shine yayi daidai da nata, yayi ta fushi tare da cewa..ai idan aka gama mata tayi mishi tijara sai ta biya shi jinin shi.
#Mai_Dambu
[2/11, 8:16 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA HUƊU.

Wannan Shafin na kune! Usainah B Abubakar, Mrs Abubakar da Maman Shahid

Cikin ikon Allah da kudirar shi, aka cire mata katon yaron ta namiji dashi, amma sun kai shi shsshin kula da jarirai. Haka Yan uwanta suka rufa akanta, babu wanda ya damu da jaririn, Umma ma Mantawa tayi dashi.

Domin numfashin ta, yana sarkewa, da zaran tayi kamar zata farka sai ya kuma sarkewa, hankalin yan uwanta yayi mugun tashi, ban da Hafsat wacce Maman

Aminu ta gaya mata, abinda Anum tayi mata, ai kuwa taki zuwa asibitin tana taya Uwarta jin haushi.

Kowa ya cire rai da farkawan, dan haka suka zubawa Sarautar Allah ido, suna jiran su ga yadda zai yi dasu. Idan kaga Malam sun samu sosai, kasa zama yayi kuma yaki ya dawo gida, haka ya cigaba da kallon Anum, tausayin jaririn da yake can gurin kula da lafiyar shi, rike hannunta Umma tayi, tana kallon yadda tayi wani irin, duk sai ta diririce. Tana tsoron kar ace mutuwa za tayi.

Haka likitocin suka kore kowa, suka tsaya akanta, har Allah ya basu nasarar dai-daita numfashin ta, sannan suka fito, aka kaita d'akinta dan Malam yace a kaita wani shashin inda babu hayaniyar mutane.

Turata aminity aka yi, Yaron kuma Umma take kula dashi, sai da aka kwana aka wuni, sannan Anum ta farka. Shafa cikinta tayi taji shi a dinke, a hankali ta kuma buɗe idanunta. Umma da yayunta, ta gani suna mata Sannun.

Lumshe idanun ta kuma yi, sannan ta sake buɗe shi akan Maude da yake rike da Jaririn, murmushin ban mamaki ne ya kwace mata, tana me kara ware idanunta akan shi, shima murmushi yaƙe, dan ji yaƙe kamar yace yau a daura musu aure, yaje yayi jinyarta tare da kyautar da Allah ya bata, wani irin farin ciki yake zunzurutun kaunar Uwar da Ɗan.

Ta kowa yayi har kusa da ita, ya d'an sunkuyar mata da Yaron, yana murmushi. D'aga mata gira, itama ta mai da mishi tare da nuna mishi su Umma da idanunta. Tab'e baki yayi sannan ya d'aga kafad'a alamar shi bai gansu ba.

Tari ne ya zo mata, tayi maza zata rike cikin ta, Umma ta rike hannun.
"Ku nimo mana likita, ai dinkin zai warware."

"Zai bari haka yake ai." Inji wata nurse da tazo kansu,

"Taya zaki ce haka? Bayan kina ganin halin da take ciki!" Ya faɗa kamar zai mata duka.
Duk ita a tunaninta matar shi ce, dan haka tace mishi.
"Kayi hakuri dinkin matar ka bazai warware ba, wannan tarin yana cikin aikin yayi kyau ne, kuma ai idan ka lura tab'a cikinta aka yi fa, dan haka karka damu zai bari. Idan zata yi tarin tayi tayi a hankali."

Ce mishi da tayi matar shi, jin yayi kamar zai sume, zunzurutun farin ciki. Washe fararren hakoran shi yayi.
"Abban Baby! Kwantar da hankalin ka, Ummin Baby zata samu lafiya."

Juyawa yayi ya kalli Anum, b'ata rai tayi tare da dauke kanta, Allah sarki kamar sauna haka ya shiga hankalin shi, yana kallonta. Duk sai ya basu tausayi.

Haka suka shiga kulawa da ita, ranar da ta cika kwana uku. Maman Aminu tazo, ta samu Umma tana kokarin a bawa Babyn nono.
"Kin gayawa Mudi? Naga yau kwanan ku uku?"

Bata kula ta ba, mai da hankali tayi gurin bawa nonon tana narkewa Umma.
"Umma na!"
Ta kira sunan tana kallon Maman Aminu,
"Sunan Yarona Isma'il, idan Malam yazo yai mishi huduba da haka,"
Make goshinta tayi, tana fadin.

"Allah ya shirya min ke! Maman Aminu, ki gaya mishi babu wanda yake da number shi."

Daga haka suka ci-gaba da hidimar su, shigowar Maude da laida, sai kayan tea duk da Malam ya sayo mata, amma bai hana shi kawo babban gwangwanin madara da Ovaltine ba, sugar me iyali. Sai nutella, ya ajiye.
"Abban Isma'il, wallahi ka bar asibitin nan, kafin na mike naci Uban wata mace."
Fita Umma tayi tare da cewa.
"Idan kika warware dinkin naki, sai ki nemi me zama dake."

Tura baki tayi, tana hararar shi. Tsaki Maman Aminu tayi sannan ya fita. Tasowa yayi ya zauna a kujera, tagumi yayi sannan yace mata.
"Ranki shi dad'e, kayi hakuri. Wallahi babu abinda ya haɗa ni da wata mace. A amshi tubana."

Dauke kai tayi kamar ba zata yi magana ba. Ganin yadda take kokarin cire nonon a bakin yaron shi kuma yana faffutikar ganin ya rike nonon, ya sashi cewa.
"Don Allah bar shi ya sha!"
"Babu ruwanka dani"
"Idan akwai abinda ya fi ruwan dani acikin kuma zan shanye shi tass"
Ya faɗa yana kashe mata ido, rufe bakinta tayi tana cewa.
"Ka shiga uku, kai kan fita ka bani guri. Zan gyara rigana!"
"Oho dai! Yarinya duk boye boyenki wata rana, muna manne da juna sai naga kwal uwar daka!"

"Abban Isma'il, tsoro kake bani Wallahi, don Allah fita umma ta samu ta shigo min," ta faɗa tana ware idanunta.

Tab'e baki yayi sannan yace mata.
"Ba mamaki, ina cikin dangin dodanni, shi yasa zan cinye ki. Yarinyar ni ba haka nake ba, ko mace aka ajiye min gayarta kamar sabon tuwo dauke kaina zanyi.

Ni halittar mace baya birkita min lissafi, ko lokacin da naje yak.."
Shiru yayi sakamakon subul da bakan da yake son yi.
Dariya ya bata, tana yi yana kallon shi.
"Wato lokacin da kaje me?"
"Eh toh gaskiya lokacin da naje Laberiya cirani."
"Hala kaga mata zuka zuka!"
"Ai ba hala bane, domin na tab'a zuwa Somalia, matan su larabawa ne, kyakyawa irinki."

Dauke kanta tayi tana murmushi jin dad'i, shigowar Nurse yasa ta tsuke fuskar ta.
"Kije idan ya tafi sai ki dawo!"
Ta faɗa tare da tsare gida, zai magana ta d'aga mishi hannu, dole nurse din nan ta fita, dan tana lura da Anum ba mutunci bane ya wadacce ta.
"Allah da kayi magana da kaga rigima."
Daukar yaron yayi tare da sumbatar goshinsa, sanan ya kuma sumbatar kumatun shi, yace.
"D'aya naka, daya na Umminka!"

"Ai na tsani sumbatar nan, shi yasa wancan tsohon banzan ban.tab'a yarda ya sumba..."
"Mhh-hmm! Wannan tsakanin ku ne, babu ruwan me shayi!"
Daukar ledar ruwa tayi wanda Umma yasha ta rage ya watsa mishi.

Ajiye yaron yayi yana cizon lebban shi na kasa, tare da sake murmushin jin dadi, ya shafa yalwataccen sumar kanshi, wanda yake kwance, asalin ta buzayen ce. Maude kamar mace yake yana son gyara gashin kanshi.

"Wata rana zamu kasance abu ɗaya! Zamu zama inuwa d'aya, anan ne zamu tabbatar da Abu daya muke so, ba kome bane sai kanmu, a ranar zan watsa miki ruwa cikin so da kauna, zaki kuma kare fuskarki cikin farin ciki da shagala, a lokacin ne kaunar mu zata tabbatar gaskiya ce."
D'aga kai tayi tana hango yadda suke wasan agwagi da ruwa, tare da dariya da farin ciki, tana kare fuskar ta, yana watsa mata ruwan. Sai kokarin take ta boye fuskarta.
"Malama don Allah dawo daga duniyar mafarki, Allah ya nufe ki da shirya."

Jan matashin kanta tai tare da buga mishi tana dariya.
"Wallahi ka cuce ni, duk bayanin da kayi min, duk na ganshi a zahiri."
"Toh ai kuwa kina da aiki, domin mafarkan mu,.ba zasu kare ba Anum sai ranar da muka tabbata a tare! Daga nan duk bayan shekara daya sai."

Shiru yayi, lokaci guda ya sauya fuskar shi, bai yi niyyar tafiya ba, haka ya sallame ta.

Tunda yayiwa Umma sallama, tare da Maman Aminu, yake zancen zuci.
IDAN NA FAHIMTA NINE BANA HAIHUWA! TUNDA GASHI NAN YA AURI HAJJO BATA TAB'A KO B'ATAR WATA BA! INNALILLAHI WA'INNA ILAIHI RAJIOUN UBANGIJI NAGODE MAKA DA JARABTA NA DA KAKE YA ALLAH KA BANI IKON CINYEWA
Da wannan tunanin ya isa shagon shi, cikin damuwa ya kalli Ila.
Anya ila bani ne bana haihuwa ba kuwa?"
"Kai haba, nafi dauka a kan lokaci ne bai yi ba, sai kaga idan yazo kamar habo."

"Amma baka ga har yanzu Hajjo babu labari ba?" Shiru ila yayi, sannan ya sauke kanshi kasa, kafin yace.
"Nafi zargin cewa lokacin ne da saura, karka yiwa Ubangiji butulci, kasan dalilin da ya baka aron numfashi a karo na biyu bayan an saka duk wanda ya ganka ya harbeka ka? Yana da dalilin shi na sake baka damar ka cimma wata rayuwar shi yasa har kake raye sai kace mishi Alhamdulillahi."

Kuma sai jikin shi yayi masifar sanyi, domin Ila bai barshi haka ba, Cigaba yayi da mishi nasiha ta hanyar nuna mishi yadda rayuwa ta juya mishi baya, lokaci guda ya koma me shayi, dan haka kar ya ce zai d'aga hankalin shi akan haihuwa.

Jikin shi yayi mugun sanyi, fiye da baya, dan haka yayi ta astigifari, yana niman yafiyar Ubangiji.

**Kwanan su Anum shida aka sallame ta, tare da dan ta, da lafiyar shi lau, sai da aka sallame su sannan Alhaji Mudi ya samu labarin haihuwar ta bakin XOXO wacce suka dinke kamar da baya can.

Ya kwaso kayan shirmen shi ya kawo amma Anum taki amsa, yaron ma Sai da aka mishi Addu'a sannan aka kai mishi zaure, gashi yaron ya dauko kalar fatar uwar shi, jajjur dashi har gashin gaban goshin Anum, haka yaron ya dauka. Haka ya gama santin yaron, sannan ya bada aka mai da mata D'anta da bera dubu goma, tsigai ta fito zata bala'i. Maman Aminu ta tare ta da nata bala'in dole ta koma, tayi ta kuka, ita kar Alhaji ya cinye mata yaro tunda duk cikin sa take samu shine sanadin su.

Daukar yaron Umma tayi ta mishi Addu'a, sannan ta mai da mata D'anta. Ai dan ráshin yarda sai da ta saka Rulwanu a gaba da tijara, ya kaiwa Maude dan ya duba mata shi.
"Kan Uba! Ni sa'anki ne? Wato na baki jini na kuma ba zama boyi boyinki, ga katon dan iska."

"Babba ma kuwa da kahonka." Cikin masifa ya fara bala'i.
"Idan na yarda Dan iska nake, yarinya dawo min da jini na, na fasa kyautar, wallahi zaki dawo min da jini na, ai na gaya musu da zaran kika min rashin mutunci zaki biya ni jini na."
Itama cikin jin haushin yaki kai mata yaron ta shiga mishi tijara,
"Dalla matsa wani banzan jininka mara kyau, da nasan jininka za a saka min na rantse da nace su bar ni da cikina yar yau, dube shi zololo dashi kamar bishiyar rimi."

"Umma kina jin ta ko?"
"Ai ta jima da jina bata da lokacin ka malam ficce mana a dakin mu ko na maka ihun Barawo."

Aikuwa ya bude murya yana masifa kamar zai daki Anum, Umma kuwa taki magana, domin daga Rulwanu har Anum sun gama bata haushi, matukar tayi magana toh ba makawa, zata iya binsu da Muciyar tuwo.

!Dariya suke tare da cewa.
"Yanzun Aunty Anum, har yanzun kuma kuna irin wannan abun?" Dariya nayi tare da dauke kaina. Nace musu.
"Ai sabida na dauke mishi Ummar shi ce yasa yake kishi dani, so muna kaunar junan mu, amma fadar mu tafi wanzuwa cikin jama'a har umma tasan muna kaunar juna, Rulwanu yayi min halicci ainun, Rulwanu ya min abubuwan da bazan tab'a matan dashi ba, dan haka bana jin zai iya daukar fadar mu a matsayin k'iyayya ce da kishi, a'a kaunar muce haka."

"Aunty Anum!"
"Na'am Badi'ah!"
"Kin koma gidan Abban Isma'il?"

Murmushi nayi sannan na matsa yatsun hannuna,.kafin na cigaba da basu labarin.

Aikuwa haka ya fita yana hayagaga. Sai bayan fitar shi Umma ta shigo itama, dariya suka bata, tare da cewa.
"Keda Rulwanu zaku mannawa mutane hauka, gashi can Maman Aminu tana dariya har da zama sai dariya take tana kumawa"

Itama Anum sai lokacin ta fahimci fadar nasu, kai abin dariya.

Satin su daya aka yi suna, kasancewar sunan Bauchi da yamma ake shiga basu yi wani gayya ba, Ranar sunan Alhaji ya kawo raggo, Maude ma ya saya nashi. Aikuwa Anum tace sai dai a yanka mata Ragon Maude shi take bukata.

Haka kuwa akayi malam ya sayar da Na Alhaji aka sayo wani Ragon dashi, ita dai Anum abin hannun Alhaji ne ba zata amsa ba.

Bayan suna,Umma ta cigaba da kula da mai jego da D'anta, sunyi kyau kamar basu ba. A yanzun hidimar da Maude yake tasa yan gidan suna jin idan Anum bata aure shi ba, su zasu mata dole ta zauna dashi sabida yadda yake hidima dasu ita da D'anta.

A hankali rayuwa take tafiya, cikin hukuncin Allah. Tare da buwayar, domin shine Buwayi gagara misali.

**Bayan wata goma sha bakwai.

Mafi yawancin mutane suna daukar abinda suke so ko suke bukata shi zai tabbata, a'a shi Ubangiji ikon shi yake wanzarwa,. ita zanen ƙaddara a rubuce take tamkar yadda zanen tafin hannun yaƙe, babu wanda zai iya isa inda kaddarar shi bai kai shi ba, haka zalika wani lokacin hakuri da sadaukarwa takan cikawa Muminin kwarai mizanin shi.

Alhaji Hamisu Natsira me shagon gwala-gwalai....
#Mai_Dambu...
[2/12, 10:20 AM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA BIYAR
_Wannan shafin na yan Groups ne musamman grps ɗin da nake cikin su. Fitilar hikayata! Sansanin Mai_Dambu! Zanen Qaddara ta Fans grp, Zanen qaddara ta Novel Group! Zanen Qaddara ta Grp 3! Muamalata Novel Group! Matan Quarts Novel Group! Furucina Grp B, Duniyar Littafin Hausa!Zainab Bawa Novel Group! GOBE NA Comments section!Aisha Muh'd NOVEL GROUP, Aunty Halisso Fans grp Tare da Inda ban ambata ba, Kuna Raina□□□ □ Don Allah karku manta da hayewa katanga 🙏hank You Heart You all...._

Hamisu Natsira...

Wato alamarin Ubangiji, cike yake da mabanbanta ƙaddara, domin sai ka shirya naka tsarin Ubangiji sai ya kawo nashi tsarin, kina da tsari.wancan yana da tsari amma duk tsarin Ubangiji yana sama da na kowa.

!kallon su nayi naga jikin su yayi sanyi, sannan na sunkuyar da kaina na cigaba da cewa.!
Al'amarin aure tankar habo ne, duk yadda ka so tsayar da jinin da ya hudo daga ƙwaƙwalwar ka ba zai tsayu ba. I zuwa yanzun na fahimci dalilin da Ubangiji ya nisanta mu, ya kuma tabbatar da ikon shi bayan faffutikar ganin mun zama tsintsiya madauri ka daya.

A iya yau gare ni, gobe ga wani na ne, karka sake damar moran lokacin ka ta wuce maka baka ribanci abinda ya dace ba, iya yau kawai zaka riskar.
(Wayyo Allah na! Wallahi hannuna ya fara ciwo fa□☺ bari mu gani ko zan kai labari)

Nayi rashin Abubawan da yawa, kuma nai laifi da kaina,.wanda na sani har abada ba zai yafe min ba, amma ita ƙaddara idan tazo maka babu makawa sai an isar dashi gare ka."

....
Wanke take sabida kayan Isma'il da take tarawa, d'azun suka gama raba hali da Rulwanu, ba kome ya janyo haka ba, sai dan ta yayye Isma'il, yaron yana ta kuka har da ajiyar zuciya, shine ya kawo mata shi.

"Dan Iskanci kin san ba zaki iya kula dshi har ya girma ba, kika yaye shi. Toh wallahi ki bashi abincin shi ko muyi rigima dake."

"Ina ga kamar akwai nono a kirjinka? Tunda a kwai sai ka bashi ka huta da jin haushin abinda na mishi" ta faɗa tana dariya.
"Maman Aminu, kina jin abinda yake gaya min ko?" Ya Fada kamar zai saka kuka,

"Ke Anum bana son rashin hankali, ki dauki yaron nan ki bashi abincin shi." Ta faɗa mata a hasale,

"Ba zata bashi wani nono ba, kawai ya hada mishi kunun shi ta zuba a fidar shi ta bashi ya sha, wannan me kama da zabiyar. Kwana yake yana tsotson nono"
Inji Umma, garin ta mike kawai wata zare ta rike mata zoben gwal ɗinta. Aikuwa ya karye.

"Innalillahi wa'inna ilaihi rajioun, Umma zobena ya karye." Ta faɗa da ƙarfi,
Cire zoben tayi kamar zata fashe da kuka.
"Toh ai sai ki shirya ki kai central yanzun."

Umma ta rike tare da juya.
"Ina da kudi kawai na sayar musu na sayo wani."
Dan gwara mata goshi Rulwanu yayi tare da cewa.
"Ba zaki gyara ba?"
"Ai ba naka bane, balle kace sai na gyara maka, Umma kice ya fita harkata."

"Wai Rulwanu, hanjin juna kuke gani ne kai da Anum?" Inji Malam yana shigowa,

"Wallahi kuwa malam sai kace wuta da auduga." Inji Umma,
"Amma ai Anum bata da gaskiya." Inji Maman Aminu,

Anum bata kuma bin takan su ba, ta shiga wanke kayan da sauri ta dauraye, sannan ta shiga ban daki tayi wanka, tana fitowa ta shafa mai me gurguwa, sannan ta shirya cikin riga da zani na atamfar bakar mace.

Tayi kyau sosai musamman da ta daura farin hijab da Nikkab akai, sanan ta dauki Isma'il, ta rungume shi zasu fita.
"Ummana Maman Aminu, Malam dina, bari na shiga Central market yanzun zan dawo." Ta ce musu.
"Toh Ubangiji ya dawo dake lafiya,ya kuma tsare hanya."
Juyawa tayi tana murmushi, sannan ta fita daga gidan.

Tana fita, ta tsaya a gaban shagon Maude, wanda yake ta lissafin shi.
"Takuttuta tiya!" Da sauri ya d'ago kanshi yana dariya, sannan yace mishi.
"Haba da gaske!" Aikuwa Yaron ya kuma lallaiyayo mishi wata gwarancin ya makawa maude. Shi kuma da taya bera barna yace.
"Don Allah? Umminka naji labarin mugun aikin da tayi maka."
"Ke shige zaure, ki gaya min waye ya baki shawaran yaye min yaro daga jikin dadin da yaƙe?"

Dariya tayi sannan ta ajiye mishi yaron, tace mishi.
"Zan je Central market na dawo, idan na dawo sai na baka amsa dai dai da tambayar ka."

"Lallai kin ci Amanar yarda da muka baki,sai kin dawo amma ki tafi da yaron kar wani ya ganki ya dauka budurwa ce." Ya faɗa alamar babu wasa a maganar shi.

Kuma ta fahimci abinda yake nufi, dan haka ta amsa, fitowa yayi tare da tsayawa a gabanta.
"Karki damu, idan aka ganki babu wanda zai dauka budurwa ce, Ina Kaunar ki ne. Shi yasa bana iya sarrafa kishina"

Gyada mishi kai tayi sannan tace mishi.
"Toh bari naje na dawo."
Shi ya tsare mata keke napep, suka shiga ya kuma biya kudin kai su.

Jikin shi yayi sanyi, musamman yadda yake ganin wannan karon ya Sami Anum Insha Allah, ya sashi kuma samun kwarin gwiwa..ya nufi gurin aikin shi. Mutane na mishi tsiya, murmushi yayi sannan yace musu.
"Anum ta sauya fa, ba wacce kuka sani bace."

---- Lokacin da ta isa kasuwar, shagon mijin Aunty Binta ta fara zuwa ta ajiye Yaron kasancewar akwai yaran Anunty Binta Babaji da kuma Bababa, sai Muddamsir. Da Muh'd Takwaran Malam, Shukrah itace babban su. Sai yar autar su me suna Farha.

Yana ganin su ya kama d'aga musu hannu, aikuwa ta zauna tana cewa.
"Angona! Ya naga sai hada kumatai kake? Gaskiya Aunty Binta ta iya riko"
Dariya ya saka mata, suka gaisa sannan yace mata.
"Karki damu, sai ayi musaya dan naga zaki fi dacewa dani!"

"Tabdijam! Yasin bana wannan wasan da kai." Tun tana yarinya yake cewa, a sauya ta Aunty Binta.

Dariya yayi ta mata sannan ya tambaye ta, me ya kawo ta kasuwa, anan ta ciro zoben gwal dinta ta nuna mishi. Kallon Babaji yayi sannan yace mishi.
"Zoka kai ta Shagon Hamisu Natsira!"
"Toh Abba"
Babu musu ya shiga gaba zata tafi da Isma'il yaki dole ta barshi a shagon, tabi bayan babaji.

Basu yi wani tafiya me nisa ba, suka isa shagon, nan babaji ya nuna mata shagon wanda yake dankare da gwala-gwalai, ga cctv yana juya ko ina, abinda ya kawo tayi, yana can kuryan shagon, yana bin duk wani shiga da fitar mutane ta tv, d'aga nikkab din tayi, tare da cewa.
"Barka dai, na kawo zobe na ne, ina son naji nawa gyaran shi, idan ba zai gyaru ba nawa za a sake min wani,"

Yadda take maganar da yadda idanunta suke kiftawa, ya sanya mishi wani irin yanayi, wanda rabon shi da yaji tun shekarun bayan, haduwar shi da matar shi.uwar yaran shi.

Kura mata ido yayi, ta tafi da Zuciyar shi, dan haka da kanshi ya taso. Ya tsaya suka fara ciniki, karshe ya duba zoben yace mata.
"Ranki shi dad'e,me zai hana a baki wani irin shi amma wannan ai ta karye ta wuya tane, kuma ai ba girmanki bane amsar joni joni,"
Sam bata kawo akan da wata manufa yake maganar ba, dan haka tayi murmushi tace mishi.
"Babu damuwa, muga wasun!"
Haka ya ciro mata wasu masu kyau.

Ta zab'i wani me kyau sannan tace mishi.

"Nawa zaku sayi wannan ɗin?"
Murmushi yayi sannan ya zuba mata ido, kafin yace.
"Kamar yadda me shi take da tsada!"
Ware idanu tayi akan shi, sanan tace mishi.
"Toh don Allah kayi magana ina sauri ne na bar Yarona a shagon Alhaji Ahmed Bababa!"
"Ai ke yar uwan matar shi ce ko? Sai yanzu naga kamar ku da Maman su Bababa, toh ba damuwa, dan haka zan saya."

Nan suka tsayar da cinikin itama ta biya wanda ta dauka.
"Baki ce min kome ba?"
"Eh toh ni matar aure ce"
Ta bashi amsa, zata juya.
"Sam maganarki ba haka bane,baki yi kama da matar aure ba, zan yarda idan kika ce min ke bazawara ce, amma hankalina ba zai dauka ba da kice min me matar aure ce."

Shiru tayi sannan ta juya ta fita abinta, dan tasan zai iya biyota.
Tana isa shagon ta samu sun sayawa Isma'il doya da kwai, an saka mishi a gaba da namar kaza.
"Ni tafiya zan dan ba zan jira ka ba!"
"Toh guguwa! Ko nace ruwa ba, ki nad'e mishi a cikin laida sai ku tafi." Yadda take sauri sauri yasa shi cewa.
"Khadijah!"
A firgice ta juya tana kallon shi.
"Wani abu ne?"
"A'a yallabai, guduna take. Ashe sunan ta Khadijah. Taki ta gaya min sunanta"

"Anum baki gaya mishi sunan ki ba!" Inji Mijin Aunty Binta,
"Sai anjimar ku!"
Ta dauki danta suka bar kasuwar kirjinta yana bugawa da sauri da sauri.
"Alhaji! Kanwar matar ce?"
"Eh autar su Binta ce."

"Don Allah kayi min jagora mana zuwa ga sirikinka" Inji Alhaji Hamisu Natsira,

"Gaskiya ba zan boye maka ba, Kwai wanda aka hada ta dashi mijinta na farko, kuma yanzun ina ganin zata koma gurin shine." Ya faɗa.
"Amma an yanke rana ne?" Ya tambaya.
"A'a ba a yanke ba, amma kuma."
"Don Allah ka taimaka min mu jaraba, sai an gwada akan san na kwarai."

Haka yayi ta rokon mijin Aunty Binta, har ya shawo kanshi. Suka ajiye maganar tunda gobe Juma'a sai su je su gwada sa'ar su.

"Alhamdulillahi!" Ta furta lokacin da ta iso gida, murmushi suka sakewa juna, sannan ta tsaya a window shagon ta nuna mishi zoben, nan suka tab'a hira, sannan ta shige cikin gidan.

Hafsat ta samu, gaisawa suka yi sama sama,har zata wuce tace mata.
"Har yanzun baki sami abin wuyana bane, ko mutuwa nayi ina da wanda zai ci min gado, gaskiya a nimo min abuna, ko na kai karanki gurin Malam"

"Karki min rashin kunya, akan wasu kayan banzan ki can,kuma ba zan biya ba." Ta faɗa a gadarance.
"Wallahi zaki biya, tunda babu guminki a cikin shi. Sai kin biya ni kayana."

"Ba zan biya ba, ƙaruwar banza ƙaruwar wofi, wacce tayi cikin shege." Ta faɗa tare da dariya tana kallon Anum wacce jikinta yayi mugun sanyi.
Kowa a gidan sai da yayi bakin ciki da abinda ta faɗa.
"Naji Ni karuwa ce, amma a biya karuwa kayanta, idan ba haka ba , wallahi na rantse da wanda rayuwata da mutuwata take hanun shi, sai na nuna miki karuwanci a garin nan, ba Ni kika kira karuwa ba? Zaki ga.."

"Ya isa! Bani Bin wuyarta, dan shine a jikinki?"
Shiru tayi tana kallon Anum, sannan ta mike ta cire kome, sannan ta mika mata.
"Insha Allah, yadda kika amshi she kin amshi bakin ciki har karshen rayuwarki, mu zuba ni dake."

Shigewa daki Anum tayi, Umma ta juya ga Hafsat.
"Kika ce zata ga bakin ciki har karshen rayuwar ta? Toh shi kenan, ke ki zauna kiga farin cikin da zai hanaki Fahimtar bakin ciki. Hafsat ba dai ANUM ta tsone miki idanu bane? Hafsat ba dai ANUM ta tare miki soyayyar da kika rasa bane, Hafsah Allah ya baki sa'a , Ni kuma zan tsaya tsayin daka, na cigaba da nima mata kariyar Ubangiji. Allah ya baki sa'a!"

"Wannan ai shirmen su ne, kuma nasan Hafsat ba zata cutar da yar uwarta ba, dan haka ki kwantar da hankalinki Umman Anum." Inji Maman Aminu, sannan ta juya tayi ta fadawa Hafsat, tana nuna mata illar furucin da tayi, idan wani abu ya sami Anum kar tayi tunanin dan ita ta haife su,ba kyaleta za ayi ba.

Shigar Anum daki,saka yaron tayi a gaba tana kuka.
"Kaga abinda kwaɗayi na yaja min ko? Kaga abinda Baban ka ya ja min ko? Gashi nan ya b'ata min suna ya kuma lalata min rayuwa ta, Allah sai ya bi min hakkina."

Ta faɗa tana kuka, shima Yaron matsowa yayi jikinta tare da sake ajiyar zuciya, dan kuka yake son taya Maman shi..

Fushi Hafsat tayi tare da barin gidan, tana me rantsuwa sai ta yi abinda ta saka kanta. Bayan tafiyar ta Maman Aminu ta shiga dakin Umma domin yiwa Anum fada, ta same ta tana kuka.
Dan haka ta fita daga dakin.

Tana jin ciwon abinda ya kuma faru, dan haka ta hakura da yiwa Anum faɗa, tunda ko tayi ma, ai na rashin gaskiya ne, tunda akan...
*Ana barin halal dan kunya....
Yasin 46 na kasa, kuyi comments na sake muku shi bayan sallar juma'a □□□
#Mai_Dambu
[2/12, 2:53 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA SHIDA

*_□ Toh ba zance kome ba! Zan cigaba da zama a saman katanga □_

FATAN ALKHAIRI AUNTY SA'AH tare da YAR UWATA RABI'AH □□□

Gaskiyar tane, dan haka ta kyale Anum ɗin. Umma ce da ta shiga dakin tayi ta mata nasiha, har tayi shiru.

Washi gari Jumma'a.
Ina zaune aka kawo min kayan Isma'il, sunyi min kyau musamman yadin da Maude ya saka yau, wanda irin shi ya umarci Rulwanu da ya ce mata ta sakawa yaron. Da karamin hular shi daidai kan shi.

Haka ta shirya yaron suka tafi masalaci har da Malam. Bayan sun idar da sallah ne, suka dauko hanyar dawowa malam yana gaba Maude yana baya.

Dan haka koda suka iso kofar gidan, sun sami Mijin Aunty Binta da Alhaji Hamisu tare da wasu dattawa har su uku, na cikin kasuwar Central market.. Nan suka gaisa harda maude shi kuma ya wuce da yaron shi shago.

Bayan sun shiga cikin zauren gidan ya dauko musu taburma, nan suka zauna aka kuma gaisawa, sannan suka gabatar da abinda ya kawo su. Tare da nunawa malam sabida mutuncin da kimar gidan..yadda suka nuna girmamawa tare da mutuntawa,.yasa jikin Maude yayi masifar sanyi, dan haka yaji a ranshi indai mijin Aunty Binta, yazo sabida darajar malam da Binta tare da girmama surukinsa.
Bai ga amfanin ya so kan shi da yawa ba, ai ko babu kome. Malam ya zame mishi uba. Amma da ya tuna yadda Anum take son shi, take ya share batun ya ji a ranshi Anum tashi ce.

....
"Eh toh gaskiya nagode da mutuntawa, amma na tsayar mata da miji, wannan me shagon shayin, Insha Allah nan da sati shida zan bashi ita." Ya faɗa cikin tsayawa akan ra'ayin shi.

Nan suka yi shiru, tabbas malam ya burge dattawan nan, musamman yadda ya gaya musu, ai ya badda yar shi ga bakon haure. Dan haka suka yi godiya ya basu hakuri ba a kawo musu ruwa ba, suka ce.
"Babu kome wallahi."

Koda suka fito, kallon shagon Maude suka yi, dake yasan mijin Aunty Binta, fitowa yayi suka gaisa cikin mutunta juna.
"A gaida min Hajiyar mu"
"Taji!"
Cikin mugun kishi Alhaji Hamisu, yace mishi.
"Anya zaka iya rike Khadijah da shagon shayin nan kuwa?"
"Me zai hana! Ai ki dako nayi na rike dijangala tame gari! Ba auren talaka ba,.talaka noma da sassabe."

"Ka tsaya iya matsayin ka, ita matar Manyan mutane ce, ba talaka irin ka ba, wanda fatara da talauci ya sashi niman inda , zai tsira da yan hanjin shi." Inji Hamisu.
Murmushi yayi sannan ya juya zai tafi,ya kuma gayawa. Maude.
"Sana'ar shayi takai maka tunda har ka iya saka turaren dubu dari uku."

Bai kula shi ba, dan ya fahimci shine yazo niman Auren Anum, ya rasa shine zai mishi rashin mutunci. Dariya yayiwa Hamisu, ai kuwa ya fusata ainun. yayi ta zage zage.

Haka suka bar wajen sauran mutanen na bashi hakuri, Mijin Aunty Binta shima ranshi ya b'aci tare da nuna mishi illar abinda ya aikata..
** Lokacin da malam ya shiga cikin gidan, yake labartawa Umma labarin. Zani a hannun har tana tuntube zata zube tacewa Malam.
"Yanzun sabida rashin adalci, miji na gari yazo ka kore shi ka hadata da alfakara'u alala lalurati, wallahi ba zai sabu ba! Indai ince na haifi Anum ba zan tab'a lamunta ba!"

Haka tayi ta maganar ta, daga Malam har Umma zuba mata ido suka yi har ta gama, sannan ta koma dakin ta, ai tunda taji labarin hankalin ta ya tashi dakyar take haɗa kominta.

"Malam Ni kam da ka daura auren ne, domin akwai yan bakin ciki da basu son ganin Allah yayi kome, dan haka Ni yau Jumma'a a daura auren dan kar na rasa Maude.".

Rulwanu da ya shigo yana shan zobo, yaji rashin kunyar da Anum take, sai da ya kware. Yana zare idanu zobo har ta hanci ya kalli Malam da Umma yace.
"Na shiga uku na lalace, don Allah Malam ku daura mata auren kafin mu wayi gari muji labarin ta tare a gidan Oga Maude. Ke kam inda kunya yabi kunyi hannun riga da shegen idanu kamar na budurwan tsaka."

"Umma kinga irin su ko? Ai kome girman munafuki Allah sai yayi yadda yaso." Inji Anum.
"Umma ki gaya mata ta bar kirana munafiki!"
"Sunan da ya dace da kai kenan." Inji Umma,

Haka akayi ta raha Maman Aminu tana can tana tufka da warwara.

Wayyo Allah na, tunda Malam ya shaidawa Maude maganar shi da Anum, ya shiga hidima ai kuwa suka kama rikici da Hajjo, sosai suka rikice shi yace auren Anum babu fashi, ita kuma ta nace ta kafe ba zai auri Anum ba.

Bai bi takanta ba, dan yana ganin ita ba kishi take ba, shirme take yi.

A hankali lokacin yake kuma zuwa, tare da shirya kome, kayan aurenta na gidan Alhaji sayar dasu tayi, ta kuma cika kudi ta sayi sabo a bakin kura dan akwai masu kayan furnitures, sai kayan kitchen da ta kuma kara wasu.

A wannan lokacin Maman Aminu tayi kokarinta amma Abine bata kamu ba, dan ta dage da Addu'a da Ibada, sai Allah ya kare mata imaninta. Kuma babu wani abinda ya tab'a lafiyar ta.

Dan haka ta bude mata wuta, itama kuma Anum ta birkice mata. Inda take cewa.
"Wallahi aka hana Ni abinda nake so, idan ba sai na yanke jijjiyar hannuna ba, ko kuma na shiga duniya yawon karuwanci dama ai ana goranta min, kuma na kwaso abin kunya da cutar zamani na mutu a dakin mutum.

Haka kuma zai yi jinya ta, shima kuma ya dauka nace Umma da Malam su gudu dan ba zan saka musu ba."

Yadda tayi maganar zaka matukar sha mamaki,(😁domin babu wasa a cikin al'amarin Allah ya takaita malam baya gida, Umma ma ta fita islamiyya. Aikuwa ta rufe kofar gidan, zata daki Anum ta dauki D'anta ta rike. Tana kallon Mamanta.

"Me yasa kika daura buri a kaina? Me yasa ba zaki gane abinda Zuciyata ke so ba? Don Ki barni na auri Maude, shi kawai nake bukata a rayuwata, don Allah ki barni na zauna da shi duk sauran Yaranki suna farin ciki me yasa Ni ba zanyi ba?"

Ajiye itaccen tayi sannan tace mata.
"Ba hanaki farin ciki nake ba, Anum Allah yayi miki nasibi, don Allah karki sake damarki!"

"Wani dama wani dama kike ganin ba zan sake shi ba? Maude shine dama ta! Wallahi ba zan iya rayuwa da wani namiji idan ba shi ba, don Allah ki barni na rayu dashi!"

Duk ta inda ta bullo Anum zata toshe.karshr dai haka Maman Aminu tayi tsirara a gaban Anum, gwiwar dukka biyu a kasa, juya mata baya Anum tayi tare da fashewa da kuka.
"Idan har haka na haife ki, ki janye aurenki da Maude ga Hamisu nan, idan kuma son ranki kike so, Insha Allah sai kin wulakanta sama da yadda na wulakanta kaina a gabanki!"

Girgiza kai tayi sannan tace.
"Har abada ba zan kuma miki Biyayyar da zan rayu cikin kunci da bakin ciki ba, Maude nake so? Shine muradina, shine farin cikina. Ruwanki ne ki so shi ruwanki ne ki kishi. Amma Tabbas saura kwanaki ƙalilan mu kasance a duniya daya!"

Wani irin kuka Maman Aminu take yi, haka Itama kanta Anum kukan take yi, bata jin zata iya kyale Maman Aminu ta Cigaba da wulakanta mata farin cikin ta, dan haka, ta shiga tuno yadda Alhaji yake saduwa da ita, cikin kazamta, tare da mata sanadin rashin yaranta har biyu.

Kuma duk sanadin dogon buri, haka bawan Allah nan yaso haukata mata rayuwa, duk mahaifiyarta bata gani ba. Kuka take tun daga tsaye har ta durkusa kasa, rungume da Yaronta.
"Me yasa kika zab'i son ranki sama dani? Sauran Yaranki ba haka kika lalata musu nasu rayuwar ba, amma ni kin mai dani hajarki, Ni ba zan auri abinda kike bukata ba, koda kuwa shi kuɗi ne da kanshi.Allah ya bani miji na gari ban san meye Matsalarki da kika tsani maude, Ni ya dace ki tsana na har abada, don Allah ki cire ni daga cikin Yaranki, ki barni da Umma. Idan kuma ba ke ce kika haife ni ba ki gaya min, na nono uwar da ta haife ni!"

Wannan maganar yayiwa Maman Aminu zafi, dan haka ta fincike Yaron hannun Anum ta wurgar dashi, ta rufeta da duka da wani itaccen marke, sam dukar bawai bai shigeta bane, D'anta kawai da ya kwalo da kofar dakin Umma yasata rarrafawa ta dauki yaron tana kuka.
"Ina zaki san darajar shi? Ina zaki zafin shi, Uwar da ta amsa sunan Uwa kare D'anta take daga jin ƙishirwa, dan haka Dake ni Maman Aminu, ki dake ni ki cire haushin ki, bakin cikinki ne zaki fanshe domin ba zan miki yadda kike so ba, dan haka dake ni ki cire damuwarki" tana kuka tana gaya mata duk abinda ya fito bakinta, tare da kafewa da gaya mata.
"Auren maude babu fashi ko kina so ki baki so! Zaki ganni dauke da gidan jinin me shayi."

Haka ta wurga da itaccen ta fincike Yaron a karo na biyu ta rike dan ta, goshinta yana zubda jini.

"Ki sake min Yarona, lokacin da Ubanshi yasa a kashe ni dashi baki kawo min dauki ba, lokacin da yake zubda min cikina baki kare ni ba, kin saka kwaɗayi da son zuciya akai na, toh wallahi kinji sai dai gidan MAUDE."

Ta faɗa tana kallon Maman Aminu, wanda idanunta yake zubda kwalla.
"Ni kike gayawa magana Khadijah? Insha Allah kare sai yafiki daraja, wallahi sai kinyi yawo tsirara, sai kinyi hauka tuburan Insha Allah sai Kinga mugun karshe. Ni kika zabi wulakantawa saboda namiji"

Daukar yaron ta tayi ta shige daki dashi, tana kuka.
"Kamar yadda kika gaya min magana, Insha Allah dan da kika haifa sai ya dake ki, sai yaja ki kamar kare zuwa kofar gida yana tozarta ki. Wannan yaron hannun sai ya miki abinda kika min sama dashi. Kai Khadijah Allah ya isa tsakanina da ke, ban yafe miki Haihuwar ki nayi ba!"

(Addah Ramlat! Ki isar da labarina duniya ta Fahimci halin da iyaye suke cilla yaran su cikin shi! Addah Bakin Uwa masifa ce! Addah Ramlat baki ce kome ba, kuma kina kallon sakona! Please said somethings!)

(Tun da nake rubutun labarin hausa ban tab'a ganin labarin da ya tsaya min a rai ba, dan kusan shekara biyu zuwa uku nake son rubuta zanen ƙaddara ta, samun labarin Anum ya kuma zaburar dani wannan labarin ya tab'a zuciyata)

Haka Maman Aminu ta cigaba da kwashe mata albarka, tare da mugayen alkaba'i, tunda ta shiga dakin Umma take kukan har ta kwanta..tana rungume da Yaronta. Wanda take ji ba zata iya barin shi a hannun Ubanshi ba ita tafi dacewa da rikon danta, dan ba zata rab'a yarda ya tashi a wulakance kamar yadda take gani a gidan Ubanshi.

Koda Umma ta dawo ta tambayeta me ya faru, amma Anum taki magana, sai ma kukan da take yi.
"Toh Allah ya kyauta, ya sa mu dace duniya da lahira."

Haka Maman Aminu ta cigaba da gayawa Yan uwan Anum ta zare hannu akanta, kuma ta tsame albarkan da yake kan Anum, wannan abun yayiwa Hafsat dadi, dan haka take mata dariya da nuna mata ai ita kan ta kad'e har buzunta.

Bata d'aga ido ta kalle su, hidimar bikinta ne a gabanta, wanda ya rage saura kwanaki huɗu.

Kuma kullum suna tare da Maude, ko fasa mata goshin da Maman Aminu tayi sai da ya rikice mata.kuka ne ya zo mata, amma haka ta had'iye. Rike hannun shi tayi sannan tace.
"Don Allah ko na aureka karka juya min baya, Ni kuma zan tsaya na kare aurenka da kimarka.

Ba zan taba barin wani ya tozarta min kai ba, Maude kai ne kawai nake bukata, bayan haka duk inda ka ga ya dace ka kai ni zan zauna da kai."

Rike yatsun hannunta yayi suka yace mata.
"Insha Allah ba zan tozarta kimarki ba, kuma zan zauna dake kar karshen rayuwata Amma....

Hmmm... Inji me ciwon hakori

#Mai_Dambu...
[2/13, 9:44 AM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA BAKWAI.

Hawayen da take kokarin dannewa ne ya fara saukowa, bakinta na rawa tace mishi.
"Amma me? Abban Isma'il. Don Allah karka sanya min shinge a zuciyata, na gama yarda *KAI RABO NA NE*, karka sani jin cewa bani da Sa'a mana, idan ma laifi na maka don Allah ka min hakuri karka sara min baki."

Kalmar KAI RABO NA NE, ya cigaba da yawo a cikin kanshi da kunnen shi, sake hannunta yayi yana kallon yadda take zubda kwalla, cikin wani irin yanayi me dauke da ban tausayi, hannun shi dukka biyu ya saka a fuskarta yana cewa.
"Nima nasan *KE RABO NA NE!* Shi yasa nake faffutikar ganin na same miki a rayuwa ta, amma kuma idan zanen ƙaddarar mu bata so haka ba, zan cigaba da miji fatan Alkhairi, Anum nasan inda rai da rabo wata rana ba zamu yi kuka haka ba."

Daga haka ya juya tare da barin zauren, tsayawa tayi tana kuka me matukar ciwo. Da tashin hankali. Da yau bata bi ta mutane ba da basu kaita sun barota ba.
Duk kukan da take da musayan kalaman da take da maude duk akan kunnen Maman Aminu. Murmushi tayi tana faɗin.
"Yarinya haka zaki yi hakuri tunda Allah ya kawo ki a cikina, ya kuma yanka min ke da araha dole ki auri miji ready made."

Haka ta koma gida, tana tsakar gida, tare da yar wake waken su na Igala, tana yi tana gyada kanta, Ismail ne ya fito yana kallon hanyar waje tare da kiran Maman shi. Amma Maman Aminu bata juya ta kalle shi ba.

"Ummi!"yayi wani gwarancin shi tare da cewa "tiyaaa!"

Amma Maman Aminu bata d'ago kai ba, can ta mike tare da shiga kitchen ɗinta, ta dauki ruwan zafi a butar karfe, ita kanta bata yi haka da wata manufa ba, sai dai kaddara. Tana zuwa ta juye ruwan a bokitin ta koma kitchen. Ganin an.juye ruwan ya taso yana cewa.
"Af.. af.....af!"
Yana kai hannun shi jikin bokitin, sai ya saka dariya ta kuma saka hannun shi ya tab'a bokitin, ko ya aka yi ya kayi kawai yaron nan ya fada da fuskar shi cikin ruwan zafin nan.

Wani irin ihu yayi, tare da hantsilawa, ita Maman Aminu bata Fahimci abinda ya saka yaron ihu ba, amma Anum da ta shigo gidan tana share kwallar ta, ta ga danta yana birgima. Wani irin kuka ne ya kuma zuwa mata ta fara kwalawa Umma kira, tana gyaran murya. Alamar tana sallah.

Da sauri ta isa bakin randa ta saka hannu, tare da d'aga shi yana wani irin nishi..jikin shi yayi jaɟjur, wurga shi cikin randa tayi. Tare da saka hannunta tana juya shi cikin uwa, sai lokacin Maman Aminu ta fito. Ta samu Anum ta ciro yaron, tana girgiza shi.
"Umma don Allah fito zai mutu!"
Ta faɗa cikin wani irin fitar kuka, da sauri Umma ta fito Maman Aminu tana kallon su, Umma ta yaga rigar haka ta zare da fatar jikin yaron,komawa gefe Anum tayi,

tana kallon D'anta. Daukar shi Umma tayi ta ajiye shi sannan ta koma d'akinta ta dauko kudi da wayarta ta fita dashi.

"Ya Allah!"
Ta iya furta kalmar, tana zaune har Rulwanu yazo ya taimaka mata suka bi bayan umma, Maman Aminu bata ce mata Allah ya sawwaka ba.

Haka suka nufi asibitin, bayan sun isa suka nufi inda aka kwantar dashi, a lokacin kowa sai da ya zagi Anum bata iya magana na, sai yake tana murmushi hawaye na zuba mata.

Bayan ta gama abinda zata iya Umma ta bar asibitin, ta dawo gida. Haka yaron nan yake kuka, can itama ta fara kuka. Yan uwanta ne suka zo. Ana ta sami sauki amma dukkan su bata laifi suka yi kamar yadda Maman Aminu tace ta, fita gurin Maude ta bar yaron ya faɗa ruwan zafi.

Karshe haka suka barta a gurin, tana rike da hannun shi Me lafiya, tana share kwalla. Wajen karfe shida taga Umma bata dawo ba, ta kirata. Amma yadda Umma ta bata amsa ya saka Anum rudewa tana tambayarta lafiya.
"A'a babu kome, kawai bana son damuwa ne, ki zauna a jikin yaron Rulwanu zai kawo miki kome."

Da tasamu yayi barci, haka ta fita wajen asibitin, ta zauna tayi kuka iya kukan da bata jin zata kuma yi a rayuwar ta, haka kawai take ji a yanzun babu abinda zai iya sakata zubda kwalla matukar ba me hujja bane. Mahaifiyarta da kowa nata ya wulankata ta, sabida bata da Arziki bata auren me Arziki, bata jin ko duniya aka ajiye mata zata zab'a.

"Ke! Kece Maman Isma'il?" Da sauri ta mike,.garin amsawa nice ta tauna harshenta. Bakinta yayi nauyi, dan haka ta ce mishi.
"Hmm!"
"Toh sai ki barshi kuma? Gashi can ya lalata alluran hannun shi"

Da gudu ta kwasa tare da nufar hanyar ward ɗin, tunda ta shiga Nurse suke balbale ta, duk sai ta rasa ya zata yi, ta fashe musu da kuka..tare da zuwa jikin yaron tana shafa kanshi.

Bayan sun maida mishi alluran suka barta tana kuka, mika mata hanky aka yi ta amsa. Da sauri ta juya, wani katon abu ne ya tsaya mata a wuya, da sauri ta faɗa jikin shi. Tana sauke ajiyar zuciya. Cak ya tsaya kamar Status, ya kasa kome. Zuciyar shi tana wani irin bugawa, hannun shi ya kai kanta, tare da cewa.
"Kiyi hakuri!"

Kukan ne ya tsaya ta d'aga kai tana kallon shi. Kafin ta janye jikinta daga gare shi, tana kuka.
"Sun juya min baya!"
"Allah bai juya miki ba"
"Sunce nice nayi silar fadawan shi ruwan zafi"
"Allah yana tare da masu hakuri."
Duk yadda take son kawo mishi maganar yaki bata damar haka, har zuwa karfe goma. Kallonta yayi sannan yace mata.
"Kin ci Abinci?"
"Sai kana da gata zaka samu!"
"Inji waye yace baki da gata?" Malam ya tambaye ta, sunkuyar da kai tayi tare da mik'ewa ta nufi malam, a hankali ta kai kanta kafadar shi, tana cewa.

"Umma ta guje ni!"
"Ina tare dake!"

Kukan da take yi ne yake tab'a shi, dan haka ya shiga ya fita aka mai dasu daki na musamman, daga nan suka zauna su uku, a jikin yaron, Malam da Maude, ita kuma shiga cikin abincin da malam ya kawo mata, tusawa take amma bata jin dadin shi.

Tana gamawa tayi alola da sallah, sannan ta koma zata takura malam yace ta kwanta a kusa da Yaron, da Malam da Maude suka kwana akan yaron, da zaran ya fara rikici zasu lallaba shi, suna ƙoƙarin tayi barci.

Abinda ya faru kuwa, Maman Aminu. Hada gurmi tayi wanda ya janyo aka yi fada tsakanin Yaran Umma da Yaran ta, karshe ta fidda abinda Umma take mata, yadda ta makale Anum, a jikinta. Tare da kundumawa maude Sharrin da Yaranta suka ce ya bar musu kofar gida, Yaran Umma suka ce basu san da haka ba fada har kofar gida.

Gagarumin rikici aka yi, shine Umma ta ware yaranta da kuma cire Anum a jikinta. Tare da rokawa Anum din mafita A gurin Ubangiji.

--- Asuban Fari suka bar asibitin, bayan sun tashi Anum daga barci. Ya rage saura kwana ɗaya auren su. Dole Maman Aminu tazo asibitin tana murna, kota kanta Anum bata bi ba, ta ficce.

...tana isa gida, ta kwanta ta huta a falon Umma. Sai da Rulwanu yake gaya mata abinda ya faru, tare janye auren ta da MAUDE yayi.

Ihu ta saka tare da fita da gudu tana zuwa tayi wurgi da kayan shayin shi.
"Meye nayi maka? Ka tsaya ka bani amsa meye nayi maka da zaka fasa aurena, sadaukar dani kayi?"

Ta kafe shi da manyan Idanun ta. Bai mata magana ba, ya shiga tattara kayan shi da ta fasa, cikin masifa da zafin rai ta tsallaka gaban shi.
"Ka gaya min meye laifina? Meye nayi maka da zaka cutar dani? Duk dimbun kaunar da mukewa juna da wannan zaka saka min?

Na zata zaka iya rayuwa dani ashe kai naka tunanin."

"Kinga nan gurin sana'a ce, ki shiga cikin gidan zamu yi magana da..."

"Fuck and hell You! Maganar banza" ta faɗa da karfi.
"Wallahi ban tab'a kawowa zaka karya min zuciya ba, Amma Insha ALLAH. Maude na Barka har karshen rayuwata, ba zan maka kuka ba, amma kai sai kayi min kuka, Allah ya bamu rai da lafiya me amfani."

Ta juya tare da barin gurin, tana shiga cikin gida, ta fashe da wani irin kuka, wanda har kofar gida ana jin muryanta. Kuka take tare da zuba gwiwar ta a tsakiyar tsakar gidan, duk da Maman Aminu tana Asibiti. Umma tana jinta haka bai saka ta fito ba, sai da tayi ta koshi sannan ta tattara abinda tazo dauka.

Ta fita, zunzurutun zuciyarta ta karkashe, tun daga bakin kura har babban Asibitin da kafa ta taka, lokacin da ta isa, kallon Maman Aminu tayi cikin wani irin murya me matukar ban tausayi tace mata.
"Tashi ki koma gidan mijinki!"

Kallonta Maman Aminu tayi zata yi magana ta dakatar da ita, sannan tace.
"Bana son na dauki bakin mutane ne, don Allah bar asibitin nan kafin raina da naki ya b'aci."

Tasan Anum kuma tasan zata iya aikata kome, dan haka ta mike tare da ajiye mata 10k.
"Zoki dauki kuɗin ki"
"Baby!" A fusace Anum ta zuba mata jajjayen Idanun ta,
"Karki kuma, kar ki yarda ki kirani baby! Dauki kudinki."

Babu musu ta dauka, sannan ta fita, tana zane a dakin Rulwanu yazo. Dauke kai tayi tana kallon yaronta da yake barci, ajiye mata abinci yayi tare da kallon ta. Kanwar shi wacce suka raba kuruciyar su tare, kullum cikin fada da tsokanar juna suke, ta kowa yayi a hankali, ya rike hannun ta, janye hannunta yayi. A hankali hawaye ya zubo mata.

Zama yayi tare da cewa.
"Maude bai da niyyar rabuwa dake"
Watsa mishi kallon banza tayi, sannan tace mishi.
"Dauki abinda ka kawo ka bar asibitin nan!"

"Anumullah!"
"Rulwanu!"
Ta kira sunan shi da karfi,
"Amma ki Fahimci Maude bai da nufin."
"Idan kanin Ubanka ne sai kaje can ka kare shi!"

Yasan yadda take cikin fushin nan ba lallai bane ta fahimce shi, dan haka suka zauna a dakin yana kallon yadda yake share kwalla, har ya gama zai tafi.

Fuskarta kawai zaka kalla ka fahimci abinda yake ranta, dan haka bayan tafiyar shi ta shiga ban daki tayi kuka har ta godewa Allah, sannan ta fito ta sami Maude a tsaye. Abin sallah ta shimfid'a ta fara gabatar da sallah, zunzurutun bata kulla gaskiya a sallah ba. Tayi raka'a kusan sha biyar. Daga karshe ya zo gabanta ya zauna tare da saka kafar a kasa, yana zaune a gaban sallah, hannun shi yana kan gwiwar shi.

Shafa kan shi yayi sannan yace mata.
"Sallah tayi yawa."
Cikin fushi ta juya zata bar kan abin sallah ya riko hannunta, tare da fincikota ta faɗa kan shi, kirjin ta yana wani irin bugawa, rabonta da ta kusanci inda namiji yake wata goma sha bakwai ana niman na sha takwas .
Zare hijab ɗinta yayi tare da janyota jikin shi, ai kuwa ta fara kiciniyar kwace kanta.
"Ki nutsu!"
Amma haka ta mike tare da ture shi, mik'ewa yayi tare da isa gabanta.
"Ka fita min a daki kafin nayi maka ihu."
Ajiyar zuciya ya sauke sannan ya kalle ta, tare da hada ta da bango. Aikuwa ta shiga kai mishi duka da yakushi, ture shi take amma yana nan a manne da ita, bai kuma ji ya hanata ba, a hankali ya kai bakin shi kunnenta.
"Zan cigaba da jiranki, ba zan tab'a sarewa da aurenki ba, Ba kome nake bukata a jikinki ba, kece nake so mu karasa rayuwar mu a tare, ANUMULLAH ba zan iya gaya miki irin kaunar da Ni Aliyu nake miki ba, ANUM KHADIJAH, Sabida ke na kasa komawa daga inda nafito.

Khadijah Mahaifiyarki bata kaunar mu a tare, kuma ta wani gurin banga laifinta ba.

Mahaifina bai da lafiya! So idan na farka da asuba kafin na tafi asibitin zan na muku typing ɗin, idan kuma baku gani ba! Ku rike a ranku bana gida ne! Domin dole zan zauna a can don Allah na fadi Uzurina, dan wani lokaci mutane bamu da Uzuri
#Mai_Dambu
[2/13, 11:38 AM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA ARBA'IN DA TAKWAS.

"Duk da na bata dukiyar da take bukata,sai dai ta gaya min gaskiya, kuma na gamsu."
Ture shi nayi tare da matsawa,
"Anum!"
Bude mishi kofa nayi, tare da nuna mishi hanya. Ban kalle shi ba.
"Ki bar hawayenki ya zuba mana! Yana rage zafin zuciya!"
Shanye hawayen tayi tare da kallon shi tsaf.
"Zaka iya fita!"
Wannan fushin baya kaunar shi, dan yana jin kamar tabo ce da yayiwa Zuciyarta, dan haka ya rufe kofar, tare da fincikota ya matsata da kofar, tare da kai bakin shi kan nata, kiciniyar kwace kanta take ya kai hannun shi dukka biyu, ya matsa hannunta da kofar, ture kanshi tayi tare da juyar da kanta..tana wani irin huci.

"Bana son kazamta! Bana son ka b'ata min jikina da najasa, bana son ka karya min tsarkin da yake jikina da zuciyata, karka ajiye min abinda ba zan iya cire shi ga kowa ba, karka manta ni uwa ce, karka rabani da sauran abinda na tanadawa rayuwa ta, don Allah karka sare min gwiwata.."
Hade goshin su yayi tare da sake hannunta.
A hankali ya maida kanta kirjinshi, tana jin yadda zuciyar shi take bugawa, shafa bayanta yake tare da lallashinta, tana jin saukar ruwa me zafi a dokin wuyarta. Dan haka ta d'ago kanta zata mishi magana ya kyale ta, ya sauke soft lips d'inshi akan nata, wanda ake wani irin wet. Sakamakon yadda take bit d'inshi idan ta tuna abinda aka mata.

Cikin idanun juna suke kallo, she can think how long time. Da ta tab'a kallon romantic film, da yadda suke kazamtar shan bakin juna, but yau a madadin warin bakin da take tsammanin yana dashi kamar yadda take jin bakin Alhaji Mudi yana buga doyi, sai taji wani kamshin minti fresh, ya daki hancinta har zuwa makoshinta.

Tunda take haduwa da maza bata tab'a haduwar da namijin da take hango madarar kaunarta cikin eyes d'inshi kamar Maude ba, tana son yin breaking kiss din, amma ta kasa sakamakon wani irin kewar shi da yake zuwa mata unexpt, a hankali ta janye bakinta tare da sauke kanta kasa.
"Nagode da kasanya ni na samu nutsuwar kwalkwal, tunda baka jin rokon da nayi maka, karka sani na rasa."

D'ago kanta yayi sannan ya bata wani light peck a goshi, sannan ya kai bakin shi kunnenta yace.
"Daga gobe ba zaki kuma gani na ba, Insha Allah." Yadda yayi maganar numfashin sa yana sauka a dodon kunnen ta, yasata zuβewa jiki ba kwari by now ta kasa kuka.

Sai zafin zuciya, haka ya zauna a gabanta sannan ya ciro zoben azurfan dake makale a sarkan da take yawan gani a wuyar shi ya b'alla igiyar ya saka mata a cikin yatsunta. Tana zaune quiet bata iya ko d'aga kai ta kalle shi ba, zuciyarta ne yake bugawa sosai.

Kallonta yake ta masifar bashi tausayi, shima zama yayi a gurin yadda bata tashi ba haka shima bai tashi ba, yana yawan hango murmushinta tun daga yaranta har zuwa girman ta, har zuwa karfe biyu na dare tana zaune bata d'ago kai ba, shi kuma bai ji a ranshi ya tafi ya barta cikin damuwa ba, kiran sallah farko yasata mik'ewa tana sauke ajiyar zuciya.. sannan ta nufi ban daki, sai lokacin ya lura da inda ta tashi ya b'aci. Tashi yayi tare da zare key din kofar ya rufeta, koda ta fito duba jakar kayan su tayi taga bata zo da pant din ta ba, kuma babu pad. Wayarta ta duba.

Ta shiga duba kayan kwanciyar Yaron, ta sami wata tsohuwar tsumma, ta ninke sannan ta nufi ban daki. Ta saka sannan ta wanke pant din ta, ta koma fito ta goge inda ta b'ata, sai lokacin ya shigo. Kallon juna suka yi ya ajiye mata laida, b'ata kalle shi ba, bata kuma damu dashi ba.

Haka yazo ya tsaya a bayanta,ya kai hannun shi kafad'arta.
"Ki bani damar na kare kain.."
Shiru kake ji, yayi maganar duniyar nan Anum bata d'ago kanta ba, bata Kuma ji a ranta zata amsa mishi ba, haka yayi ta surutu har ya kusan rasa sallar asuba, daga nan ya fita tare da mata fatan alkhairi.

Lumshe idanun ta tayi tana kuma shaƙar kamshin turaren shi a jikinta, kwalla ne suka shiga mata wasan tsare akan fuskarta, kuka take kamar ranta zai fita, dan haka tayi maza ta dauki ledar da ya kawo mata ta rungume a kirjinta, tana kallon kamar yau ta farka daga cutar mkanta.

Kmshin turaren shi yana tafiya da rayuwar ta, dan haka ta bude ledar, always da pant ne, sai kuma madara da maltina shi yasa ledar yayi nauyi, zama tayi ta ci kuka sannan ta shiga ban dakin ta saka pant din. Tayi mamakin yadda aka yi yasan irin wanda take sakawa.

Sai dai fushin da zuciyarta ta dauka dashi bata jin zata kuma yafe mishi. Har abada.

Tana fitowa ta samu wani mutum a tsaye dan lokacin gari ya waye. Ajiye mata kayan kwali yayi, abun mamaki daga kayan ci har zuwa na sha, sai 50k.

Zan cigaba da jiranki har karshen rayuwata

A.A.H.T
Maude.....

Kai takardan nayi saman hancina, kokarin cusa k'iyayyar shi nake zuciya ta, amma yaki shiga.
"Mugu ka zalince Ni zaka turo min kudi ka mayyar kuɗi ko!"

Ta faɗa haka a fusace, tana kuka.

Zama tayi tasha kukanta, abinda ya kawo mata a kwalin ta fara dubawa, manyan gwangwanin madara da Ovaltine, sai suga. Tarkacen yara dangin chocolat.

Sai pampas, da man shafawa. Sai always. Da kuma wasu maganin yaron, dauke kai tayi tare da share kwallar ta.

Zuwa karfe takwas, Aunty Binta da Aunty Rabi suka zo. Dake Aunty Binta da unifoam yasa Aunty rabi bata wani samu matsala ba, har dakin da Anum suke tana kuka rike da takardan maude, wanda bata damu da son sanin waye shi ba, duk da tasan sunan shi na gaskiya Aliyu ne. Wannan ba damuwarta bane.

Matsalar ta dashi akan me zai tafi ya barta cikin damuwa, bayan dashi ya dace su raba matsalolin rayuwar su. Tunda su Aunty Binta suka shigo. Sau daya ta kalle su, bata kuma kallon inda suke ba.

Daukar takardun yaron Aunty Binta tayi, cikin sauri ta rike hannun ta, tunda suke da Anum bata tab'a musu wani abu na reni ko rashin kunya ba, asalin ta irin yaran nan ne masu matukar kiyayyewa da girmama na gaba dasu.

Wani abu dan gane da Anum tana da wasa da dariya, amma tana da mugun taurin kai da kafiya, sai dai tana iya jure kowani irin abu, duk abinda zaka ga tayi magana akai, toh tabbas babban al'amari ne, shi yasa Aunty Binta ta d'aga hannunta kan takardun. Nuna musu hanya tayi, suka kalle ta zasu yi magana ta saka hannunta ta toshe kunnenta.

"Tunda Umma ta juya min baya bana bukatar kowa a tare dani!" Ta faɗa da karfi tare da nuna musu hanyar fita.

Babu musu suka fita, Aunty Rabi ta kira Umma ta gaya mata, abinda Anum tayi, kuma babu karya sun nuna mata cewa ai tuntuni ya dace ta zare hannunta akan Anum bata zare ba, sai yanzun da Anum take buƙatar ta zata juya mata baya, sai da kome ya jagule mata mata zata bi na Maman Aminu.

A'a tayi kuskuren, dan haka ta dawo ga Anum dan tafi bukatar ta a halin yanzun.

Jikin Umma tayi matukar sanyi, dan haka suka tawo da Rulwanu, wanda shi kawai Anum ta iya amsawa gaisuwar shi, sau daya ta kalli Umma, tace mata.
"Ina kwana!"
"Lafiya lau Anum, ya me jiki!"
Bata amsa mata ba, sai jan Rulwanu da tayi gefe ta rufe shi da masifa, tare da ɗaukar kudin tace.
"Ka mai da mishi tsiyar shi, Ni ba mayyar kuɗi bane, kuma Nagode da ya sayar min da kaunar da nake mishi."

"Anum!"
"Kaga Malam idan ba zaka kai mishi ba ka gaya min! Kowa ma gudu na yake, Malam bai kuma zuwa min ba, itama wacce nake kallonta a madadin farin cikina, ta juya min baya kawai ka kai mishi kace mishi nagode."

"But;"
"Karta yarda raina ya b'aci."

Cikin fushi ya wanketa da mari, cak taji kome ya dauke mata, sannan ya rungume ta, yana fadin.
"Haka yaji lokacin da aka kai karan shi ga Ofishin immigration. Haka Suka tozarta mana mahaifiya, haka suka yi ta gaya mata magana marasa dad'i ita da shi, kinsan halin da Malam yake ciki? Duk saboda aurenki, ki buɗe ido da kyau, ki buɗe zuciyarki da kyau, Domin Ya Gaya musu cewa, Idan *KE RABON SHI NE* duk

duniya babu wanda ya isa raba ku, sannan ya ajiyewa mutumin takardan shaidan zama ɗan ƙasar Najeriya tare da na lasisin zama ɗan bauchi, Anum me Umma tayi a rikon da tayi miki?

Wallahi har abada ba zan tab'a wulakanta Maman Aminu ba, amma ta tozarta mana mahaifiya, ta sanya malam yankan jiki ya fadi. Ban mare ki dan ina jin haushin Abinda akawa Umma ba, jiya yazo da bakin cikin ki saurare shi amma haka kika ki kallon shi" jan iskar bakin shi yayi sannan ya fesar.

Ya cigaba da cewa.
"Ya hakura ne dan babu yadda ya iya, kuma idan ya tirje zasu cigaba da d'agawa Malam hankali. Don Allah ki dube matsalar da idon basira, Maman ki tana son ki auri Hamisu. So ki aure shi kawai."

Daga haka ya cireta a jikin shi, kallon idanunta yayi da suka juye zunzurutun tashin hankali da dimuwa. But ba zata iya cewa kome ba, kowa ma haushinsa take ji, ta kasa magana, dan haka ta koma gefe ta jingina da bango.

Wasa wasa sai da ta shafe awa daya da rabi, kafin ta bar gurin sabida kukan da Yaron ta yake yi, taje ta rungume shi da ciwon shi tana kuka. Daga Rulwanu har Umma tayata kokawa suke.

Haka ta cigaba da jinyar Yaronta, Umma tana zuwa ta wuni a jikin Yaron, Maman Aminu kuwa idan tazo kamar zata goya Anum, murmushi take idan ta nuna yadda take kwashe mata albarka, yau kuma tana fadar wasu kalmomin yabo da saka albarka a tare da ita.

Ranar wata Jumma'a, Alhaji Hamisu tazo musu, daga yadda yake barin kudi ta Fahimci matakin da ta ajiye mutumin, gashi nan dai bai da aibu, bafulatanin Bauchi ne, kyakyawa baki dashi, yazo yayi ta mata zuba tana kallon shi, yana gamawa yayi mata sallama, sannan ya bar Asibitin.

Nan Maman Aminu tayi ta gaya mata irin yayyafin nera, haka suka sami sati biyu aka sallame su, tunda ta shigo Unguwar, idanun jama'a yake kanta, ta tsime kamar ba ita, ba, tana isowa kofar shagon shi, tana jin kaifin dara darar idanun shi a jikinta yana mata wani irin sauka a jikinta, a hankali ta d'ago kanta,ta zuba mishi ido.

Murmushin takaici tayi mishi sannan ta dauke kanta, tayi imani da ita ce, ba zata tab'a barin shi ba, ko Office din yan sanda aka kaita, zata tsaya akan shi.

Amma shi fa, yayi wani wurgi da ita, kamar wani abu mara daraja, tana sab'e da D'anta a kafad'arta, ta shiga cikin gidan su.

Da matukar ban tausayi yadda take kallon Maman ta tana wani rawan kai zata amshi D'anta, ta wuce dakin Malam da shi, ta zauna a kasa, tana kallon malam din da aka sanya mishi roban ruwa, dan sun jima da sallamo shi.
"Malam!"
Murmushi yayi mata, sannan tace mata.
"Allah yayi miki albarka! Insha Allah sai kin zama musu Inuwar gajimare, ke daya ce tal zaki zamewa kowa bango. Insha Allah kukanki zai zame miki dariya, Khadijah, nasan albarka zata zagaye rayuwarki, Insha Allah mijinki sai ya mai dake sarauniya a cikin duniyar shi."

Allah Ka bawa mahaifina Lafiya□□

#Mai_Dambu
[2/18, 8:45 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Ka

BABI NA SITTIN
□□ Alqur'an koda gudu da tsalle tsalle zanyi wuf da Labarin nan😀

My Emterh da sauran barkanku....

A fusace ya juya zai bar falon ta rike hannun rigarshi, hawaye na zuba da mugun gudu akan fusakarta. Girgiza kai tayi sannan ta rike shi, tana shesheka.

"Barrak da Annur sunce min yar bola ce ni, shi yasa bani da Mama, Dadda Mama na ta mutu ne? Wai duk wanda bai da Mama ko an dauko shi a gidan Marayu ko kuma an yarda shi a bola, Dadda ka kai ni naganta."

Murza hannunta yake yana huci, tare da rintsa idanun shi, jijjiyar kan shi yana mik'ewa sosai.
"Yaushe zaku yi hutu?"
"Ban sani ba!"
Ta faɗa a sanyayye.
"Hoor, ina da tafiya aiki. ne, Insha Allah idan na dawo da kaina zan kai ki, gurinta sai dai Mamanki bata sona!"

Hannunta takai fuskar shi, tana dariya tace.
"Zunnoon yace min wai tenta din Class din mu tace wai ai kai hadadden mutum ne kace Mama bata sonka,.Dadda kayi mata laifi ne amma nasan Mama tana sonka."

Yadda take dariya sai yake hango Anum a lokacin da take shekara goma, hatta gashin sajenta wanda suka haɗu da na goshinta, hatta gashin giranta a hade suke kamar na Uwarta, murmushin takaici yayi, tare da ɗaukar ta, suka fita yana saukowa, ya kalli Sharifa da take faman da yaran Zulkhalainie, Yaran kanwata ce.

Kallon zaki gamu dani yayi mata, sannan ya fice da yar shi. Bai gaya kowa ba, ya zuba mata ido zai yi ya ga gudun ruwanta.

--- Part din Innar shi ya shiga da ita, zama yayi da ita, ta kalli Yayar Maude Rufaidah wacce tazo gida yanzun nan duba Innar mu da take fama da ciwon kafarta.

Mika mata hannu tayi, Rufaidah tayi, da sauri ta sauka a jikin Uban nata, ta nufi gurin Rufaidah, tana zuwa ta faɗa kirjin ta, tana sauke ajiyar zuciya tare da zubda kwalla. Hannunta a bakinta.
"Asadullah! Ba dai kana nufin ba zaka kai ta taga uwarta ba?" Ta tambaye shi, tana kallon, hade ranshi yayi tare da hararar Nusaibah da sauri Rafi'a suka bar d'akin. B'ata rai yayi ainun.

"Addah!"
"Asadullah! Ni ban hanaka laifin matar ka ba, amma kasani Uwar Yarka ce, tana bukatar mahaifiyarta ka duba kwayar idanun ta. Cike yake da maraici ta rasa soyayyar Uwarta, don Allah."
"Addah karki roke ni, zan kai ta idan na dawo daga aikin da zanje."

Murmushin jin dadi tayi sannan tace mishi.
"Yarinyar nan zata yi hakuri, gata da sakewa."
"Haka Mahaifiyar ta take, sai dai yanayin kaddara ya sauya ta."

Ya faɗa a sanyayye, ciro wayar shi yayi, sannan ya mika mata hoton Anum, gata nan lokacin tana yarinya. Akwai na lokacin auren mu.

A hankali take bin hoton, shigowar Nusaibah da ta leka wayar tace.
"Kamar nasanta, amma na manta inda na tab'a ganin ta."

Rafi'a ma ta leka, tace.
"Kai nasan wannan matar"
"Kusan me? Kafin na kareraya kafaffunku, ku bar nan."

Simi simi suka wuce, dakin Maman su, suka same ta zaune Hoor ta kwanta a cinyarta suna karatu, Hoor ta dage sai gyara mata take.
"Innarmu! Kuna hira ne da Hoor?"

Kallon su tayi sannan ta maida kan Hoor din, tana kaunar yarinyar kwatankwacin yadda take kaunar Y'aya'nta, duk da bata san Uwar Yar ba, amma taji a ranta tana kaunarta har cikin jinin jikin ta, shi yasa ta kira Rufaidah ta gaya mata abinda yake damunta, tunda tun shekara biyu da suka wuce suke tattaunawa akan lallai ya dawo da Uwar yarinyar, amma yaki magana haka ta saka Muh'd Aasim yayi mishi magana yace karsu dame shi akan Anum.

Duk sai da ta tara yaran mata da maza, amma duk suka ce wallahi tsoron shi suke ji. kuma tasan Rahama da Hajara basu gari tunda Ita Rufaidah a tahwa take aure, ita kuma Hajara a maradi, amma duk ta saka Rufaidah tayi musu magana.

Toh Allah ya taimaka sanadin abinda yarinyar ta faɗa yaji tsoron kar tsautsayi ya fadawa rayuwar shi ko ta Yarinyar bata gana da Mahaifiyar ta ba.

Bayan ya bar yarinyar a gurin Innarmu, ya nufi gidan shi. Yana shiga ana kiran magarib, dan haka yana shiga yayi alola ya wuce masalaci, bai koma ba. Sai da akayi isha, yana sane yau girkin Sharifa ne, dan haka ya wuce dakin shi ya sauya kaya tare da nufar cikin gidan su, ya shiga dakin Hajiya Hakamah, ya amshi tuwon alkama miyar kuka, da manshanu. Har ya fara cin abincin sai ga wata Yar uwarshi ce, itama kakarta Kanwar Dijimah ce, dan haka suka gaisa dake bazawara ce, bata jima da mutuwar Auren ta ba, tasan halin shi idan zai ci abinci Kowa barin gurin yake ita kuma tazo ta zauna ta saka shi a gaba tana mishi kallon kurilla.

Fitowar Hakamah tayi mata magana tare da cewa.
"Zuwairiyya! Ya zaki saka mutum a gaba haka, dalla tashi bana son shirme, ko kanen shi basa mishi wannan haukar"

Mik'ewa tayi ta barshi a gurin.
"Asad kayi hakuri!"
"Hmm!" Yace mata, yana gamawa ya mike tare da nufar shashin Gajeh suka gaisa, kallon shi tayi tare da cewa.
"Yau banga Amaryan Alhaji ba"
Murmushi yayi sannan yace mata.
"Yau a gidan Innarmu take!"

Gyda kai tayi sannan tace mishi.

"Ayya yarinyar tana girma tana wayo, jiya ina jin su sa Amir yana ce mata wai Mamanta ta mutu shi yasa bata da mama,.ai kuwa yar nima tana tashi tayi ta marin shi nace yau naga zafin rai a jikin Yar nan duk girman shi sai gashi da kuka. Dakyar na kashe fadar ma."

Murmushi yayi sannan ya mike tare da mata sallama, ya nufi gidan kakan shi, ya zauna suka tab'a hira Dijimah ta kawo mishi fura kadan yasha sannan ya musu sai da safe,.bai wuce gidan shi ba, ya nufi shashin Mahaifin su, ya zauna a inda yake hutawa suka gaisa. Sannan ya gyara zama ya fara labarta mishi yadda suka yi akan zai kai Hoor ganin Mahaifiyarta.

"Asadullah! Ni a nawa nazarin me zai hana ka dawo da ita, ba mamaki kaga Allah ya kuma kara maka wani Haihuwar." Shiru yayi yana kallon yadda me shayi yayi.
"Nasan da zafi yanayin da kashiga, duk da ban san meye ya hadaku ba,. amma indai horo ne na tsawon shekaru uku zuwa huɗu ta horu, kuma ka duba kodan Albarkacin yarinyar nan ai tayi kome."

D'ago kai yayi tare da kallon Abban shi, sannan yace.
"Shi kenan Abba!"
"Allah yayi maka albarka. Ya kuma baka Zuri'ar dayyiba, ya Albarkaci rayuwar su."

"Amin Ya Allah Nagode sosai Abba!"

Sannan yayi mishi sai da safe ya bar d'akin, tunda ya fito ya nufi gidan shi, ko ta kansu bai bi ba, amma tabbas dole ya rama abinda Anum tayi mishi, da wannan ya rage kayan jikin shi, sannan ya kwanta. Har ya fara aiki a laptop din shi, ya tashi ya kulle d'akin, yana rufewa kuwa yaji Alamar Sharifa. Tayi bugun duniyar nan yaki buɗewa.

Karshe ya kashe wayoyin shi, tare da kwanciya, nazarin abinda kowa yake cewa akan ya dawo da Anum yake, toh idan sun kai auren shi kotu fa aka raba? Kai ba zai yiwu ba. Haka yayi ta tufka yana warware, har barci yayi gaba dashi.

Da asuba bayan sun fito masalaci, suna zama suyi karatun safe da Sheikh a masalaci, nan ya shiga kawo mishi karar shi da Sharifah tayi. Kallon liman yayi sannan yace mishi.
"Zan sako maka ita sai ka nima mata wani mijin!"
Ya faɗa yana shan mur, karshe kamar zasu haura sama, su rikito. Kafin suka dawo suka shirya zunzurutun yaji haushi yana tashi daga masalacin ya shirya kayan shi ko sallama bai yi ba, yayi tafiyar shi bayan ya kira Ahmadou (ila) sai bayan tafiyar shi ne ya bada sako a kaiwa matan shi yayi tafiya, aiko sunji haushin abinda yayi musu.

Suka ce zasu jira suga ya dawo da Matar shin da yake musu Iskanci akan ta.

**
Bauchi.
"Ke da za a taimakawa, shine kike wani gadara da bude hanci, wani irin Iskanci ne baki buga ba a cikin Unguwar nan, har labarin cikin da kuka zubda naji, dan haka mu taru mu rufawa juna asiri, mu more rayuwar babu shegen da zai san muna irin wannan shagalin, gaki mace daga sama har kasa, bayan ne ko gaban masha Allah, kiyi tunani me kyau, akan."

"HM! Wallahi baka da imani ko tausayin rayuwarka baka ji, nice zanyi zina da aurena? Kai kasan ni ba sa'ar ka bace, amma kasan me Insha Allah, Ubangiji zai

kawo min wanda zai bi min hakkina, idan nayi magana ma cewa zaka yi sharri nayi maka. Allah ya ganar da kai"

Ta fadi haka tare da barin Office din, tun daga lokacin ya takura min, kullum sai na samu ya rigani saka hannu ko yace naje Office din shi, na saka hannu nazo ko zan tashi.

Da naga an fara amfani da Iskancin da yake min, sai na daina zuwa.aikuwa ana zuwa bincike daga Ministry aka tace bana zuwa aiki.. karshe suka dakatar dani, ban damu ba. Har na kwashe sati shida.

Sannan na koma makaranta, bai fasa min Iskanci ba.

Zama yayi tare da cewa.
"Maman Uncle aminu, kin cika rigima ki zauna na kwashe miki ruwan zafin, ke ba lafiya ba kinzo zaki fadi akan ruwan zafi."

Kallon yaron take a duk lokacin da yake mata wani abu, ji take kamar tayi ta kwanciya a kasa tana rokon shi gafara, haka yayi ta diban ruwan yana kaiwa ban daki, yana gamawa ya kai mata ban daki, sannan ya dawo ya rike hannun ta suka shiga ban ɗakin, sannan, yana jiran ta.

**
Yau satin shi daya da dawowa daga tafiyar da yayi, yana ta haɗa mata kayanta a cikin jakarta, tare da shirya kome, sannan ya koma gefe ya haɗa kayan tsarabar malam da na Umma sai na Isma'il, da na Yan biyu Hishmah da Hisham, ya haɗa kayan cif. Kallon shi Hoor tayi sannan tace mishi.
"Dada ina na Mama?"

Hararar ta yayi sannan yace mata.
"Ba zan yi asarar kudi na ba, tana da kudi."

Ya gaya mata, shigowa A'isha tayi sannan ta zauna tana kallon kayan murmushi tayi sannan tace.
"Banga kayan tsarabar Maman Mariah ba?"
"Ke nake jira ki kawo naki na kai mata,!" Ya fada yana murmushi.
"Hmm! Toh me zaka kai mata, sai na hada mata?"

"Ina ruwa na da abinda zaki bata ,.kawai shiga ki fito. Ke hada mata sai na kai ta." Ya fada.
"Toh idan kuma ka samu tayi auren fa?"
Kura mata ido yayi tare da mamakin dalilin wannan maganar,
"A'a ITA RABO NACE" ya faɗa cikin nutsuwa, yana hada kayan,

"Toh maji ma gani matar maji taki fadar sunan maji , Amma nasan zuwa yanzun matar nan tayi wani aure dan ba zata zauna zaman jiran gahon shanu ba"....
Meye A'isha take nufi ne?.....
#Mai_Dambu...
[2/19, 9:01 AM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Ka

BABI NA SITTIN DA DAYA.

Wannan shafin Sadaukarwa ce ga Masoyan A-K....

Murmushi yayi sannan ya cigaba da shirya kayan, yana mamakin yadda take iya fadar mugun fata akan tafiyar shi. Karshe sai da ya kare ya zuba mata ido sannan yace mata.
"Ranki shi dad'e! Idan naje ban ce miki dawowa zanyi da mace ba! Amma naji zantuntukarki, baki daya babu sauki ko ban dawo da ANUMULLAH ba, tabbas Asadullah aure zai kara, dan haka a kiyaye furta kalmomi masu gwafa, dan ba zata rataye ni ba, amma zata iya rataye zuciyar mutum."

Cikin borin kunya tace.
"Allah ya sawwaka, Ni zanyi kishi da matar da ban.santa ba? Ai ba zan fara shirmen ba, kawai naga yadda kake nunawa kamar tafi mune!"
Ta fada tana me tsare shi da yan madaidaitan idanunta, murmushi yayi sannan yace.
"Ai nima nasan Indona bata kishi, amma dole idan kika ga Anumullah ki kuma jin babu abinda zai saka kiyi kishi da ita. Sabida bata kai ki ba, nifa idan ban yi karya ba, kina da zuciyar zinari ce shi yasa baki kishina."

Wani farr tayi da idanunta, duk da ta girma, dan kuwa da ta haihu tabbas zata iya haihuwar Anum, babba ce haka ma Sharifah babba ce, Anum ce yarinya karama a cikin su. Tsayawa yayi yana kallon ikon Allah,bawai dan bata da kyau bane a'a asalin kyakyawa ce kuma fara kamar tsada.

Matsalar da aka samu tana da jiki ne sosai, musamman bom-bom ɗinta, manya ne.. har sun rinjaye kafarta.

Murmushi yayi a ranshi, sannan ya gama kimtsa kayan shi, bai san dadin mace ta haɗawa namiji kaya ba, sai dai shi ya hada abinshi,

Yana gamawa ya cire agogon shi ya shiga ban daki, koda ya fito ya same ta, ta kwanta, takowa sake jikinta zata fara kwasan barci ya mari cinyarta, bude ido tayi sannan tace mishi.
"Ya Asad baka da kirki, meye nayi na duka."

"Toh raguwa! Daga make ki zaki fara mita, jikinki yana da kyau da bukatar namiji irina, yanzun ina farawa zaki ce hmm! Ita kuma wancan bata da aiki sai na shan kayan mata." Daga haka ya fice daga d'akin, yana me musu fatan shirya.

* Washi gari tare da ila da rakiyar wasu manyan motocin sojin kasar, suka nufi kasar Nigeria a mota dan yace yarinyar shi tana son kallon garuruwan kasar da na Nigeria.

Tafiya ce tare da lafiyayyun ababen hawa, koda suka dauki dogon lokaci suna tafiya suna isa garin Maradi suka kwana, washi gari suka kuma ɗaukar hanya.

**
Ban san me ya faru ba, amma tabbas naga Umma ta fita da sassafe, har na shirya zuwa makaranta, ban dawo ba sai karfe biyar na yamma dan karfe sha biyu nake tafiya, ina shigowa na samu Maman Aminu tana kuka, kallon Isma'il nayi naga ya zuba hannu bibbiyu a kumatai.
"Kai bana son iyayi, uwar me aka maka?"

Kamar wani Babba dan ya iya manyance yace min.
"Wai su Umma Hafsat ce suka yi hatsari a hanyar tula."

Sake jakar hannu na, nayi tare da zuba mishi ido. Zama nayi tare da fashewa da kuka, zunzurutun tausayin Hafsat.
" A wani hali take?"
"Hmm! Allah ya kyauta, ban san meye Hafsa take nima ba, ban san meye kika tare mata ba, Umman ku ta dawo tace."

"Allah ya kyauta ya kuma bata lafiya yasa Zakkar jikine." Daga hakan na shige d'akina, bana son damuwa tunda nayi mata addu'o'in shi kenan.

--; A can asibitin kuwa Hafsat tana fama da buguwar da tayi akanta sai surutu take kamar me, babu wanda ya kulata.. a hankali ta fara surutun abinda ta aikata.

"Yanzun haka zan cigaba da kallon Anum tana tattara kome, itace soyayyar malam, Umma Sonta take, itama Maman Aminu da nake nuna mata Anum bata jin maganarta ta tsine mata haka zan cigaba da kallon su, a'a dole naje tura na fidda Ruwaidah. Wallahi ba zan yarda ba, dole naga bayan su. Anum da Ruwaidah. Nice nayi mata sharrin maita, na kuma je har gidan Hamisu na ce karsu yarda ta zauna, itama Ruwaidah ai sawa naii a rufe mata bakin mahaifar ta, yadda ba zata TAB'A Haihuwa ba, shi..."

Cikin mugun takaici Mijinta ya juya ya kalli Aminu da Usman, Sai Abdul Hakim.
"Kun dai ji da kunnen ku? Ba karya aka mata ba, Ni dai zance Allah ya bata lafiya, amma na yafe zama da ita, taje can da jika bakin halinta ta sha." Wucewa yayi gurin da Nurse suke ya amshi takarda ya saketa,

Sannan ya ajiye musu yayi tafiyar shi,

Yadda take magana da yadda tayi ta haɗa Anum da yan uwan, sai da ta fadi kome, karshe alluran barci suka mata. Tana fara barci zata tsalla ihu, tace.
"Gashi nan yazo zai dauke ni, wayyo Allah na, karka tafi dani."

Dakyar tayi barci.
**
Kwana biyu ina jin suna ta zirga-zirga tsakanin Asibiti da gida, Maman Aminu taje ta dawo da kuka, ga ciwon Isma'il da ya tashi gadan gadan, kamar nayi hauka.

Kudin salary na, duk ya kare a hanyar asibiti, tun da na kai shi suka duba kodar, suka ce zasu wanke mishi. Ana bukatar dubu dari biyu, nazo na hada gwal dina da wasu abubuwan hannuna, kudin Balance din na hada, sannan na, cewa Umma.
"Bari na leka makaranta nayi musu bayani, zan kai Isma'il asibitin."

"Toh shi kenan, nima ina son zuwa na duba Hafsat, Insha Allah amma sai kun dawo na tafi sabida kar mu bar Maman Aminu a gidan."

"Toh bari naje!"
Na fita da sauri, haka kawai nake jin bakon yanayi a raina, dan haka na nufi makarantar, ina shiga sai dariya ake min, ban damu ba, na nufi Office din mu, nayi abinda zan yi na nufi Office din wancan watsatsen na shiga.

Ma same shi da wata yarinya yar aji shida, yana ta matse ta, kasa hakuri nayi na fincikota na wanka mata mari.

"Dake baki da hankali, zaki bari ana niman..." Kwace hannunta tayi tare da cewa.
"Kema fa ansan kina zuwa gurin shi, kuma ance saboda kina da kanjamau yasa yake korank..."

Marin ta na kuma, tare da turo ta waje, na shiga gayawa headmaster magana, tare da cin mutuncin shi, fada sosai muka yi dashi dan na manta aure ne dani, muna cikin haka ashe an sami wanda ya kira Rulwanu, haka yazo yaja hannuna bai damu ba.

Ina kuka ina masifa, dan ma Allah ya takaita akwai nikkab a fuskana, haka na bar gurin faɗa nake ina kuka.

Ganin dandazon matasan Unguwar mu, ya sani juyawa na kalli Rulwanu, murmushi yayi sannan yace.
"Kiyi hakuri, za a ci Uban koma waye, ki daina kuka, Madam."
"Nabi Madam da gudu ba takalmi, wallahi zan maka rashin mutunci."
"Ai ni dake dan jima ne da dan Jummai maza yi min."

.. Kirjina ne yayi min nauyi, sakamakon kamshin turaren shi da nake kuma jin yana kutso ni, raba idanuna nayi ina niman ta inda yaƙe, amma ina wasu kartin maza naga sun lullube wani Zaune, had'iye yawu nayi sannan na sunkuyar da kaina kasa, jikina yana rawa,

Tabbas ina jin kaifin idanun shi cikin jikina, wayyo Allah na, ina...
"Dadda!" Na tsinkayo Muryan yar wata baby doll a gabana, kura mata ido nayi, zunzurutun tayi min kyau, ga gashin kanta har gadon baya, cusa hannu na nayi a keya na naji wutsiyar gashina.

Kallona take tana leka fuskana, nima haka nake ta mata. Hannuna na kai zan kad'e mata kuran da ya haura mata saman gashin goshin ta, ya daka min tsawar da na zabura.

Da sauri na juya jikina ya dauki rawa, da sauri na d'aga nikkab din, na kura mishi ido.
"Karki kuma tab'a min Yarinya ta, uwar masu ya'yan Arziki, bar min Y'ata algunguma. Kuma ki bar kallona, domin nafi karfin ki yanzun."

Da sauri na juya zan shiga cikin gidan, yarinyar ta rike hannuna, kuka ne yazo min domin ina jin lokacin da ya zare hannun ta a cikin nawa ya ce mata.
"Karki yarda da ita."
Shiga cikin gidan nayi na samu anata muhawara tsakanin Yan uwana maza. Wasu na cewa naje ayi min test wasu na cewa a'a bani dashi,har shima Zakin Fama ya shigo gidan. Fita yayi tare da bawa Yaran shi damar su shiga cikin makarantar suci mishi Uban headmaster. Sannan ya koma cikin gidan.

"Khadijah bata da wani ciwo, domin ni ne wanda nayi mu'amala da ita na karshe, sannan kuma nayi imani ba zata tab'a wasa da igiyar aurena akan ta ba, dan haka zan yi tafiya gobe Insha Allah, da Isma'il. Sati biyu zamu yi idan na dawo zan kai ta Afrika ta Kudu,zata ga likitan fata."

Duk wannan maganar da suke iya tsakanin su ne, dan ban ji me suke cewa ba, dan tun da na shiga d'akin, na sami Isma'il a zaune yana game a tap din da nake da yakinin na wancan katon mutumin ne, kamshin turaren shi ya cika min daki, ina kallon yaron. Yadda yake ta murna yace min.
"Ummina, nawa ne fa Abbana ya kawo min, shi da Princess hoor, Hoor!" Ya kwala mata kira.
"Assalamun Alaikum! Na shigo."

Wani irin kwalla ne ya shiga saukowa daga idanuna, wato yarana rayuwar su, nagartacce ne domin kowanne su cike yake da kamala,
"Shigo!" Tana shigowa ya gyara zaman shi yace mata.
"Ga Ummin mu!" Ya nuna mata ni,
"Kullum tana kukan Allah ya dawo mata da ku, ina jin kullum idan tayi sallah tana addu'a, tare da niman Allah ya yafe mata, karki yi fushi da Ummin mu tana son mu"

A hankali ta tako har gabana, tare da saka hannun ta a baki, tana kallona idanunta cike da kwalla, sannan ya cigaba da bata labarin su Hishmah ya gaya mata ita ta rasu, amma Hisham yana nan. Fadawa tayi jikina.
"Zan iya manta kome, amma ban da maraicin da na gani a kwayar idanun yarinyar da ta faɗa da'irar zanen ƙaddara ta, sake min Y'ata;"

"Don Allah kayi hakuri, wallahi nayi kuskure masu yawa, na zalince ku, amma na rantse da Allah, na tuba, karka kuma raba ni da ita. Don Allah Aliyu!"
Na fada ina kuka tare da zuba gwiwata a kasa, saka hannu yayi ya zare yar shi.
"Abbana!"
Kallon yaron yayi, itama kuma Yarinyar tace..
"Dadda!"
Duk suka kafe shi da idanun su.
"Ni Dadda Ummina nake so!"
A hankali Isma'il shima ta tako gaban shi, tace mishi.
"Kayi hakuri! Bata da lafiya, kaga maganin da take sha, Umma tace wai zuciyarta ne ke mata ciwo. Dadda, nima sabida ciwonta nake boye mata nawa ciwon don Allah ka daina barin Ummin mu tana kuka."

Ajiye min yar yayi, sannan ta dawo jikina tana dariya, riko hannun Isma'il yayi tare da ɗaukar jakar shi suka fita.

Ba zan iya gaya muku farin cikin da nake ciki ba, dan haka da kaina na fito zanyi girki aka kawo cefane aikuwa na fata aiki babu kama hannun yaro, ba shirya tuwon shinkafa miyar danyen kub'wa aka fita dashi a babban kula, saboda sojojin shi, ita kuma nayi mata wanka, na shirya ta cikin kayanta masu kyau da tsada, haka na fito na wanke kayan, sannan na zauna na sakata a gaba ina kallonta, a ranar Ya Abubakar ya dauke ta suka nufi gidan shi. Bayan yasha masifar Umma.

Ban damu ba sabida suma suna kaunar Yarinyar kuma, dake tasake ranta, tana son kowa. A can suka kwana, washi gari ya dawo da ita, Ya Usman ya dauka. Haka duk ta zaga yan uwana.

Domin duk inda ta tafi sai ta kwana, su goma sha din nan sai da ta kwana hannun su, banda Hafsah da take asibiti. Sai ranar na ke tambayar Umma.
"Wai ni Umma ina wancan BANIJARE ya kai min yaro ba lafiya!"
Abinda ya sani maganin tun ranar da ya bar gidan Umma ta sani a gaba da wasu abubuwan, da kanta take sarrafa su, haka kawai ta sani jin kasala babu gaira babu dalili, haka take haɗa Hulba da wasu abubuwan tana bani ina sakawa a boons dina, ina matse su da bra me kyau, haka ta haɗa min sabulun wankan, da na tsarki. Ga baki daya ta sauya min halitta ta, wai duk sabida wancan BANIJARE, lalle kuwa haka nake kunsawa kullum ko tsakar gida da hijab nake yawo, wallahi ni kaina nasan na sauya oba, dan haka nake tambayarta inda ya kai min Yarona.

Make kaina Maman Aminu tayi tare da cewa.
"Baki da hankali har yanzun, Uban Yaranki kike kira haka, dubi yadda ya dauki yaron nan ya maida shi nasa karfi da yaji, sai kin ga na mutu da bakin cikin ki zaki

huta da wulaknta bawan Allah nan. Wato zai sayar miki da d'a shi da yabar lu'lu'un shifa"

Tura baki nayi, domin Maman Aminu har yanzun ba wani lafiya ya ishe ta ba, a haka take rayuwa, dan bata sati jininta bai haura ba .
"Allah Mama karki ce min haka, dauke shi yayi ko gaya min bai yi ba, ina laifin yace min."

"Toh ai gwara ki kafe, yar masu taurin kan tsiya, Maman Sadeeq. Wallahi Anum da a zamanin fir'auna tazo za a wahala da ita kafin ya yarda da Annabi Musa, yar banza me taurin kan tsiya."

Ta kuma min keya, Ita kuwa Hoor dariya muka bata, tana cewa.
"Ummi! Dadda ya kai Yaya Isma'il asibiti ne,kuma shi yace kar a gaya miki Dan zaki damu, wai ke kina kuka kamar baby."

Kallon yarinyar nayi idanuna kwalkwal, ai kuwa ta fashe da dariya.
"Ummi tana kuka!"
Tace.
"Wallahi kin sha kunya, Anum yaushe zaki girma."
.tura baki nayi, tare da cewa.
"Ina ruwana da girma."
"Allah ya kintsa min ke"

Haka muka yi ta hira, yarinyar ta a gefe mun tana nata, wasan dan Maman Aminu ta koma kusa da ita, ina kallon ta daura kanta a kirjin Maman Aminu, suna hira.

"Kin san duk abinda yarinyar nan take duk kuruciyarki ce!"
"Kai Umma ban halin tayi abu sai kuce Ni"

**
Washi gari.
Bakuwar Number na gani.
Ummi muna hanya da Dadda
Tabe baki nayi tare da gyara kwanciya ta, ba Dadda ba daddo.

Ina sane suna hanya. Nayi biris dasu, sai da Rulwanu ya shigo da cefane yake gaya min wai suna hanya.
"Kai bana son munafunci, na lura tunda wannan me kama da samudawan yazo kake wani rawan kai, da kanin Ubanka ya dawo daga balagoron da yayi ko?"

Sune suka tsaya min, wunin ranar hidima ake tayi dasu. Tun daren jiya motar da zata kwashi kayana, ta iso. Dan har da tambarin sojojin ƙasar nijar, a cikin shi aka kwashe min kayana, wanda yan uwana suka min sabo dall, kamar na budurwa. Har da gas da kome na amfani na, sai da suka sabunta min.

Ga kayan furnitures dina da aka min manyan kujerana. Haka suka fara tafiya, domin su isa da wuri. Dariya Ila yayi tawa Rulwanu, dan yace sai ya bi motar kaya, har da ɗaukar jakar shi, kuwa hakan yabi su. Yana cewa.
"Ku gayawa Anum, na rigadata isa d'akin ta."
"Zaka sha tafiya!"
"Babu damuwa,"

Haka ya suka bar garin Bauchi, sai da naji kewar shi.
..... Washi gari muma bar garin bauchi, dakyar suka rabani da jikin su Umma da Maman Aminu, aka fitar dani. Tunda na shiga motar da ta kawo su, da zata kai mu kano.

Tunda na kifa kaina, akan gwiwata nake kuma nazarin abinda Umma ta faɗa min, tare da auna shi, a matsayin mizani.

Karfe sha biyu muka isa Kano, daga nan muka nufi airport.
***
Nijar.
Ya koma gurin aikin shi, sakamakon niman shi da a kayi, duk abinda yake yana yine amma bawai yana fahimtar wasu abubuwan ba, ya shiryawa Anum abubuwan, murmushi yayi tare da cigaba da aikin da yake gaban shi, yana waya da Hajara da take can Damagaran akai akai.

***
Mun riga su Rulwanu isa, duk da mun isa karfe biyar na yamma sabida mun bi jirgi ne, dan haka muna sauka motar aikin shi na soja suka zo daukar mu, aka wuce damu gidan su. Tunda muka isa gidan, yan mata da yara Tare Da yan uwan shi na family suka shiga zuwa kallon Anumullah.

Kaina nad'e yake da alkyaba, me kyau. A hankali na sauko daga cikin motar, a hankali Ummul Salma ta riko hannuna, tare da riko hannun Hoor, tana murmushi, kowa sai bin mu suke da ido, tunda muka isa shashin Liman, duk jikokin shi suna zagaye shi.

Tunda muka shiga yake addu'a a kwanon sha, yana gamawa ya mika min, na amsa tare da cewa.
"Nagode!"
"Toh kunga yadda ake mutuntawa, kunga na bata tace ta gode."

"Kai wannan tsohon da rikici kake, idan ka gama mu tafi da ita," juya harshe yayi cikin Yaren buzanci yace su bashi guri.

Haka suka fita daga d'akin, har su Aunty Binta. Suna da fita,
Ya kalle ni, tare da yace. "Anumullah"

"Na'am!"
"Kudi ya baki ne dan ki so shi ko kuma ya nuna miki bakin bindiga ne?" Gyara zama nayi sannan na kuma sunkuyar da kaina, nace mishi.
"Nagartaccen Mutum ne shi, mutum ne me hakuri da juriya, mutum ne da yasan darajar kanshi da mutanen da suke tare dashi, Abban Isma'il, yana da hakuri da sanin ya kamata. Iya wannan kawaicin da yayi min ya sani amincewa na bashi rayuwa ta,!"

Kafe ni yayi da ido, sannan yace.
"Indai haka ne, hausawa sunce idan kana da kyau ka kara da wanka, ki rike Mahaifiyarshi da Amana, ki kambama ki nunawa duniya cewa ke Matan Asadullah ce, ki nuna musu bambancin daga inda kika fito."

Bayan nan ya kira Ummul Salma, ta fitar dani, cike da mamaki.. haka yayun shi mata, suka yi ta nuna min ni matar da yake so ce dan haka ga mahaifiyar su, itace suke fatan na rike musu ita hannu bibbiyu.

Haka ranar muka kasance sau zuwa suke suna kallona, duk da dai ina kunshe a cikin d'akinda aka bamu. Na sashin matar baban shi,an kawo mana abinci.
Tunda Hoor ta ga danginta, bata kuma zuwa mana ba, har dare sannan su Rulwanu suka iso anan suAunty Safiya suka nufi inda aka nuna musu shashina.

Suka shiga jere, duk da gidan Babba ne, amma kuma part uku.
Biyu a kasa daya a sama, da manyan falo biyu, duk nashi ne. Sai da zai dawo da Ni, ne ya ce zan zauna a sama. Suka tadda rigima, nan ma shima ya ɓalle musu, domin ya rantse da Allah zai ajiye aikin shi, ya dauke ni da yar shi mu bar kasar baki daya ba zasu kuma jin labarin shi ba.

Sanin zai aikata yasa suka shafa mishi lafiya, a saman aka min jera min kayana tsaf, sannan suka fito, lokacin tara na dare yayi.

..... Koda suka dawo nasiha suka min, sosai dan sun ce zasu koma babu zaman da zasu yi,. Washi gari da karfe tara gidan suka yi karamar walima, bayan an tashi suka dauke ni zuwa shsshin Liman, suka ajiye mishi ni, sannan Aunty Binta tace mishi.
"Baba gamu nan mun kawo maka Anumullah! Gata nan dai itace yar autar mu, kuma bana tunanin ta haɗa shekaru ashirin da biyar, Baba idan Anum tayi laifi idan ka hukuntatta ka rage mana aikin da sai mun niko gari munzo mata fada.

Idan tayi kuskuren kayi mata fada, ka rage mana aikin saka katin dubu daya muyi mata fada, Baba ga Anum nan, duk fadin kasar nan da kewayar shi bata da dangi da suka wuce kai! Bata da Uban da ya wuce kai, bata da uwar da ya wuce kai, Baba muna niman Arzikin ka mai da Anum cikin iyalinka yadda ba zata yi kukan rashin mu ba."

Kuka ne ya ɗan so hanata magana sannan tace.
"Baba, iyayen mu suna matukar kaunarta, amma kaunar da suke mata da Asadullah yasa mun rintsa idanun mu, mun bashi ita. Don Allah Baba idan tayi mishi laifi ya dube ta a matsayin Kanwar shi, ko kuma yar da zai iya tsawarta mata, ya mata nasiha. Don Allah kar yayi fushi da ita.

Bata da hankali, ba zata iya gane tashin hankalin da yake ciki ba, amma idan ya tuna mata nisan gidan da inda take zata Fahimci yadda ake rayuwa, Baba banda aure da ya kawo ta, har abada ba zamu tab'a shigowa wannan babban zuri'a ba."

Kuka da kewar Anum yasa ta kasa magana, Aunty Rabi ce ta cigaba da cewa.
"Itace yar autar mu, mafi soyuwa a zuciyar iyayen mu, Kanwar da muka fi so, Baba ga Khadijah nan, zamu tafi mu Barka da aiki da fama, ayi mata Uzuri idan tayi laifi, dan mun san bata jin magana."

Matan Yayuna suma kuka suke, Sai Rulwanu ne da ya iso inda nake ya zauna a gaban Liman. Yace mishi.
"Abokiyar faɗa tace, kuma kanwata ce, Shalelen Mama da Malam, Hasken zuciyar Ummana. Daga karb'an da muka samu, na fahimci Allah ya kawo Kyautar Allah Cikin Babban Ahali, Baba Insha Allah ba zaka tab'a samun ta da laifi ba, duk da dai ta kasance mai kan tukunya dan bata jin magana, ta rena ni yanzun zamu ga wanda zaki mishi renin hankali da tsaurin ido. Baba ga kanwata nan na mika maka amanarta duk da naji Oga Maude yana cewa yana hanya. Amma haka ba zai hana mu, nuna maka soyayya da muke mata ba. Ayi hakuri da yadda take Insha Allah. Nan da shekara me zuwa zan zo suna."

Murmushi Liman yayi, sannan yace musu.
"Wallahi tunda nake ban tab'a ganin yan uwa masu kawazuci ba, gashi kuna ta bani amanar yar uwarku, nan abu daya nake so da ita, idanunta su zame mata aikin su gani! Kunnenta ya zame mata aikin shi ji, bakinta ya zame mata faɗan alkhairi, zuciyarta ya kasance me taushi, idan tayi wannan abun babu wanda ya isa ya takata, matukar ina raye."

Duk sai kansu ya daure, shi kuma yayi haka ne dan baya kaunar Asadullah ya cigaba da fuskantar matsala daga matan shi, musamman yadda basu da hakuri, idan suka mishi abu ya kamata ya samu inda zai tsuma ranshi yaji sanyi.dan haka yayi ta musu bayani a dunkule.
"Kunga yanayin rayuwa da irin aikin shi na soja,yana bukatar mace me sanyi, ba wacce zata zame mishi lalura ba, wacce a koda yaushe tana sanyayye domin shi, idan tayi haka Insha Allah zata iya rike ragamar kome na cikin ahalin nan baki daya."

Haka suka bar shashinsa, a filin waje muka hadu dashi.
"Hajiya Binta! Toh gashi na ce a bari sai gobe ayi muku booking, don Allah kuyi hakuri gobe ku bar garin nan."
#Mai_Dambu...

ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Ka

BABI NA SITTIN DA HUDU.

😊 Da Alamu dai wannan labarin so yake sai na kai saba'in Yaushe na fara free book har haka 😕😑😏

"Kayya amma dai da kabar mu,munyi tafiyar mu wallahi,ai mun rigada mun gama kome."
"A'a don Allah, Aunty B karki tafi!"
"Wallahi tafiya zamu yi, ji min munafuka. Kina murnan an kawo ki gidan mijinki, yanzun muyi"
"Aunty Binta, kinji shi ko?"
"Ko ba Aunty Binta ba! Yarinya anan zamu barki."

Aikuwa na sake kuka, tare da buga kafana a kasa, kallona yake yana rike da Hoor, sai kallon yadda nake boye fuskana ina kuka.

"Tafiya kan sai gobe, Insha Allah" ya faɗa tare da kafe ni da ido,lekowa nayi tare da jan mayafina nayiwa Rulwanu gwalo.
"Inji gwiwar tuzuru kafin Gwauro barna!"
"Kutt melesi!ina wasa dake? Ni sa'an kine, Abban Isma'il wallahi zan mata shegen duka, kafin na bar garin nan."

"Oho dai tuzuru kawai an gaya maka tuzuru." Na fada ina karkada mishi harshe.
Aikuwa yaji haushi, sai gashi wai zai make ni, da sauri na koma bayan Aunty Rabi,ya kuma biyo ni duk da suna fada, hango wasu kyawawan mata nayi, irin kyan nan suke dashi me daukar hankalin, suna kallon mu. Garin tsayawa ina kallon a ina na tab'a ganin su naji yana fadi.
"Aunty Safiya kyale ni na ji mata Kafin mu bar garin nan."
.yadda yayi maganar na fahimci suna tare tare dashi ne,da sauri na koma bayan Dadda. Tare da buga kafana ina cewa.
"Don Allah boye ni, karka bari ya min kome"

Kasa motsi yayi sakamakon yadda nake kara rike shi ina dariya.
"Don Allah ku shiga cikin gida, ga su A'isha can ki tsaya ku gaisa dasu."
Lekowa nayi ina kallon su,.kafin nace mishi.
" Su din suwaye?"
Sannan na kalli inda suke, ashe ina zuwa bayan shi, su Aunty Binta suka kara gaba. Fuskar shi babu walwala yace min.
"Mata na ne?"
Gaba nane ya fadi, na kura mishi ido. Shima ni yake kallo, a hankali na zare hannuna daga cikin na shi, sannan muka jera.
"Kin razana ne da ganin su?"
Murmushi nayi sannan nace mishi.
"Kai ina kawai dai ina musu kallon kamar na tab'a ganin su."
Har inda suke, muka isa. Ya bude baki zai magana suka yi tafiyar su a fusace. Sharewa nayi maganar umma tana dawo min, amma kuma da ban mamaki,yadda suka mishi dan bana ce ni suka yiwa ba. Rakani yayi har inda muke,

Da dare suka kuma rako ni, cikin gidan shi,shi kuma yana can gurin Dattijo, tunda muka shiga gidan muke sallama babu wacce ta leko, dan haka suka wuce dani shashina, sannan suka min nasiha, kafin suka sauko.. babu kowa a falon.

Bayan fitar su, ne suka jajjanta abun kafin suka shiga hada kayan su.

Har karfe goma sha biyu babu miji babu dalilin shi, dan haka ban yi barci ba, na tashi na fara sallar dare, sai karfe biyu ina zaune akan abin sallah ya shigo ranshi a b'ace, mik'ewa nayi tare da nad'e abin sallah. Sannan ya kalle ni.
"Hmm! Baki kwanta bane?"
Girgiza mishi kai nayi, sannan nace mishi.
"A'a!"
"Ok mu kwana lafiya!"
Ya fadi haka tare da barin d'akin, bance mishi kome ba, dan bani da abin cewa.

**Washi gari.
Na tashi cikin natsuwa, amma akwai guntun damuwa a raina, kawai na adana abina ne, na shirya cikin atamfar Vlisco riga da skirt, me ratsin ruwan hanta.

Farin mayafi na yafa sabida kayan akwai farin sirki, nayi karamin kwalliya mara hayaniya.ina shirin fitowa ya shigo sanye da farar yadin material na maza, fuskar shi babu walwala ya kalle ni.
"Kin tashi lafiya?"
"Alhamdulillahi! Ya ka kwana kai ma?"
"Masha Allah, Alhamdulillahi." Daga haka ya juya ya fita na bi bayan shi da kallo,ina tsaye a inda ya bar ni, ya kuma dawowa da kudi CF ya ajiye min, su tuli guda, sannan ya ajiye min wasu yan dubu dubu na kudin Nigeria.

"Me zanyi da su?" Na tambaye shi,
"Ki bawa yan uwanki mana,!"
Daga haka ya juya ya fita, haka na shirya ya fito, kallon shi nayi shida Daya matar shi, wacce take kallon kofar dakina, ranta a b'ace.
"Ina kwana?"
"Dan ban kwana ba, zaki ganni!"
Kallonta nayi sannan na sunkuyar da kaina, ina son tuna inda na tab'a ganin su, har na sauka kasa, kallona shi nayi tare da zuwa inda yake na zauna.
"Dadda!" Na kira sunan shi kamar yadda yaran shi suke kiran shi.
Zuba min ido yayi yana jin sunan har cikin jinin shi.
"Kina kina da matsala ne!"
"Ban da bakin jaraba, ai sai kiyi hakuri idan ya dawo girkinki ba."
"Esha!"
Ya daka mata tsawa, sunkuyar da kaina nayi. Sannan na mike zan fita.
"Anumullah!"
Ya ajiye kofin hannun shi bayan ya kirani.
"Jirani na kai ki, kuyi sallama." Murmushi nayi sannan na tsaya ina kallon yadda suka juya harshe suna masifa, mai da kaina nayi ina kallon wani african magic, wanda sune ta harshen faransanci..

Har ya gama abinda yake yazo ya sakani a gaba muka bata su. Tunda na isa gurin su na zauna na karya, shima ya wuce cikin gidan su. ina karyawa ina kuka, sun tambaye ne me ya faru bakie magana karshe sai da na basu haushi,kamar zasu doke ni. Nace.
"Ni wallahi bana son ku tafi ne!"
Sake baki Aunty Binta tayi cikin jin haushi tace.
"Qaniyarki!"
Tayi min dakuwa, dakyar na iya karyawa, domin sun dake sai sun bani a baki, bayan na gama ne suka kuma kara min nasiha, domin daga yanayin kishiyoyin da na samu, sun san zanci kaniyar kaina, bayan sun gama min fada suka kuma ɗaukar kayan su, zasu tafi anan ne nace ban ji ba.

Kuka nake tare da rike Aunty Binta, idan na kasa hakuri na koma kan wannan, dukda abinda Hafsat tayi min sai da naso da yau zan ganta na yafe mata abinda tayi min. Gabaki daya na hana su tafiya fa.

Dan shiga motar nayi, na zauna ina kuka. Wiwi.

Sun yi fadan kamar zasu dake ni, karshe suka kuma dawo suna rarrashina, ai kuwa nayi tsalle nace ban san da haka ba, sai da Yazo gurin, yaga yadda ake yi dani.
Bai ji haushi ba, domin abinda ya faɗa musu babu wanda bai yi dariya ba.
"Au ku har haushinta kuke ji? Bayan yaushe Anum ta daina kuka daga ita sai yar pant a kofar gida ba zata ci ciwo ba."

Aikuwa suka saka dariya, dole na fito, tare da fadawa jikin shi ina kuka, kai hannun shi yayi bayana, yana shafa bayana a hankali. Tare da cewa.
"Ke ko ina sai kin nuna, musu ke yarinya ce!"
"Ina ruwa na, don Allah kace karsu tafi"
"Toh uwar masu hankali, mazajen su da?"
Aikuwa na fashe da kuka, ina kuma rike rigar shi, tare da buga kafana a kasa, ni ba zan yarda ba sai su tsaya, haka ya samu ya janye daga jikina, suna barin gidan na saka kuka, kamar zan fasa ihu. Rike ni yayi lokacin da yaga na kifa hannuna akan fuskana, ina shashekar kuka. Hannun shi ya kai kan cikina, tare da kai bakin shi kunnena.
"Ki shirya! Domin kuwa aure kika zo yi ba tunanin gida ba!"
Daga haka yaja hannuna muka shige cikin gidan.

Tunda na shiga falon naga suna ta karyawa, tare da min kallon yarinya ce ko nace yarinya ke damuna, haka na wuce ina kuka.
"Yarinta manyan kai kuma Ya Asad irin wannan ka dauko?"

Bai kula su ba, sai da yaga na haura sama da gudu ina kuka, sanan ya juya ya bar min gidan, tun daga ranar ban kuma gane mishi ba,.kullum zai ajiye min kudin, dan wancan kudin rulwanu na mikawa ya basu.

Amma wannan karon kullum sai ya ajiye min, babu batun rayuwar auren mu, zai shigo ya tambaye ni, daga nan ya juya ya fice a dakin, abinci kuwa. Basu bani.

Gashi ban saba da kowa ba, dan ma Yan uwan shi suna shigowa na basu kayan tsaraba, sannan muyi hira dasu.

Farisa da Safina, Matan Aasim sun shigo min. Tare da min wuni a ranar,.nayi hira sosai gashi ban san me zan dafa musu ba, dan babu Kitchen a sama, cikin gidan suka zo suka amshi abincin suka kawo min, tun daga ranar. Aka fara kawo min abinci.

Ban san me ya faru ba, ya shigo a fusace.
"Akan me zaki na amso abinci a cikin gidan?"
"Kayi hakuri!"
Na fada mishi kai na a sunkuye,sake magana yayi.
"Bana son munafunci da hada husuma, idan girki zaki yi,.ki sauka kasa kiyi mana! Sai ki na zuwa kina amsar abinci har a kai karana."
"Kayi hakuri ba zan kuma ba!"
Na gaya mishi, kaina a kasa.
Tsaki yayi min tare da barin d'akin,
Ban ce kome ba, amma naji wani irin bakin ciki ya tsaya min a raina.
Washi gari na nufi kitchen zanyi girki na samu a rufe, murmushi nayi domin, kuwa ban san me suke nufi da haka ba, ban damu ba. Na koma dakina na kwanta, kayan tea na hada nasha, sannan na shiga kiran yan uwana ina jin ya suka koma, mun sha hira dasu wanda kusan nasiha ce akan rayuwar aure.

Umma kan ba zan ce kome ba, dan tayi min nasiha sosai.
*** Sai dare ya shigo gidan ina jin motsin shi na sauko kasa da gudu, na fada jikin shi.
"Ina kewar Rulwanu, ko na kira shi baya dauka. Don Allah ka kira min shi."
Ware idanu yayi yana kallon Sharifa da ta cika dam. Kasala ce ta sauko mishi tare da wata gajiya mara iyaka, sauke ni yayi tare da cewa.
"Zan tura miki kati ki kira su."

Ya wuce zai tafi na bi bayan shi kamar jela ina sake mishi kananun magana, na niman rigima between ni da shi. A gajiye ya kalle ni.
"Anum!"
"Dadda!"
Na kira sunan shi,
Share ni yayi, har muka haura zama, zan bi bayan shi naji an finciko ni, ban yi aune ba sai jin saukar mari nayi akan fuskana.
"Kina mare ni?"
Sake baki nayi ina kallon makirci, kiri kiri.
"Anum!" Ya daka min tsawa,
"Rashin kunyar ki har takai ki marar min mata? Meye tayi miki? Ba tambayar ki nake ba?"
"Wallahi!"
"Kiyi min shiru! Wuce dakinki"
Haka na juya na tafi ina sheshekar kuka ina rufe d'akina yana kifa mata mari. Ya kuma kara mata,
"Nayi haka ne domin idan na karya taki a gabanta ba zata cigaba da ganinki da kima ba, kin manta kofana yana da glass ne, ki mareta ki kuma mata sharri. Kun saka min doka a gaban iyayen mu, karku tab'a min mata na, domin zaku ji a jikinku."

Kasa magana tayi dan bata dauka zai ga abin ba.
Haka ta sauka, abinda tana jin a ranta sai ta kuma marina,
Koda yayi wanka ina bukatar Anum, amma horon da yake mata yasa ya ajiye bukatrta ya cigaba da aikin shi da yake a laptop.

--- haka nayi kuka har na godewa Allah,.na rasa waye zan gaya mishi, haka na kwanta duk sa yunwa da nake ji.
Dakyar nayi barci.
.....
Da safe suna karyawa na fito na nufi kitchen, na fara kokarin niman abinda zanci.
"Uban me zaki mana a kitchen?"
Shiru nayi tare da kallon ta.
"Ba tambayar ki nake ba?"
"Don Allah ki daina damu na." Na gaya mata tare da hada abinda zan ci. Kawai kashe gas din sannan ta watsa min ruwa a cikin abinda zan dafa.

"Ya Asad!"
Ta kwala mishi kira,
Kwalla ne ya cika min idanu, yana shigowa cikin harshen buzanci ta gaya mishi abinda nayi mata.
"Wai Anum me yasa baki jin magana ne?"
"Kayi hakuri!"
Tsaki yayi sannan ya fita, nima fita nayi na same shi ya kasa cin Abincin shi, kallon shi nayi, sannan na haura sama abuna. Dan ban ga amfanin.....
#Mai_Dambu.....
[2/21, 11:15 AM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Ka

BABI NA SITTIN DA BIYAR.

"Ina abincin ta?"

Kafe shi da idanun A'isha tayi, tare da cin abincin ta,
"Ba tambayar ku nake ba?"
Ya kuma daka musu tsawa,
"Ya Asad"
"Tambayar ku nake?"

"Toh waye bawanta da zai mata girki, tunda ta iya kwana da namiji girki ne ba zata iya ba?" Inji Sharifa,
"Me yasa kuke niman hanyar da zata rena ku? Idan ta fara muku na yarda zan hukuntatta, amma me yasa kuke azabtar da ita da yunwa?" Ya tambaye su,

Cikin ko inkula suka cigaba da cin abincin su, mikewa tayi ta dauki nashi da tea din ya bi bayan Anum, tsaki Sharifa tayi da karfi. Cak ya tsaya, kafin ya wuce bai musu magana ba,

Ina kwance ya shigo d'akin, zunzurutun yunwa, ji nake kamar ba zan iya kara awa daya ba, ajiye min abincin yayi, sannan ya fita, can sai gashi da tulin kudi ya ajiye min, ganin har zuwa lokacin ban kalli Abincin ba, ya sashi zama kusa da ni, ya d'ago ne ni.

Tashi nayi zan bar gurin shi, jiri ya nemi yar sar dani, da sauri ya tare ni.
Kuka nasa mishi tare da rike rigar shi gam, idanuna a rufe.
"Meye haka?"
"Ka kai ni gurin Umma na, zan mutu da yunwa."

Na fada ina ƙoƙarin mik'ewar, shima mikewa yayi, tare da kai hannun shi dukka biyu baya na,
"Bana son damuwa, ki zauna kici abincin."
Wani irin kuka ne ya kuma kwace min, ina girgiza kai tare da rike shi gam, ina buga kafana a kasa, tare da sake shi ina kuka.jirin da ya kuma dibana ya sashi rike ni sosai,

"Kiyi hakuri kici abincin."
"Don Allah ka kai ni gurinta ba zan zauna ba"
"Toh naji."
Zaunar da ni yayi, tare da mika min tea, kamar mahaukaciya haka na shanye tass, sannan ya kuma mika min Farfesun kayan cikin rago. Karnin namar ya sani ji kamar zanyi aman tea din, na ajiye mishi.

"Kici."
"A'a, bana son shi"
"Me zaki ci?"
"Gurin Umma na zaka kai ni."
Na fada tare da sake kuka,
"Baki da hankali ne? Babu inda zaki."

Mik'ewa yayi abin shi ya barni cikin kuka,yana sauka ban san me ya faru ba, sai dai naga an turo Kanwar shi Rafi'a kirana.
Babban hijab na saka har kasa.

Sannan na nufi gidan, tunda muka shiga babban falon Liman. Naji Sharifah tana kuka, A'isha kan kasa magana tayi, shine yake magana.

"Liman a nan kuka ce tunda naje can ba zan raba musu kwanaki ba, sai tayi sati biyu! Naji kuma na dauka, me yasa zasu mata horon yunwa? Sannan kuma idan tazo

girki su tadda husuma? Gidan su ko Gidana ga Sharifah nan da ranta akan idanuna ta" d'aga mishi hannu liman yayi, Shiru kowa yayi.
"Ai inda ranka kasha kallo, kayi magana ace ana fifiko, ke Khadijah kizo nan kina amsar abinci, shi kuma ki bar musu shi, ki zubawa Sarautar Allah ido.kiga yadda karshen munafukai zai kare!" Kakan su Ta faɗa tana yarfe hannunta.

"Dijimah! Danyi hakuri na kammala wannan yanayin." liman Ya fada kallona.

"Kin karya?" Gyada kai nayi,
"Me yasa baki dafawa da kanki?"
Sunkuyar da kaina nayi, duk yadda naso rike kwallar idanuna sai da suka shiga sauka.
"Khadijah! Ana cutar ki ne?"
Ya kuma tambayana, rike baki nayi cikin kuka nace.
"A'a ina son komawa gida ne?"
"Toh shine kike kuka?"
Gyada mishi kai nayi. Shiru yayi sannan yace.
"A duk lokacin da yaro ya bukaci iyayen shi, toh inda yake yana fuskar damuwa ce, A'ishah da Sharifa meye kukewa Yar mutane?"
" Liman me zamu mata banda munafunci irin nata, girki ne dai babu shegen da zai mata." Inji Sharifa,

"Toh yayi kyau!"
Ya faɗa,
Kare mana kallo yayi, sannan yace.
"Daga yau kabawa kowa hakkin shi, karka yarda ka tauye wata dan wata, sannan karabawa kowa key din kitchen ɗin, idan wata ta miki rashin kirki ki rama, idan ba zaki rama ba, ki kawo min karar su. Kai kuma ka zama namijin duniya a gidanka."

Daga haka Kakar su ta rike hannuna muka shiga cikin d'akinta, abinci ta shiga jera min.

Haka na ci na koshi sannan tace min.
"Kin samu ganin Mamar ku kuwa?"
"A'a bai kai ni ba!"
Kura min ido tayi sannan tace min.
"Kamar na sanki? Da jimawa"
Dariya nayi sannan nace mata.
"Tunda naga Sharifa na tuna da mun tab'a haduwa a aikin hajji."

Aikuwa muka balle da hira, a hankali muke hira, tare da gaya mata lokacin ai da auren shi nazo, bayan komawa muka samu saba'ni, gashi na kuma dawowa rayuwar shi karo na biyu.

Nasiha tayi min tare da nuna min dole na jajjurce akan mijina ba kuma nuna mishi nima mace ce, su kuma wadancan lusaran nayi tsayin daka kar a manta da azumi da sallar dare, tare da azkar. Kar nayi wasa da lahaula!

**
Tunda aka yi magana shi kenan, na sami sauki. Amma a ta bangaren ai babu sauki, sannan ya raba mana kwana ɗaya rak, haka ya zaga kansu. Ranar da zai shigo d'akina ya ajiye min kudi yayi tafiyar shi gurin aikin shi.

Ganin baya nan suka kuma ɓullo min da Iskanci, har kofar dakina suke zuwa zasu dake ne.gasu ba kananun mata ba,.balle na biye musu.

Ban tab'a gayawa kowa nawa ba, amma na barshi sai ranar da Maude ya shiga hannuna zasu Fahimci dalilin shigowa rayuwar su.

Idan na shiga nayi girki bana fita sai na gama, domin ina kuskura na fita zan samu an kashe gas ko an zuba min ruwa a cikin abincin. Dan haka babu wani abun da zanyi dan na rama.

Kallon su kawai nake, ina kwasan ilimin kishi. Sai da yayi sati Uku. Sannan ranar friday ya dawo.

Dan a tunanina d'akina zai sauka yasa na wuni ina aiki, abin har mamaki yake basu, yadda nake ta hawa da sauka, Hoor ma ban ganta ba, sai da suka shigo gaishe ni, sannan nace taje ta kira min Rafi'a. Dake idan nayi girki ina saka musu, su kaiwa Innarmu.

Shima sai da aka ririta alamarin aka kai karana, gurin Liman, ban san ya akayi ba, dan shima ina kai musu abincin, sai ji nayi ana sake min habaici da bakar magana, nazo da asirin Nigeria, na mallake tsoho me adalci.
Ban kula su ba, haka na cigaba da rayuwa na, ina tsaye Rafi'a ta shigo na mika mata nasu, sannan nace mata.
"Ga nasu Dijimah, zan haura sama da na yayanku ne ko zaki dan jirani na kai na dawo."

"Karki damu ina jiranki"
Haka na kwashe abincin na haura dashi, sannan na dawo na samu suna fada da Sharifah, da yaren su.
Dan haka nayi tsam da raina duk yadda aka yi tazo b'ata min abinci ne, dan haka na kwashe sauran nace mata.
"Ki kai musu naso!"
"Mun gode!"
"Ba kome!"
Ina haurawa na shiga ban daki, ina cire pant naga bako na yazo, shiru nayi, sannan nayi wanka. Doguwar riga na saka tare da zama nayi kwalliya.

Kallon kai na nayi kawai na cire kayan na saka wani doguwar gown mara hannu, kallon agogon d'akina nayi, nasan yanzun zai shigo tunda anyi isha.

Fitowa nayi, na kefawa kofar gidan ido, ina jiran shi.
Yana shigowa na sauka da gudu, na rungume shi, tare da sumbatar kumatun shi da goshinsa.
"Barka da hanya? Ka dawo lafiya!"
"Baki san zaki karya ni ba?"
"Ayya Daddaaaaah bani da nauyi fa!"
"Don Allah da gaske?"
"Sosai kuwa!"
Na fada ina dariya, amsar jakar shi nayi, muka haura sama. Dakin shi na bude naga ba a kintse ba, juyawa nayi tare da kallon shi.
"Ko zaka bani aron dakinka na minti arba'in! Sai kayi amfani da nawa"
"Toh!"
Haka na kai shi d'akina, bayan na saka mishi ruwan wanka, sannan na fito, sai da na wanke kome na ban dakin shi na wanke har da gajerun wandon shi, sannan ba kuma hada zanin gadon na fito dashi, kayan shi na nima mishi masu kyau da rashin nauyi.
..na shigo mishi dashi d'akina,

Yana fitowa daga ban daki kwanciya yayi, yana jirana. A kwance na same shi. Ina shiga na dauki mai na fara shafa mishi, tashi yayi zaune.
Yana kallon yadda nake kokarin shafa mishi mai,
"Ki gama ki bani abinci yunwa nake ji!"
Da sauri na gama kome na mike tare da jera mishi abincin, sauka yayi ya fara kallona. Fuskar shi ba a sake ba.

Zuba mishi abincin nayi,.ya fara ci. Sannan na mike zan bar gurin yace min.
"Yaushe kika fara al'adar ki?"
"Yau;"
Dauke kai yayi, ya cigaba da cin abinci juyawa nayi ina duba jikina.
"Ba anan na gani ba? Audugar da kika ajiye na gani,"
Ajiyar zuciya na sauke sanan nace.
"Ai!"
A hankali ya gama ci, Ni kuma na bude show glass na dauki turaren wuta na nufi dakin shi da shi.
Ina gama sakawa na fito.
Da Sharifah muka hadu, bata min magana ba, nima ban bi ta kanta ba.
D'akina na dawo yana cin abinci har zuwa lokacin, zama nayi nima na dauki cokalin ina taya shi ci.
"Me yasa zaki cinye min nawa?"
"Me maganar ma idan ya sake ba kama shi, fyade zan miki;"
Na fada ina tsare gida kamar yadda yake min.
Dariya na bashi, haka muka gama cin abincin na kwashe kayan na fito dashi, ina sauka na gan su, kowacce tana cin abincin ta.
Bayan na gama wanke kayan na ajiye sauran abincin a firij na juya zan fito. Suka tare ni.
"Jikinki yana rawa zaki kwana da mijin mu ko?"
Dariya suka bani, sannan nace musu.
"A'a me zan cire a jikin shi? Kawai dai zanji yadda kuke ji ne."
"Ke mu kike wa rashin kunya?"
Rabawa nayi zan wuce suka kuma matse hanyar, tare da kai min duka fa, ihu na saka, ko kafin ya fito, tulatulan mata masu manyan dantsuwa sun make ni, duka sosai suka min.
Lokacin da yazo ina kwance a kasa, bakina ya fashe haka ma hancina.

Ranshi ya b'aci dan haka ya juya zai fita.
"Ka kyale su! Ai kai ka basu damar su min haka, dan haka babu amfanin kullum kayi min fada ni me nake yi.da bazan yi fadar kai na ba,"

Haka na hana shi musu magana, ya taimaka min na haura sama, da kanshi ya kula da ciwon da suka ji min, bayan nan haka yayi ta kallona, karshe kwanciya nayi abuna,ina son nayi kuka amma ban son hankalin shi ya tashi.

Duk yadda naso na tare su, ba zai yiwu ba, dole sai ya daina fushin nan dani, idan ya kasance haka toh zan iya haukata su. Haka yayi kwana dayan shi, kowanne mu a dakin shi ya kwana, washi gari na shuga kitchen nayi mana abin karyawa na kai sama, na kuma zuba na su Hajja Dijamah da Mamn shi, na kai musu da kaina na gidan liman na fara kaiwa.

Sannan na nufi cikin gidan su, na gaida Matan baban shi, sannan na shige shsshin mahaifiyar shi, ban tab'a shigowa ba sai yau.

A hankali na shiga cikin dakin, da sauri Sharifa ta amshi basket din hannuna,
"Barka da safiya, da kanki kika kawo?"

"Babu kome!"
Zama nayi a kasa, kasancewar mahaifiyar su tana saman kujeran falon, a hankali na d'ago kai tare da cewa.
"Ina kwana Umma?"
Kallon juna muka yi,
"Ikon Allah! Khadijah"
Sai lokacin na tuna itace matar da ta bani shawara akan aurena da shi wancan lokacin, kunyarta da girman ta, ya cika min ido. Nan muka gaisawa.

"NUSAIBAH, zoki saka mata abinci." Ta kira wata Kanwar shi. Yarinyar bata da sakin fuska, dan haka tana zuwa ta zuba min tare da dangwarawa a gaba, tana ja min karamin tsaki.
"Nagode!"
"Munafuka;"
Kallonta nai sannan na sauke kaina ƙasa, a hankali na fara cin abincin, kadan naci. Na bar sauran sai kunun tsamiya ce fa nasha sosai, anan muke hira da ita jifa jifa, jiran duk nasiha ce da godiyar da tayi na...
#Mai_Dambu

ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Ka

BABI NA SITTIN SHIDA.

Na yadda na mai da ta mutum, ba tare da kallon yanayin ta na saniyar ware ba. Murmushi nayi sannan na nuna mata ita Uwar mutumin kirki ce, kuma wanda ya bawa rayuwata gudummawa. Babu abinda zata nima na gaza mata.

A nan muka yi ta hiran mu, har ya Shigo, zama yayi tare da harara na.
"Me yasa baki gaya min kina nan ba!"
"Babu inda zanje bayan gidan Liman da nan!"
"Asadullah! Kana takura mata fa"
"Innarmu kawo miki kara na tayi?" Ya tambaye ta yana kallonta.
"Na gaya maka kowacce mace sakarya ce da zata mai da kai kara wani abu me muhimmanci a rayuwar auren ta? Ko daya karka kuma zarginta domin bata yi kama da ballagaza ba."

Murmushi yayi Ni kan, ban ce mishi kome ba, bayan amsar da na bashi, idan ya fara kananun magana zata dakatar dashi, ta hanyar buzanci dole ya hakura, sai karfe ɗaya saura na bar gidan na nufi kitchen gidan ban ga kowa ba, dan haka na gama girkina da sauri dan bana son tashin hankali.

Ina gamawa yana shigowa, ban san ya shigo ban dan ina wanke hannuna, jin hannun shi nayi a bayana, a firgice na juya da wuka.
"Anum!" Sake wukar nayi, tare da fashewa da kuka.
"Me aka miki?"
"Na zata sune suka kuma dawowa"
Jinjina kai yayi sannan yace.
"Daga yau karki kuma daukar mataki domin kare kanki, ba dai ina nan ba."

Wuce shi nayi na haura sama da gudu, karasa sauran aikin yayi ya biyo ni,yaji kofana a rufe. Na sha kuka sosai. Sannan ba share idanuna.

Ban fito ba sai ƙarfe biyar, na sauko kasa, yana zaune a falon.
"Meye nufinki?"
Banza nayi dashi, tasowa yayi tare da juyar dani!
"Ina magana kin mai dani dan Iska!"

"Toh kayi hakuri;" nace mishi tare da barin gurin shi. Abincin da na saka mishi naga bai ci ba, juyawa nayi na kalle shi.
"Baka ci abincin ka ba?"
"Ba zanci ba!"
Hawaye ne na ya fara sauka min,
"Yanzun Dadda!"
"Idan da kina son naci ba zaki barni a waje ba, me nayi miki kike azabtar dani?"
Kura mishi ido nayi, sannan nace mishi.
"Kayi hakuri!"
"Wai Anum me yasa mike bani hakuri? Babu wani abun da zaki min nayi magana baki ce min nayi hakuri ba."
"Toh Afuwa!"
Na gaya mishi, karshe haka ya zauna na zuba mishi abincin yaci yana mita, wai zamu haukata shi. Ban ce mishi kome ba. Kallon shi kawai nake yi.

Haka ya gama kwanakin shi ya koma, sai lokacin naga matan shi sun dawo, ashe koran su yayi. Bayan ya bayan yabi su da belt yayi musu duka suma, bayan fitana zuwa gidan Innarmu.

Aikuwa suna dawowa suka taso ni gaba, ba halin na fito girki suce zasu dake ni, dan haka na daina fita suna nan, abin karyawa da na rana nake yi, na dare kuma na nufi gidan kakan su.

Zunzurutun bana son ya Mani da laifin na saka shi tashin hankali. Amma matan nan basu Fahimci haka ba, sai suka d'aga min hankali. Ranar ina wanka suka biyo ni zasu dake ni, Allah yasa na rufe kofar d'akin, dan haka ina fitowa na kira shi, na gaya mishi.

Shine ya turo Zurkhalaini ya fita dani, daga nan ya kai ni gurin Liman, ai kuwa ya gayawa Liman ya same su da bulala zasu dake ni.

Babu shiri aka hada family meeting, abin da ya matukar girgiza ilaihirin Zuri'ar su kenan. Har shima sai da aka nimo shi ya dawo.

Tunda muka hadu, Liman yace.
"Zurkhalaini kace ya kasame su?"

Gyara zama tayi sannan ya ce.
"Wallahi na same su da Bulala zasu dake ta, suna buga mata kofar d'akinta."

Shiru iyayen su, suka yi.
Wannan ba shi bane karo na farko da suke dukar ta ba, sun tab'a haduwa suka mata duka, wanda yaji shima ya rama mata, har kuke cewa na fufita shi akan su. Yau ma banda Allah yaso haka zasu taru du dake ta, sabida ba yar dangi bace. Dan haka Ni na maka izini ka dauki matar ka, ku tafi, idan ka sami lokaci zaka na zuwa kamar yadda na ce maka."

"Amma Baffa baka ganin ya shiga hakkin su?"
Kallon Hajiya Gaje yayi sannan yace mata.

"Dani dake waye ya san ya kamata? Ko mijinki bai da ikon tsallake abinda nace, ka dauki Khadijah ka tafi da ita!" Daga nan ya yiwa kowa tass, sannan yayi mana addu'a.

A ranar muka bar garin, bayan ya taimaka min na hada kayana, ina kallon shi, yana b'ata rai, a raina nace.
Gulmamme kawai
Haka muka bar garin, wanda sanadin haka na sami Yanci.

Koda muka isa babban gida ne me kyau sosai, haka ya nuna min d'akina. Tunda muka samu damar Ni shi. Ya kuma tsiro min wulakancin, baya shiga min, ko nayi abinci zai dawo yace ya koshi yaci a waje..

Kudi kuwa wallahi har na rasa inda zan saka shi, Ni kuma ina jin kunyar nayi mishi magana akan hakkina, sai na zuba mishi ido.

Lokacin da muke waya da Aunty Safiya nake tambayar ta ya jikin Hafsat da Isma'il, nan take gaya min ai ya jima a Saudiyya, ya tafi karatu. Amma Dadda bai gaya min ba, nayi kukan farin ciki sabida ya cika alkawarin da ya dauka min, da ya dawo na mishi abinda na saba yace ba zai ci ba.

"Akan me ake wulakanta ni?"
"Saboda zuciya ta tana gurin yarinyar da nake so! Dan haka kiyi hakuri."
"Aure zaka yi?"
"Ai zaki hana ni ne?"
"Allah ya sanya Alkhairi!" Na fada ina kuka, kiran Aunty Binta nayi ina gaya mata, dariya tayi min.
"Anum! Kina da diri me kyau, kika sake kina kuka, idan kika kuma kira a irin wannan yanayin, sai na baki mamaki, kiyi fada domin mijinki, sai kace baki zauna da su Xoxo ba, kin manta baya ne? Kiyi kokarin daidaita rikicin ku, sauran kuma zan miki bayani."

Kashe wayar nayi kafin na fito, ina kallon shi, komawa dakin nayi na sha wanka, tare da tsefe gashina, jika shi nayi tare da tsantsame shi, sannan na saka wasu shegun kayan barci, na dawo da gashina zuwa kirjina, kitchen na wuce, Ban ko kalli inda yake ba.

Haka na tsiro mishi Iskanci nima, ai ba dutse bane shi balle yace ya fi karfin sha'awa.
Kullum ina update Iskanci kala kala, tun yana share ni. Har ta kai idan ya ganni sai ya make min mazauni na,

Cizon bakina nake, tare da kallon shi na wuce. Tsakanin mata da miji sai Allah, sai gashi da yar murya yana cewa.
"Ni bana son damuwa, wani irin Iskanci ne Zakina yawo tsirara? A cikin gidana."
"Ai haka ne? Toh bari nayi fuck dinka yadda bakin ka ba zai kuma cewa ina yawo tsirara ba."

Aikuwa na shiga aika manyan makaman yakina, tare da nuna mishi yau ko ni ko shi, hmm.
Hmmmm! Gulmamme, sai gashi ya ma fini zakewa, fushin da ba kwanaki da gajiyar shi ya sauke.

Yo mijina dai jarumi ne, mutum ne nagartaccen me sanin ya kamata,.yana da kyau da sanyin hali, yana da kokarin isar da mace bukatar ta, sai da ya jiyar dani, kome sannan ya kwantar da ni yana shafa bayana, ajiyar zuciya ya sauke yana kallona.

---- Tun daga ranar muka bude kofar SOYAYYA, irin na bugawa a jarida, sosai muke bawa juna hakkin mu, ina ƙoƙarin bashi hakkin shi, shima yana ƙoƙarin sauke nauyina.

Wata na biyu, muka tawo Damagaran, matan shi kamar zasu cinye shi da korafi, musamman da yayi wata haske da haiba, nutsuwa ta same ruhin shi.

Shi kanshi yana jin cewa, kamar ya samu duk abinda yake so, dan haka ina dawowa na gyara gurin mu, tare da niman abinda zanci.

Duk da ina ƙoƙarin kiyayye musu, sai na lura da kishinsu Jahilin kishi ne, sai na fara aiki na yadda ya dace,

A ban kowa ina iya barke mishi tare da kirkiro rigima, haka yake sake kome yana tambayana lafiya.

Tunda na fahimci yana tare dani, na fara shiririta da shirme, saka kayan da yayi min, ko kuma nazo nayi mishi oyoyo,

Haka yana matukar bata musu rai, dan haka. Aikuwa sai ga A'isha ta fara mishi oyoyo, gata ba kadan ba. B'ata rai yayi sannan yace mata.
"Ke ina zaki? Tsaya anan ke ko kunya baki ji ba? Abinda yara suke yi zaki yi? Koda kika ga ina daukar Anum ai dan yarinya ce qarama, dan haka don Allah ki daina wannan haukar dan bata miki kyau ba."

Yana gama fadar haka ya wuce abun shi, nan dai suka ji haushina, dake naga Hoor bata tare da mu, dan haka shigar kananun kaya nake, sosai ina murza iskancina, dan Allah ya taimake ni yana juyin karshen shekara.

Aikuwa ganin yadda nake saka English wear,sai ga Sharifah. Gata ba kadan ba, ga teb'a. Yadda take tafiya da cikin riga da wando sai da ya sani boye kaina nayi dariya sosai. Sannan na wuce ta niman abinda zanci.

Dake baya nan, yana shigowa ya ganta,
"Sharifa! Meye haka? Dube ki don Allah cire kayan nan, aiko Anum bata."
."ai mune kayan baya mana kyau amma ita dake matar So ce yana mata kyau ko?"
"Toh Allah ya baku hakuri."

Ina jin su, na kama dariya sosai sabida abin dariya yake, aikuwa nasake taku, na shine sai na saka shi a daki ranar girkina ba zai fito ba sai sallah yana Sallah zai koma, karku ce wani abu meke, a'a kawai shirme da bashi labarin abinda ya faru, ko kuma na bashi labarin film, sosai nake shige mishi duk da nasan kafin ya manta abinda nayi mishi zai jima, amma na kuma samun kusanci dashi, sosai.

Kamar yadda bana tsammanin, haka na shige mishi. Ga mahaifiyar shi da nake bata kulawa, ana haka watan azumi ya kama, muka tafi Umra dashi da sauran matan, bamu dawo ba sai da aka yi Azumi da sati biyu, muna dawowa muka cigaba da faffatawa domin duk kusan addu'o'in akan shi da yarana suka kare, dan haka da zan dawo na dawo da kwarin gwiwar akan shi.

Bana wasa da addu'a da Ibada, shi yasa yake makale min, na mikawa Allah Al'amarin mu, kuma yana bani nasara akan duk abinda nake so.

Yana masifar kaunar mahaifiyar shi, sai na nuna mishi ni nafi shi sonta, domin kuwa kome ina mata, hatta wankinta nakan shiga nayi mata, kitso da gyaran farce, wani irin ɗaukar hankalin mutane nayi, duk da yana da yayu mata, amma shine namiji babba, dan haka na nuna musu shi din mijina ne, Mahaifiyar shi kuwa uwa ce min.

Koda aka yi sallah, kayan da yayi mata sai da na kara mishi bai sani ba, dan Ni ya dauka muka je sayayyar ta, kome sai na dauka mata, na kanen shi kuwa kamar bazai musu ba, nice na saya musu da wannan kudin da yake ajiye min, na kai musu, amma Nusaibah ta ki dauka karshe ta min rashin mutunci, Innar ma ta mata tass.

Sabida suna mutunci da Sharifah kuma ana maganar yayan Sharifa shi zai aureta, shine take tsoron karta tsaya min dangin mijin su mata caa, idan anyi auren.

Aunty Rahama da Rufaidah, aka ya aika musu da nasu, Hajara da Ummul Salma, suma haka.

Sai matan Baban shi da Baban shi din,. Da baya musu sai da nice na tuna mishi, aikuwa suka fara girmama al'amarina.

Da basu tab'a tunanin zasu samu ba, sai gashi ya basu daga aurena.

Duk da nasu yake aure, tuni suka ce nayi musu asiri ne, na rufe idnun su,

Bayan sallah hutun shi ya ƙare, anan ma suka dauki kananun magana, anya nice na haifi Hoor, tunda gashi nan har yanzu Ban kuma haihuwa ba. Ina jin su nayi banza dasu..

Sai ranar da muka koma, ne shima ya damu, dan haka ya dauke ni zuwa asibitin aka gwada ni, suka ce lafiya lau lokacin ne da saura.

Sai da muka shafe wata shida, duk karshen wata yana zuwa duba gida, sannan Allah ya dube mu da idanun rahama ya bani ciki. Babu laulayi babu kome. Da farko ban yarda ba, sai da nake asibitin barrack din aka tabbatar cikin ne dani, dashi yana cewa zamu tafi Damagaran.

Kamar ba zani ba, haka na shirya muka nufi garin, tunda muka isa ba fara zazzaɓi sama sama, tare da yawan kwanciya dukda ina yin kome, amma sai da suka fahimci bani da lafiya, dan haka Sharifa take gayawa Nusaibah, suka zo duba ni.
"Amma ciki ne sake?"
"Me kika gani!"
Na tambaye ta, fuskana babu wasa. Ganin zasu rena min hankali, na Barsu gurin.

Ranar wata Alhamis na amshi girki, dan haka nayi abincin rana da na har da zobo, bai ci da wuri ba, sai dai ma kanen shi maza suka ci ya dauki zoben na kai mishi firj, da dare da yaci tuwon dare yasha zobon muna hira, naga yanayin shi yana sauya wa na zata ko yar kullum ce, dan haka na biye mishi muka koma dakin.
Tun ina jure abinda yake min, har na fara girgiza shi, ina gaya mishi marana ya ciwo..

Bai saurareni ba, har sai da yaji numfashina yana daukewa sabida yadda nake jin kamar ana hura min wuta, yana zare jikin shi jini ba biyo shi. Jijjigani yayi yaga bana ko motsi, a tsorace ya saka min jallabiyar shi, ya nufi asibiti da Ni.

Duk yadda aka so tare al'amarin cikin sai da ya tab'u, kiran Liman yayi ya gaya mishi ai ga halin da nake ciki, akan lokaci yayi addu'a aka kawo min, toh ina sume, ana kawo min, yace a tabbatar ruwan ya shiga bakina, haka kuwa aka yi suka dura min har na had'iye, jikin su a sanyayye....
Allah sarki Murna ya koma ciki, Ba rabo ba dan fari ya koma
#Mai_Dambu
[2/21, 8:36 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA SITTIN DA BAKWAI

Ya ilahi AUNTY Sa'a da MAMAN ABUNA ga Pagen kun nan □□□

Dafe goshinsa yayi tare da shiru. Sun kai awa daya a waje kafin Nurse ta fito da sauri.
"Wani hali take ciki?"
"Alhamdulillahi, cikin ya tsaya amma ita din ce har yanzu numfashin ta bai zauna dai dai ba."

Haka suka zauna har bayan minti arba'in kafin ya suka fito da likitan, kallon shi yayi sannan tace mishi.
"Muje office."
Babu musu ya bi bayan likitan, sun zauna likitan ya kalle shi sannan yace mishi.
"Naga kamar kana damuwa, cikin ya tsaya amma don Allah a d'aga mata kafa, daga wannan yanayin domin dan cikin ya tasa"

"Ko tasha wani abu ne?" Ya tambaya a dame,
"A'a sai dai kai ne dai nake tunanin ko ka sha wani maganin kuzari ne, tunda kana tare da ita jinin ya ßalle."

Shiru yayi sannan ya dauke kanshi yana fad'in.
"Ta bani zobo nasha bayan nan kuma ba zan iya cewa kome ba, dan daga haka muka fara."

"Toh gaskiya akwai matsala tunda, kawai kayi bincike." Mika mishi hannu yayi suka yi musabaha, sannan ya fita inda ya sami yan uwan shi duk sun tawo.
"Ya Anum da jikin?"
"Alhamdulillahi cikin ya tsaya!"
"Alhamdulillahi! Alhamdulillahi!"
Inji Liman, suna tsaye. Aka fito da ita tayi Fayau gwanin ban sha'awa, aka wuce da ita. Juyawa yayi ya nufi gidan, abun da ya fara bincike zobon ya dauka sannan ya wuce dakin Anum. Garin bincike ya hango parket din maganin kuzari.

Juyawa yayi yaga yadda tayi amfani da har kwaya biyu, cikin masifar tashin hankali yayi wanka tare da shiryawa ya dawo asibitin,

Tabbas ya yarda Anum bata shirya zama dashi ba, abu daya zuwa biyu ya dawo da ita rayuwar shi, Yarta da kuma abin hannun shi da tasan yana dashi. Shi yasa tayi

yunkurin zubda gudan jinin shi. Dan haka ya zauna har kusan asuba sannan ya dawo gida.

Gabaki daya ya juye Aliyun shi, dan abinda bai kai ka fada ba, kowa sai yasha faɗa, kanen shi kuwa sai da ya mari Nusaiba, sabida tasaka Hoor a gaba tana zaginta tare da kiranta yar me ido kamar na mujiya,

Ya tsare ta sai ta gaya mishi meye na mujiya a idanunta. Dakyar ya kyaleta, daga nan ya nufi asibitin, lokacin na fito wanka a hankali nake tafiya, kallo daya yayi min, sannan ya juya kan Kanwar Maman shi da take tare dani.
"Sannu Innai! Kin kwana lafiya?"
Kallon shi nayi, zuciyata tana bugawa sabida yadda ya daure fuskar shi.
"Abban Isma'il!"
A fusace ya juyo tare da kafe ni da ido.
Sunkuyar da kai nayi, tare da zama a bakin gadon, ina haki.
"Sannun kinji!" Karamin murmushi nayi ina wasa da yatsun hannuna,

"Zan tafi! Innai ki saka ido sosai akan cikin domin akwai wasu da samuwar su duniya ce a gaban su basu damu da mutanen da suke faffutikar rayuwa domin su amfani ba."

Dake bata fahimci abinda yake nufi ba. Kallon shi nayi naga ya hade rai kamar yadda ya shigo. Babu shakka akwai matsala.

Bai iya hakuri ba, sai da ya gayawa Liman abinda nayi mishi,
Tsam yayi yana kallon shi kafin yace mishi.
"Ni kuwa nake ganin ba zata tab'a wasa da cikin jikin ta ba, sabida tana kiyaye zaman ku.

Sannan kasan zata fika kaunar cikin sama da yadda kake tsammani, akwai abinda baka sani bane amma Allah zai magance kome!"
"Liman kalli maganin da na samu a dakinta wato dan ina sonta bari ta wulakanta ni ko?"
"Kai dai kana ci da zuci!"
Karshe fushi yayi tare da ɗaukar jakar shi ya bar magana garin.

Duk yan uwansu da dangin nesa sun zo gidan, Amma babu wanda yasan da cikin yana nan, kowa a tunanin shi ya zube.

Lokacin da Hajja Dijimah ta sako matan shi a gaba suka zo min. Yadda na ga kishi a idon su na Fahimci sune suka tab'a min lafiyar cikina, dan haka dakyar na amsa musu gaisuwar su. Daga nan na dauke kaina akan su.

Kwana na biyar aka sallame ni,. A gurin mahaifiyar shi na cigaba da zama, dan Mahaifin shi yace na zauna a gurin mahaifin shi har cikin ya zauna a jikina. Haka na zauna. Ina kula da lafiyar cikina da kuma kai na.

A hankali na Fahimci irin tsanar da aka min a cikin gidan baki daya, hatta matan yan uwan shi, sun tsane ni irin tsana me mugun cin rai, sabida yadda Mahaifiyar shi ta nuna min kauna ba ita kadai ba, hatta Liman da kan shi yake kawo min Addu'a, har cikin ya shiga wata biyar.
Ranar da ya cika biyar sai ga Ahmad (ila) ya dauke ni muka tafi inda yake aiki. Tunda muka isa naga ya wuce sani asibiti. Hankalina ya tashi, ina zuwa na same shi babu yadda yaƙe, ga gefen kirjin shi ta dama an mishi daurin, kan shi ya ma haka,

Zama nayi ina ambaton Allah, rike hannun shi nayi ya bude idanun shi.
"Me yasa kika zab'i zubda min cikina? Da abin nake kwana nake tashi Anum kin san yadda nake kaunarki?"

"Kayi hakuri!"
Lumshe idanun shi yayi tare da cigaba da barci,

"Ila meye ya same shi?" Na tambaye shi,
"Wallahi tun da ya dawo daga Damagaran, yake fama da yawan damuwa, wallahi duk lokacin da ya zauna haya iya kome, toh jiya ya fita, ne yayi hatsari. Shine yace koda ya mutu don Allah na tambaya mishi ke me yasa kika yi kokarin zubda mishi cikin jikinki? Anum wallahi ban tab'a ganin wanda so bai wa Adalci irin Yallabai ba.

Yana miki kaunar da bayawa matan shi, amma kin kasa ganewa yana girmama al'amarin ki amma baki ganewa. meye laifin shi da zaki zubda cikin?"

Ban ce mishi kome ba, kawai hawaye ke zuba min daga idanuna, tare da kallon Abban Isma'il. Gabaki daya sun kasa yarda dani akan ba zan zubda cikin ba, gani suke da gayya na zubda.

Haka ya tafi ya barni a gurin shi dake babban soja ne, tunda nazo nake dawainiyya da shi, tun bai farka ba, har ya dawo nutsuwar shi, suka sallame mu..na cigaba da jiyar shi a gidan. A can kuwa babu wanda ya san halin da yake ciki, amma sun san ya turo a dauke ni.

Anan aka tadda kananun magana wai yana nuna min so, haka dai aka yi ta kananun magana.
-- ana kuwa horani yake kamar ya sami baiwa, dukda cikin yayi kwari bai hana shi idan yaji abun ya ciyo shi ya murtsike ni ba. Ga wulakanci kala kala, ban taba tambayar shi akan meye yasa yake min haka ba, asalima kallon shi nake hankali kwance.

Wata na biyu da zuwa mishi yaji sauki, wata weekend ya dauke ni, muka dawo gida, tunda muka dawo aka kuma sake bude tashin hankali musamman idan suka ga cikin jikina. Har tsoro abin ya fara bani.

Dake Allah yaso wanke ni, ranar yana zaune Sharifa ta fara zagina, Ni kuwa na rama.
Shine ta mike zata buge ni, ya hanata, bayan yayi mata barazanar idan wani abu ya same ni zai sake ta har abada. Dan shima yana ganin yadda suke fatan wani abu ya sami cikin jikina. So ya tafi masalaci sallar azhar na miki zan haura sama, muka yi karo da ita.

Kawai ta shiga zagina. Ban kulata ba, sai da tace min.
"Ko ance miki bamu san asalinki bane karuwa sai da kika gama karuwanci sannan kika dauko cikin kika lika mishi!"

Idan nace zanyi magana kuka zan mata, dan haka ban san lokacin da na wanke ta da mari ba. Dake muna kan step. Ban san ya akayi ba, ta kai hannu zata rama, A'isha ta shiga tsakiyar mu.

Ba zan iya cewa ga yadda abin ya faru ba, amma tabbas naji lokacin da aka tura cikina dani kaina,. muka hantsilo faduwa bana wasa ba, duka duka cikin wata bakwai da sati Uku. Haka jini ya tsinke min.

"Sharifa!" A'isha ta kira sunan ta,
A rud'e ta kalli Aishan tana faɗin.
"Wallahi ban tura ta ba, na rantse da Allah bani na tura ta ba"

"Amma dai kin san raba ku nazo yi,?" Ga baki daya suka rikice sabida abinda ya faru, har ya shigo ganin suna musu, ya zuba musu ido, ga Anum cikin jini, kamar ya fadi haka yake ji. A sanyayye ya nufi inda take, ya dauke ta, tare da barin gidan.

Zuciyar shi har rawa take zunzurutun tashin hankali, haka yasa yaran shi bude motar aka sata, koda suka bar gidan, Hankalinsu a tashe suka tsaya musu, karshe sai faɗa ta kaure a tsakanin su, kamar zasu daku.

***

A asibiti kan aiki aka wuce da Anum, inda aka yi nasarar cire mata yaronta dan karami, dashi, sak Ubanshi har yafi Hoor kyau da kama da Ubanshi, haka suka wuce dashi inda ake saka yan bakwai ni, aka shiga hidimar boye shi yana jin dumin kwalbar.

Itama aka gyarata, sannan aka mai data dakin da zata zauna kafin sallama, sai daga baya ya kira liman ya gaya mishi, tare da Umma da Yan uwan Anum.

Bai iya cewa kome ba, amma lokacin da aka taru a asibitin ya gaya musu abinda ya faru. Da kuma hukuncin da ya yanke, fada aka mishi tare da cewa.
"Ai tunda basu suka ture ta ba, sai kayi hakuri ka manta tunda."

"Gaje kika ce nayi hakuri bayan yunkurin kashe min mata na da ciki da suka yi, haba wato ita da bata da kowa idan ta mutu babu wani abinda za ayi domin hakkinta?" Shiru tayi bata iya magana ba, a hankali ya ciro takardan su, ya mikawa iyayen su.
"Nayi kokarin fahimtar dasu, bata da matsala sai yadda suka yi da ita, amma suka kasa, daga su dake ta dan sun fi karfinta sai su zageta. Alhamdulillahi, tunda na gaya musu suka sake wani abu ya sami cikinta zan iya sake su basu yarda ba, kowa ya kama gaban shi su barni da Uwar Yarana mu zauna lafiya!"

Babu wanda ya dakatar dashi, asalima tsoron kar Liman ya kuma taso rikicin suka hakura, amma basu jin zasu sake wannan damar.

--- kwana ɗaya nayi da wuni guda, na farka inda na same shi yana kallona, kafin ya mike yana faɗin.
"Sannun ya kika ji da jikin?"
"Da sauki"
Na fada a hankali, shafa cikin nayi sannan na dauke kaina, ina kallon window.
"Kina son ganin yaron kin ne?"
Girgiza kai nayi sannan nace.
"A'a kawai umma nake son gani "
"Anum kiyi hakuri, ki samu sauki sai..."
" Ba zaka kira min su bane?"
"Zan kira su!" Ya kira min Umma muka yi magana, akan lallai tazo ta dauke ni, tace min toh.

Ina kallon shi ya shiga damuwa, bata shi nake ba. Ta lafiya ta nake, tattara shi nayi na zuba a gefe,

Wato abinda na Fahimta dangane da zaman gidan shi, duk wani abinda yake faruwa, A'isha ce fitinanniyar, sannan kishi irin na Sharifa idan za a bani irinta zan zauna dasu sabida bata iya boye kishinta.

Abinda ya sa na fadi haka, sabida ina kallon A'isha ta ture ni, ina kallonta kafin na suma take murmushi, irin su idan suka sami mutum kashe shi zasu yi, ita kuma Sharifa bata da matsala ba zata iya danne kishinta ta cutar da mutum ba.

Ina cikin wannan yanayin Sharifa ta shigo, tana kuka.
"Anum! Wallahi bani bane na ture ki!"
"Toh taya zan yarda bayan ke da kanki kuka ce ba zan haihu ba, don Allah ki kyale ni!"
Na gaya mata ina dauke kai na, dole na bawa Asad hutu na fita harkan shi.

Sati Daya aka sallame mu, yaron ma lafiyan shi lau, wanda aka mishi huduba da Muh'd Bello, amma ba a'a daukar shi.

Daga ni saiHajja da kuma Innarmu, Sharifa ma tana zuwa duba mu, amma bata tab'a kai hannunta ta dauki yaron ba sabida mun nuna mata rashin yarda. Kuma tayi hakuri,

A bakin Hajja nake jin ya sake su....Na gaji wallahi.
#Mai_Dambu
[2/22, 1:20 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA SITTIN DA TAKWAS.

Nagode sosai Allah ya saka da Alkhairi □□□□

Kwalla ne yake zuba min daga idanuna zunzurutun tashin hankali, taya zai sake matan shi sabida ni.

Haka nayi ta tuka abin a raina, tare da nazarin yadda zan ßullo mishi, washi gari bayan mun yi wanka na dauki Muh'd Bello wanda muke kiran shi da Jaish, tunda na fito mutanen gidan suke bina da ido, ban damu ba tsakani na dasu gaisuwa.

Lokacin da na isa falon Liman na zauna muka gaisa, ya mika min hannu na bashi d'an jikan shi yayi mishi Addu'a, sannan ya kalle ni. Gyara zama nayi sannan na sunkuyar da kaina kasa, na fara magana cikin nutsuwa, tare da fidda ma'anar kowacce harafi.
"Baba Liman! A wannan lokacin idan nayi kuskure kokarin kuke ku tankwara ni, amma me yasa Idan Abban Isma'il yayi kuskuren baku tankwara shi.

Tabbas anyi Mishi laifi, amma kuma saki bashi ne zai gyara kome ba, ina ganin idan aka"
"Anumullah!" Da sauri na d'ago kai na, tare da zuba mishi ido.
"Babu ruwanki da matan Asadullah!"
"Liman idan na cire ruwana tabbas ban musu adalci ba, domin dukkan su babu wacce ta ture ni, zamewa nayi na fadi, idan aka musu haka toh ba ayi musu rashin adalci ba."

Murmushi yayi sannan yace min.
"Me kike bukata?"
"Liman idan aka dawo dasu nice zan fi kowa murna amma idan aka ki dawo dasu, zan koma cikin ahalina na hakura da zama dashi, tunda na shigo cikin familyn nan ake samun matsala da ni, amma idan bana cikin su zai zauna lafiya da matan shi, yara kuma Allah ya albarkaci rayuwar su, ka duba magana ta da idanun rahama."

Shiru yayi sannan yace min.
"Baki tunanin idan ya dawo dasu zasu iya samun damar cutar dake?"
Murmushi nayi a karo na babu adadi sannan nace mishi.
"Zanyi fatan Allah ya tsare na gaba, su kuma Allah ya bani ikon zama dasu da Amana, tsakanin mu da su. Alkhairi ce babu wani abu da zan karar a gaba akan su.

Sannan shi kan shi ya zartas da hukuncin ne ba tare da yayi bincike ba, Sharifa tace ba ita bace ta ture ni, Sannan A'isha tace ba ita bace, toh idan ana son a fidda gaskiya dole sai an kuma bawa juna dama ta gaba, idan ba haka ba za a iya shiga hakkin wasu ba a sani ba, ka bani damar ya dawo da matan shi. Nayi maka Alqawarin sai ya kama wacce ta ture ni a cikin su."

"Wato kina nufin ya dawo da su, sannan za a iya samun wacce ta ture ki?" Gyada mishi kai nayi,
"Amma ina son idan na gama mishi wannan aikin zai sallame ni"
"Ba zan iya saka shi ya sake abinda yake bukata a rayuwar shi ba, idan ma laifi yayi miki,.ki kara mishi dama idan bai sauya ba, nayi miki alqawarin raba ku koda baya so"

Gyada mishi kai nayi, sannan nayi mishi godiya, tashi nayi na bar mishi Yaron, bayan tafiya ta ne suke magana da matar shi, yake gaya mata yadda muka yi, shiru tayi sanan tace mishi.
"Yarinyar tana hakuri da halin karanci, idan kuwa ya sake ya rabu da ita ya kwal asara domin matar arzikin shi ce."

Haka suka yi ta tattaunawa, har Liman ya kira shi ya saka dole ya dawo da matan shi, sannan, suka rabu. Koda suka dawo tsakanin su babu jituwa.

Domin Sharifah tana ganin sharri A'isha tayi mata, ita kuma A'isha burinta, ta gogawa Sharifah kashin kaza,.yadda kowa zai tsane ta, duk da kuwa kowa yana jin haushinta amma ba kamar yadda suka tsane ni ba.

Bayan wani lokaci yan uwana basu sami zuwa ba, sabida rashin lafiyan Hafsat sai aika suka min ta hannun Rulwanu, wanda yazo yayi sati biyu, ranar da zai koma ne nayi kuka saboda kuwa dan uwanka idan yazo inda kake, ba karamin dad'i kake ji ba, idan zai tafi ne kuma ake yinta, musamman Ni da nake wata ƙasar.
"Idan ka koma kacewa Umma da Maman Aminu, ina kewar su. Suyi ta min Addu'a."

Maida kwallar da ta cika mishi ido yayi, sannan ya ce min.
"Insha Allah zan kawo miki Umma da Maman Aminu."
Hawayen da yake tarewa ne suka zubo.
"Anum kina cikin damuwa ko? Kiyi hakuri duk yana cikin qaddarar ki, kiyi hakuri wata rana sai labari, muma muna jinki a ranmu, domin muna matukar kewarki."

Mika min yaron Yayi bayan ya shafa kan Hoor, har ya shiga motar da aka kawo shi ya fito tare da ɗaukar Hoor ya matso kusa dani, ya dauke mu hoto,

Sannan ya shiga motar, muna kuka muka rabu, Ni da abokin fadana, a cikin sati biyu nan babu fada sai dai wani irin shakuwa wanda ban san muyi ba sai yanzun.

Bayan tafiyar Rulwanu, Dadda ya dawo, nan ya tsiro min wani abu na daban, dan yaji nice nasa ya dawo da matan shi, shine ya tsiro share ni, dama ban dawo gidan shi ba, ina gurin Innarmu. Ina kuwa jego na me kyau, Yarona yayi kato tare da girman ban mamaki, kuma dukka watan mu uku ne,

** Shigowa yayi ya samu ina nad'e kayan mu, Daukar Yaron yayi tare da barin d'akin, wallahi ko kallo bai ishe ni ba, dan nima yar daru ce.

Haka ya tafi dashi bai dawo dashi ba sai dare, tun karfe biyar na yammacin ranar, ina kwance ya shigo min dashi ina jin yaron yana kuka, nayi banza dashi.

"Tashi ki bashi nono!" Ban yi musu ba, na tashi tare da kunna wutar dakin, a hankali na amshi yaron na fara bashi nono yana sha, na zata zai tafi ne sai naga ya haura gadon, tare da rage kayan jikin shi, ina samu yaron yayi barci, na kwantar dashi.

Ina Kwanciya yana janyo ni jikin shi, kamar wanda ya sha wani abu, haka yazo min babu tausassawa, babu yadda na iya dashi haka ya gama kidar shi yayi rawan shi ban bude ido ba, balle nasan me yake ji a ranshi.
Aikuwa yaji haushina nan yayi ta faɗa da gaya min maganar banza, ban kula shi ba.

Tunda ya saka kayan shi ya fice na mike dakyar na shiga wanka, na gyara jikina. Sannan na koma gurin kwanciya na.

Washi gari Innarmu ta saka aka gyaran min shashina, a gurin Liman na koma, dan sunce ba zan kuma zama cikin matan shi su kashe mu ba. Nan ma yayi mamaki da aka yanke hukuncin ba tare da an tuntube shi ba.

Sai ya kuma ɗaukar fushi dan yanzun na haihu nice nake juya mishi gidan shi da zuri'ar shi, wato har na kai matsayin da sai yadda nayi da kowa, toh me zance.

Dan haka ya hana a dauko min kayana daga cikin gidan shi, dan dole na koma cikin gidan, ina zaune da manyan matan shi.

Makirci kuwa kamar sake samun damar haka A'isha tayi, ido da ido tace min.
"Ki gama haihuwarki, ki bani guri na rike yaran ke kuma ki kara gaba, Ban damu da yaran ba kamar yadda na damu da mutumin da tun tasowata nake kaunar shi, lokacin guda kin mai damu gefe!

Kiri kiri yake fushi da fushinki, ido da ido yake jin haushin mu da haushinki! Mu mata ne kamar ke meye kika fimu? Meye kike da shi? Waye ya tsaya miki?"

"Allah! Shi ya tsaya min! Allah shi ya bani Aliyu a matsayin mijina, duk abinda zaki yi, wallahi kiyi ko kadan ba zai rage kaunar da mukewa juna ba."
Daga haka na bar gurin, Amma wannan matar Shaidaniya ce.

--- tunda muka dawo ya raba mana kwana ɗaya rak, haka muke, gudanar da rayuwar mu.

Duk inda A'isha tasan zata haɗawa Sharifah bom bi take, dan haka sai ita kuma bata sani ba, ni kuma ina sane da takun ta,

Dake Yanzun da kan shi yake fitar da Yaron sai ya kasance idan ya fita waje yakan bada yaron a shigo da shi, toh idan aka shigo aka samu A'isha, karb'an Yaron take ta ajiye shi a kujera, sai ta tashi ta bar gurin, Yaron yayi ta wutsil wutsil.

Garin haka ya fado, ihun shi Sharifa taji ta fito, daga dakin ta a guje. Koda tazo ta dauke shi, lokacin Ni na sauko daga sama, Ubanshi ya shigo muka sami Yaron tana jijjiga shi.
"Sharifah wato saboda bakin kishi shine zaki kashe musu Yaro? Kowa yasan cewa har Hoor ta bar hannuna bata tab'a kuka ba. Sai dake, wallahi."
"Don Allah ya isa"nui
Na gaya mata ina kallon idanunta,
"Nagode sosai, Sharifah." Na amshi Yarona, sannan na bar gurin, bayan tafiya na. Ya cima Sharifa mutunci.

Kallon shi tayi cikin kuka tace mishi.
"Wallahi zargina kake Amma ita kanta Uwar Yaron ba..."
Banza yayi da ita ya bar su nan, ya hauro sama. Ina bawa yaron nono.

"Waye me kika dauke ni ne?" Nan ya shiga masifa bal-bal-ba, ajiye yaron nayi tare da takowa gaban shi, hannun na nakai keyar shi.
Na d'aga kafana, tare da hada bakin mu, daga nan bai kuma bashi damar yayi magana ba. Komawa muka yi gadon muka yi tare da gyara zaman mu.

** Wannan shi ya kawo karshen rikicin da yake damun gidan, sai ya koma kan Sharifa da Dadda. Sosai kuwa domin tsakani da Allah ya tsane ta. Kuma yana zabga mata rashin mutunci.

Yarona yana da wata takwas na kuma samun ciki, anan hankali na ya tashi, Sharifa kuwa murna kamar itace da cikin, yana gurin aiki ta gaya mishi ai ina da ciki, zunzurutun murna bai san lokacin da yace mata.
"Ki gaya min me kike so na baki?"
"Aadheen zaka bani! Idan kayi min haka wallahi kayi min kome a duniya."
"Toh idan na baki Uwar shi da?"
"Allah ya bata wani"
"Toh zamu yi magana da ita"
Da wannan suka rabu, bayan ya kirani yake tambaya na ya jikin? Nace mishi da sauki, sannan ya kawo min zancen Sharifa ya kawo min.
"Toh ai ni nawa a wanne? d'an ka ne, kuma duk abinda kace a kai ni zan bika da toh ne"

"Nagode sosai!"
Duk da ban yarda da ita ainun ba, amma bana jin zan iya kin bata yaron, dan haka ya turota ta kwashi kayan yaron, sannan ta kai shi asibiti aka basu magani da wani alluran da zasu na dauka duk kullum,

Tunda na bata yaron na fara laulayi, har ana cewa ko mace zan haifa, karshe zuwa yayi ya dauke ni. Na koma gurin aikin shi.

Ban samu kai na ba, sai da cikin ya isa wata hudu, kuma Alhamdulillahi. Domin ina jin dadin zama da shi, abu daya ne yake niman kawo mana cikas, ba kome bane sai ajiye min kudin da yake har yanzun. Shi yasa yau da yazo ajiye min nace mishi.

"Ka dauki kudinka bana so abinda kake min, idan ka cika ni wallahi zan tafi na bar rayuwarka har abada." Bai ce min kome ba yayi tafiyar shi.

Wai ana cewa yana sona, amma Iskancin da yake botsara min yaci Uban na matan shi, wani lokaci kuma zai sake min yayi ta yadda yaso dani, da zaran ya tuna da yadda muka yi akan Hoor sai ya kuma ɗaukar fushi. Ina ruwan dingayi.

*** Ina shiga wata takwas ya dawo dani, wannan karon sunce babu aikin da za a min, nima kuma ina tsoron Allah ina tsoron aikin dan cikina yasha yanka.

Wasa wasa cikina sai da ya kai wata goma, kafin na fara nakuda, dan tunda na dawo Liman yake kula da al'amarina, wanda kullum ina karban ruwan addu'o'in daga gare shi.

Bikin Nusaiba da Muh'd Awwal aka yi, wanda muka yi hidima sosai kasancewar dan Uwan Sharifah ne, ranar da akayi wunin na tashi da ciwon ciki, kafin a kai ga zuwa asibiti na haihu a cikin gidan, dan a dakin Innarmu nake kwance, su kuma suna can ana ta hidima.

ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Kai.
BABI NA SITTIN DA TARA.

Tunda na samu daya ya fado, na koma ina hutawa, kafin na kuma yunkuri daya ya diro, Aikuwa gidan Ya dauki Murna, an musu haihuwar yan biyu,

Ana gama kintsa yaran aka kai su gurin Liman, ina kwance dan sun dauko nurse tana duba ni.

Tana gama min abinda zata yi sannan ta min Allura, tana fita suka hada min ruwan wanka, na shiga na gasa jikina, ina fitowa na sami Sharifah.
"Allah Yarona yafi Yaranki kyau!"
"Eh naji, na yarda."

Haka muka yi ta hira, da ita kafin na sha tea barci ya dauke ni, bayan fitar ta aka dawo min da yaran.

Da dare ya shigo tare da A'isha, muka gaisa kallon yaran yayi sannan yace min.
"Duk wannan kyautar Allah ne ya bani su?"
Murmushi nayi sannan na gyara zama ina kallon shi,
"Gasu nan!"
Zama yayi muka shiga kallon juna ina murmushi, sannan naja numfashi ina kallon A'isha wacce take cike da b'acin rai.
"Yallabai! Dare yayi zan kwana na huta"
"A'a sai dai muje gida ai na gayawa Inna zamu koma can shashi mu."

Murmushi nayi sannan nace mishi.
"Zaka iya daukar mu dukkan mu! Domin ba zan yarda na bar yarana a nan ba,"

"Me zai hana?"
Ya faɗa yana dariya, ganin da gaske yake ya sani mik'ewa ina daukar Alhassan na goya sannan na dauki Alhussain, shi kuma ya kwashe mana kayan mu, tsinke A'isha bata dauka ba. Sai da muka shiga gidan ya kai min kome d'akina ya kuma dawo ya kwashe sauran kayan mu, ya dawo dashi.

Sanan ya zauna yana kallon yaran, da suke niman nono, tunda na basu, nima ina gyangyadi.
Dawowa bayana yayi tare da gyara min kwanciya a jikin shi, ina barci suna shan nono.

Da yaga sun koma barci ya cire min su, ya kwantar dasu. Sannan ya dawo bayana ya kwanta tare da sanya ni a jikin shi.
Yau shine kwance da Anum, ta haifa mishi yara huɗu, Hoor da Aadheen, yau gashi da zaratan maza. Lokacin da Ya kawo Hoor yana kuka a gaban mahaifiyar shi, murmushi tayi sannan tace mishi.
"Arzikin ka yana jikinta, matar kace ta har abada, dalilin rayuwa yasa ta juya maka baya, idan kayi hakuri wata rana zaka yi dariya,"

Bai yarda da haka ba, sai ranar da tace mishi idan ya cigaba da ajiye mata kudi zata barshi har abada yasa shi, yarda da Anum da ya sani a baya ba ita bace wannan, ita wannan tana raye ne sabida shi, tana kuma neman hanyar da zata dasa soyayyar ta a zuciyar shi, murmushi yayi sannan ya kuma maida ita jikin shi.

***
A hankali aka shiga mana hidima musamman shi, tare da nunawa duniya an mishi haihuwa, dake wancan yazo da matsala yasa bamu sani damar yin suna ba, amma wannan kam yana nan Damagaran aka fara hidimar sunan. Wancan raguna biyu aka yanka wannan kuwa hudu ne da saniya, aka kawo, sannan ana jibi suna Aunty Aminatu da Matan Ya Abubakar da Bashir da Musa, Baba Hama, Ummana, Shukrah.

Da sauran yan ya'yan uwana suka tawo, karku ga tarban da muka yi musu, ba na wasa bane.

Washi garin zuwan su, suka shiga hidimar kayan kayan cake da donut, sai kajin turawa da ya kawo mana, su kuma sunyi jakar da hoton yaran da Ya turawa Rulwanu.

Ranar suna yara suka amsa sunan, Abubakar da Aminu. Abun ya basu Mamaki. Dan haka muka saka musu.

Alhassan muke kiran shi da Asif Alhussain kuma Asil, ranar suna kowa ya san cewa Abban Isma'il yana kaunar abinda na haifa mishi, rawan jikin da yake sai Allah, har aka watse.

Ina tsaye a gaban Madubi, ya shigo dakina, gaisawa yayi dasu Umma, sannan ya saci kallona ina tsaye da towel, daya ina goge gashina, daya kuma ina daure dashi.

"Anum ko zan sami Black coffee ne?" Juyawa nayi a gajiye nace mishi.
"Abban Isma'il, kayiwa Sharif..."
"Zata kawo maka yanzun!" Umma ta bashi amsa, fita yayi yana satar kallona, musamman yadda cinyoyina suke waje.

"Amma ke kan Allah ya taro min ke, dama haka kike hauka ban sani ba? Kin zama sakarya sai Addu'a, Ubangiji yayi miki shiryar casbi. Kuma ki wuce ki hada mishi abinda ya tambaya mara kunya!"
"Ni wallahi umma yanzun ina zuwa dakin shi, wani cikin zai kuma min, shi ko damuwa da lafiyata bayayi!"

"Don Allah ku bani, tsintsiyar kwakwa na zane wannan mara kunyar" da sauri na dauki hijab na fita ina tura baki, haka na sauka na hada mishi , sannan na wuce sama, ina shiga najiyo muryan shi suna fada da A'isha, da harshen buzanci. Ina shiga yana juyawa ya nufi ban dakin.

"Wallahi sai kin bar min mijina, daga ke har Sharifah."
Dauke kai nayi kamar ba dani take, ajiye tea nayi tare da nufar ban ɗakin, ina shiga na same shi tsaye yana sauke ajiyar zuciya.

Ruwan dumi na sauko mishi, a hankali na rufe kofar. Sake towel ɗin nayi tare da ajiye hijab din,. Zuwa nayi na kwantar da kaina a bayan shi hannuna na saka ta kirjin shi, ina murza gargasar jikin shi.

Juyar dani yayi tare da zuba min ido.
"Kin sami danginki, kin manta da Ni?"
"Ban manta da kai ba, gani nayi kana da wasu matan zasu iya kome."
"Mata na daban ke daban, Anum bana son kina hana ni sakewa dake, sai nayi ta ganin ko har yanzun baki sona ne!"
"Ina sonka mana, kawai kar mu wuce iyaka ne!"
"Naga kinyi wanka jinin ya dauke ne?"
"A'a bai dauke ba! Kawai dai na wanke kai nane!"
Daga haka bai kuma magana ba, ya daura min kan shi a kafada na, rike shi nayi. Sabida yadda yaƙe birkita min lissafi.

Wasa wasa sai da muka raba dare, sannan na bar dakin shi bayan naga barci ya dauke shi. Ina shiga dakina na samu yaron yana hannun Umma, a sadadde na shigo.
"karki kuma bijirewa bukatar mijinki akan wani dalili can."

Sunkuyar da kai nayi ina wasa da zoben hannuna. Sannan ta mika min Asil na bashi nono, sannan na kwanta. Washi gari suka gyara min namar da aka yanka tare da soyawa.

Suka kintsa min gurina, bayan suna suka tattara kome na, sannan, suka bar kasar da dinbun alkhairin Mijina.

A hankali nake kula da Yarana, tare da samun goyan bayan mijina, dan ma Aadheen yana gurin Sharifa, karshe shima sai da A'isha tayi dalilin da aka dawo min da yaron sabida hada su fada da tayi da Aliyu.

Fada sosai, har ya nemi dukarta sai da na shiga tsakanin su, nace mishi.
"Kana niman shekaru hamsin amma har yanzun ka kasa Fahimtar meke faruwa a cikin gidan ka, sanin kanka Sharifa ba zata cutar da kai ba, balle d'anka.

Kishin da take dani, ban tab'a ganin shi akan Aadheen ba, amma ka d'aga hankalin ka, ka dawo min da shi, kiyi hakuri Allah zai saka miki."

"Rashin kunya zaki min? Karki ga mun tara yara dake kice zaki min rashin mutunci, wallahi sai na baki mamaki."
Ganin yadda yake niman kawo mana tashin hankali ya sani baki daya, na ajiye mishi Yaran shi, tare da ɗaukar kudin da yake bani na hada kayana. Na fara saukowa daga sama da kayan, ganin da gaske nake, ya sashi rufe kofar gidan,

Aikuwa na tubure mishi, sai na bar gidan, abinda ya daga mishi hankali kenan, ya rasa wanda zai dakatar dani, karshe ya kira Innar shi, tace babu ruwanta, ya san inda dare yayi mishi.

Da ya sami Liman shima yace babu wani abinda zai iya, gaba daya suna juya mishi baya, kamar zai yi hauka, dan haka ya kira Umma, ya gaya mata. Itace ta kira ni tayi min fada sannan na hakura.

Lokacin da muka cika wata biyar anan ya dauke mu,. muka zo nigeria, ganin gida. Haka muka zaga dangi da yan uwan, har lakwaja muka je,,

Bayan mun yi sati biyu muka dawo Bauchi, muka je har badara, da Dewu.

Muka yi sati Uku, sannan yazo ya kai mu Umma, muga Hisham, tunda muka isa gidan su. Dadda ya kasa ya tsare shi nan kar na sake baki nayi ta dariya, sai na kame kaina ina kallon shi.

Haka koma masaukin mu, ina sauke Asil ya ajiye Asif, nan yaja tare da cewa.
"Na lura har yanzu Ban miki yadda zaki daina kwadayin wancan mutumin ba."
"Kaga ni bana son zargi, waye ya gaya maka ina kaunar Ibrahim banda zuciyarka da bata maka adalci, ka duba cikin idanuna kaunar kace zalla, amma kullum baka da aiki sai na korafin wani. Gani ka cinye ni, idan ka sami abinda ya rage ka barni haka."

Sanyi jikin shi yayi tare da rungumo ni, sai lokacin na sami damar sake kuka, na rasa yadda zanyi da Maude kishin tsiya ne dashi. Tunda yaga na mishi bori ya kyale Ni haka, yaran kan A gidan Ibrahim muka Barsu, sashe shima yazo wani taron Ecowas ne dan haka muka yi sati biyu anan Abuja sannan muka dawo Bauchi, anan muka samu har an wuce min da tsarabar da aka mana,

Kwanan mu biyar muka wuce, Riyadh, gurin Isma'il. Inda na same shi yayi kyau yaron ya kara girma, kallon shi nake gwanin ban sha'awa. Idan yana Hausa kamar ba bahaushe ba, larabci ne akan harshen shi, sai da muka zo masauki na rike hannun shi nace mishi.
"Me kake son nayi maka bayan Alkhairin da kai min Asadullah?"

Murmushi yayi min, sannan ya kashe wutar dakin, ya shiga kashe arna tare da karatun zungura da raruka.

. bayan mun shiga Makka munyi umra da Isma'il din da yake gaya min ai Dadda yana zuwa duk karshen wata uku, kallon Shi nake ina mamakin shi, yadda yake rufe min kome, yayi kai tsaye.

..... Tun lokacin da naga Hafsat zuciyata ta karaya, domin shi alkhairi da sharri suna tafiya akan turba daya ne, kuma idan suka yi abinda zasu yi suna dawowa ne, dan haka abinda ka shuka shi zaka girba.

Haka nayi ta mata addu'o'in a dakin ka'aba, bayan mun dawo daga gurin Isma'il, ina renon Yarana, mijina yana kuma kara sake min ragamar rayuwar shi.

Wani irin kauna yake nuna min , Sharifa kan babu ruwanta dani, dan haka A'isha face dai ta daurawa kanta damuwa akai na.

** Matar Ahmad ila, yau muka tashi da bakin labarin Allah yayi mata rasuwa, dan haka. Bayan anyi jana'izar ta a can gurin aikin shi, anan aka yi zaman makokinta.

Kasancewar Ni nake kula da abubuwa da ake girkawa ya sani fara tsanar kamshin albasa, da kayan miya ta fashashe, ina jin tiririn shi zan fara kokarin amai.

Lissafin da nayi yarana watan su goma cif, tsoro ne ya kamani, dakyar aka yi sadakan bakwai dani, ana gama zaman makoki na fara laulayi.

Kuka nasaka mishi ina rokon shi don Allah muje a cire cikin, ya kafe sai na Haifa mishi. Dan haka na nufi gurin Liman na gaya mishi, shima ya kira Asadullah aka yi magana yace.
"Tsoho shekaru na hamsin cif, Allah ya dube ni da idon rahama ya bani haihuwa sai a cire dan kawai akwai wasu a hannun, ba zan zama butulu ba, tayi hakuri gaskiya gidana babu inda za a dakatar da haihuwa, wallahi banki ace dukkanku uku kuke haihuwa ba, dan haka kiyi hakuri ki haifa mana shi kinji."

Bayan sun rarrashe ni ashe, har an gama bazani a cikin family na cika haihuwa kamar akuya. Bayan kwana biyu matar Mubarak ta haihu muka shiga Barka shine nake jin ana gaya min magana.
"Wasu matan yadda kuka san akuyoyi, sabida dadin aci Arziki ana d'aga bujen su, sai ciki."

Suka kwashe da dariya, murmushi nayi yadda suke fadar maganar har da A'isha a cikin su, daura daya ayi akan daya, nace musu.
"Ai dadin gindi yasa kullum bunsurun ku yake barbaran yar akuyar shi, shi yasa wasu dake gindin su bata da dad'i kuma bata iya fitar da kan d'a ba, suke niman hanyar kashe yar akuya, so ni bani da damuwa da ku saboda ina da Taure a kusadani kuma ya iya cin mace a tsanake har sai yayi mata ciki, wasu kuwa sun manta da Allah keyi shi yasa suka turoni daga saman step dan na zama tarihi, haihuwa kuwa ba zan tab'a dakatawa ba, sai ba jerawa Aliyu Asadullah yara goma sha biyu cif da Yardan Ubangiji sannan zan huta meye amfanin gindi idan ban bashi yaci ya kuma min ciki ba."
.ina fadar haka na mike abuna na Barsu da kallona baki dake...
Ko ban gaya muku ba, Next page Insha Allah zai zama ƙarshe
#Mai_Dambu
[2/22, 9:07 PM] MRS USMAN😘: ZANEN QADDARA TA..!!

Mai_Dambu

Da sunan Allah Mai Rahama Mai jin Ka

BABI NA SABA'IN.

Karhe 😉

"Dama yarinyar nan ta iya bakar magana, kaji shegiya mara mutunci. Har mu zata gaya mana mara dadi. Wallahi sai mun gayawa Asad yayi mana waje da shegiya" ina nasan suna yi,

Bayan sallah Isha, kawai ya shigo min yana huci, ko kallo shi banyi ba na cigaba da bawa Yarana abinci.
"Har ke kin isa kiyiwa mutane gorin rashin haihuwa? Toh bari na kwashe sai ki cigaba da musu."

Haka yayi ta masifa ban kula shi ba, sai da zai tafi min da yarana nace mishi.

"Wallahi karka kaiwa ko wacce shegiya kayana, wato ga mara hankali, na zauna na cigaba da kallon su suna zagina, wallahi ba zan yarda ba ko kai ka zage ni sai na gaya maka magana, kuma ka ajiye min Yarana tunda a gindinsu fito."
Na fada da karfi, kamar yadda nayi haka ya saka kai ya fice min da Yarana, kam Uban can.

Haurawa sama nayi tare da dauko hijab dina, na sauko lokacin ya shigo gidan, kallona yayi sannan yace min.
"Ina zaki?"
"Gidan Mahaifina ka rike Yayan ka, sabida nasan Rabon sune yake dawainiyya da ni, zan.."
"Kinga Khadijah bana son tashin hankali idan Yayanki kike so zan dawo miki dasu amma ba...."

"Kasan Allah, na gama zama da kai." Wasa wasa har su Sharifa suka fito, juyawa nayi, zan haura sama yace min.
"Don Allah kiyi hakuri, mu sassanta" ban kula shi ba na haura da gudu, kamar zautacce ya biyo ni da gudu, haka muka yi ta bala'i a sama, karshe fita yayi ya dauko kakan shi. Dakyar suka shawo kaina, sannan na hakura.

Yarana aka kawo min su, na cigaba da abinda yake gabana, bawai dan ina da dadin dandano bane, a'a kawai mun kai matakin da dole a rayuwa mu zauna da junar mu, kuma ko ba kishiya dole zan zauna da mijina, kuma ya zama wajibi nayi hakuri da halin shi, balle kuma kishiyoyin da suka zama dole na zauna dasu.

Dama dan shi nake dauke kaina, toh wannan karon da na sami.damar zama a gidan dindindin. Rashin mutunci nakewa Aishan domin tana yi min zan mata, na kuma gaya mishi idan zai zauna da Sharifa kishinta a fili yaƙe,

A'isha kuma munafuka ce, bawai na kai tsaguminta bane, kawai ya gaya mishi ne musamman yadda yake kushe Sharifah. Dan ko yanzun da muke shiri da ita idan kishin ya motsa mata kiri kiri take gaya min yau bana son ganinki da mijina,

Murmushi nake mata kawai nace mata.
"Yau kishin ya motsa kenan?"
Murmushi kawai take min, idan na ga haka toh bana kuma sakewa na shiga harkanta, domin tana da zafin kishi wanda sai tayi kwana uku bata min magana ba. Sai idan abun ya saketa tayi ta niman yadda zamu daidaita..

Koda wasa bai sake min ragamar shugabancin gidan shi ba, amma yana matukar sauke hakkin mu.

*** Cikina yana da wata hudu, na tashi ina son zan daura abinci, ina saukowa na gansu cirko cirko. Kallon su nayi sannan na kalle shi yana zaune ya dage goshinsa.
"Gadanga kusar Yaki lafiya?"

Kallon Center table din gaban shi, nayi naga ai kunun tsamiyar da nayi ne d'azun na sha kadan sauran akan idan na tashi zan sha. Kai hannuna nayi zan dauka yace min.
"Ajiye Anum! Akwai kwaya a cikin kunun!"
Kallon A'isha nayi wacce jikinta yake rawa.
"Wai meye ya faru?"
"Hmm! Sharifah ce ta dauki hoton A'isha tana zuba miki kwaya a cikin kunun,da nazo nace mata meye ta zuba a kunun tace babu kome Sharri aka mata. Anum can you image maganin zubda ciki, ta zuba a cikin kunun?

Sannan badan Sharifah ta dauko min hoton ba, wallahi da itace zata ce ta zuba miki, kuma na zarge ta akan itace bata kaunarki. Anum A'isha tayi abubuwa dayawa wanda na boye miki, amma Sharifah wallahi ina da yakinin ko kyankyaso ba zata iya kashewa ba.

alhamdulillahi nagodwa Allah da bani na zalince ki ba, kije Allah ya hada ki da rabonki na Alkhairi, zan zauna da Mata na wanda suka kasance *RABO NA NE*"
Ya mike tare da fita daga gidan, ya sami Kakan su, yayi mishi bayani sannan ya sake ta zama saura igiya biyu ne, dan haka ya karasa sauran igiyoyin, sannan ya kawo mata. Kamar Mahaukaciya haka take rokon mu, tare da rike kafar mu.. wallahi duk yadda kaso ka ɗauke kanka sai kayi kuka sabida tabawa Talatin da takwas baya wajen arba'in yau ace miji ya sake ki akwai tashin hankali, sanan ya sake ki da tabon zata zubda mishi cikin matar shi.

Lokaci guda muka shiga hankalin mu, ni da Sharifah, ganin zaman mu baya karan mu da kome muka shiga islamiyya, wanda ake a cikin masallacin gidan, har da Aishan muke haduwa nan ta dauki sabon tsanar mu, wai mun hade kai mun saka an sake ta.

Kuma ba kome yaja mata haka ba, sai mugun nufinta.

Bayan na haihu na kuma samun namiji, inda aka saka mishi Suna Abdullahi, a lokacin aka zaka bikin Rafi'a da Ahmad ila, muka sha biki, bayan nasu da wata shida nazo na Rulwanu, da wata yar uwan Umma suke Ganjuwa. Sai tsiya suke min wai na zama uwar maza ga kunika ya amshe ni.

Tunda nazo bauchi naso nayi tsarin iyali amma ban iya yi ba tsabar tsoron kar wani matsala ya biyo baya, haka na hakura, muna nan muna shan hutu Alhaji Hamisu Natsira yazo niman yafiya ta, akan abinda yayi min.

Nace na yafe, Mudi kan yana can gidan shi ba a cewa kome,domin yaran da ya tsafe su, sune suka yi ajalin shi, dan haka Aliyu ya boye Asalin Isma'il. Domin yadda ya nunawa kowa dan shi ne, idan ka matsa ne zai ce ya aure ni da goyan shine.

Na samu labarin mutuwar Salmanu Adam Firo, ya rasu sakamakon jinyar da tacinye kafar shi.
Ibrahim da Yaron shi sun zo bikin Rulwanu, zamu tafi dinner haka Aliyu ya hanani tafiya, ya tattarowa Umma yaran da Maman Aminu, ya kai ni cikin gidan shi, wallahi sai da nayi danasanin amsa gaisuwar Ibrahim, dan baya kishi da kowa kamar yadda yake kishi da Ibrahim. Tunda ya sani a daki yake abinda yaso dani.
Da ya bani haushi nace.
"Tsohon kawai,.dalla kyale ni na fita, bana jin dadin jikina ka isheni da jaraba"

Haka ya cigaba da turmushe ni, sai da ya ji dan kanshi sannan ya kyale ni, anan na kwana Abdul yana gurin Umma na, da safe aka kawo min shi, muna kwance Aka yi mana sallama, tashi nayi na bude kofar. Hajjo na gani, murmushi nayi sannan na bude mata kofa ta shigo, sannan na shiga dakin ta taso shi ya fito. Suka gaisa.

Anan suka tab'a hiran yaushe gamo, har take gaya mishi inda tayi aure yaranta uku yanzun,
"Allahu Akbar! *RABON* Shi ne ya raba mu fa, kinga da Allah ya nufa *RABO NA CE* Anum gashi har da yara biyar, Dan haka mu godewa Allah da yasa ka babu *rabon Ajali* a cikin mu sai *Rabon Alkhairi* "

Haka suka yi ta tattaunawa, sannan zata tafi ya dauki kudi ya bata dan ko bata fada ba tana cikin wahala, washi gari yasa aka kira Mishi mijinta yayi mishi alkhairi sabida ita, yasa aka saya mishi napep yayi mishi barazana akan koda wasa yaji labarin ya karo aure zai bashi mamaki dan ya bashi keken ne sabida ita, kuma babu amfanin bata mora ba.

.haka yasa ya amsa, Mijina mutum ne me yawan alkhairi, dan haka nake godewa Allah da ya bani shi a matsayin mijina, bayan aikin gwamnati babu abinda zan ce yake sai kasuwanci sosai yake yi,

Bayan mun gama hutun, muka dawo gida, anan ya kawo min Isma'il, wanda ya zama ɗan saurayi, ba laifi yazo yayi min kwanaki ya koma.

*** Bayan shekara goma.
Zuba mata ido nayi yarinyar da na haifa yar autana, ji nake kamar na fasa ihu, ta saka tuwo a gaba tana kuka, yar shekara biyar.
"Wallahi bazan ci tuwon nan ba, idan naci Allah ya tsine min." Tayi kwallon da tuwon.
Zama nayi ina kallonta, ni dai a shekara goma, na tsani tuwo.

Amma Maman Aminu karama Hauwa ta tsani tuwo, ga shagwaɓe kamar me, idan aka hanata abu kafewa take zata yi, yayunta maza basu da abinda take yi, asalima suka tsorona bakamar Abban su da Mame dinsu ba, wato Sharifah.

"Don Allah idan ba zaki bata wani abincin ba ki ce tayi hakuri mana," kallon Sharifah nayi sannan nace mata.
"Wallahi bazan bata hakuri ba, dan qaniyarta na kamata sai na fasa jikin ta" aikuwa haka ta fice da gudu tana ihun Wayyo Allah zan ta mutu, karshe suka haɗu da Jamal dan gurin Addah Rufaidah ya kaita gurin Innarmu taci shinkafa.

Bata dawo gidan ba sai dare da Babanta wanda ya biya ta dakin Innarmu ya daukota, tayi barci. Yarana maza takwas, mata biyu. Bayan Abdullahi da Muhammadu Bello, da Alhassan da Alhussain, na kuma na kuma haihuwar yan biyu, maza, sukan an bar musu sunan su ne, sai Aliyu d anayi, da Muh'd Aasim, sai auta ta, Ha'uwa.

Wacce muke kiranta Khairat, ina kasuwanci sosai, ake shigo min da kaya ta nan maradi.

*A'isha tayi wani auren babu dad'i haka tayi ta fuskarta matsala,, nan ta hanamu sukuni taje can kishiyar tace ita ba zata zauna da kishiya ba, ta tasota a gaba, sai da auren ya mutu sannan hankalinta ya kwanta, nan ta fara zawarcin mijin mu, muka ce bamu yarda daba. Tabi wani sarkin ba namu ba.

*** Wato wani abinda na Fahimta a iyakan rayuwa, yarda da ƙaddarorin masu kyau ko marasa kyau,.nayi hakuri da ƙaddara, domin idan Allah ya haɗaka da Maman Aminu a matsayin Uwa baka ramin tashin hankali bane, sai gashi na amsheta hannu bibbiyu, na kuma yi hakuri da ita.

Bayan nan hakkin miji, idan Allah ya tashi kama ka, dashi ba zaka ji da dad'i ba, wallahi na fahimci duk abinda ya faru dani da hakkin Aliyu, sai hakkin Yar shi.

Sai na gaba bakin Mahaifa, masiface babba, duk wani takadiri a duniya zaka samu yana tutiya da sawan albarkan Uwa, Ni kuma sai na fuskanci ciwon bakin Uwa, wanda yaja min watangaririya a rayuwa ta.

Sai wani abu da zan ya kiran shi Na gaba *KAUNA* wannan shine linzamin da na rike zuciyar Aliyu dashi, ban da shi babu abinda zai ja min Aliyu ya dawo rayuwata.

Addu'o'in mahaifina da tsayin daka da Umma tayi akaina, sune Mabudin canji rayuwata, wannan yanayin da Malam ya barni da shi Allah ya amshi bakin shi ya maidani tauraruwa a duniyar mu, ya kuma karawa min daraja a gidan Aurena, wanda nasan hakuri da juriya suka dawammar dani a gidan mijina.

Idan kayan mata yana hana ayi Iskanci wa mace toh Aliyu shi zai baki, kudi har da na kayan mata, idan kika yi tasty dayawa yace miki kinyi zaki dayawa, karku kuma shan maganin, ko idan ya gama rayuwar aure dake yace miki baki yi yadda yake so ba.

Kayan mata ana shan shi ne, dan gyara zama bawai dan kiyi yadda kike so da mijin ba.

Dan haka karki yarda ki sake mutumin kirki da yazo miki da Alkhairi ki kama na banza, shi rayuwa akan tsarin Ubangiji yake wani bai isa ya ture wani ba, dan haka muyi hakuri da abinda yazo mana, Allah yana son mu ne yake bamu dama ta biyu.

Tarbiyyar Umma na samu shi yasa wani shashin rayuwata ya boya ba tare dangin Aliyu sun san nayi wani mugun abu a waje ba, nayi kokarin koyawa yarana Kaunar junan su, yadda idan wane baya nan sai an nimo shi.

Ko Khairat ce tayi laifi na make ta, dukkan su suke kuka har Hoor, bana son na koyawa yarana Irin wahala da nasha a rayuwata, akan makauniyar soyayya..kuma naki na bar Khairat a matsayin auta na, dan kar na cutar da ita, Uban ne yake kiranta da Auta.
Rulwanu ma yaran shi uku, idan muka.hadu sai munyi halin...

Mijina ya ajiye aikin soja, yayi kokarin fadawa siyasa, muka hana shi, dan karya zama bai da lokacin mu, Ashe hana shi da muka yi Alkhairi ce, domin kuwa sai gashi an tura shi jakadar Nijar a kasar Germany, haka muka tattara muka koma can, soyayya me tsafta da kaunar juna muke, yarike mun Yarona. Haka kuma Hisham.yana zuwa min hutu.
Alhamdulillahi
Adda Ramlat kinji labarina, kuma kinji gwagwarmayar da nayi, wasu abubuwan ma na manta, masu muhimmancin na iya rikewa, shi yasa da naji ana magana akan Safinah ta masarautan Jordan tana da daurin kai, dariya suka bani sabida banga taurin kai a gurinta ba, dan nice matattarar taurin kai, Alhamdulillah gashi na baki labarina kicewa mutane suyi hakuri haka labarin faru da yar uwansu mace, shi yasa ya tafi a hankali.

Nima Nagode da kika bani damar na rubuta labarinki, Gashi nan salon labarin anata daukaji wata wai don Allah tana son Ganin hoton ki da Abban Isma'il

Hhhh! Ki rufa min asiri, wallahi mijina yana da kyau daidai misali, ina tsoron kar yan mata suyi crushing din shi, dan wallahi kishine dani, kice ina musu fatan Alkhairi Nagode sosai zanyi kewar su

Toh mai karatu anan na kawo karshen Labarin ANUM KHADIJAH MUH'D BELLO.... Allah ya hada mu a wani labarin Insha Allah! Muji wata Chakwakiyyar ce a cikin shi. Alhamdulillahi Nagode sosai masu daukar salon labarin ku Cigaba bani da salo amma ina da Chakwakiyya zalla idan kin shirya mu hadu A Daula biyu

Masu son sayan Daula biyu... Ga damar shi. Me kike yi har yanzun baki saya ba....kusan bana Allah ya isa bana zagi.. amma akwai mita ③dan kin karanta masarautan Jordan, Bahaushiyah, Magajin Izzah, Ruwa biyu, Matar so! Wai Casss.... Mu hadu a wata badakalar. Amma don Allah nafi son ku biya ta bank ₦200 babu tsada bani da VIP.... amma zan baku labarin da ku kanku baku tsammani ba.. Please kuyi payment ta bank, idan kuma katin mtn 300₦ ne,
Acct: 0472282105
Ramlat Abdulrahman Manga GTBNK! +2347035133148